RABON AYI

©FAREEDA ABDALLAH

*_BABI NA ƊAYA_*

"Wayyiiihuhuhuuuuu... jama'a ku saurara, kowacce yar abu kaza-kazan uba ta tsaya cak a inda take! an sace jakar uwar amarya cike taf da maƙudan kuɗaɗe..."

Ta jiyo wata murya mai tsananin taratsi da hargagi daga can cikin ɗakin uwar bikin tana faɗin haka, a daidai lokacin da ta ɗaga cinyar kaza ta nufi bakinta da nufin yi mata wani yaga na wulaƙanci, irinna an daɗe ba'a gamu ba.

Kirjinta ne ya yanke ya faɗi rugugum! ta ɗaga idanu a tsorace ta kalli Fatima, akayi arashi suka haɗa idanu.

Amma ita saɓanin Fareeda da ta ƙame da cinyar kaza a hannu baki buɗe, ita tauna take yi, hankalinta kwance kamar tsumma a randa, ga faskeken rabin ƙirjin kaza nan a hannunta ta kusa cinyewa.

Muƙut ta haɗiyi wani kakkauran miyau da ta ji yana barazanar yaga mata maƙogwaro, ɗauke kai tayi daga kan Fatima ta waiga gefe kusa da ita, sai taga jakarta tana ajiye inda ta barta.

Nannauyar ajiyar zuciya ta sauke, jikinta a sanyaye kamar wacce aka naɗawa na jaki ta aje naman hannunta cikin soyayyiyar shinkafar da aka shaƙo mata cikin faranti. Lumshe idanu tayi, ta girgiza kai, ta fara maganar zuci.

'Yau babu sa'a, daga zama da niyyar ɓarje gumi sai ace anyi sata? Sawuna a likkafa gara in tattara tsumman rayuwata in san inda dare yayi min, tun kafin wata tsautsayin ta rutsa da ni in shiga uku.'

Hannu tasa ta ɗauki jakarta ta maƙala a kafaɗa, ta kalli Fatima da maɗaukakin mamaki a fuskarta, ganin har lokacin cin naman take yi a nutse, bisa ga dukkan alamu hankalinta a kwance yake, har wani ƙara balance tayi a cikin kujera don taji daɗin loda abinci, kamar bata ji satar da aka ce anyi daga can cikin ɗaki ba.

Wani kakkausan kallo ta watsa mata, ta yunƙura za ta miƙe tsaye daga zaunen da take sai ta ji caraf Fatima ta dafe hannunta.

"Ferry?"

Ta kira sunanta da mamaki a muryarta.

"Ina za ki? baki ci komai ba fa, ko naman ma baki ci ba, kuma kin san dai bamu daɗe da zuwa ba, ko Jiddah bamu gani munyi mata Allah ya sanya alkhairi ba balle har mu fara tunanin tafiya a daidai lokacin da ake tsaka da shagali."

Ta ƙarasa maganar da murya ƙasa-ƙasa yadda babu mai jin abinda ta ce, in dai ba a kusa da mu sosai ake ba.

Kafin ta ce uffan wata kakkauran mata mai ƙiba ta fito daga cikin ɗakin uwar amarya gudu-gudu sauri-sauri, ta nufi babban ƙofar falon da ake shiga da fita ta rufe, ta ƙara da murza key ta datse ƙofar ɓam.

Ta zare makullin, ba tare da kunyar kowa ba ta janyo wawakeken wuyan rigarta yayi ƙasa-ƙasa har ana hangen tudun ƙirjinta ta jefa ɗan makullin a cikin rigar mama.

Ta juyo tana kallon cincirindon matan da suke zaune rukuni-rukuni a makeken falon, fuskarta ɗauke da wani mummunan murmushin da ya fi kama da na rainin wayau, sai wani irin numfarfashi take saukewa kamar wacce tayi tseren gudu.

Ta fara magana da garjejen muryarta mai kama da na magidanci.

"Sas-sannunku fa, kuyi haƙuri don Allah, kar ku tashi hankulanku!! Abu ne kamar wasa ƙaramar magana tana neman zama babba! Kun dai ji anyi shelar sata ko?

To wallahi ta tabbata! da gaske anyi satar, Kamar ɓatan dabo Ƙasa ko sama mun nemi jakar Hajiya Mariya yanzunnan akan gado mun rasa, abu kamar layar zana ƙad-da-bus jaka ta ɓace ɓat!

Ba zarginku muke ba fa, Don Allah ku kwantar da hankalinku kamar tsumma a randa. Yanayi ne na rayuwar duniyar da ta canza, kun san mutane ba gaskiya... inji bahaushe yakan faɗi kai dai ga mutum, sanin zuciyarsa sai Allah..."

"Aunty Kubura menene haka? me nake gani haka? me nake ji haka? ya kike ta wani lallaminsu kina basu hakuri? Sata ne dai an riga anyi kuma na tabbata kwarankwatsa dubu a cikinsu ne akwai ɓarauniyar nan. Duk inda jakar nan take na tabbata bata bar cikin falon nan ba, don ƙasa da minti bakwai da suka gabata jakar tana kan gado a ajiye.

Don haka wallahi tallahi yau in za a kwana a yini sai sun fito da jakar nan sannan ko wacce za ta fita daga nan! Caje ne daga sama har ƙasa sai munyi in ta kama daga nan har caji ofis sai mun je!"

Idanu warwaje Fareeda take kallon wata figaggiyar matashiyar mata da ta fito daga cikin ɗaki tana faɗin haka cikin fushi da masifa, bakinta har yana kumfa da tartsatsin miyau saboda bala'i.

A tsorace ta sake mayar da idanu kan Fatima da har lokacin hannunta ke damƙe da na ta, da rawar murya mai cike da tsoro tayi ƙasa ƙasa da murya ta raɗa mata

"Fatee na shiga uku na lalace! Wallahi Mukhtar bai barni ba na fito gidan bikinnan, yau idan suka riƙe mu anan ina zan saka kaina?...!"

Kafin Fatima ta ce wani abu ɗaya daga cikin hamshaƙan matan da suke zaune a can wani ɓangare na falon ta miƙe tsaye a fusace ta kalli tsigaggiyar nan ta fara maida mata martanin maganganunta cikin fushi

"Wai wane irin zancen banza kuke yi haka? ku kalle mu dakyau ku gani, kusan duk cikar mu babu wata wulaƙantacciya mai wulaƙantaccen sutura balle har ku maƙala mana satar yɑn kuɗin da kila ma ba wasu masu yawa bane."

A ɗarare Fareeda ta kalli kayan jikinta, inda Allah ya taimaketa zaninta na ƙasan akwati ne a jikinta, Chiganvy Gold, atamfar da daƙyar da jiɓin goshi ta mallaketa, tsabar ta so siyanta bazata iya ƙayyade kwanaki nawa tayi tana ƙwangen kuɗin cefane da na karyawa kafin ta tara kuɗin siyanta ba. Naira dubu goma sha uku cif haka ta caskewa Hajiyar Barrister kafin ta samu nasarar mallakar atamfar, ta ƙara tara asusun dubu huɗu cif ta ba Yayanta Musty don yayi mata ɗinkin kece raini na fita ko wane irin muhimmin taro.

Ajiyar zuciya mai nauyi ta sauke, ta mayar da hankali kan matar nan inda ta ji ta ci gaba da cewa

"Mun ci, mun sha, mun rufa mun tada kai balle har ayi tunanin za mu gani mu ɗauka.

To Satar me za ayi? ina ƙudan yake balle romonsa? in dai da gaske ne ma anyi satar to kuwa na tabbata ko rantsuwa nayi babu kaffara yɑr iskar ɓarauniyar baza ta wuce a cikin ku yɑn'uwanta na jiki-jiki da kuka maƙale kuna zaune a cikin uwarɗakinta ba..."

Maganar da tayi sai ya zama kamar mabuɗin bakin ko wace mace da take zaune a falon, nan take aka fara cece-kuce da ƙananan maganganu, aka fara zage-zage da wannan figaggiyar matar, kamar za aba hammata iska.

Tana masifa ana maida mata martani, ko wacce mace na ƙoƙarin kore gaskiyar zancen anyi satar balle har a maƙalawa ɗaya daga cikinmu mazauna falon.

Fatee ta gallah ma Fareeda harara, ta fusge hannunta da ta riƙe, cikin fushi da ƙarfin hali ta fara magana da faɗa-faɗa.

"Ke dallah banza ki nutsu ki kwantar da hankalinki, to miye don ba'a barki ba kika fito? kanki farau satar fita? da wannan mutsu-mutsu da zare-zaren idon da kike yi ai sai ki zama abar zargi a cikin mat..."

Wani mahaukacin ƙaƙƙarfar ihu mai cike da amo da amsa kuwwa da aka ƙwallah daga cikin ɗakin uwar bikin yasa kusan duk mazauna falon suka miƙe tsaye a tsorace, tsit kake ji ! duk hayaniyar mata ya tsaya cak kamar ɗaukewar ruwan sama.

Hankalinsu bai ƙara mugun tashi da ɗugunzuma ba sai da wannan ƙatuwar da aka kira da Aunty Kubura ta fara jero sallallami tana tafa hannaye, fuskarta bayyane da matsanancin tashin hankali, da saurin murya mai ɗauke da damuwa ta ci gaba da magana

"Shi ke nan! Ta faru ta ƙare anyiwa mai dami ɗaya sata. Abinda muke ta gudu da alamun shi ne ya faru. Mugayen aljanun da suka yi dafifi a jikin Aunty Adama ƙanwar Hajiya Mariya sun tashi.

Wallahi duk wacce tasan ta ɗauki jakar nan ina bata shawara ta fito salin-alin sawunta a likkafa tun kafin a fito da ita a tozarce a wulaƙance.

Don wallahi aljanunta yɝan fallasa ne, kuma duka suke yi, idan suka zuciya babu ruwansu da mai gaskiya da mare gaskiya, kan mai uwa da wabi suke yi da wacce ta ji da wacce bata gani ba su naɗi fata"

Kayan cikin Fareeda ne suka tattaru suka cure guri ɗaya, lokaci ɗaya jikinta ya ɗauki rawa kamar ana kaɗa mata ganga, hanjin cikinta sai mazari suke yi kamar ana tsakiyar hunturu. A ƙanƙanin lokaci idanunta suka cicciko da hawaye, bayan wasu daƙiƙu sai ga hawayen sun zubo shar...

Ta kalli Fatima ita ma ta kalle ta, a wannan gaɓar ƙuru-ƙuru ta hangi matsanancin tausayinta a idanun Fatiɓa, domin ta san Mugun tsoron aljanu ne da Fareeda.

Ta tsani aljanu, ta tsani tashin aljanu a gabanta, tun tana yɔar ƙanƙanuwar yarinya duk idan taji labarin wata wacce ta sani tana da aljanu ta rabu da mace kenan haihata-haihata.

Ko a cikin dangi ne takan guje ta faufau balle kuma a cikin ƙawaye ko kuma yɔan ajinsu, a islamiyarsu ta canza aji fiye da sau goma saboda tsoron tashin aljanu.

Kafin wata a cikinsu tayi wani yunƙuri don motsawa ko cewa wani abu sai suka fara jin buge-buge daga cikin ɗakin kamar ana watsi da kayayyaki, ko kuma ana mugun dambatuwa.

Can kuma sai suka ji an sake yanka ƙaƙƙarfar ihu a karo na biyu, aka buɗe ƙofar ɗakin buf sai ga wata gajeriyar mace mai kama da wada wacce da alama ita ce Aunty Adaman ta fito falon a guje daga cikin ɗakin.

Daga ita sai shimi a jikinta, yɔan uwanta har da uwar bikin suna biye da ita da gudu suna yunƙurin riɓeta, fuskokinsu cike da maɗaukakin damuwa suna cewa

"A tara jama'a... ku tare mana ita. Taimako jama'a ku riɓeta kar ta futa waje, yunƙurin guduwa da ita suke yi ako wane lokaci."

Abin mamaki da tsoro Aunty Adama tana zuwa kusa da ƙafafun Fareeda ta zube ƙasa yaraf kamar an taɗiyeta, takai wa ƙafafunta wani mugun damƙa da wawaso da yasa tayi taga-taga kamar za ta faɗi amma ta tsaya daƙyar bayan ta damƙi ƙugun Fatima da take kusa da ita, Aunty Adama kuwa ta riɓe ƙafafunta tamau.

Tsananin tsoro da firgici yasa Fareeda ƙamewa a tsaye tana jan numfashi daƙyar, kamar wata mutum-mutumi, ta kasa ƙwaƙƙwaran motsawa ta kasa numfashi mai ƙarfi, gani take da tayi wani ƙwaƙƙwaran yunƙuri za'a zare mata rai.

Sama-sama take jiyo ringing ɗin waya a cikin jakarta da ke kafaɗa tana rera waƙar

"Fareeda gimbiya... fareedah kin zama sarauniyar mata..."

Waƙar da idan ta ji ta tabbatar mijinta Mukhtar ne yake kira...

'Na shiga uku!!!'

Ta faɗi hakan a zuciyarta, wasu sabbin hawaye suka sake ɓalle mata kamar an buɗe famfo.

A Fusge kamar daga can nesa taji muryar wata mata tana cewa

"Baiwar Allah ki nutsu, ki kwantar da hankalinki. Da alama aljanunta suna son ki ne..."

Ƙaƙƙarfar kukan da Fareeda ta buɗe baki ta fashe da shi yasa mai maganar ta kasa aje numfashin maganarta daidai.

'So dai? aljanun ne suke so na? A duniya in rasa suwa za su so ni sai aljanu? ni kam yau wace irin mummunan baƙar rana ce a gare ni?'

'Fareeda kar ki tafi gidan bikinnan, in dai ni mijinki ne kuma na isa da ke ban baki izinin ki tafi gidan bikinnan b...'

'Haba Baby haba haba don Allah? me yasa kake irin haka ne wai? Jiddah ce fa za tayi aure ba wata ƙawata can nesa ba. Fisabilillahi duk yadda muke da Jiddah ace bikinta ya zo bazan samu halarta ba? haba! ai duniya ma sai ta zage ni, ka tuna yadda tayi uwa tayi makarɓiya a bikinmu...

Ni na sata dole tayi? na dai faɗa miki kar ki fita ko ina, gobe zan dawo. Idan kuwa kika fita wallahi tallahi duk abinda nayi miki ke kika jawo wa kanki. Domin a wannan karon zan ɗauki mummunan mataki a kanki. Ƙit ya katse wayar ba tare da ya sake sauraren abinda zan sake ce ba.

A cikin ɗan taƙaitaccen lokaci taƙaddamar da muka kwasa da mijina Mukhtar a ɗazu da safe ya faɗo min arai, da yake ni ɗin mai kunnen ƙashi ce tsautsayi da

rabon ayi yasa nayi fatali da hanawarsa, kashedinsa, rantsuwarsa nayi fitowata bayan ƙawata Fatima ta shirya ta biyo min har gida da direbanta.

"Baiwar Allah kiyi haƙuri, kibar kuka, yanzunnan za mu ɓamɓare hannuwanta daga jikin ƙafafunki, ki nutsu, kiyi hakuri babu abinda za tayi miki."

Ɗaya daga cikin yʼan uwan Aunty Adama ta faɗa ma Fareeda haka, da sassanyar murya mai ɗauke da alamun rarrashi don kwantar mata da hankali.

Sannan ta kalli matan da suke tsattsaye cirko-cirko a falon ta buɗe murya ta ce

"Ina Hafizai mahaddata Alƙur'ani? ku marmatso kusa da ni kuyi aikin lada"

Sai tayi zaman dirshan a gabanta tayi basmala da zazzaƙar murya ta fara rero karatu cikin suratul-baƙarah.

Tsoro ne ko kuwa rashin iya karatun ne oho! a cikinsu babu wacce ta tayata karatun, sai zazzaƙar muryarta ne ya ci gaba da ratsa dodon kunnuwansu cikin wani daddaɗan sauti da iya ba ko wace kalma haƙƙinta.

Bata yi mintuna bakwai cikakku tana karatun ba Fareeda ta ji hannuwan da sukayi ram da ƙafafunta sunyi sanyi laƙwas, motsawa tayi ta ji za ta iya janye ƙafafunta ai a saba'in ta matsa can gefe guda tana zazzare idanu kamar wacce tayi ƙarya a gaban sarki, sai kallon Adama take yi da wani irin kallo mai bayyana tsananin tsana da ƙyama, a zuciyarta babu abinda take ja mata sai Allah ya isa na firgici da tashin hankalin da ta ƙara jefata a ciki, a daidai wannan lokacin ta tabbata da za a auna jininta za aga yayi mugun hawa.

"Alhamdulillahi! Yau an taki sa'a, sun jirge da gaugawa."

Uwar bikin ta faɗi haka fuskarta na bayyana matsanancin farin ciki, wani abu a cikin kwalba mai kama da magani ta miƙawa wacce tayi karatun tana faɗin

"Ungo nan Aliyah, yi sauri ki shafa mata a goshi, idan tayi barci ta tashi za ki ganta garas kamar ba ita ba."

Ana gama shafa mata suka yi kama-kama suka kaita cikin ɗaki, sannan suka dawo cikin falon.

Umarnin zama suka mana sannan wannan wacce tayi Ruƙya ta fara mana nasiha tana janyo ayoyi da hadithai, a ƙarshe ta dire da haɗamu da girman Allah da na ma'aiki kan duk wacce ta ɗauki jakar nan ta dawo da shi cikin mutunci da lalama ba tare da anyi tsiya-tsiya ba.

Hajiya Mariya ta ƙara da cewa

"Ni wallahi ba kuɗin jakar ne ma yafi damuna ba, akwai muhimman takardun His Excellency a cikin jakar! I'm sorry to say idan ba'a ga jakar nan ba gaskiya daga nan sai dai a kwashe mu zuwa station din gidan gayu..."

Da rarrafe Fareeda ta ƙarasa gabanta saboda tsananin tashin hankali

"Hajiya... don ya rasulillahi ki rufa min asiri... kin sanni tun ba yau ba wallahi bazan taɓa ganin abin wani in ɗauka ba. Ki min rai ki sallameni in koma gida, bikinnan ba da izinin mijina na taho ba, ga shi yayi min saƙo yana hanyar shigowa kaduna. Idan ya dawo ya tarar bani a gida na mutu kawai, na tabbata a zafin rai da rashin hakuri irinna Mukhtar igiyoyin aurena da suke hannunshi tsaf zai tsittsinka su..."

"Kiyi haƙuri Fareeda, a al'amarin sata irin wannan kowa ma abin zargi ne, kinga har ƙannaina ban cire su a cikin ɓarayin ba."

Tsabar tashin hankali yasa ban ankara da waya take dannawa a hannunta ba sai da naji tana cewa

"Hello... Inspecter..."

Y'an'uwa barkanmu da Yamma. Kun tuna wannan labarin? yanzu na shirya mishi tsaf, za mu cigaba in Allah ya yarda. Y'an kasuwa masu buƙatar a tallata musu kayan sana'arsu cikin farashi mai rahusa su tuntuɓeni ta private ta wannan lambar 07039080978.

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Na shiga uku!!!"

Fareeda ta faɗi haka idanunta a warwaje, hannu bibiyu ta ɗora akai wasu sabbin hawaye suka sake ɓalle mata. Babu abinda take hangowa a idanuwanta da ji a kunnuwanta sai masifar da Mukhtar zai sauke mata, ba shi da haƙuri ko kaɗan.

Balaɣayɣe ne na bugawa a jarida idan aka yi kuskuren shiga gonarsa, ba shi da uzuri ko misƙala zarrah. Har wani kirari yake yi wa kansa cewar

"Ni fa kamar kunama nake, a taɓa ni aji ɗau."

Da waɗannan tunanin da suka yiwa zuciyarta ƙawanya yasa ta fara jan wani irin numfarfashi sama-sama, kamar mai cutar athma.

Hankalinta yayi gaba saboda tsananin ɗimuwa da fargaba haɗe da tashin hankali, duk hayaniya da surutan da mazauna falon suke yi sam hankalinta ba shi a kansu.

Tana cikin wannan mawuyacin halin jiniyar yɗan sanda ya karaɗe unguwar, kasancewar unguwar ta masu kuɗi ce babu hayaniya sosai sai suke jin jiniyar yɗan sandan yana tashi tamkar a cikin gidan.

"Alhamdulillahi, ga yɗan sanda nan sun iso."

Uwar biki Hajiya Mariya ta faɗi haka da fuska kadaran kadahan, duk hasashen mutum bazai taɓa gane farin ciki take ciki ko akasinsa ba.

Nan take waɗanda suke zaune suna ganin abin kamar wasa duk suka miƙe tsaye, hankula ya ƙara tashi, nan take ƙaton falon ya ruɗe da surutai haɗe da cece-kuce.

Ƙarara ake jingina rashin kyautawa ga Hajiya Mariya da daga taron arziki ya koma na tsiya da rashin mutunci.

Wata Aminiyar Hajiyar da ta sha kwalliya cikin wani danƙareren leshi da gwala-gwalai wuya da hannu ne ta taka ta matsa kusa da Hajiyar, ta fara magana fuskarta na bayyana matsanancin ɓacin rai.

"Yanzu ke Hajiya Mariya kina ganin wannan mutunci ne? Da girmanmu da arzikinmu daga zuwa miki taron Allah ya sanya alkhairi sai ki haɗa mu da yɗansanda? wannan ai tozarci ne da wulaƙanci. Tunda haka ne ni na ɗauki lamunin kuɗin, ki ƙiyasta nawa ne a cikin jakarki in Allah ya yarda biya bazai gagar..."

"Dakata Hajiya Balaraba, dakata dan Allah. Kar ki nemi ki faɗa min baƙar magana, kin sanni sarai bakina ba ya haila."

Uwar biki ta katse ta tana harhaɗe girar sama da ƙasa.

Ta miƙe tsaye ta riƙe ƙuƙuminta kamar wata ƙaramar yarinya, ta ƙanƙance idanunta suna kallon juna ta fara magana cikin fushi da fusata.

"Tun farko na faɗa ba kuɗin cikin jakar ne damuwata ba. A can cikin jakar akwai muhimman takardun His excellency, ko yanzu da wacce ta ɗauki jakar za ta fito min da takardun na rantse da girman Allah zan iya bar mata kuɗaɗen ciki duk yawansu."

Da faɗin wannan magana sai aka fara kallon kallo a tsakanin mata, ko wacce a zaƙe take ta ga ta inda takardun cikin jaka zai ɓullo, wace jajurtacciyar ɓarauniya ce za ta iya fitowa tsakiyar cincirindon matannan ta kawo takardu tunda anyi alƙawarin bar mata kuɗaɗen cikin jakar?

"Yʻan'uwana mata don Allah don darajar fiyayyen halitta muji tsoron Allah, duk wacce ta san ta ɗauki jakarnan ta fito da shi. Don Allah, ta rufa mana asiri mu koma gidan mazajenmu lafiya."

Malama Aliyah mai ruƙya ta faɗi maganganun fuskarta na bayyana matsanancin tashin hankali da damuwa.

Bayan maganar da tayi har aka kwashi daƙiƙu sittin babu wacce ta motsa, izuwa wannan lokacin kuma yʻan sanda sun shigo cikin gidan har sun adana motocinsu, mata a cikin yʻan sandan ne suka matsa ƙofar babban falon suka fara bubbuga ƙofar da ƙarfi.

"Ai shi kenan! Tunda duk haka kuke so bari in basu dama suyi aikinsu, mu tafi caji ofis ɗin kawai. Acan ko ma wacece ɓarauniyar za tayi bayani idan ta ji matsa."

Tana gama faɗin haka bata saurari magiyar da aka fara yi mata ba ta nufi ƙofar fita daga cikin falon da niyyar buɗewa, a kulle ta ga ƙofar, kuma babu ɗan mabuɗi a jikin ƙofar.

Ɓangaren da yʻan'uwanta suke tsaye cirko-cirko hannuwa naɗe a ƙirji alamun tashin hankali ƙarara a fuskokinsu ta kalla. Da cusasshiyar murya ta ce

"Ina ɗan makullin ƙofar nan?"

Cikin sanyin jiki Aunty Kubura ta zura hannunta a rigar mama ta ciro makullin ta miƙa mata.

Yamutsa fuska tayi, a ƙyamace ta kalli makullin sannan ta kalli fuskar Kubura da take miƙa mata makullin.

"Wani irin iskanci da ƙazanta ne za ki wani cusa min key ɗin ƙofa a rigar nono? ki tabbatar bayan kwaranyewar wannan al'amarin kin wanke min makulli tsaf sannan ki mayar min da shi jikin ƙofa."

"To Hajiya, kiyi haƙuri."

Ta bada haƙurin cikin ƙanƙan da kai.

Kʼasa-ƙasa ta ja tsaki, ta hararetа, sannan ta bata umarnin buɗe ƙofar.

Tana murza makulli ta buɗe tiƙa-tiƙan yʻan sanda mata su takwas suka shigo cikin falon fuskokinsu a ɗaure, sai zare-zaren idanu suke yi kamar za su ci babu. A hannayensu riƙe da ƙananun bindigu.

Cikin girmamawa suka kai gaisuwa ga Hajiya, ta amsa musu a gadarance.

"Ga su nan, dambu da taliya na juya sun ƙi fito min da jakata, idan aka kwashe su zuwa caji ofis ko ma wacece ɓarauniyar za tayi bayani."

Duk da a cikin matan gurin akwai masu dakakkiyar zuciya yʻan rajin rigima ubanwa ta kashe irinsu Fatima, da yawansu jikinsu yayi sanyi. Zuwa wannan lokacin ba Fareeda ba ce kaɗai mai kuka da hannayenta ɗore akai, mata da yawa sun fara kokawa ne da ƙarfi suka zube a ƙasa suna roƙon Hajiya Mariya ta rufa musu asiri, daga masu cewa idan aka kaisu station aurensu zai samu matsala, sai masu cewa tunda suke a rayuwarsu basu taɓa zuwa ofishin yʻan sanda ba, tayi haƙuri kar su fara zuwa daga sha'aninta.

Hajiya Mariya kuwa ta shafawa idanunta toka tana tsaye tana karkaɗe jiki ta ce bata san kalmar haƙuri ba, za tayi haƙuri ne kawai idan ɓarauniya ta fito mata da jakarta.

Masu ɗan ƙarfin zuciya a cikinsu ne suka zaro wayoyinsu da nufin su kira makusantansu don sanar da abinda yake faruwa, amma yɜn sandan nan suka katse musu hanzari ta hanyar ƙwace wayoyin hannayensu. Cikin waɗanda aka karɓewa waya har da Hajiya Balaraba.

Haka nan suna ji suna gani aka tarkatasu a motocin yɜn sanda shiga ba biya fita da Allah ya isa a cuccushe wata kan wata a wulaƙance ba tare da banbance talaka da mai kuɗi ba zuwa Ofishin yɜn sandan gidan gayu.

A gurin kashi biyu da rabi cikin uku na matan wannan abin da Hajiya Mariya tayi musu shi ne ƙarshen tozarci da wulaƙanci da aka taɓa yi musu a rayuwarsu. Masu arziki a cikinsu sun ɗauki munanan alwashi da yawa a kan Hajiyar, talakawan cikinsu kuwa a zukatansu suke ja mata miyagun alkaba'irai iri-iri.

Wani ƙarin abin haushi da Hajiyar tayi shi ne na ƙin shiga ɗaya daga cikin motocin yɜn sandan a tafi da ita, da ƙyamar shiga motar ƙarara a fuskarta ta ce su tafi, za ta biyo su yanzunnan ita da direbanta, ta ja kunnen yɜnsandan ko da sun isa bata ƙaraso ba kar a kuskura a fara wani bincike sai ta ƙaraso, da haka suka bar gidan.

****

Sun shafe awa biyu cur a cikin cell kafin Hajiya ta ƙaraso, tafe take tana taku ɗaiɗaya irinna manyan mata masu duniya.

Ta canza wanka, ta cancaɗa gayu a fuskarta wanda ya taka muhimmiyar rawa gurin ɓoye shekarunta. Saɓanin ɗazu da take sanye da leshi, yanzu wata ɗanyar shadda ce a jikinta wacce aka yiwa ɗinkin doguwar riga, an ƙawata rigar da aiki irinna zamani.

Tana shiga cikin gurin da sauri aka bata kujerar zama, a ƙasaice ta zauna tana huhhura hanci.

"Ya ake ciki? sunyi bayani?"

Tayi tambayar idanunta ba kallon yansandan.

Ko da suka tuna mata ta ce kar ayi komai na bincike sai ta ƙaraso taɓe baki tayi, irin alamun rashin damuwar nan. Ta buɗe baki za ta sake yin magana aka kira ta a waya, ko da ta duba fuskar wayar mijinta ke kira, wanda take yiwa inkiyar His Excellency saboda takarar gwamna da yake yi.

"Excellency barka da yamma."

Tayi maganar a tausashe fuskarta na bayyana murmushi.

"Yauwa Hajiya. Na dawo gidan sai ban tarar da ke ba, ko har kun wuce mothers day ɗinne?"

Ya tambayeta daga can ɓangaren.

Yanayin alhini ta sakawa fuskarta sannan ta bashi labarin abinda yake faruwa, ta kuma ƙara da faɗa mishi inda take a halin yanzu.

"Hajiya? kinyi hauka ne?"

Abinda ya fara cewa kenan cikin fushi daga can ɓangarensa.

Da mamaki ta buɗe baki tana kallon wayar kamar shi ne a gabanta, ta buɗe baki za tayi magana ya katseta cikin fushi.

"Wane irin haukar tunani ne ya shiga cikin ƙwaƙwalwarki da za ki wulaƙantar da mata masu yawa haka waɗanda muke saka ran ba ƙaramin muhimmiyar rawa za su taka mana a zaɓen da ke tafe ba? To in dai wannan jakar taki mai ruwan madara ce ga ta nan ajiye akan gado cikin ɗakina. Ki gaggauta sakawa a sallami matannan yanzunnan, ko da yake ga ni nan zuwa in basu haƙuri da kaina."

Kafin ta ce komai ƙit ya katse wayar.

Ya barta riƙe da tata wayar a hannu, baki sake, zuciyarta cike da maɗaukakin mamaki jin cewar a ɗakinsa ta bar jakar.

Sai kuma ta tuna ƙasa da mintuna sha biyar kafin ta ankara da ɓacewar jakar tabbas ta shiga ɗakinsa, don ta ɗauka ma Amarya Jidda set ɗin sarƙar da uban ya siya mata, za ta ba direba ya kai mata can gidan ƙanwarta inda suke tare da ƙawayenta. Ashe can ta ajiye jakar?

Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un! wannan wane irin abin kunya ne ta aikata ga ƴan uwa da abokan arziki har ma da manyan aminanta? Da wane ido za ta sake kallonsu tayi musu magana, ya rabbi ya rabbi.

Ta ɗaga idanu ta hango su can cikin cell, wasu daga cikinsu na tsaye, wasu kuma a zazzaune sun haɗa kai da gwuiwa. Fuskokinsu damalmale da matsananciyar damuwa da tashin hankali.

"Hajiya? Mu fara basu jikinsu ne ta yadda ɓarauniyar za tayi gaggawar bayyana kanta?"

Ɗaya daga cikin ƴansanda mata ta faɗi haka da salon cusa kai gareta.

Wani mugun kallo da ta aikawa ƴarsandannan ba shiri ta ja da baya tana sosa gefen wuya.

Da wata irin muguwar kasala da sanyin jiki ta miƙe tsaye ta tambayesu ina ne ofishin DPO?

An nuna mata kenan za ta shiga sai ga isowar mijinta Alhaji Lukman Mai Dala, a bayanshi motoci ne masu yawa. Tun kafin direbanshi ya gama daidaita fakin a harabar gurin ya buɗe ƙofa ya fita zuwa cikin ofishin, sai saɓa babbar riga yake yi cikin tashin hankali.

Cikin masifa ya bada umarnin a fito da matannan yanzunnan, saboda yawansu sun cike gurin taf. Ganin yawan matan da Hajiya ta sa aka kulle a wulaƙance saboda rashin tunani da rashin hankali irin nata ba ƙaramin sake ɗaga mishi hankali yayi ba.

Irin mugun kallon da da yawa daga cikin matan suke aika musu shi da matarshi da take rakuɓe a gefenshi ya bala'in ɗaga mishi hankali.

A matsayinshi na babban ɗan siyasa mai neman takarar kujeran gwamna ko ƙanƙani ba ya fatan abinda zai janyo mishi matsala tsakaninshi da jama'a, ya san idan bai ɗauki mummunan mataki nan take ba lallai aikinshi ba ƙaramin jiƙewa zaiyi ba.

Ya juya inda Hajiya take ya aika mata da wani haukataccen kallo mai cike da tozartawa, cikin fushi da fusata ya balbaleta da bala'i kamar bai san daga inda ta fito ba, ba kuma tare da ya duba yawan mutanen da suke gurin ba.

A ƙarshe ya dire maganganunshi da cewar lallai tana buƙatar saiti tunda har ta iya wulaƙanta iyaye da yayye da ƙannenshi mata haka akan abinda bai taka kara ya karya ba, nan gaba bai san me za ta ƙara yi ba na tozarci da rashin hankali.

Idan ya haye gadon mulki haka za ta tafiyar da al'umma a wulakance. Ta tafi gidansu ya saketa saki ɗaya.

Duniyar ce ta fara hajijiya da Hajiya Mariya, tunaninta ya tsaya cak! saki shi ne kalma na ƙarshe da ko a mugun mafarki bata taɓa tsammanin zai shiga tsakaninta da maigidanta ba.

Wannan abu da Excellency yayi ga Hajiya shi ya wanke kaso tamanin cikin ɗari na baƙin cikin da matannan suka ƙunsa. Rai fes sunan wata zani. Hatta yan'uwanta na jini sun ji daɗin wannan saki da aka yi mata, daman tuntuni ta ishe su da kaɗifiri da girman kai na tsiya, ko cikin dangi sai abinda tace ake yi, ko babu komai yanzu an karya alkadarinta.

Da kallo ɗaya yaga sassaucin tsana da ɓacin ran da yake kwance a fuskokinsu.

Duk a ƙoƙarinsa na sake wanke zukatansu nan gabansu ya zube gwuiwarsa a ƙasa yana sake basu haƙuri.

Idanu suka bubbuɗe, alamun mamaki. Babban mutum irin wannan shi ne ya durƙusa musu a ƙasa? bakinsu har rawa yake gurin cewa

"Honorable don Allah ka miƙe tsaye. Wallahi har ga Allah mun yi haƙuri, mun yafe abinda tayi mana. Yanzu kawai babban burinmu a sallamemu mu koma gidajenmu."

Talatin da biyunsa a waje ya dinga yi musu godiya da fatan alkairi. Ya umarci direbansa ya ɗauko masa jakarsa a mota, ko da ya buɗe envelope ne ɗauke da kuɗi naira dubu ashirin-ashirin. Haka ya bisu ɗaya bayan ɗaya ya damƙa ɗai ɗai a hannayensu, sannan ya umarci direbobinsa su kwashe su ko wacce a aje ta a gidan mijinta.

Mata masu sukunin cikinsu kuwa waɗanda Allah ya huwacewa arzikin mallakar mota gidansa ya ce a mayar dasu, idan suka ɗauki motocinsu sai su wuce gida.

Sai a wannan lokacin aka damƙama su Hajiya Balaraba wayoyinsu da aka ƙwace. Suka fita daga gurin fuskokinsu babu yabo ba fallasa.

Farida da Fatima hanyarsu ɗaya ne, ita Fatima tana da mota, direbanta ne ma ya ɗaukota suka je gidan Fareeda aka ɗauketa daga can ya ajiye su gidan bikin.

Kasancewar yaranta suna daf da tashi a islamiya sai ta sallami direban da cewa yaje ya kwashi yara ya mayar gida, ƙarfe shida na yamma ya koma gidan bikin ya ɗaukosu.

To yanzu ƙarfe biyar da rabi, wannan abu da ya faru yasa jikinsu a sanyaye yake kamar an lakaɗa musu duka. Har gara ma Fatima akan Fareeda, ita kam har wata ƙwarya-ƙwaryar rama tayi kamar wacce ta yini tana amai da gudawa.

Idanunta sunyi ƙozai-ƙozai saboda kukan da ta kusan yini tana yi, wannan uban kwalliyar da tayi kafin su taho yanzu ko ɓurɓushinsa babu. Duk da an sallamesu har da ladan kuɗaɗe hankalinta ya ƙi kwanciya, tana ji a ɗazu yadda Mukhtar yaita kiranta akai-akai, ta kuma ji shigowar saƙonni a jejjere, saboda fargaba da tsoron

abinda za ta tarar ta ma kasa ciro wayar ta duba abinda saƙonnin suka ƙunsa, babban burinta da fatanta bai wuce ta buɗe idanu ta ganta a tsakiyar falon gidanta ba.

*_Ina sayar da datar MTN mai aminci da ƙarko. 1GB□□N300, 2GB□□N600, 3GB□□N900, 4GB□□N1200, 5GB□□N1500. A tura kuɗin sayen data ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB, sai a tura screenshot na shaidar biyan kuɗi da kuma bayanin yawan datar da ake so ta nan whatsapp a lambar wayata 07039080978_*

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/EjmQJ7W13K97BCI2wgWNWY

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*3*_

Duk da mota ɗaya suka shiga wajen komawa gida zaman ƙuda ne a tsakaninsu, kamar ma waɗanda basu taɓa sanin juna ba.

Ko wacce ta jingina kai da ƙofar mota ne suna kallon can waje.

Ita Fatima babu wani fargaba da damuwa a tattare da ita, babu nauyin miji a kanta balle ta shiga ɗimuwa, shekarar mijinta biyu da rasuwa, shi yasa take dama kununta yadda take so.

Ganin yadda Fareeda ta ɗaure fuska ta juyar da kanta ɓangaren ƙofa ne yasa itama tayi hakan, don kar ƙawartata taga kamar bata damu da halin da take ciki ba.

Gidan Fareeda aka fara isa, da wata muguwar kasala ta buɗe ƙofar motar tana ƙoƙarin fita, hannunta ɗaya da Fatima ta riƙe yasa ta juya a hankali ta kalleta.

"Na san duk inda Mukhtar yake ya dawo duba da yadda yaita kiranki akai-akai, ko in raka ki cikin gidan in taya ki ba shi haƙuri?"

Murmushin yaƙe tayi, ta zare hannunta a hankali.

"Babu komai, ki ƙarasa gida kawai. Zanyi masa bayani, babu abinda zai faru sai alkhairi in Allah ya yarda. Za muyi magana a waya"

Bata jira komai ba ta mayar da ƙofar ta rufe, ta juya ta nufi ƙofar gidanta da sassarfa ƙirjinta yana luguden daka. Bakinta ɗauke da addu'o'i kala daban-daban.

Ganin ƙaramar ƙofar gidan a buɗe saɓanin rufewar da tayi kafin ta fita shi ya ƙara tabbatar mata da Mukhtar ya dawo, ko da ta shiga cikin gidan sai ta rakuɓe a jikin ƙofar.

Idanunta tsaye ƙyam akan motarsa da yake fake a tsakar gidan, jikinta babu inda ba ya rawa.

Mara gaskiya aka ce ko a ruwa gumi yake, duk da sanyin iskar hunturu da ya fara kaɗawa bai hanata jiƙewa sharkaf da gumi ba.

Ta lumshe idanunta, wasu zafafan hawaye suka silalo daga idanuwanta, zuciyarta cike da takaici da Allah wadai na wannan taurin kai da rashin jin magana irin nata.

Ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba sun sha samun saɓani da Mukhtar kan fita unguwa mara muhimmanci.

Ya sha zaunar da ita yayi mata karatun dalla-dalla kan ra'ayinsa na rashin son ganin matarsa tana fita unguwa barkatai.

Ko sha'anin yɗan'uwanta ko nasa idan ba mai matuƙar muhimmanci bane bai cika barinta ba, ballantana sha'anin ƙawayenta waɗanda kai tsaye yake kiransu da tarkace.

Ta kai tsawon mintuna biyar a gurin tana tufka da warwara ba tare da samun hanyar da zai ɓulle da ita ba, daga bisani kawai sai tayi shahadar ƙuda ta mayar da ƙofar ta rufe, ta nufi cikin gidan ƙafafunta na harhardewa saboda rashin gaskiya.

"Daga ina kike?"

Ta jiyo fusatacciyar muryarsa yana tambayarta cikin tsawa.

Ƙam ta tsaya guri ɗaya, a hankali ta ɗaga idanunta ta kalleshi, yana zaune kan kujera mazaunin mutum ɗaya yana fuskantar ƙofar shigowa. Ya ɗaura ƙafa ɗaya kan ɗaya yana karkaɗawa, alamun da ke nuna tabbas tsiya yake ji.

Ƙyifƙifta idanu tayi, lokaci ɗaya suka cicciko da hawaye.

"My de..."

"Na ce daga ina kike?"

Ya katse ta tun kafin ta ƙarasa faɗin abinda tayi niyya.

Runtse idanu tayi, ta haɗiye wani kakkauran miyau sannan tayi ƙarfin halin cewa

"Daga gidansu Jiddah..."

"Na je har gidansu Jiddar ban same ki ba, ban tarar da kowa a gidan ba. Ki faɗa min gaskiyar daga ina kike yanzu Fareeda, idan ba haka ba Wallahi tallahi zan nuna miki wani ɓangare nawa da baki taɓa sani ba."

Idanunta ta sauke ƙasa, cikin sanyin murya ta kora mishi bayanin zallar gaskiyar daga inda take a halin yanzu. Tun daman can ita ba gwana bace a ƙarya, ko tayi nan da nan ake ɓaro jirginta, shi yasa ako wane irin hali ta gwammace ta faɗi gaskiya duk abinda zai faru ya faru.

"Ofishin yan sanda? Ke Fareeda? daga Ofishin yan sanda kike yanzu? Taɓɗijan! Lallai ma!!!"

Ya faɗi kalaman da wani irin yanayi mai bayyana kaiwa ƙololuwa a takaici da baƙin ciki haɗe da mamaki. Fareeda ta goge mishi hadda, ko da ya dage ta faɗa mishi daga inda take yayi tsammanin za ta faɗa mishi sun fito gidan walimar Amarya ce.

Matarsa a ofishin yan sanda sanadiyyar fita da tayi ba tare da izininshi ba shi ne ƙarshen tozarci da cin mutuncin da Fareeda ta taɓa yi mishi mai bala'in ƙuna a iya zamantakewar aurensu na shekaru shida.

Tabbas zai ɗau mataki, ya zama dole ya ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki kan Fareeda, ta yadda nan gaba ko da da amincewarsa ba ko wane karabitin unguwa za ta dinga tambayarsa ba.

Tsam ya miƙe tsaye daga kan kujerar da yake zaune, hannayen rigarsa ya fara nannaɗewa yana yi yana ciccije baki.

Idanu warwaje take kallonsa

'Rufe ni da duka zaiyi?'

Ta tambayi kanta a zuciya.

A iya zamantakewar aurensu duk bala'in Muktar ko dungurinta da yake yar yatsa bai taɓa yi ba. Lallai yau ta kai ƙololuwa wajen ɓata masa rai.

A tsorace ta zube ƙasa ta ɗora hannaye biyu a kanta ta runtse idanu haɗe da fashewa da ƙaƙƙarfar kuka. Cikin kukan ta fara magana tana yi masa magiya

"My dear... don girman Allah da darajar fiyayyen halitta SAW ka yi haƙuri... ka yafe min don Allah, wallahi in Allah ya yarda daga rana mai kamar ta yau bazan sake fita ba da izininka ba, kayi haƙuri don Allah kar ka duke ni..."

"Yi min shiru Fareeda!!!"

Ya katseta ta hanyar daka mata wani gigitaccen tsawar da yasa ta fara sakin fitsarin da tun ɗazu yake cike dam da mararta.

"Na yi shiru, wallahi na yi shiru, don Allah ka yi haƙuri..."

Wani murmushi mai bayyana matsanancin takaicin da zuciyarsa take ciki ya sakar mata, kan hannun kujerar da ya tashi ya ɗan ɗofana mazaunansa, da hannu yayi mata alamun ta tashi daga ƙasa ta hau kan kujera.

Da rawar jiki ta cika umarninsa.

Tsawon daƙiƙu casa'in yana ƙare mata kallo, Allah ya sani yana tsananin son Fareeda, soyayya kuma ba na wasa ba. Daidai gwargwado akwai zaman lafiya da kyakkyawar fahimtar juna tsakaninshi da ita.

Babban abinda yake haɗa shi da ita taurin kai ne da rashin jin magana, ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba ya sha sanar da ita yawan yawon zuwa gidan biki da suna shi ba shi a tsarin rayuwar zamantakewarsa da iyalinsa. Idan tana so su cigaba da tafiya cikin farin ciki da ɗasawa to tabbas ta bi abinda yake so, a lokacin za ta ce ta ji, har ma ta ƙara da ƙasƙantar da kanta ta bashi haƙuri, ta kuma ɗaukar mishi alƙawarin in Allah ya yarda baza ta sake ba.

Wannan ba shi ne karo na farko da ta fita ba da izininsa ba, ta sha yin haka babu adadi, lallai wannan karon idan bai ɗauki hukunci mai bala'in tsaurin da zai jijjiga duniyar Fareeda ba baza ta san Annabi ya faku ba.

"Ba dukanki zanyi ba Faree, a iya tsawon zamantakewarmu na taɓa dukanki?"

Da sauri ta girgiza kai alamar a'a!

"Kuma ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba kina ƙetare iyakar dokokin da nake gindaya miki ko?"

A kasalance ta ɗaga kai alamar eh!

"Ki buɗe bakinki ki amsa min."

"Eh! Don Allah..."

"Saurara Fareeda, ki daina haɗa ni da Allah, na yi haƙuri, na kuma yafe miki."

Da mamaki ta ɗaga idanunta tana kallonshi baki buɗe.

"Eh tabbas na yafe miki. Rufe bakin."

Kamar wata sakarya ta rufe bakinta, wani tsinkakken miyau da ya taho mata ta haɗiye da sauri.

"Ki shiga cikin ɗaki yanzu kiyi wanka, kiyi alwala, ki gyara jikinki kiyi sallar magriba. Sai ki nemi abu mai sauƙi ki dafa min, rabona da abinci tun karin safe."

Yana gama faɗin haka ya naɗe hannuwansa a baya, da wani irin taku na ƙasaita ya nufi cikin ɗakinsa, saɓanin ɗakinta da in dai yana gari anan suke gudanar da kusan komai na rayuwarsu.

Ko da ya shige ta fi minti biyu tana kallon hanyar da ya bi, mamaki take yi, mamaki mai matuƙar yawa.

'Me yake damunsa ne? kai ko dai ba shi lafiya? Duk faɗa irinna Muktar shi ne za ta mishi irin wannan laifin kai tsaye ya ce ya yafe mata? Me yake faruwa?'

Ire-iren tunanin da ke cikin zuciyarta kenan har ya ɗauro alwala ya fito ya tarar da ita a inda ya barta.

Idanu ya buɗe da mamaki ƙarara a fuskarsa.

"Menene haka kuma Sweety? Na faɗa miki fa yunwa nake ji."

Yayi maganar da sanyin murya idanunsa a kanta.

"Yi haƙuri, yi haƙuri Dear, yanzu zan samar maka abinda za ka ci."

Tayi maganar cikin sauri, a zabure ta miƙe tsaye ta ɗauki jakarta da mayafin da ya faɗi ƙasa ta nufi cikin ɗakinta da sauri, har tana harɗe ƙafafu.

Tana ɓacewa ganinsa ya ɗaure fuska tamau, yayi ƙwafa, ya cije gefen bakinsa na dama ya ƙanƙance idanu. Hannun rigarsa da ya naɗe don yin alwala ya warware sannan ya nufi hanyar fita daga ɗakin don zuwa masallaci.

Tunani yake, tunanin irin matakin da zai ɗauka akan Fareeda. Lallai ya kamata ya ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki, zai buge ta irin bugun daga kai sai me tsaron gida, ta inda zai lallasata tayi laushi, laushi kuma na har abada.

Wani tunani da ya kurtso zuciyarsa lokaci guda ya saka shi sakin wani tattausan murmushi, ya girgiza kai alamun samun gamsuwa.

*_Kar dai ku manta ina sayar da Datar MTN, mai so ta tuntuɓeni ta private 07039080978_*

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*4*_

Kasancewar tana da lafiyayyiyar soyayyar miyar da tayi jiya da daddare, sai kawai ta ɗora sanwar farar shinkafa.

A gurguje ta faɗa bayi tayi wanka ta ɗauro alwala, tana fitowa ta wanke shinkafarta ta zuba sannan ta tayar da sallar la'asar da basu samu damar gabatarwa ba suna gurin yan sanda.

A mafiyawancin lokuta in dai yana gari idan yayi sallar magriba ba ya fita daga masallaci sai ya sallaci isha'i, akwai karatun littattafan addini da Limamin masallacin yake musu tsakanin magrib da isha'i, in dai yana nan ba ya son rasa karatun.

Ko kafin ya koma gida ta kammala girkinta tsaf, tana da ƙanƙarar pure water a frig, sai tayi amfani da wannan damar ta dafa zoɓo da kayan ƙamshi ta jejjefa ƙanƙara a ciki. Ya shiga falon ne a daidai lokacin da ta gama shirya komai kan ɗan madaidaicin teburin cin abincinsu da yake can gefe ɗaya a cikin falon.

"Sannu da dawowa Masoyi."

Tayi maganar a tausashe, fuskarta ɗauke da lallausan murmushi, tana kallonshi cikin ido.

"Yauwa"

Ya amsa a taƙaice, da fuska kadaran kadahan.

A taƙaice ya kalleta ya ƙara kalla, ta yi kwalliya cikin wasu riga da wando na shan iska, kayan ko a ido basuyi alamar nauyi ba, kuma roba ne duba da yadda suka bi fatar jikinta suka lafe, sun fitar da ainihin shape ɗin jikinta.

'Fareeda ba dai ƙirar jiki mai kyau ba, tubarkallah ma sha Allah, baƙa ce a kalar fatar jikinta, amma ba irin baƙinnan ƙirin ba, baƙinta mai kyau ne da ɗaukar idanun mai kallonta.

Doguwa ce a yanayin halittarta, sai dai irin tsawonnan da bai yi ma mace yawa ba, ga kuma yar ƙiba da cikar baya da ƙirji da take da shi, waɗannan abubuwa uku su suka taka muhimmiyar rawa gurin daidaita tsawonta.

A fuska baza a kirata kyakkyawa ta gaban kwatance ba, amma kuma baza a jefata layin munana ba, tana da kyau daidai gwargwado.

Kuma kasancewarta wacce ta laƙanci sirrin gayu da iya ɗaukar wanka idan ta fito baza'a taɓa cewa bata yi ba, za'a kalleta a ƙara kallah, ba kuma wai ɓata lokaci take a gurin shafa wannan goga wancan a fuskarta ba, a'a!

Yʻar powder kawai take shafawa sama-sama, sai ta goga man baki a laɓɓanta da suka kasance masu ɗan tudu, sanin sirrin gayun yʻa mace kuma yasa take ɗan ƙara tsuke bakin, lokaci bayan lokaci kuma tana ɗan tura leɓen ƙasa gaba sak na shagwaɓaɓɓun mata.

Idan ta ɗan zizara kwalli a idanuwanta, kasancewarta mace mai yalwar gashin gira tana ɗaukan wasu daƙiƙu gurin tacewa da daidaita kwanciyarsa.

Har yanzu da take cikin shekarunta na ashirin da tara fuskar yʻanmata yʻan sha takwas take da, idan ba sani aka yi ba baza'a taɓa cewa ita ce tayi haihuwa uku yʻayʻa huɗu ba saboda kyawun jikinta.

Haihuwarta na farko da na biyu duk basu zo da rai ba, sai na uku ne ya tsaya, da lokacin haihuwar yayi ta haifi yʻan biyu duk maza.

Sun shekara ɗaya da wata takwas cif kafin mahaifiyarsa wacce suke kira Hajiyarmu ta ɗauki yʻayʻan yaye, a yanzu haka suna can gidanta a unguwar dosa. Ta ko wane ɓangare Fareeda ta kai irin macen da ko wane namiji mai hankali zai so aura a matsayin matarsa, babban matsalarta rashin jin magana da taurin kai. Shi ya ƙi sakar mata mara ta dinga fita yadda take so, ita kuma a matsayinta na wacce take ƙasansa ta ƙi haƙura ta watsar da tsarin rayuwarta ta bi abinda yake so. Sai yaushe ne za ta gyaru...?'

"Masoyi lafiya dai ko? ga abincinka na gama haɗa duk abinda za ka buƙata"

Saukar muryarta shi yayi nasarar dawo da shi daga duniyar zurfin tunanin da ya afka. Bai ce mata komai ba, kuma a maimakon ya nufi ɓangaren da ta jera mishi abinci sai ya kama hanyar zuwa ɗakinsa.

Da sassarfa ta bi bayanshi, yana shiga ɗakin ta ɗora ƙafa a inda ya cire tasa.

"Ya aka yi?"

Ya tambayeta da mamaki a fuskarsa.

Narai narai tayi da idanu suka cicciko da ƙwallah, ta riƙo hannayensa guda biyu a cikin nata.

"Na san na ɓata maka Mijin Fareeda, don Allah kayi haƙurii..."

"Na zaci mun gama wannan maganar?"

Ya katse ta idanunsa a cikin nata.

Ƙwayoyin idanunta ta saukar da su ƙasa a hankali, sai a lokacin ta ba hawayen damar sauka zuwa kumatunta, sai ta sake ɗaga idanu ta kalle shi

"Walwalarka nake buƙatar gani Masoyi, idan baka huce ba don Allah kayi min faɗa, kayi ta faɗa idan ta kama ma ka haɗa min da duka har zuwa sadda za ka ji sauƙin zuciyarka. Wannan yanayin damuwar da nake gani shimfiɗe a kyakkyawar fuskar mijina sam ba na jin daɗinsa."

Sai kuma ta fara ɗan jan hanci tana shessheƙa, hawaye wasu na korar wasu.

Ya buɗe baki zaiyi magana ta yi saurin katse shi da cewar

"Don Allah ka yafe min mijina..."

A sannu ta silale zuwa ƙasa za ta durƙusa kan gwuiwoyinta yayi saurin riƙe kafaɗunta, ya ɗagota tsaye ya rungumeta a jikinsa.

Kamar daman hakan take jira, da saurin gaske ta sa hannayenta biyu suka zagaye bayansa ta ruƙunƙumeshi, tana cigaba da jan shessheƙar kukanta a hankali, da wani irin salo na karyar da zuciyar wadda aka yi ma laifi. Ta sani Mukhtar ɗin yana da faɗa, amma duk masifarsa ba shi da riƙo ko kaɗan, faɗarsa kamar mai hawa da saukar aljanu da yayi suka jirge shi kenan zai koma kamar ba shi ne ya gama zazzage tsiya ba.

Ko yanzu ta tabbatar yana wannan ciccijewar ne don bai samu ya sauke tsiyar da ke cunkushe a cikinsa ba, haƙuri da uzuri akan laifin da aka yi masa ba halinsa bane sam, ko ɗan yaya ne sai ya zazzageta. Da wannan rashin walwalar da ya tsira ita kam gara ya balbaleta da bala'i a wuce gurin.

Ƙananun kitson kanta da suka bayyana saboda hularta da ya faɗi ya shafa da hannunsa na dama, yayi ƙasa ƙasa sosai da muryarsa, faɗan dai da take jira yayi yau ba ya ra'ayi.

"Faree, ina tsananin sonki kin sani. Me yasa baza ki taushi zuciyarki ki bi abinda nake so mu zauna cikin farinciki ba?"

"Wallahi zan bi, na ma bi in Allah ya yarda. Don Allah kayi haƙuri, kayi min faɗa."

Ɗago kanta yayi daga ƙirjinsa yana kallon fuskarta, hawaye ne kaca-kaca, yƴar kwalliyar da akayi mishi duk ta gama ɓaci da hawaye. Ƙayataccen murmushi ya sakar mata, yasa babbar yatsarsa ya fara ɗauke mata hawayen, har lokacin murmushin da yake yi bai bar kan fuskarsa ba.

"Wannan faɗan da kike ta maimaitawa inyi miki yau dai ba na jin yin ta. Ko dole ne?"

Ƙara shagwaɓe fuskarta tayi ta girgiza mishi kai alamar a'a!

"Ki gane wani abu Baby, ba abin arziki bane kusan ko wane lokaci a gidannan inyi ta ɓaɓatu ina maimaita faɗa kan abu ɗaya. Maganar fita unguwa ba tare da izinina ba daga jiya na ɗaukar ma kaina alƙawarin in Allah ya yarda bazan sake miki hargagi na tashin hankali ba. Ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba kin sha fita ba tare da izinina ba, na kuma faɗa miki ba na so, in dai faɗa da tashin hankalin miji na sa mata ta daina laifi da tuni kin daina.

Ya kike so inyi miki? wane mataki kike so in ɗauka a kanki? ko so kike in fara bi cikin yƴan'uwanki ina kai ƙararki?"

Ya girgiza kai sannan ya cigaba.

"Baza'ai haka da ni ba in sha Allah! Ni bani da ra'ayin in kai ƙarar matata gurin iyaye ko yan'uwanta. Soyayya ta sa na auro ki, wannan soyayyar ita za ta sa in cigaba da haƙurin zama da ke iya yadda zan iya. Amma fa ki sani, ni dai a matsayina na mijinki bazan daina hana ki zuwa unguwa marasa muhimmanci ba, tsarina ne wannan, ra'ayina ne.

Ke kuma ra'ayinki ne kibi dokar da na shimfiɗa miki, idan ba ki so ba kuma ki bi son zuciyarki. Ni kuma duk sadda haƙurina ya gaza zan ɗauki ƙwaƙƙwaran mataki ne da baki taɓa tsammanin zan iya ɗaukar irinsa ba.

Magana ta wuce, don Allah kar mu sake tayar da wannan zancen. Na haƙura, na yafe miki fitar da kika yi jiya, ina roƙon Allah ya yafe miki tsinuwar da mala'iku sukai ta miki jiya tun daga ficewarki a gidannan har zuwa dawowarki."

Jikinta ne yayi sanyi, sanyi kuma sosai. A iya zamantakewarsu basu taɓa zama yayi mata irin waɗannan maganganun masu bala'in kashe jiki da jefata cikin tunani ba.

A hankali ta mayar da kanta a ƙirjinsa ta kwantar, zuciyarta cike da addu'ar Allah ya bata ikon daina fita ba da izininsa ba, Allah ya bata ikon daina aikata duk wasu abubuwa da ta san ba ya so a halayyarta.

"Na gode Mijinah"

Ta faɗa mishi haka da muryarta mai bayyana sanyin da jikinta yayi.

Bata mishi alƙawarin za ta daina satar fita ba, domin ba wannan ne karo na farko da tayi mishi alƙawarin ta daina ba. Amma ta sha alwashin zai gani a ƙasa, za ta daina in sha Allahu, daga jiya in Allah ya yarda baza ta sake ba.

"Wayyoooo... Faree cika ni mana? Yunwa fa nake ji kin sani, na shigo ɗaki kuma kin biyo ni kin ƙwaƙumeni. Ko kema yunwar abinnan kike ji in fara ƙosar da ke kafin in ƙosar da cikina?"

Da saurin gaske ta sake shi tana ɗan dariya haɗe da sunkwui da kanta ƙasa alamun ya bata kunya, ta kasa cewa komai.

Dariyar shi ma yayi, yana son matarsa, ganinta cikin farin ciki ba ƙaramin jefa shi a farin ciki yake yi ba. Ƴar soyayya ce ita, ta san salo-salo na kwantar da hankalin ɗa namiji, a mu'amalarsu ta auratayya tana ba shi ƙololuwar farin ciki, shi yasa ko wane lokaci kishi da soyayyarta yake ƙara ninninkuwa a zuciyarsa. Shi fa bai ƙi ace a duniyarta bata san kowa ba sai shi kaɗai, shi kaɗai yake so ta fuskanta kuma ta sa a gabanta, idan ya ce mata baƙi fari ne ta kalle shi a fari tas tas! Idan kuma ya ce a'a ya zauna a a'a har abada.

"In kawo maka abincin nan ne?"

Ta tambaye shi bayan ta riƙe hannunsa na hagu a cikin na damanta.

"A'a! zan fita falo. Wai da so nake in ɗan watsa ruwa a gurguje ko zan fi jin daɗin cin abincin."

Da sauri ta shige banɗakinsa ta tara masa ruwan ɗumi daidai yanayin zafin da yake so.

Ko da ta koma cikin ɗakin har ya gama shirin shiga wanka.

"Allah yayi miki albarka."

"Ameen mijin Fareeda. Ko inzo in cuɗa maka baya?"

Ta ƙarasa tambayar haɗe da kashe masa ido ɗaya.

"Ina maraba da hakan ƴan matana"

Musayar murmushi suka yi a tsakaninsu, ya damƙi ƙugunta ya riƙe suka fara taku a hankali kamar wasu indiyawa zuwa cikin banɗaki, sai musayar kallon cikin idanun juna suke yi da lallausan murmushi kan fuskokinsu, masana sun ce kallon cikin idanu tsakanin miji da mata yana ƙara danƙon soyayya.

A ƙarshe dai sunyi wanka sun fito, bayan sun ɗauki lokaci mai tsayi suna murje juna da salon soyayya.

A gurguje suka gama shiryawa suka nufi falo, kai tsaye teburin cin abinci suka wuce, cike da girmamawa taja mishi kujera ɗaya daga cikin huɗu da suke gurin ya zauna.

Ita ta ciyar da shi cikin yanayin soyayya yana ci tana kora mishi da sassanyar zoɓo har ya bata tabbacin ya ƙoshi. Ko da ya nemi ya ciyar da ita ɗan kaɗan taci, tashin hankalin da ta shiga a yinin yau ya taka muhimmiyar rawa gurin cunkushe mata cikinta, ba ta jin yunwa sam, kuma ba ta jin cin komai.

Falonsu ya koma ya zauna kan kujera mazaunin mutum uku yana kallon labaran duniya ƙarfe tara. Ita kuma ta tattare kayan abincin ta kai kicin, a daren tayi wanke-wanken kwanonin da suka ɓata, sauran abincin kuma ta adana shi yadda bazai lalace ba.

Har ta kama hanyar fita daga kicin ɗin sai ta koma. Kofi ta ɗauka ta tsiyayi ruwan zafi ta jefa lipton a ciki.

Ta fasa ƙwai guda ɗaya a wani kofin daban ta karkaɗa shi sosai ya tsinke, sannan ta sake ruwan lipton ɗin a ciki ta jujjuya ya haɗe jikinsa. Runtse idanu tayi ta shanye.

Da sauri ta buɗe ɗaya daga cikin durowar kicin ɗin ta ɗauki cingam ƙwara ɗaya ta ɓare ta jefa a bakinta saboda tashin zuciya.

Ita ɗin ba gwanar shan magungunan mata bane, amma duk wani abu da za ta ji an ce natural ne tana ƙoƙarin gwadawa don ta ga ingancinsa. Ƙwai da lipton tun da ta gwada sau ɗaya ta ga yayi mata aiki sosai, da gaugawa yake saukar da ni'ima a jikinta, shi yasa tun da ta riƙe sirrin ba ta wasa da shi.

Can falo ta koma, a gefenshi ta zauna, ta zame ta ɗan kwantar da kanta a kafaɗunsa suka cigaba da kallo.

Basu tashi daga kallon ba sai sha ɗaya da kwata na dare, bayan labaran duniya arewa24 ya maida suka kalli shirin da ake haskawa a daidai wannan lokacin.

Da ganin take-takensa ta san a ɗakinsa za su kwana, don haka ta ba shi uzurin za taje tayi shirin barci a ɗakinta. Kwalbar zumanta mai kyau da yake ajiye a gaban madubi ta ɗauka ta tsiyayi cokali uku ta shi, ta dangwali kaɗan tayi matsi da shi. Yana saurin saukar da ni'ima, ko a bushe kike ƙayau mayau in dai ya karɓeki minti biyu yayi yawa za kiji saukar lema a ƙasa.

Wani irin biyayya da soyayya take sabunta masa a wannan dare, ta faranta masa fiye da yadda yake tsammani, ita ta riƙe linzamin dokin ta barshi yayi sukuwa yadda yake so, ko kaɗan bata nuna gajiyawa ba, sai shi ne ma ya dinga tausaya mata yana shi mata albarka.

*

A iya tsawon kwanaki huɗu da ya ɗauka na hutunsa zama na zallar farin ciki da soyayya ne a tsakaninsu. Har wani suna ya raɗawa kwanakin

"Ranakun sabunta amarci."

Tun ranar litinin ya kamata ya koma gurin aikinsa can kudancin kaduna, amma saboda armashi da daɗin da yake tattare da waɗannan kwanaki ya kira Ogansa yayi ƙaryar ba ya jin daɗi.

Kwanaki biyu aka ƙara masa, bahaushe ya ce daɗinsa da gobe saurin zuwa. Sai ga shi kuwa har ranar tafiyarsa ta zo. Soyayya ruwan zuma, kamar wasu sabbin aure haka Fareeda ta tasa shi gaba da yɣan koke-koke duk inda ya ɗaga kafa nan take mayarwa.

Sai da ya dakatar da duk wasu shirye-shirye da yake yi yayi rarrashi mai dalili, ya kwantar mata da hankali tare da alƙawarin ranar juma'a da wuri zai dawo in Allah

ya yarda. Haka dai suka rabu ba tare da zukatansu sun so rabuwa a daidai wannan lokacin ba.

Da gaske ne fa soyayya ba ta tsufa sai dai masoyan su tsufa, ko ɗan kaɗan ne mu dinga ƙoƙarin sabunta soyayyarmu a zukatan mazajenmu.

****

Tsawon sati uku da suka biyo baya zaman lafiya da ƙaunar juna ne a tsakaninsu. Yau litinin yayi sammakon komawa gurin aiki, tun da ya tafi ta kwanta tana sharɓar barci, wayarta na ajiye a daidai kanta, amma da yake ta rage ƙarar wayar shi yasa aka kira ta har sau biyu bata ji ba, sai a kira na uku ta jiyo ƙarar kamar a mafarki.

A kasalance ta buɗe idanu, miƙa tayi haɗe da salati, ta ɗauki wayar yana daf da tsinkewa. Ƙanwarta Masrura ce take kira

"Hello, Ummu Sultan barka da rana."

"Aunty Fareeda, kina gida ne?"

Ta tambayeta da murya mai baiyana damuwa da rashin walwala.

Ƙirjinta ne ya buga dam! da sauri ta miƙe zaune daga kwance, hankali tashe ta amsa da cewar tana gida, me yake faruwa?

"Tun ɗazu ga mu a asibitin Garkuwa da Aunty Binto, kiyi sauri ki zo, haihuwa ce ta zo mata da gardama, ni da Mustapha tun ɗazu ga mu a asibitin..."

Ƙit wayar ta katse...

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*5*_

Cikin wani irin matsanancin tashin hankali da fargaba ta dira ƙasa daga kan gadon, hannunta na hagu ɗore akai, hannun dama kuma riƙe da wayarta tana bin bayan kiran ƙanwarta, amma sam ya ƙi shiga, amsa ɗaya kwamfuta yake bata, wayar a kashe take.

Sai daga bisani ne tayi tunanin kiran yayansu Mustapha, ta kira shi kuma sau uku wayar tana ringing amma ba'a ɗauka ba.

Hankali tashe ta kira Aunty Murja. A ɗakinsu su Biyar ne, kuma iyayensu sun rasu tun kafin suyi aure, Aunty Binto ce kawai aka aurar da ita kafin rasuwar iyayensu.

Da yake mijin Aunty Binto mai halin dattako ne, shi ya tayata riƙon ƙannenta har zuwa aurar da su. Shi yasa Binta kamar uwa take a gurinsu, ta wahala da su, ba ƙaramin ƙauna da shaƙuwa ke a tsakaninsu ba, da wannan dalilin yasa idan abu ya samu ɗaya ji suke kamar ya samu dukkansu ne.

Hankalinsu bai kwanciya sai an samu maslahar wannan matsalar. Aunty Binto yaran da ta haifa a cikinta biyu ne kacal, wannan cikin shi ne na uku, ta same shi ne a lokacin da ta daɗe da fitar da tsammanin sake haihuwa.

Kuma cikin sai ya zo mata da matsaloli, da farko taita zubar da jini kamar bazai zauna ba, sai kuma Allah yasa cikin ya tsaya bai fita ba, saboda wannan zubar jinin da tai ta yi akai-akai yasa cikin ƙara watanninsa, yanzu cikin yana cikin wata na goma sha uku ne.

Dukkansu cikin zakwaɗin hauhuwar suke, hankalinsu a ƙumba, duk addu'arsu Allah ya sauketa lafiya. Ba'a kwana ɗaya biyu basu kira ta a waya sun ji lafiyarta ba. Ba ƙaramin shiri suke yiwa wannan haihuwa ba, saboda an daɗe ba'a yi ba.

Fatima wacce kakanninsu suke kira da Bintoto ita ce babbansu, sai Aunty Murjanatu, sai Yaya Mustapha, sai Fareeda, da autarsu Masrura.

Irin yadda ta ji muryar Aunty Murja a sanyaye tayi sallama bayan ɗaga wayar shi ne abinda ya ƙara ɗugunzuma hankalinta, a bayan sallamar kuma duk surutu irin na Aunty Murja shiru tayi, bata ce komai ba.

Sai Fareedar ce kiɗime ta ce

"Aunty Murja ya mai jikin? ta haihu kuwa...?"

"Har yanzu dai Fareeda, sai dai mu cigaba da tayata da addu'a, haihuwa ta ƙi zuwa sai uban wahala take sha. Likita ta ce nan da minti arba'in idan bata haihu da kanta ba sai dai ayi mata aiki a cire babyn..."

"Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un"

Tayi salatin jikinta na rawa, kasancewarta mai saurin kuka nan take idanunta suka cicciko da hawaye, babu abinda take tunawa a ranta sai yadda tun farkon samun cikin Aunty Binto ta yanke tsammani da rayuwar duniya, gani take kamar sanadiyyar ajalinta take ɗauke da shi.

"Ba komai, mun dogara ga Allah, za ta haihu lafiya in sha Allahu, kina hanyar zuwa ne asibitin ne?"

Murja ta tambayeta.

"Eh! gani nan zuwa yanzu. Allah ya sauketa lafiya."

Tayi addu'ar da wani irin sanyi a muryarta, lokaci guda hawayen da suke cikin idanunta suka gangaro zuwa kuncinta.

A ɗarare ta nemi gefen kujera ta ɗosana mazaunanta, kamar mai ciwon baya, saboda yadda jiki da hannayenta suke rawa daƙyar ta iya lalubo lambar mijinta ta kira.

Kiran biyu tayi mishi bai ɗaga ba, kafin ta kira na uku sai shi ya biyo bayan nata kiran.

"Paradise"

Ya kirata a tausashe, da ɗaya daga cikin kyawawan sunayen da yake kiranta da su.

Sai da ta ɗan ja shessheƙa sau biyu, sannan a kasalance cikin hawaye ta faɗa mishi abinda yake faruwa.

"Kukan ya isa haka don Allah, kiyi shiru, ki kwantar da hankalinki matata. Kin ji ko? Za ta haihu lafiya in sha Allah. Zan taya ki yi mata addu'a..."

"Hubbyna, don Allah, ka barni in je dubata a asibitin."

Ta ƙarasa maganar a marairaice.

Daga can ɓangarensa ɗif ya ɗauke wuta, kamar tana ganinsa lokaci ɗaya yayi kini-kini da fuska.

"Idan kin je me za kiyi mata a daidai wannan gaɓar da take ciki?"

Ya tambayeta da cusasshiyar murya.

"Duk su Aunty Murja fa suna can, har da Ya Mustapha, ni kaɗai ce ba na nan. Don Allah ka bar ni in je ko fargaba da tashin hankalin da nake ciki zai ragu..."

"Look Fareeda, a daidai wannan lokacin addu'arku ita tafi buƙata. Kuma ko daga ina za ki iya yi mata ya iske ta, su ma su Mustapha suna can ne kawai ba don za su iya sakawa ko hanawa ba. Don haka kiyi haƙuri, babu inda za ki je ayau, idan ta haihu lafiya na yarje miki gobe da misalin 11am ki shirya kije ki duba ta a gida ko asibiti. Faƙat!!!"

Ƙit ya katse wayar, ba tare da ya jira ko za ta sake cewa wani abu ba.

A kiɗime ta ɗaga idanunta ta kalli agogon falon, ƙarfe sha ɗaya da minti hamsin na safe.

Idan ta tuna ya hanata fita, kuma Aunty Binto da take matsayin uwa a gare su ita ce kwance a gadon asibiti, ƙafarta ɗaya a duniya ɗaya a lahira, amma mijinta ya hanata fita. Ƴan'uwanta duk suna can, ita kaɗai ce anan, tana zaune ba tare da sanin halinda ƴar'uwarta take ciki ba.

Kawai sai ta ɗora hannu biyu akai ta fashe da wani balaƴaƴɣen ƙaƙƙarfar kuka, a daidai lokacin kiran Ya Mustapha ya shigo wayarta, sai tayi cilli da wayar kan kujera ta cigaba da rusa ihu, hannu biyu akai, sai bubbuga ƙafafu a ƙasa take yi kamar ƙaramar yarinya.

"Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un! Me zan gani haka ni Fatee? Fareeda lafiya? Wa ya rasu?"

Fatima da shigarta gidan kenan ta tarar da ita cikin wannan mawuyacin halin ta jero mata tambayoyin fuskarta na bayyana matsanancin tashin hankali.

A irin yadda ta tarar da ita ta sa a ranta kawai rasuwa aka yi, rasuwar ma irin mai matuƙar muhimmancin nan.

Sai da ƙyar ta samu ta rarrashi Fareeda tayi shiru sannan ta sanar da ita abinda yake faruwa, kafin ta ce komai kicin ɗinta ta wuce ta buɗe frig ta ɗauko gorar ruwa mai matsakaicin sanyi da kofi, falon ta koma ta tsiyayi ruwan ta kafa mata kofin a baki.

Ba ta da zaɓin da ya wuce shan ruwan, sai sauke ajiyar zuciya take yi a jejjere irin na wacce ta daɗe tana kuka.

A gefenta Fatima ta zauna, cikin rashin damuwa ta fara cewa

"Ke kam Fareeda na ga ranar da za kiyi wayau. In banda rashin wayau irin naki ai da bari kikai sai kin isa asibitin sannan ki kira Mukhtar ki faɗa mishi abinda yake faruwa. Kinga a lokacin kin riga kin fice, ko ya ce ki dawo gida kin dai riga kin gano halin da yar'uwarki take ciki. Amma ni a ganina ko yanzu bai ɓaci ba, ba kin ce yau ya koma gurin aikinsa ba?"

A kasalance ta ɗaga kai, alamar eh!

"To ga shawara, amma fa idan kina so, kuma idan kin ga dama..."

"Wace shawara ce ƙawata?"

Ta tambayeta cikin zakwaɗi, da tunanin za ta sama mata mafita cikin sauƙi kamar yadda ta saba samar mata a baya.

"Ba kin ce yau Mukhtar ya koma gurin aiki ba?"

"Eh! Ɗazu da safe."

Ta sake amsawa a ƙagauce.

Fari da idanu Fatiman tayi, ta buɗe jakar hannunta ta ɗauki cingam guda ɗaya ta ɓare ta jefa a baki, ta yasar da ledar nan tsakar falon cikin rashin damuwa.

Hannunta da ta yar mata da ledar cingam a tsakar falonta da yake gyare tsaf ta bi da kallo, sannan ta kalli ledar cingam ɗin, ta cuna baki gaba, idan akwai abinda ke yawan shiga tsakaninta da ƙawartata ƙazanta ne, ba ta kiyaye inda ya kamata ta yasar da datti.

Ƙoƙarin danne ɓacin ran da yake yunƙurin taso mata take yi, ta haɗiye miyau sau biyu a jere.

"Kin fara magana kuma kin yi shiru."

Tayi maganar tana kallon yadda take tauna cingam ɗin cakal cakal babu aji ko miskala zarrah, kamar ba ɗiya mace ba.

"Hajiyata ai kawai ki fice abinki, maganin dai tsinuwar mala'iku kina tafe kiyi ta istigfari. Aunty Binto ta fi ƙarfin komai a gurinku, ba ma kamar ke, ki tuna yadda duk cikinku ta fi shaƙuwa da ke da fifitaki? sau nawa tana ba ki abu ba tare da ta ba sauran ba? Dubiyar mare lafiya za ki je da sadar da zumunci, Allah ma bazai kama ki da laifi ba. Amma fa kar ki daɗe, kiyi sauri ki dawo ɗakinki."

Shiru tayi cikin tunani, a yanayin da take ciki Allah ya sani hankalinta ya fi karkata kan tafiya a bisa zaman. Ta san zance ne kawai na Fatima da ta ce maganin tsinuwar mala'iku istigfari, amma dai ko ba yau ba za ta roƙi mijinta ya yafe mata. Ta san in sha Allahu har za ta fita ta dawo ba tare da ya sani ba, tunda yau ya koma gurin aiki, babu yadda za ayi ya dawo balle har yasan ta fita, za ta je ta dawo lafiya ba tare da ya sani ba, idan ya dawo ko cikin hira ne za ta roƙi ya yafe mata ba tare da ta faɗa masa laifin da tayi ba...

Tana wannan tunanin Fatima ta katse ta da cewa

"Kin ga ni fa daman kasuwa zan tafi siyayya na ce bari in leƙo mu gaisa ko kina da saƙo? kin tuna kuɗinnan da Baban Jiddah ya bamu? ko za ki sayi wani abu a kasuwa? ni kam wata haɗaɗɗiyar doguwar riga na gani a jikin Nabila, irinta zan siyo."

"Taɓ! Ai ni babu abinda zan siya. Kina ganin hidimar kuɗi ya taho min, zagewa zanyi inyi ma Aunty Binto hidima ta bajinta, Allah dai ya sauketa lafiya."

"Ameen ya Allah"

Da haka suka yi sallama, Fatima ta fice daga gidan, ita kuma ta fara shirya tafiya duba yar'uwarta a gaggauce, ta rasa dalilin da yasa ƙirjinta ke yawan bugawa akai-akai, amma wannan fita ta riga ta yi niyya, babu abinda zai hana ta zuwa.

Tana kulle ƙofar falonta kiran Mukhtar ya shigo wayarta, ƙirjinta ne ya sake wani ƙaƙƙarfan bugun da yasa ta tsuguna a ƙasa tana jan inna lillahi, daƙyar ta iya daidaita kanta sannan ta ɗaga wayar, da cusasshiyar murya mai bayyana matsananciyar damuwa.

"Matata? ya Auntyn tamu da jiki? kin samu labarin ta haihu kuwa? na kira Mustapha in ji ya mai jikin amma bai daga ba."

"Da sauƙi dai, har yanzu basu kira ni ta haihu ko aikin za'a shiga da ita ba."

Ta jera mishi maganganun a hankali, ƙirjinta na cigaba da bugawa.

"Za ta haihu lafiya da yaddar Allah. Ki kwantar da hankalinki kin ji ko?"

Yayi maganar da kulawa.

"Tam! Allah yasa."

"Kiyi haƙuri Baby, na san kina jin babu daɗi na hana ki zuwa, idan kin duba ko kin je ba abinda za ki iya yi. Ki cigaba da yi mata addu'a daga gida kin ji?"

'Hmmm! Dole ka ce haka tunda ba yar'uwarka bace.'

Ta faɗi hakan a zuci, a fili kuma sai ta ce.

"Ba komai, na gode mijina. Allah ya huta gajiyar tafiya.'

"Ameen"

A zahirin gaskiya da wannan wayar da suka yi jikinta yayi sanyi da fitar, kamar ta haƙura ta zauna, amma shaiɗan ya cigaba da azalzala mata kan ta fita. Yana ƙara tunasar da ita muhimmancin yayarta a gare ta. Da saƙa mata wasu tunanika na banza da wofi.

'Ba fata take yi ba, yanzu idan Auntyn ta rasu fa? shi kenan duk yan'uwanta sun gana da ita itace basu haɗu ba? saboda wani umarni na namiji da ba shi da tabbas? mijin da za ta iya canza shi amma baza ta iya canza yar'uwarta ba'

Kawai sai ta miƙe tsaye, ta kalli jikinta, ɗinkin doguwar rigar atamfa ce, ta yafo babban gyale a kai. Sai ta buɗe ƙofar falon ta shiga cikin ɗakinta ta aje gyalen akan gado ta ɗauki hijabi ta saka. Da sassarfa ta fice daga gidan bayan ta kulle ko ina.

******

"Langes, hanga ta arewacin gabar kaga wata fatsa da take tahowa, idan ba gizo idanuna suke min ba sai naga kamar rangaji take tamkar reshen bishiya a cikin iskar damina."

Da jajayen idanunsa ya waiga zuwa inda abokin nasa yake magana, sai yayi arba da ita, duk da hijabi ne sanye a jikinta bai ɓoye asirin ƙirar jikinta ba, hijabin ya kwanta a jikinta, ƙirjinta ya taso sosai ta gaban hijabin, duk da tashin hankalin da take ciki ba bazar-bazar take tafiya ba, a nutse take tafiya, ga wanda bai santa ba zai iya cewa yanga take yi, amma a zahirin gaskiya haka yanayin tafiyarta yake.

"Kai, gaskiya ni fa na fola, miyau na ya tsinke. Ya kamata in mayar da kwaɗayina ta hanyar ɗanɗanawa..."

"Kai fa Villa ɗan iska ne, ba ka da mutunci, don Allah ka ƙyaleta ta tafi..."

Ko kafin abokin nasa ya rufe baki har ya fita daga cikin napep ɗin ya nufi gurinta.

"Hajiya ya? tafiya ne?"

Manyan idanunta ta ɗaga ta kalleshi a kaikaice, sai tayi arba da napep ɗin da yake fake a can bayanshi.

"Eh! shatar napep nake nema zuwa asibitin garkuwa."

Saukar tattausan muryarta a kunnuwansa yasa shi lumshe idanu kamar tsohon kwarto, ya haɗiye tsinkakken miyan bakinshi, ya fara magana da yanayi mai baiyana farin cikin da zuciyarsa take ciki.

"Hajiya kiyi murna kakarki ta yanke saƙa, zo muje kawai."

Yayi maganar yana wani irin dariya da ta rasa gane inda ya dosa.

"Nawa zan baka?"

"Haba kar ki damu Hajiya, bazai gagareki ba in Allah ya yarda."

Ya juya ya nufi napep ɗin tana biye da shi a baya, signal yayi ma abokin nasa da yake zaune a bayan napep ɗin da sauri ya fice ya koma gaba, bayan ya kakkaɓe mata kujerar bayan.

Ba tare da tunani ko fargabar komai ba tayi basmala ta shiga ta zauna, tana ƙara rungume jakarta a jikinta.

"Hajiya kiyi haƙuri, abokina zai ɗan raɓe nan kusa da ni zan sauke shi can babban titi..."

"Ba damuwa."

Ta amsa idanunta na kallon waje, zuciyarta cike da tunanin yanzu ko a wane hali yayarta take?

*_Kuyi haƙuri da jinkirin posting ɗin da nake yi. Kar dai ku manta ina sayar da datar MTN_*

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*6*_

Ta kasa kiran ko ɗaya daga cikin ƴan'uwanta a waya, bata san wane irin labari za ta ji kan Auntynsu ba, mai daɗi ko akasinsa? Da wannan dalilin yasa ta zaro wayarta a jaka ta kashe, aka ce zuwa da kai ya fi saƙo, gara ta je ta ga halin da ake ciki da idanunta.

"Langes, yanayin iskar garin ya canza, ɗan fesa min turarennan ta baya-baya ko za mu shaƙi iska mai daɗi."

Kalaman da kunnuwanta suka jiyo daga bakin direban napep ɗin kenan, ko kafin ta ce wani abu ko yunƙurin yin wani abu kawai sai jin feshin wani irin turare mare daɗin ƙamshi tayi a fuskarta.

Cikin fushi da ɓacin rai ta buɗe baki za tayi magana kawai ta ji jikinta ya mutu, gaɓoɓinta suka yi sanyi gaba ɗaya, ko ɗan yatsarta ta kasa ɗagawa. Cikin ƙasa da minti ɗaya idanunta suka yi wani irin nauyi sosai, lokaci guda wani nannauyan barci yayi awon gaba da ita.

Kusan a tare abokai biyun suka waiga baya suna kallonta, lokaci guda suka haɗa idanu sukayi murmushi, sai kawai ya cigaba da ɓanana wutan napep ɗin don zuwa inda suka nufa.

Langes da Villah taƙadiran matasa ne da suka addabi unguwarsu da sace-sace, neman mata, shaye-shaye. Duk yadda suke waɗannan tsiyatakun an sani ba wai ba'a sani ba, amma an kasa ɗaukan wani ƙwaƙƙwaran mataki a kansu. Ko yan sanda sun kama su basa wuce kwanaki biyu a kulle, saboda ɗaurin gindin da suke da shi a gurin Ciyaman ɗin ƙaramar hukumarsu.

Bisa shawarar mai unguwa da dattijai a cikin unguwa sai aka yanke shawarar nema musu sana'ar yi, wataƙil hakan ya zama sanadiyyar shiryuwansu. Kafin tunkararsu da batun sana'a sai da aka ɗauki sati uku cur ana jan su a jiki, yi musu nasiha, tare da nunar musu da illar munanan ayyukan da suke aikatawa, aka kawo musu manyan misalan da ya tabbatar musu Chairman fa ba gata yake musu ba, yana amfana da su ne don ya cimma manufa ta ƙashin kansa, ba don ya tallafi rayuwarsu a matsayinsu na matasa ba. Sai da aka fahimci sun fara laushi sosai, hankali ya dawo jikinsu, sannan aka bijiro musu da tambayar wace irin sana'a suke so suyi? su faɗa in dai jarin da suke nema bai zarce naira miliyan ɗaya ba in Allah ya yarda za'a ba su.

_Bayan shafe sati guda suna shawarwari a tsakanin su biyun sannan zukatansu ta tsayu akan a sai musu keke napep. Babu ɓata lokaci kuwa aka siya musu, amma an aje musu sharaɗin cewa duk bayan kwana uku za su dinga bayar da balance a fadar

mai unguwa har su tara kuɗin da za'a sake siyan wata napep ɗin, su mallaki kowa ɗai ɗai. Suka ce sun amince._

Da farko sun fara aikinsu da zuciya ɗaya, kamar abin arziki. Kuma sai Allah ya tarfawa garinsu nono, balance ɗin da suke kaiwa har ya zarce adadin kuɗaɗen da aka yanka musu da farko. Komawarsu ruwa tsundum a ɓangaren zina ya biyo bayan wata Kilaki ce da suka ɗauka, tun daga kawo har zuwa maraban rido, da suka nemi ta basu kuɗinsu sai ta ce sai dai ta biya da albarkatun jikinta, idan kuma sun yafe to ba damuwa. Langes har ya kawar da kai shi kuwa Villah ya ce sai ya ɗana kuɗinsa.

Tun daga wannan rana kuma sai abun ya zame musu jiki, tun suna haka da ballagazun matan da suka amince har suka fara tsallakawa kan waɗanda basu ji ba basu gani ba, ana haka har wata rana Villah ya ratsa gonar yarinyar da ta zame masa alaƙaƙai kuma ƙarfen ƙafa, ganin irin abubuwan da suka faru tsakaninsu da wannan yarinya yasa Langes shan alwashin in Allah ya yarda bazai ƙara ba, yanzu haka ma dai shi aure yake nema.

Fareeda da suka ɗauketa a tudun wada basu ajiyeta ba sai da suka je can unguwar rimi, inda suke da ɗaki na musamman don gudanar da lamari irin wannan. Ɗakin ɗan ƙarami ne, kuma unguwar irin lungunnan ne da babu zirga-zirgan mutane sosai, ko napep ɗinsu daƙyar suke raɓata ta shige cikin lungun.

Fareeda bata buɗe idanunta ba sai da ta ji ana kici-kicin cire mata hijabi, kamar a mafarki haka take gani da jin komai. Ko da ta fahimci a ina take da kuma mummunan abinda yake shirin faruwa da ita a firgice ta make hannuwansa, idanu warawaje ta buɗe baki cikin ƙaraji tana faɗin

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Ɱalam me kake ƙoƙarin yi min? na shiga uku!! ina ne nan kuka kawo ni?"

A zabure tasa hannuwa biyu ta hankiɗa shi baya ya faɗi ƙasa daga kan ƴar yaloluwar katifar ita kuma ta miƙe tsaye da sauri.

Ba tare da damuwa da rashin hijabi a jikinta ba ta nufi ƙofa da gudu shi kuwa yasa mata ƙafa ya taɗiyeta, ta faɗi ƙasa yaraf, bakinta da goshinta suka daki dandaryar sumintin tsakar ɗakin. Ihu ta ƙwala saboda azabar zafin da ya ratsata har ƙwaƙwalwarta.

Kafin ta dawo hayyacinta ya ɗaga ƙasar katifan ya ɗauko wata sharɓeɓiyar wuƙa, sai ƙyalli take yi a cikin ɗan madaidaicin hasken ɗakin, saitin wuyanta ya nufo gadan-gadan da wuƙar idanunshi a zazzare ya ɗora yatsarsa manuniya kan laɓɓansa alamun tayi masa shiru ko ya yankata.

A tsorace cikin wani masifaffen tashin hankali da ya ƙara lulluɓeta ta ɗauke kukan da take yi ɗif, ta ɗora hannu biyu akai hankali tashe sai murgina kan gefe da gefe take yi tana wani irin nishi mai kama da gurnani, kamar mai naƙuda.

"Dan ubanki ni kika ture na faɗi ƙasa?"

Ya tambayeta da wata ƙatuwar murya mai bayyana ɓacin ran ture shi da tayi.

Da sauri ta girgiza kanta alamar a'a! ta haɗa hannuwanta biyu alamun bada haƙuri tana yi tana jan shesshekar kuka, hawaye wasu na korar wasu kamar an buɗe famfo.

Gefen katifar ya laluba ya zauna, har lokacin bai ɗauke tsinin wuƙar daga saitinta ba, kallonta yake yi yana mamakin farkawarta a daidai wannan lokacin. Maganin da suke amfani da shi wajen fesawa mata mai kama da turare yana da ƙarfin da har su kusan gama komai da yarinya ba ta iya farkawa, ko ta farka za ta buɗe idanu ne kawai, amma jikinta shakaf za ta ji shi babu ƙarfi ko na sisin kwabo, ko ɗan yatsa ba'a iya ɗagawa balle har yarinya tayi ƙoƙarin yi musu gardama ko tayi yunƙurin ƙwatar kanta. Ita kuwa wannan sai ga shi ta farka da ƙarfin jiki da na zuciya, wannan wace irin yarinya ce?

Sassauta ɓacin ransa yayi, ya ɗan rage ƙarfin muryarsa, ya kawar da wuƙar daga saitinta ya fara magana ba tare da fushi ko hargagi ba.

"Kin ga, ki kwantar da hankalinki. Wannan kukan da kike yi ba na son shi. Ban saba ina biyan buƙatata ana min kuka ba kamar mai aikata fyaɗe ba, ba na so. Kin gane?"

Da sauri ta dinga ɗaga kai alamar eh, ta ɗaga ya fi sau goma, saboda tsananin tashin hankali da ɗimuwa, kuma har lokacin hawayen basu daina tsere daga idanuwanta ba.

"Ki buɗe baki ki amsa min, ba na son maganar kurame..."

"Don Allah, don girman Allah, don darajar Fiyayayyen halitta SAW ka rufa min asiri ka ƙyale ni, ka barni in tafi ba tare da ka keta min rigar mutunci na ba... Wallahi tallahi ni matar aure ce..."

"Ni ma ai mijin aure ne."

Ya amsa kai tsaye, fuskarsa na nuna rashin damuwa da magiya da roƙonta.

"Na shiga uku..."

"Baki shiga ba tukun za dai ki shiga, don wallahi tallahi babu yadda za'ayi ki fice daga ɗakinnan ba tare da na kashe ƙishin ruwan da arba da tsayayyun ƙirjinki ya haddasa min ba. Matso nan in duba ma ko ciko kika yi, don matan yanzu bala'in yaudara gare ku, har mazaunai na acuci kuke sakawa, matso salin-alin in duba ta yadda za ki daɗi nima zanji, idan kuma ba haka ba ko da tsiya-tsiya sai na duba, sannan in damuƙa, in yamutsa, in tsotsa yadda nake so..."

Duk abinda yake faruwa a tsakaninsu Langes yana zaune ta waje a ƙofar ɗakin yana ji, hankalinsa a ɗugunzume, zuciyarsa cike da matsanancin tausayin wannan matashiya da ko sunanta basu sani ba. Basu taɓa ɗauko yarinyar da tun a karon farko ya ji zuciyarsa bai nutsu a ratsa gonar mutuncinta ba irin wannan. Waya ce riƙe a hannunsa yana ta dokawa wata lamba kira, tun ɗazu an ɗaga ta kuma ba shi tabbacin ga ta nan zuwa da gaugawa amma har yanzu bata iso ba.

Yana wannan zaman ya ji bala'yʏayʏyʏen dambe da buge-buge ya kaure a cikin ɗakin, sai kuma ya fara jin ƙarar saukar mari tas tas ba ƙaƙƙautawa, muryar Villah na tashi cikin hargagi yana zagin Fareeda ta uwa ta uba yana faɗin shi za ta ciza har ta zubar mishi da jini?

"To sai na yi yaga-yaga da mutuncin naki sannan in kashe ki inga uban da ya tsaya miki a garinnnan."

Hankalinsa ne ya ƙara mugun ɗugunzuma, duk iskancin da suke aikatawa a baya basu taɓa kashe rai har lahira ba. Idan Villah ya kashe wannan yarinya da basu san ko wacece ba ina za su kai hakkin rai? A zabure ya miƙe tsaye da niyyar buɗe ɗakin don ya shiga ya dakatar da Villah kawai sai yayi ido biyu da ita, saboda tashin hankalin da yake ciki ko tsayuwar ɗan mashin ɗin da ya kawota bai ji ba.

Riga da wando matsattsu ne a jikinta, sun matseta tamau, sun fitar da duk wasu siffa na shape ɗin jikinta. Kimono mai shara-shara ta ɗora akan kayan, duk da haka bai ɓoye girman tuma-tuman mazaunanta ba sadda ta juya baya da nufin magana da mai mashin ɗin da ya kawota.

Mardiyya wacce gayu yasa ta yanke sunan zuwa Baby Mardy irin ɗima-ɗiman matannan ne, ga tsawo ga ƙiba. Ita ce alaƙaƙan da Villah ya haɗu da ita, duk da kasancewarta ta daɗe da rabar ma gayu mutuncinta kan titi shiga gonarta da Villah yayi abu ne da bai faru bisa amincewarta ba, ta kira abinda yayi mata mummunan fyaɗe na cin zatafi, ko da ta dawo hayyacinta shaƙeshi tayi sai da ƙyar ta sake shi bayan Langes ya zube mata duk kuɗaɗen da ke jikinsu. Kafin tafiyarta ta sha musu alwashin daga kanta Villah ya gama ratsa gonar da ba tasa ba, kamar motar kwana-kwana haka take musu dirar mikiya ta kashe wutar zinar da suke niyyar aikatawa ba zato ba tsammani, duk sadda ta bushi iska zuwa take ta karɓe kuɗaɗen da ke hannunsu. A bayan idanun Villah ta ritsa Langes da bindiga ta rantse da girman Allah duk sadda suka ɗauko wata mace idan bai kirata ba sai ta kashe shi har lahira. Wannan ne abinda ya tsorata Langes, ya daina biye ma Villah, yayi ma kanshi karatun ta nutsu ya fara neman aure.

Wani uban ihu da Fareeda ta ƙwallara lokacin da Villah ya riƙe gashin kanta ya buga fuskarta da bango shi ne abinda ya ɗaga ma Langes da Baby Mardy hankali suka buga ƙofar da ƙarfi tare da afkawa cikin ɗakin a guje.

Fareeda ce yashe a ƙasa a sume cikin jini, shi kuma Villah yana tsaye a kanta yana huci, lokaci guda kuma yana cire Belt ɗin wandonsa.

Kimonon jikinta ta cire tayi hurgi da shi, ko kafin ya gama kallonsu fuskarsa na bayyana mamakin shigowarsu a daidai lokacin da yake gaf da cimma mummunar buƙatarsa ta kaima mararsa wani irin naushin da yasa shi ƙwallah ihu ya durƙushe a ƙasa, hannuwansa biyu dafe da inda ta nausa yana runtse idanu haɗe da cije baki.

"Da na faɗa maka tun da ka zura gugarka a cikin rijiyata ka yi ƙarya ka sake yin ninƙayi a cikin wata rijiya balle har ka ɗebi ruwa ka zaci wasa nake ko? To ka jira ni zuwa anjima, duk inda ka shige zan lalubo ka. Zan lalata gugar taka ta yadda ko kyauta aka umarci ka shige cikin wata rijiya sai dai ka kawar da kai."

Gurin Fareeda ta nufa da sauri hankalinta a tashe, ganin yadda ya fara samun nasarar yaga wani sashe na gaban rigar Fareeda har wani ɓangare na ƙirjinta ya baiyana a fili yasa ta jan tsaki, siririn gyalen da ta yafo a kanta ta cire. Da sauri ta ɗanyi dabara ta rufe gurin, har za ta ɗauke ta a haka sai ta hangi hijabin Fareeda da jakarta yashe can gefe ɗaya.

Langes ne ya kamata suka mayar mata da hijabin, ta maƙala jakarta a kafaɗa suka fice da ita hankalinsu tashe, tunaninsu da addu'arsu ɗaya ne.

'Allah yasa bata mutu ba.'

******

Ko da suka isa asibiti sai da ƙyar likitoci suka karɓeta saboda yanayin jikinta. Sun dage sai an sako yan sanda cikin case ɗin, tunda sunyi ƙaryar hatsari tayi. Sun karɓe ta ne bayan Mardy ta kira wani saurayinta ƙusa a jiharnan, shi yayi magana da likitan, ya ɗura masa wasu yan kuɗaɗe sannan aka karɓeta da gaugawa.

Cikin ƙanƙanin lokaci likitoci suka rufu akan Fareeda, aka yi mata duk wani abu da ya kamata, ta cigaba da barci da taimakon alluran da aka ɗura mata a cikin ruwa.

Idan ka kalli Fareeda sai ta bala'in baka tausayi, saboda yadda siffar jiki musanman na fuskarta ya canza gaba ɗaya, goshi da bakinta sun kumbura suntum, idanunta duk da a rufe suke sun tasa luhu-luhu. Shatin yatsu kwance ɓaro-ɓaro a kuncinta hagu da dama.

Daga bayanan da Langes yayi wa Mardy sam bata ji makaman da za su riƙa don gano ahalin Fareeda ba. Lokaci na farko da zuciyarta ya kitsa mata duba cikin jakarta, ko za su samu wani abu da zai sauƙaƙa musu gano inda ahalinta suke kafin ta farka.

Wayar da ta fara cin karo da ita yasa ta sauke ajiyar zuciya, kunna wayar tayi, ntwk na hawa wayar kiran Mukhtar na shigowa.

"Alloooo..."

Mardy ta faɗa da wani irin murya da yasa Mukhtar cire wayar daga kunnensa a can ɓangaren, ya duba lambar ya tabbatar dai tabbas Matarsa Fareeda ya kira ya ji wata baƙuwar murya, kamar ya katse kiran, amma sai ya sake mayar da wayar kunnensa yana tambayar ina mai wayar?

Gyatsine baki tayi, da jin muryar gayen a wani cuccushe zaiyi jin kai da ɗagawa, bai burgeta ba sam, amma sunan Habeebe Da'iman da ta ga anyi saving ɗin lambar ya tabbatar mata yana da muhimmanci a gurin mare lafiyar nan.

"Ita asalin mamallakiyar wannan wayar da ka kira, ga ta nan kwance a asibitin Barau Dikko, ta samu hatsari ne a cikin kekenapep. Mai napep ɗin ya gudu bayan yayi mata kwatsa-kwatsa da fuska, ni kawai taimaka mata nayi..."

Kʼit kiran ya katse daga can ɓangaren Mukhtar

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*7*_

Ƙaƙƙarfan tsaki ta ja, ta gallawa wayar harara kamar shi ne Habeebi da'iman ɗin da ya katse wayar ba tare da ya ƙarasa jin bayanin halin da budurwarsa take ciki ba. Don ita duk a tsammaninta Fareeda budurwa ce.

Tana niyyar mayar da wayar cikin jaka wani kiran ya sake shigowa, ta zaci na farko ne ya sake kira, sai taga saɓanin wancan sunan, wannan an rubuta 'Luvly Bro' ne da manyan baƙaƙe.

Ko da ta ɗauki wayar bata tsaya sauraren wani rainin hankali irinna wancan ba, bayan hello kai tsaye ta cigaba da cewa

"Mai wannan wayar fa ga ta nan kwance a gadon asibiti ta samu hatsari..."

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un"

Ya Mustapha ya katseta cikin tashin hankali.

"Ɗan'uwa lafiya? ina Fareedar?"

Aunty Murja da Masrura suka haɗa baki gurin tambayarsa, a hankali yanayin farin cikin haihuwar ɗa namiji da Aunty Binto tayi ba tare da an tsaga ta ba ya ɓace daga fuskokinsu.

Tsuru suka yi suna sauraren Mustapha da yake ɗan safa da marwa hankali tashe da waya a kunnensa, yana sauraren Baby Mardy da take mishi kwatancen ɗakin da aka kwantar da su a asibitin Barau dikko.

"Ok! Na gane, ganinan zuwa yanzu."

Maganar da yayi na ƙarshe kenan tare da katse wayar. Shaf ya ma manta tsaye suke da yɗan'uwansa saboda tashin hankali, har ya kama hanyar wucewa daga gurin da sauri Murjanatu ta riƙo hannunsa na dama, sai a lokacin ya tuna tare da su yake tsaye.

Duk da kasancewarta mai ƙwarin zuciya har idanunta sun canza kala, ƙwalla ya cicciko daga cikinsu. Daga yadda ya amsa wayar duk sun fahimci wani mummunan abu ne yake faruwa da Fareeda, ƙanwarsu abar son zuciyarsu, yarinya mai bala'in faram-faram da gudun ɓacin ran kowa a cikinsu. Ita kuwa Masrura kasancewarta ƙarama kuma mai rauni har ta fara hawaye.

"Ɗan'uwa ina kake shirin zuwa? Me ya samu Fareeda?"

Ta tambayeshi da sanyin murya, idanunta ciccike da hawaye.

Hannunsa na hagu ya ɗaga ya ɗan bugi goshinsa, ya ɗan tattare naman goshin ya huro wani zazzafan iska daga bakinsa. Murmushin yaƙe yayi, don ya ƙarfafa musu gwuiwa.

"Fareeda ta ɗan samu hatsari ne a napep a hanyarta zuwa nan, mai keken ya gudu, wata baiwar Allah ce ta taimaka mata. Amma dai ta tabbatar min da sauƙi sosai, shi ne zanje in ga halin da take ciki..."

"Ka je ko mu je? Ai sai mu tafi gaba ɗaya kawai."

Murjanatu ta katse shi da faɗin haka tana gyara zaman mayafinta.

"Idan muka tafi can gaba ɗaya ita kuma Aunty a barta da wa? Ke kiyi haƙuri ki zauna, ni bari inje da Masrura mu duba halin da take ciki. Tunda Alhaji Baba ya je

tahowa da Hajiya da su Aunty Balaraba idan sun ƙaraso sai ke ma kije ki gano halin da take ciki."

"To shi kenan. Don Allah duk yadda kuka tarar da ita mu dinga waya, duk da mun fita daga fargabar Aunty Binto hankalina bazai kwanta ba idan ban san halin da yar ƙanwata take ciki ba."

Ta ƙarasa maganar fuskarta a dame.

******

Yadda suka tarar da fuskarta a suntume kamar mai keken ta kai ya dinga sukuwa da tayoyinsa ba ƙaramin ɗaga musu hankali yayi ba. Jiki a sanyaye suka zauna kan kujerun da Mardy ta miƙa musu.

Masrura kam rufe fuska da hijabi tayi tana jan shesshekar kuka, yau dai kam sun gode Allah. Tashin hankali daga wannan sai wannan, sun samu fita daga fargaba da ƙila wa ƙala kan Auntynsu yanzu ga kuma abinda ya samu Fareeda.

Da wanne za su ji?

Mustapha ma duk da yake namiji duƙar da kanshi ƙasa yayi, wani dunƙulallen abu ya tsaya mishi a maƙoshi, shi bai sauka ciki ba shi bai fito waje ba. Ina ma shi ne yake kuka kamar ƙanwarsa ko zai samu sauƙin zafi da raɗaɗin zuciyarsa?

Sau takwas yana ɗaga idanu ya kalli Mardy, ya kasa buɗe baki yayi mata godiyar irin taimakon da tayi ma gudan jininsu saboda tsananin damuwa da tashin hankali.

Sai ita Mardiyyar ce ta karya shirun da cewa

"To tunda Allah ya kawo ku yan'uwanta ni kam na yi abinda zan iya, tafiya zanyi. Sai ku ɗora daga inda na tsaya, duk wani abu da baku gane ba idan likita ya shigo

zaiyi muku ƙarin bayani. Allah ya kyauta gaba, ga jakarta da wayarta nan. Idan na samu sarari ko zuwa jibi zan zagayo in duba jikinta."

"Mun gode, Allah ya saka da alkhairi."

Masrura ta faɗi haka da ƙyar, tana jan shessheƙa.

A gefen gadon da Fareeda take kwance ta ajiye jakar da wayar, ta nufi hanyar fita daga ɗakin hannunta riƙe da wayarta tana kiran Langes, amma yana ta ringing bai ɗauka ba. Bata san Mustapha yana biye da ita a baya ba sai da ta kusan fita daga asibitin, kamar daga sama ta ji muryarsa a tausashe yana cewa

"Muna godiya ƙwarai da taimakon yɗar'uwarmu da kika yi, ina roƙon Allah ya saka miki da mafificin alkhairi."

"Ah ba komai Luvly Bro"

Ta ƙarasa kiranshi da sunan da Fareeda tayi saving tana wani dariya irinna gogaggun yɗan duniya.

Ba a wannan layin yake ba, kuma don taimakon da tayi ma ƙanwarsa bai isa ya sa shi sakar mata fuska ba, ba ma shi a cikin yanayin fara'a da sauƙin zuciya. Fuskarnan a ɗinke ya zura hannunsa a aljihu ya zaro dubu biyar ya miƙa mata da cewar ta hau keke. Ya ƙara yi mata godiya.

Ganin ba fuskar latsawa a dole ta kama kanta, ta kalli kuɗin ta kalle shi, wani irin kwarjini yayi mata sosai har ta ji baza ta iya mayar da hannun kyautarsa baya ba. Amma in banda haka mecece dubu biyar a gurinta?

Kawar da kanta tayi tana ɗan taɓe baki, sai ta karɓi kuɗin tayi mishi godiya a taƙaice da harshen nasara.

"Thanks"

Bai jira ko za ta ƙara cewa wani abu ba ya juya cikin asibitin da sassarfa. Ita kuwa ba ta da zaɓin da ya wuce bin bayansa da kallo har ya ɓace ma ganinta, ta ja tsaki ƙasa ƙasa ta cigaba da tafiya.

Ko da ya koma ɗakin ya tarar Fareeda ta farka, Masrura ta kira likitan da yake aiki a wannan lokacin yana ƙara duba jikinta.

Wani abin da ya ɗaure musu kai kuma ya ƙara ɗaga musu hankali shi ne, ganin yadda wasu siraran hawaye ke fita daga kwarmin idanunta yana gangarawa cikin kunnuwanta.

Likitan na fita da sauri suka rufu a kanta, cikin kulawa da ƙauna suka rirriƙe hannayenta ɗai ɗai a cikin nasu suna tambayarta me ke mata ciwo? kukan me take yi? ko akwai inda ta bugu a cikin jikinta ne ba'a sani ba. Kamar suna yi da kurma ko dutse, uffan bata ce musu ba, bata kuma buɗe idanu ta kalle su ba. Wani irin zafi da raɗaɗi ne zuciyarta ke yi, idan ta buɗe kumburarren bakinta da nufin yin magana babu ko shakka ƙaƙƙarfan kuka ne zai ƙwace mata, sai kawai ta cigaba da sharɓen hawaye.

Waigawa hagu da dama Mustapha yayi ko zai ga tissue yayi amfani da shi gurin share mata hawaye, da bai samu ba sai kawai ya tattare ƙasan rigar shaddar jikinsa ya cukwuikwuiye ya nufi idanunta da niyyar goge hawayen da har lokacin basu daina fita ba. Lura da abinda yake shirin yi ga shaddar tasa mai ruwan madara da sauri Masrura ta dakatar da shi.

Ɗankwalin kanta ta ciro ta miƙa mishi, a hankali da fuska mai cike da tausayi yake ƙare mata kallo yana goge hawayen da har ɗan taruwa suka yi ta cikin kunnenta. zuciyarsa cike da mamakin shatin yatsun da yake gani ɓaro-ɓaro kwance a kumatukanta.

'To ko dai bayan hatsarin mai keken ya mammareta ne?'

Ya tambayi zuciyarsa.

'Ko shakka babu waɗannan shatin yatsun na mari ne.'

Ya buɗe baki zaiyi magana sai ya ji Masrura tana cewa.

"Aunty Faree, wai kukan na menene haka don Allah? na zaci murna da godiya ga Allah ya kamata kiyi tunda kin farfaɗo cikin hankalinki? Don Allah kiyi shiru, ki daina kuka, kin san kuwa Aunty Binto ta haifo baby boy ƙato ba tare da anyi mata aiki ba...?"

Da farko damƙe hannayensu biyun tayi da ƙarfi jin maganganun Masrura da yake sauka a nutse cikin kunnuwanta. Amma da ta ji kalmar ƙarshe ai bata san lokacin da ta buɗe jajayen idanunta ta zuba akan su biyun ba.

Da ƙyar ta iya buɗe kumburarren bakinta da yayi mata wani irin nauyi kaman an ɗora mata dutse ta ce

"Da gaske? ta haihu?"

"Wallahi da gaske"

Mustapha ya amsa fuskarsa cike fal da murmushi.

"Kuma ita da jaririnta duk suna cikin ƙoshin lafiya."

Masrura ta ƙara da faɗin haka itama fuskarta taf da murmushi.

"Alhamdulillah"

Ta faɗa a hankali, ƙoƙarin yin murmushi take yi amma ta kasa, a maimakon murmushin ya fito sai ta wani irin yanƙwane fuska kamar ƙonanniya, ta ko ina fuskarta zafi yake yi kamar an bubbuga mata duwatsu, a dole ta haƙura da murmushin, tayi shiru tana sauraren yadda yɑn'uwan suke ta bata labarai na farin ciki da ban dariya don dai su ƙara kwantar mata da hankali.

Amma a zahirin gaskiya ƙarfin hali kawai suke yi, zukatansu cike yake taf da bala'in tausayinta. Gaba ɗaya halittar fuskarta ya sauya, wanda ya ganta ɗazu sadda ta fito daga gida idan ba farin sani yayi mata ba zai iya rantsewa da girman Allah ba ita ce Fareedar nan yɑr ƙwalisa ba.

A ƙoƙarin saka ta farin ciki har Vidio call ta whatsapp suka yi da Aunty Murja da Aunty Binto, tana kallon yadda suke kawar da kai gefe suna share hawaye, amma ita farin cikin ganin ƙatoton jariri kuma fari sol kamar ɗan larabawa da Auntyn ta haifa musu ya kore mata kaso sittin cikin ɗari na damuwa da ƙuncin da zuciyarta ke ciki.

Kaso arba'in na damuwarta Mukhtar ne. Duk hirar da take yi da yan'uwanta tunaninsa da tunanin girman laifin da ta aikata yana kwance malala can ƙarƙashin zuciyarta.

'Me za ta ce masa idan ya dawo ranar juma'a ya tarar da ita cikin wannan halin? wani ƙarya za tayi masa ya gamsu ba da gangar ta fita ba? Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un! ita kam satar fita bai ƙare ta da komai ba sai bala'i da masifa. Me ya kaita? me yasa bata yi haƙuri ta zauna a gida kamar yadda ya umarce ta ba? Dubi fa yanzu harkar zumunci za ta sadar, bata taɓa tsammanin wani mummunan abu makamancin wannan zai faru da ita ba, sai ga shi in banda tsarewa da taimakon Ubangiji lokacin da bawa bai taɓa tsammani ba da yanzu wani zancen ake ba wannan ba...'

"Fareeda, tunanin me kike yi haka? Me yake damunki? Kinga, tun bayan farfaɗowarki na san akwai abinda yake damunki amma kina ƙoƙarin dannewa. Menene shi? Daman akwai yar ɓoye-ɓoye ne a tsakaninmu?"

Mustapha ya tambayeta da kulawa a murya da fuskarsa. Tun bayan farkowarta daga irin kukan da take yi yasan akwai abinda yake damunta, akwai abinda ke cin zuciyarta amma tana ƙoƙarin ɓoyewa. Ita saƙonsa ce, akwai shaƙuwa na musamman a tsakaninsa da ita, tana da fahimta sosai, duk wasu matsaloli nasa da zai rakito kafin ya tunkari sauran yan'uwansa da maganar ita yake fara tunkara, ta bashi mafita, da kuma sassauƙar hanyar da zai bi wajen bayyana maganar ga yayyensu.

"Ya Mustapha, ina da damuwa. Kuyi min addu'a don Allah. Amma ina roƙon alfarma, a halin da nake ciki yanzu ba lokacin yin maganar bane, zan faɗa maka idan Allah yasa na ƙara samun sauƙi."

Tana gama faɗin haka ta lumshe idanunta, ta cigaba da sauke numfashi a hankali.

Duk su biyun idanunsu a kanta yake, kowa da irin saƙar da zuciyarsa take masa, amma dai sun share komai kamar yadda ta buƙata, tabbas! babu adalci su tilasta mata faɗin damuwarta a irin wannan halin da take ciki.

****

Ya ɗauki tsawon wasu daƙiƙu yana jan fasali bayan ya amsa gaisuwar da ta gama yi masa cikin karaɗi da rangwaɗa. Kamar zai katse wayarsa, amma sai zuciyarsa ta cigaba da azalzalarsa tana tabbatar masa da cewar shawarar da ya yanke fa shi ne daidai, mafitarsa kenan. Ƙwaƙƙwaran hanya ce mai ɓullewa ya samar ga matsalolin da suka daɗe suna addabar duniyarsa.

"Za ki aure ni?"

Ya tambayeta kai tsaye, tambaya daga can ƙarƙashin zuciyarsa.

Tsananin ruɗani da firgicin da ta shiga sau uku tana marin kunnenta, da tunanin ko ita ce bata ji daidai ba.

"Me ka ce Aban Twince?"

Wani sabon suna da ta raɗa mishi yanzu-yanzu saboda zakwaɗi, zuciyarta cike da fatan tabbatuwar abinda ta ji kamar ya ce da farko.

"Cewa nayi, za ki aure ni?"

"Eh! Eh!! Ehh!!!"

Ta amsa bakinta na mazari. Wayyo Allah daɗi, tsananin farin ciki da murna ta ma rasa inda za ta tsoma ranta, ta miƙe, ta zauna, ta sake miƙewa, ta zauna, daga bisani sai ta miƙe zumbur ta fara zagaye ɗakin da sassarfa. Bakinnan kamar zai yage saboda dariya, lallai yau larabar tata ce. Da alamun juma'arta za tayi kyau tun daga yau laraba ta zo da haske.

"Idan na aure ki, wani irin tanadi kika yi min?"

Ya tambayeta da murya ƙasa-ƙasa, kamar ba Mukhtar ɗinnan da idan tana gaida shi yake amsawa a ciccije ba.

"Zan baka farin ciki, zan tsunduma ka a kogin farin ciki, zan shayar da kai wata zallar ɗanyar tatacciyar madarar soyayya mare algus. Za ka samu har fiye da abinda kake burin samu a gurin matar aurenka..."

Lumshe idanu yayi yana saurarenta, zuciyarsa cike da gamsuwa, yana ji ko a iya waɗannan alƙawuran da tayi mishi ya samu za su gamsar da shi. Zai ƙyale Fareeda, taje can da yawarta.

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*8*_

Saɓanin yadda ya saba dawowa daga gurin aikinsa duk ranar juma'a, a wannan karon sai da ya shafe sati biyu cif bai waiwayi iyalinsa ba.

Kuma ko a waya ba ya nemanta, sai ita ce ma take kiransa amma sam ba ya ɗagawa. Kwanaki biyu da fara samun sauƙinta ta fara jera mishi kira akai-akai. Duk a tunaninta bai san abinda yake faruwa da ita ba, amma da taga ta kira sau ba adadi bai ɗauka ba sai ta haƙura, abu ɗaya da bata daina ba shi ne tura mishi saƙo mai ɗauke da kalaman soyayya, fatan alkhairi da neman yafiyar laifin da bata fito fili ta bayyana ba.

Kwanakinta huɗu a gadon asibiti aka sallameta, duk iya waɗannan kwanakin Masrura ce take jinyarta, yan'uwanta kuma suke shafe ko wace yini wajen zuwa gurinta da dafo mata abinci mai rai da lafiya. Ko kafin a sallameta jikin yayi sauki sosai da sosai, sai yan abubuwan da baza'a rasa ba.

Rashin ganin Mukhtar ko wani nasa wajen duba Fareeda shi ya dasa Yaya Mustapha ayar tambaya, ba tare da sanin Fareeda ba ya kira Mukhtar a waya, amma abin mamaki da ɗaure kai don hakan bai taɓa faruwa a tsakaninsu ba shi ne kiran Mukhtar sau bakwai bai ɗaga waya ba. Ya katse kiran da tunanin zai biyo bayan kiranshi daga baya amma har aka shafe kwanaki biyu bai kira shi ba.

Ranar da aka sallami Fareeda shi ya kwashe su a motarsa zuwa gidan Fareeda, Aunty Murja, Masrura, Fareeda, sai shi, Aunty Binto ce kawai ba ta saboda ɗanyen jegon da take fama da shi.

Daman wannan lokacin yake jira na sallamarta daga asibiti, titsiyeta yayi nan cikin falonta ya tambayeta abinda yake faruwa tsakaninta da mijinta. Duk yan'uwan sun san irin soyayya da shaƙuwar da yake tsakaninsu, in dai halin lafiya suke da mijinta ba'a shafe yini guda cur ba tare da ya kira ta a waya ko kuma ita ta kira shi ba. Sai ga shi wannan karon duk yan'uwan sun fahimci mijin ba ya kiranta a kwanakin da ta kwanta asibiti, mahaifiyarsa bata je duba ta ba, cikin yan'uwansa ma babu wanda ya je duba ta duk da kyakkyawar dangantakar da ke a tsakaninta da dangin mijinta.

"Me yake faruwa tsakaninki da mijinki?"

Yayi mata tambayar idanunsa na kanta.

Waɗannan maganganun na Yayanta kamar fami ne a inda yake mata ƙaiƙayi. Nan take idanunta ya cicciko da hawaye, ta sunkuyar da kanta ƙasa, cikin damuwa da tashin hankali ta kora musu gaskiyar bayanin duk abinda ya faru da ita.

Nan take Ya Mustapha ya rufe idanu ya fara zazzaga mata bala'i ta inda yake shiga ba ta nan yake fita ba. Ɗari bisa ɗari na laifin ya ɗora shi a kanta ne, ya kuma rantse da girman Allah ko shi ne zai ɗauki matakin share ta fiye ma da yadda shi Mukhtar ɗin yayi. Kamar zai tsinke ta da Mari saboda masifa, bata taɓa ɓata mishi rai irin na wannan lokacin ba.

Ita dai kanta na duƙe a ƙasa, sai kuka take yi gwanin ban tausayi. Damuwar da ke zuciyarta ya ƙara ninkuwa.

A ƙarshe Ya Mustapha ficewa yayi daga cikin falon ba tare da ya ƙara saurarenta ba. Allah sarki yɗan'uwa mata rabin jiki, Murja da Masrura kam sun fahimceta, rungumeta sukai suna rarrashinta da faɗa mata tausasan kalamai har sai da ta samu nutsuwa, ta daina kuka, sai sauke ajiyar zuciya akai-akai. Duk yadda Mustapha yake ta danna musu horn su fito ya sauke su gidan Aunty Binto ƙin fita suka yi, sai da suka tabbatar ta samu nutsuwa sannan suka tafi.

Ko da suka fice a gidan ta daɗe zaune inda suka barta, tunani take yi.

'Tun da take satar fita ba tare da izinin mijinta ba me ta taɓa tsinta na alkhairi? Babu! idan ba ta manta ba sau uku ne kawai ta taɓa satar fita taci lafiya ba tare da asirinta ya tonu ba. Me yasa baza ta yiwa kanta faɗa ta zauna a cikakkiyar matar gida kamar yadda mijinta yake buƙata ba? Da farko dai da take amarya ba kasafai kullen ya cika damunta ba. Amma tunda Allah yasa mijin Fatima ya rasu, ta samu yɗancin zuwa duk inda take so kai tsaye, to wani sha'anin ita take faɗa mata, kuma ta biyo mata su tafi, ko ta faɗa mata mijinta bai bata izini ba haka za tai ta tunzurata tana kwaɗaita mata ababen burgewar da ke cikin inda take so su je.

Fatima, sai yanzu da ta nutsu ta gane tabbas Fatima tana ɗaya daga cikin wacce take taka muhimmiyar rawa gurin ƙara tunzura taurin kanta wajen bijire ma umarnin mijinta.

Ita daman Fatima tun tale-tale haka take, ba dai ki je gurinta da neman shawara kan daidai ko rashin daidai ta ba ki shawarar bin daidai ba, da farko kwance-kwance za tayi ta fahimci ina ne ra'ayinki ya fi karkata? in dai ta ga hankalinki ya fi son bin rashin dai dai ɗinnan to tabbas nan za ta ƙarfafeki da bi, a gurin Fatima babu wani babban laifi da istigfari ba ya kore shi, tana fa sane kuskure za a aikata, amma za ta zuga ki ki aikata sai ta ƙara miki da cewa bayan kinyi kiyi Istigfari. Allah mai gafara ne mai jin ƙai.

Duk cikin ƙawayensu su takwas da suka yi ƴanmatanci a lokaci ɗaya Fatima ta dame su ta shanye a wayau, saboda ta fi su shekaru nesa ba kusa ba. Amma da yake ita irin mai ƙaramin jikinnan ne sai suka taso kamar sa'anni. A cikinsu ma da yawansu sun fita girman jiki, ko ita ta fi Fatima tsawo da murjewa a jiki.

Da yake a ƙawance shekaru lamba ne kawai haka suke ta cakuɗeɗeniya tare da ita a matsayin ƙawa ta ƙud da ƙud, sadda suke tashen ƴanmatanci kasancewarsu ƴan unguwa ɗaya duk inda za suje tare suke zuwa, har wani kirari ake musu su biyun, idan aka ga Wata to tabbas Zara na tafe. Mutum mai nisan hankali da wayau ne kawai zai kalli su biyun kai tsaye a ce Fatima ta girme mata nesa ba kusa ba.'

Nannauyar ajiyar zuciya ta ja ta sauke, agogo ta kallah, ƙarfe biyar da rabi na yamma.

'Yau asabar, tun jiya ya kamata Mukhtar ya dawo bai dawo ba, hmmm! Ya Allah ka kawo min komai da sauƙi don girman zatinka.'

Ta ƙarasa tunanin da addu'a, lumshe manyan idanunta tayi tai shiru, babu abinda take hasasowa sai irin bala'in da zai sauke mata idan ya dawo gidan, to ko zai dawo a wannan satin?

"Allah masani."

Ta faɗa a fili.

Wayarta da yake ajiye a gefe ta ɗauka, lambar Fatima ta lalubo ta danna mata kira, lallai ya zama wajib ta bata labarin duk iftila'in da ya afka mata a dalilin fitar da ta tunzurata tayi ba tare da izinin mijinta ba. Sannan za tayi mata gargadi daga yau ko da wani abu ya faru a cikin ƙawayensu ko abokan arzukinsu kar ta kuskura ta sake faɗa mata, ita yanzu ta shiryu, ta tsallake manyan masifu biyu da ƙyar, baza ta afka cikin na uku tana ji tana gani ba.

Wayar tana fara ringing sai aka katse daga can ɓangaren, ita kuma aka rubuta mata User busy. Da sauri ta sake danna ma lambar kira ba tare da tunanin komai ba, a wannan karon sai ta ji Fatima tana waya daga can ɓangaren, jin haka sai ta katse kiran, ta san duk halin da ake ciki Fatima za ta biyo bayan kiranta idan ta gama wayar, yau kwanaki huɗu kenan cif basuyi waya ba.

Da yake ta yi sallar la'asar, sai kawai ta miƙe ta shige cikin ɗaki, kayan jikinta ta canza zuwa na zaman gida ta fara ƙalƙale gidan da ya ɗanyi ƙura a wasu guraren saboda rashinta a gidan.

Duk a ƙoƙarinta na son zama kamar yadda mijinta yake so har ranar sunan babyn da Auntynsu ta haifa ya zagayo bata leƙa ko ƙofar gida ba. Amma fa tsakani da Allah daurewa kawai tayi, ƙafafunta har wani ƙaiƙayi suka dinga yi mata. Wannan sunan sun ci mishi buri ita da yan'uwanta ba tun yanzu ba. Yanzu shi kenan duk yan'uwanta suna can suna shiga da fita a cikin ankon da ita da hannunta ta zaɓa a kasuwa ita tana nan gida? saboda zafin da zuciyarta tai tayi da yadda shaiɗan yake ta zuga ta ta fice, ta fita babu abinda zai faru, kawai sai ta shige ɗaki ta zauna a gefen gado ta fashe da kuka.

Tana wannan kukan Ya Mustapha ya kirata ga shi a ƙofar gida, cikin sauri ta share hawayenta ta wanke fuskarta, har kwalli ta zizara a idanunta don kawai kar ya gane tayi kuka.

Babban hijabinta na sallah ta zumbula da sauri ta fita tsakar gida ta buɗe mishi ƙofa ya shigo, ko da ta nemi ya shigo da motarsa ce mata yayi ba zama ya zo yi ba, ta ce ya shiga falonta ya ce nan tsakar gida ya isa.

Kanta ta saukar ƙasa, lokaci ɗaya wasu sabbin hawaye suka sake cicciko idanun amma sai tayi ƙoƙarin haɗiyesu, bata bari sun zubo ba, Har lokacin fushi yake da ita, ko da tai ta kiranshi don ta bashi haƙuri da alƙawarin baza ta sake ba ƙin ɗaga wayarta yayi.

"Kuka kike yi?"

Ya tambaye ta.

"A'a!"

Ta amsa da rawar murya.

Taɓe baki yayi ya koma gurin motarsa ya fito da wasu manyan ledoji biyu farare, shaƙe da kayayyaki a ciki. Yana shigowa kai tsaye ya miƙa mata, da cusasshiyar murya mare walwala ya ce

"Ga shi, Aunty Murja ta tilastani wai dole sai na kawo miki, girke-girke da soye-soyen da suka yi a gidan suna ne. Wai har naman ƙauri da aka rarraba kwanaki uku baya naki yana ciki."

"Tam! Na gode. Allah ya raya mana Abdurrahman"

Tayi maganar a sanyaye.

Har ya kusa fita daga gidan sai ya juya da sauri, hannunta ɗaya ya kamo ya riƙe a cikin nashi. Da wani irin kasalar jiki ta ɗaga idanunta ta kalleshi, lokacin hawayen idanunta gaf suke da zubowa.

"Kiyi haƙuri ƙanwata."

Ya faɗa a tausashe, sai ya cigaba da yi mata nasiha da salama a muryarsa.

"Ki kiyaye abinda mijinki ba ya so, sai Ubangiji ya zame miki ja gaba a cikin lamuranki. Kin manta fiyayyen Halitta SAW ya ce da ace za'a umarci ayiwa wani abin halitta sujada tabbas mace ce za'a umarta tayi ma mijinta? Ko kin manta kissar matar nan da aka aike mata mahaifinta ba shi da lafiya, saboda mijinta ba ya nan ta aika neman izini a gurin Manzon Allah SAW ya ce ta zauna tabi umarnin mijinta, bata je ba har uban ya mutu, a sanadiyyar haka ita da mahaifin suka samu aljannah. Kin manta?"

Da sauri ta girgiza kai tana matsan ƙwallah.

"To idan baki manta duk waɗannan da hadithan da suka kawo bayani kan girman miji ba me zai sa kiyi ta biye ma son zuciyarki kina saɓa ma umarnin mijinki? Duk jikanmu yɗan'uwanki mijinki ya fi girman haƙƙi a kanki fiye da mu, ke yau ko da iyayenmu na raye mijinki ya fi su girman haƙƙi a kanki. Don Allah Fareeda, don Annabi, daga wannan matsalar da kika samu a dalilin satar fita kar in ƙara ji, don Allah kar ki kuskura ki sake maimaita irin wannan kuskuren. Idan fita ya kama dole kuma ya hana ki, ban ɗaukewa kowa riga ba a cikin family, ko sha'anin waye ki kira ki bada uzurin baza ki sami zuwa ba. Kin gane?"

"Eh! Kayi hakuri. Bazan sake ba in Allah ya yarda. Don Allah kayi haƙuri Yayana"

Cikin ƙanƙanin lokaci suka shirya da ɗan'uwanta, sai ga su suna ƙyalƙyala dariya. Shi da ya ce bazai shiga ba ya daɗe a cikin falonta suna hira da dariya, cikin hikima irin tasu na maza yake ƙara nunar da ita hanyoyin da za ta bi su daidaita da mijinta. Ya faɗa mata kalaman kwantar da hankali masu yawa. Ta ji daɗin zuwansa ba kaɗan ba, sun rabu cikin farin ciki da ƙaunar juna. Sakayau take jin zuciyarta, duk wani damuwarta ta aje shi gefe ɗaya, ta fuskanci al'amuran rayuwarta, har a sallah take addu'ar Allah ya bata ikon daina abinda mijinta ba ya so, shaiɗanin da ke shiga cikin zuciyarta ya dinga uzzurata da son zuwa sha'ani Allah ya kawar mata da shi.

***

Sati biyun da Mukhtar ya shafe cif bai dawo ba ta wani fannin bai dameta ba, ciwukan jikinta sun warke sumul, kamar ma bata ji ba, kyakkyawan halittarta ya dawo tsaf, duk wannan kumburin baki, goshi, da shatin yatsun da suka kwanta ɓaro-ɓaro a kumatunta tas sun ɓace.

Kwatsam wata ranar alhamis da misalin ƙarfe biyar na yamma ba zato ba tsammani sai jiniyar motar Mukhtar ta ji daga can tsakar gida.

Allah sarki Fareeda, ita da kanta bata san ta yi kewarshi da yawa haka ba, a guje ta miƙe jikinta na rawa ta fice da sassarfa zuwa tsakar gidan, yana fitowa daga mota bayan ya gama daidaita fakin ta ƙarasa gurinsa da sassarfa ta rungumeshi.

"Oyoyo Mijin Fareeda."

Ta faɗa da wani irin sanyi da ɗokin ganinsa a muryarta.

A yadda ya tsara ma zuciyarsa ko da ya iso gidan bazai shiga harkarta ba sam-sam, duk wani ƙwainane da iyayin da za tayi domin jan hankalinsa bazai kulata ba. Amma yanzu ya rasa dalilin da yasa ya kasa gwasaleta, bai san sa'adda ya mayar mata da martanin rungumar ba, ita da shi shiru sukai riƙe da juna suna sauke ajiyar zuciya akai-akai.

Ba ita kaɗai tayi kewarshi ba, shi kanshi yayi kewarta ba ɗan kaɗan ba. Ƙarfin hali da zaƙin sabuwar soyayyar da ya fara ne suka riƙe shi a can har tsawon wannan lokacin ba tare da ya waiwayota ba.

Ko yanzu babban maƙasudin dawowarshi ba don ita bane, don ya fuskanci al'amarin ƙarin aurenshi ne gadan-gadan. Da gaske ya shirya samarwa kanshi maslaha, a shekarunsa talatin da takwas bazai tsaya wata ƴa mace ƙwallin ƙwal tayi ta wahal da zuciyarsa ba. Ga irinta da waɗanda suka fi ta nan da yawa, kamar jamfa a jos! Da ƴan kuɗaɗensa a aljihu don haka gara ya karkata akalarsa zuwa wani guri ko zai samu nutsuwar zuciya, itama wacce zai ɗauko idan bai samu dalilan da suka jagorance shi zuwa gare ta ba zai koma wani ɓangaren ne. Kamar hula suke fa, zaiyi ta gwadawa ne yana cirewa har sai ya samu wacce ta shiga daidai da yanayin jikinsa da halayensa.

Kumatunsa ta shafa a hankali har zuwa kan laɓɓan bakinsa. Ɗan murmushi ta saki, ganin ya dawo daga duniyar tunanin da ya faɗa, a hankali ta sake shi, ta ɗan ja baya kaɗan.

Jakar hannunsa da sauran ledojin ta miƙa hannu za ta karɓa tana cewa

"Habeebi, barka da zuwa. Mu shiga daga ciki ka huta, ka sha hanya, ina roƙon Allah ya ƙara maka lafiya mijina da nisan kwana mijina, Allah ya ƙara tsare min kai."

"Ameen"

Ya amsa haɗe da ɗan taɓe baki, ko kaɗan kalaman ba wai sun wani burgeshi bane, Fareeda mai ladabin kunama kenan, za ta bi ka luf luf sai ka fara sakankancewa da ita sai ta sakar maka ƙari. Tsaki ya ja ƙasa-ƙasa.

"Lafiya?"

Ta tambayeshi da mamaki jin yana tsaki, abinda bai cika yi ba, ko ita tayi sai yayi mata magana.

Bai ce komai ba ya nufi hanyar shiga ciki ya barta nan tsaye jikin motarsa. Har ya kama ƙofar falonsu zai shige sai ya waiga, ɗayan apartment ɗin da aka fara gini ba'a kammala ba yake ƙarewa kallo, an kai tsawon linta, anyi rafta, an buga kwano, har ƙofofi an saka. Abinda ya rage plasta ne da P.O.P sai tiles da jan wuta. Murmushi ya saki, yana ayyana da ya huta a darennan zai nemi masu aiki su lissafa mishi adadin kuɗaɗen da suke ganin ƙarasa ginin zai iya ci. Daga haka ya shige ciki ba tare da ya ƙara kallon inda take tsaye riƙe da kayayyaki a hannu ba.

Ko kafin tabi bayanshi zuwa ciki har ya faɗa banɗaki ya fara yin wanka, bai damu da jiran ta shigo ta haɗa mishi ruwan wanka ba.

Tsananin mamaki kawai sai ta riƙe baki, jikinta a sanyaye ta ajiye mishi jakarshi nan gefen gado, ledojin da taga kayan cefane sai ta wuce da su kicin.

A tsarin da tayi ba don ya dawo yau ba sam baza tayi girki da daddare ba, shayi da biredi tayi niyyar za ta sha ta kwanta barci.

Amma sanin da tayi mishi duk ranar da zai dawo bai cika sake jiki ya take ciki da abinci ba, da ya dawo yayi sallah da wanka zai nemi abinci ne.

Don haka ta yanke shawarar a gurguje ta dafa mishi indomie da busasshen kifi, tana cikin yanka albasa sai ya shiga kicin ɗin.

"Me kike ƙoƙarin yi Baby?"

Ya tambayeta yana kallon yadda take komai cikin hanzari.

"Abinci zan samar maka, ban rage komai na abincin rana ba. Kuma baka sanar min yau za ka dawo ba shi yasa ban shirya maka komai ba..."

"Kar ki damu, dawowar ba taki bace shi yasa baki sani ba. Zo, magana za muyi, sauri nake zan fita."

Jikinta a sanyaye ta bi bayanshi zuwa falo, a maimakon ta zauna kusa da shi kamar yadda ta saba, sai kawai ta zauna gefe ɗaya a ƙasa kan kafet ta zauna, suna fuskantar juna.

"Kin tuna na daɗe ina neman transfer daga Kafancan zuwa nan cikin garin kaduna ko?"

"Eh na tuna"

Ta amsa da sanyin murya, idanunta a cikin nashi.

"Yauwa, to a wannan karon Allah ya nufa na sami transfer..."

"Alhamdulillahi ! Habeebee na taya mu murna, Allah mun gode maka. Allah yasa hakan shi ya fi alkhairi."

Ta faɗa da wani irin karaɗi na tsananin murna da farin ciki, saboda tsananin farin cikin samun abinda suka daɗe da fitar da rai har goshinta takai ƙasa tayi sujadar godiya ga Allah.

Duk wannan murnar da take yi hankalinsa ba shi a kanta, yana karanta saƙon da aka tura masa a waya ne yana sakin wani lallausan murmushi, har ta gama karaɗinta ta nutsu, ta dawo da hankalinta gare shi.

"Yauwa sai magana ta biyu, zan ƙara aure."

Wuta ne ya ɗauke mata na wucin gadi, wani hazo-hazo ya taho da saurin gaske zai gitta ta idanunta da sauri ta rufe ido.

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un!"

Ta ja salatin cikin wani irin murya mai rauni da miƙa wuya ga Allah maɗaukakin sarki. A hankali ta saukar da kanta ƙasa, zuciyarta sai wani irin bugu da tsallen baɗaken tashin hankali take yi, daƙyar da jiɓin goshi tayi ƙumajin cewa

"Allah ya sanya alkhairi."

"Ameen thumma Ameen."

Ya amsa cikin rashin damuwa da halin da ya ga ta shiga lokaci ɗaya.

Tsam ya miƙe da wayarsa a hannu zai fice, daman ya ɗau wankarsa cikin wata ɗanyar shadda getzner fara kar, sai ɗaukar idanu take yi. Har ya riƙe ƙofar falon sai ya waiga yana kallonta ya ce

"Baki tambaye ni yarinyar da zan aura ba?"

A hankali ta ɗaga idanu ta kalleshi, daƙyar ta iya fito da harshenta ta ɗan lashi laɓɓanta da ta ji sunyi mata wani irin bushewa kamar ta yini bata shafa musu mai ba.

"Ya shafe ni ne dole in san yarinyar...?"

"Kwarai kuwa! Ai tabbas ya kamata ki san wacce zan kawo miki gidannan a matsayin abokiyar zama. Ko da yake miye ma na wani kwana-kwana? abinda ba haramci za muyi ba sunnar ma'aiki za mu ɗabbaƙa, ba wata ba ce zan aura face ƙawarki Fatima, ko in ce aminiyarki..."

"Fatima? Fatima dai Mukhtar? Ita ta amince za ta aure ka...?"

"Da gudu ma, ke a banzan tunaninki akwai wata haɗaɗɗiyar mace da za ta ga sankacecen miji kamar Mukhtar ɗin Fareeda ta ce ba ta so?"

"Babu fa! Allah yasa alkhairi."

Ta faɗa cikin wani irin matsanancin ƙarfin hali da juriya, daga zaunen da take tana ganin wani jiri da yake neman rufe mata idanu, tana gani Mukhtar ya sauke mata wani ƙatoton murmushi wanda a take ta fassara shi da murmushin ƙeta, ya fice daga falon sannan ya buga mata ƙofa, bugun da ya sauka har a cikin zuciyarta.

Lumshe idanu tayi a fili cikin wani irin mawuyacin hali take ta jan addu'ar

"Laa'ilaha illallul azeemul haleem. Laa'ilaha illallahu rabbul arshil azeem, laa'ilaha illallahu rabbus samawati, wa rabbul ardhi, wa rabbul arshil kareem."

Daga zaunen da take ta dungura ƙasa kamar wacce ta tafi sujuda, amma ba sujada ta tafi yi ba, sumewa tayi.

Makaranta labarin RABON AYI ina miƙa saƙon godiya a duk inda kuke□□□□😘😘 ni Fareeda na gode da ƙauna, Allah ya bar zumunci. Da yawanku ina ganin coments ɗinku, amma ba na iya binku ɗaya bayan ɗaya inyi reply saboda hidindimun da suka sha kaina. Amma fa ina jin daɗin coments ɗin□□□□, bazan ɓoye muku ba maganganun da kuke yi kan labarin su ke ƙara min ƙwarin gwuiwar yin typing don kar in barku kuna jira. Na gode na gode□□😘😘😘😘 kar ku manta ina sayar da Datar MTN, wacce take so ta tura kuɗi ta acc ɗina da ke sama sannan a tuntuɓeni ta lambata da ke sama. 1gb 300, 2 600, 3 900, 4 1200, 5GB 1500.

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*9*_

Ba tare da ɓata lokaci ko wata damuwa a fuskarsa ba ya shige cikin motarsa. Zuciyarsa cike take taf da farin ciki.

Duk yadda Fareeda tayi jarumta wajen ɓoye tashin hankalin da ta shiga da jin sunan wacce zai aura shi kam ya gani, ai an ce labarin zuciya a tambayi fuska. Ƙarara ya ga tashin hankalin da zuciyarta take ciki zane ɓaro-ɓaro kan fuskarta.

"Kaɗan ma kika ji kuma kika gani Yarinya."

Ya faɗa haɗe da yin ƙwafa, babu tausayinta ko kaɗan a zuciyarsa.

Wannan wankan da ya ɗauka daman don Fatima yayi, tsawon sati biyun da suka kwashe suna zuba soyayya ta waya shi kam ɗari bisa ɗari ta yi masa, ya gamsu zai samu abinda yake so.

Irin alƙawurran ladabi, biyayya, gata, kogin so da ƙaunar da take ta ƙara kwaɗaita mishi idan suka yi aure shi kam ya amince ko bata kai haka a tsarin halitta ba zai iya auren ta.

Yo daman me ake biɗa a auren? ba kwanciyar hankali bane? A wannan matakin da yake kai na jin zafin irin ƙunci da baƙin cikin da Fareeda ta daɗe tana ƙunsa mishi ko tsohuwa ce zai iya aurenta matuƙar za ta bi tsarin da yake so, kuma su zauna lafiya ƙalau.

Yana gaf da ficewa daga cikin layinsu sukai clashin da motar Yaa Mustapha, da alamun gidansa suka nufa. Rage gudu Mustapha yayi da niyyar su gaisa, Mukhtar ya kawar da kansa ya ƙara ma motarsa wuta ya wuce a guje, ko fitila baiyi musu ba, kamar ma bai san motar waye ba.

Da mamaki Yaya Mustapha yake hangenshi ta mirrow har ya ɓace ma ganinsa.

"Wai wancan motar da ta wuce ba ta Mukhtar bane?"

Aunty Murja da take zaune gefen mai zaman banza ta tambaya, itama fuskarta na nuna mamaki.

"Shi ne. Ina ga bai ganmu bane."

Ya amsa yana ƙara gudu don isa gidan. Babban burinsa yayi tozali da ƙanwarsa, Shekaran jiya da ya kirata ta tabbatar mishi har ranar Mukhtar bai zo garin ba.

Yadda ya ganshi yanzu ɗinnan da yadda ya sharesu bayan sun haɗa idanu ya alamta mishi tabbas akwai matsala.

Bayan shigarsu cikin gidan sallama suke ta kwaɗawa a ƙofar falon, amma shiru suke ji. Duk su ukun kuma sun kira wayarta amma babu wanda ta ɗaga.

Cikin ɗan damuwa da ƙila wa ƙalan lafiya ko ba lafiya ba Aunty Murja da yɔar'uwarsu Rahama wacce ta kawo musu ziyara daga Rigacikun suka sa kai cikin falon don duba halin da ake ciki. Shi kuma Yaya Mustapha matsayinsa na namiji ya tsaya a bakin ƙofa hankalinsa a tashe yana jiran su gano halinda Fareeda ke ciki, domin tamanin bisa ɗari na tunaninsa ya tafi kan ba lafiya ba.

"Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un. Ke Fareeda? lafiya? me yake faruwa?"

Ya ji muryar su biyun sun faɗa cikin da wani irin karaɗin tashin hankali.

Ko kafin ya banke ƙofar falon ya shiga a sittin zuwa inda suke sai jin muryar Aunty Murja yayi ta fashe da wani irin ƙaƙƙarfan kuka.

Ganin Fareeda kwance shamɓar a ƙasa bayan gyara ta daga sujudar da tayi ba rai babu alamunsa a jikinta yasa shi ya tafi taga-taga zai kife, Allah ya taimake shi hannunsa na hagu ya dafe bango. Cikin ɗaukewar hankali da tunani ya tafi a slow motion ya zauna daɓar a ƙasa ya zuba ma gangar jikinta idanu, na wasu daƙiƙu ƙwaƙwalsa ta tsaya cak daga sadarwar saƙonni.

Rahma, wacce su Fareeda ke kira Baby saboda tsananin gayu da yanga irin nata, yar'uwa ce ta kusa sosai a gurinsu. Karatun aikin jinya tayi, duk da tashin hankalin da take ciki na ganin aminiya kuma yar'uwarta cikin wannan hali tunaninta bai ɓace kamar nasu ba. A nutse ta dudduba Fareedar sai taga ba rasuwa tayi ba, suma tayi.

Da gaggawa ta nufi kicin, gorar ruwa mai matsakaicin sanyi ta ɗauko ta dawo. A nutse ta zauna ta fara tsiyaya ruwan kaɗan a hannunta tana shafa mata a fuska, ta shafa sau uku a na huɗun Fareeda ta ja wani nannauyar ajiyar zuciya ta sauke.

Da saurin gaske kuma a firgice ta buɗe idanunta, ido biyu da sukai da Baby yasa ta miƙewa zaune a zabure da wani irin ƙarfi a jikinta ta ruƙunƙumeta, lokaci ɗaya kuma ta fashe da wani ƙaƙƙarfan kuka mai tafe da saƙon baƙin ciki da takaici tun daga can ƙarƙashin zuciyarta.

Kukan da ta fashe da shi shi ya zama kamar yarfin ruwan ƙanƙara ga Aunty Murja da Yaya Mustapha.

Da murna mai tsanani ganin ta farfaɗo suka matsa kusa da sauri, Aunty Murja ta ruƙunƙume su biyun itama tana nata kukan na farin ciki. Farkowar Fareeda ba mutuwa tayi ba ya kore mata duk wani damuwa da fargaba, a ganinta duk abinda zai biyo baya mai sauƙi ne.

Shi kuwa Yaya Mustapha gefe ya rakuɓe kamar ƙaramin yaro yana ta sassauke ajiyar zuciya a jejjere, zuciyarsa cike da farin ciki, babu abinda yake furtawa da murya ƙasa-ƙasa sai

"Alhamdulillahi alaani'imatihi tatimmussalihat."

Ganin kukan yana ƙara tsawo ya ƙi ƙarewa yasa Baby ta fara raɗa mata tausasan kalamai a kunnenta.

"Ya isa haka Besty, pls ya isa haka. Ummm?! Ba ga mu ba? ko ma wane al'amarin damuwa ne za mu fuskance shi tare, muna tare da ke, kin ji ko? duba kiga Aunty Murja riƙe da ke, kuka take saboda irin kukan da ta ga kina yi. Kin ga Yaya Musty zaune a gefenki shi ma cikin tashin hankali, kiyi haƙuri kin ji? kiyi ta maimaita Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Ko wane bala'i ne in Allah ya yarda zai zo mana da sauƙi kin ji?"

A hankali take ta rage ƙarfin kukanta, har tayi shiru gaba ɗaya, sai sauke ajiyar zuciya irinna wacce ta daɗe tana kuka.

Har wannan lokacin kanta na kwance a kafaɗar Baby. Mustapha da Murja sun matsa kusa da ita suna riƙe da hannayenta a cikin nasu, a fuskokinsu tana kallon matsanancin damuwa da tashin hankali saboda damuwar da take ciki.

"Mukhtar... zai... ƙara aure..."

Tayi maganar a rarrabe.

Su ukun gaba ɗaya buɗe baki sukai cikin tsananin mamaki suna kallonta, ƙara aure a daidai wannan lokacin shi ne abu na ƙarshe da za suyi tunanin Mukhtar zaiyi, ba don komai ba sai don ganin matsananciyar soyayya da shaƙuwar da ke tsakanin masoyan biyu.

Tuna komai lokaci ne kuma muƙaddari daga Allah yasa Mustapha rufe baki a sanyaye. Ya haɗiye wani kakkauran miyau, ya rasa da wace kalami zai fara amfani wajen kwantarwa da ƙanwarsa hankali.

Ya buɗe baki zaiyi magana Fareeda ta katse shi ta hanyar cewa

"Ya tabbatar min da zai ƙara aure, kuma babu wacce zai aura sai ƙawata... Fatima ƙawata... Fatiman Mama Laure."

Ta ƙarasa maganar da saukar wasu zafafan hawaye a idanunta.

"Kan ubancan kayyasa."

Baby ta lailayo wani ashar ta maka saboda yadda maganar ta bugi zuciyarta.

Duk su ukun babu wanda bai san Fareeda da Fatima ba, abin mamaki ne ƙwarai da jinjinawa a ce Mukhtar zai auri Fatima ƙawar Fareeda.

"Amma ita Fatiman ta amince?"

Aunty Murja tayi ƙarfin halin tambaya fuskarta na harhaɗewa da wani irin matsanancin ɓacin rai.

"Kwarai! Ya tabbatar min ta amince. Kuma daman sati biyu kenan ko na kirata a waya ba ta ɗauka, daga bisani ma sai ta kulle ni na daina samunta..."

Aunty Murja da Baby ne suka haɗa baki gurin cewa

"Kutmelesi..."

"Menene kuke yi haka kamar wasu ƙananun yara? Kun manta babu haramci ko kaɗan a cikin aurensu?"

Mustapha ya katse su da faɗin haka.

"Haba Yaya Mustapha, ai ana barin halas ko don kunya. Sai ka ce muna garin gaɓa-gaɓa(marasa hankali)?"

"Uhmmm! Baby kenan! ke dai kawai Allah ya iya mana. Amma muna cikin wani zamani ne wanda da yawanmu bamu ɗauki cin amana a bakin komai ba."

Lura da yayi maganganun matan babu abinda suke yi sai ƙara rura wutar kishi da baƙin ciki a zuciyar Fareeda duba da yadda take share hawaye akai-akai. Yasa Mustapha matsawa kusa da ita sosai ya fara rarrashinta da kalamai na kwantar da hankali.

*****

"Wai yanzu ƙawata kina nufin wannan ɗan mitsitsin turaren shi ne zan shafa a goshi na muyi tozali da Aban twince? Ni wlh na raina..."

Da saurin gaske ƙawar ta rufe mata baki, sai zazzaro idanu take yi hankali tashe kamar wacce taji za'ayi saɓon Allah.

"Ki iya bakinki. Na rantse da girman Allah ki iya bakinki. Ba'a tantama ko raba ɗayan biyu a kayan Hajiya Zainab Harka gaskiya da gaskiya. Idan ba haka ba kuwa ina tabbatar miki za kiyi biyu babu, ke ba ga biyan buƙata ba, maƙudan kuɗaɗen da kika kashe basu dawo ba."

"Hmmm! Allah na tuba. Shi kenan Ramlah. Na gode. Zan gwada sai fatan Allah yasa mu dace."

"Yauwa ko ke fa Hajiyata. Ai duk abinda zan karɓo miki gurin matarnan ina tabbatar miki kiyi amfani da shi kawai da dukkan ƙwarin gwuiwarki. Magungunanta yɾan gaske ne, manyan malamai gareta waɗanda kafin ta fara siyar da ko wane magani nata sai sun kwana sittin suna sauke izu sittin."

"Taɓɗijan!"

Fatima ta ambata cikin mamaki da jinjina girman al'amarin.

"Da gaske fa, amma na tabbatar duk abinda zan faɗa miki a yanzu baza ki yarda ba. Sai kinga Mukhtar ya zama tamkar takalmin takawarki. Fareeda kuwa ko rantsuwa nayi ba kaffara kina shiga gidan zaiyi waje road da ita..."

"Hehehehe!"

Ta fashe da wata ƙaƙƙarfar dariya na jin daɗin maganganun ƙawarta.

Sai kuma ta gyara zama a gefen gadon, ta ɗaura ƙafa ɗaya kan ɗaya tana girgizawa. Da dukkan gaskiyarta ta kalli ƙawar ta ce

"Kin san Allah? ni kuma ba na burin ya saki Fareeda. So nake cikin sanyi da wani irin taku na kissa in soya mata ɗanyar gyaɗa a hannu, ta wulaƙanta na ƙarshen ƙarshe, tana ji tana gani mijin da take tunƙaho da shi ya fi ƙarfinta, ya zamo sai hange daga nesa. Shi yasa Wallahi Tallahi Billahi ko nawa ne zan kashe don gyara kaina..."

A tare ƙawayen biyu suka fashe da wani ƙaƙƙarfan dariya haɗe da tafa hannayensu.

"Daman fa Hajiyarmu tana cewa burin kishiya abu uku ne. Ko ta fita ta bar miki gidan, ko ta mutu ta bar miki duniyar, ko tayi mummunar wulaƙantar da kare ma sai ya fita daraja a gurin mijin. Ki dage ƙwarai ƙawata ki tabbatar da ɗaya daga cikin maganganu ukun nan."

Ramlah ta faɗa da wani irin salon zuga da tunzurah zuciyar Fatima, ta kuwa samu nasara, nan take ta cigaba da shan munanan alwashi kan Fareeda.

Suna wannan halin Mukhtar ya kirata a waya ga shi a ƙofar gidanta.

Kuyi maneji da wannan don Allah. Ba nan naso tsayawa ba, wayata ne ba caji. Na gode da ƙauna yan'uwa😘😘😘.

*_Aminci + Kwarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daƌe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuƌin tsarin datar da kike so a wannan acc ƌin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane, shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*10*_

Lallausan murmushi ta saki jin cewar yana ƙofar gida. Mai gadin gidan ta kira, tayi mishi umarnin a buɗe ma babban baƙonta ƙofar gida ya shigo da motarsa.

Sai kuma ta kira ɗaya daga cikin ƙannenta biyu da suke zaune tare da ita da yaya̓nta ta bata umarnin ta shigo da baƙonta cikin falon. Daman tun tuni ta sa sun ƙalƙale ko ina an baɗe shi da turaren wuta.

Tun ɗazu ta yi wanka, zaman jiran ƙarasowarsa take yi Ramlah ta kai mata saƙonta.

Tun da ya shigo cikin kaduna ya faɗa mata ya iso, ko da ya ce mata gida zai fara zuwa yayi wanka har da kukanta na kissa.

Cikin shagwaɓa ta roƙe shi to don Allah idan ya je gida kar ya daɗe, tun ɗazu ta gama shirya mishi kayan abinci ta yi kwalliya zaman jiranshi kawai take yi.

Ta sake ƙasa ƙasa da murya tana ɗan jan hanci, kamar har lokacin kuka take yi ta ce

"Aban Twince, ka ganni zaune hannuna a kunci, idanuna sun ƙure ƙofar shigowa da kallo, babu abinda suke so da buri sai suyi tozali da kyakkyawar fuskarka mai cike da annuri da haske, irinna mai riƙo da Addinin musulunci.

Hancina a buɗe yake, babu abinda yake muradi sai ya shaƙi daddaɗan ƙamshin da jikinka ke fitarwa Nawan"

Kunnuwana a burbuɗe suke, babu abinda suke kwaɗayi sai suji saukar sautin tattausan muryarka mai cike da amo da kwarjini na ingarman namiji.

Don Allah ka tausaya ma zuciyar da kullum take ta tsallen daka tana jiran isowar abokin soyayyarta.

Kar ka bari Aunty Fareeda ta tsare ka da surutunta har mu bushe ni da abincin da na shirya maka wajen zaman jiranka."

Daga haka ƙit ta katse wayar, tana jin shi yana ta sauke numfashi sama-sama tsabar yadda kalamanta suka rugurguza ɗan ragowar kuzarinshi.

Da yake ɗan halas ne, ko da ta kalli agogo yanzu sai ta ga mintuna arba'in da bakwai kenan da gama wancan wayar tasu. Lallai Mukhtar za'a je da shi.

Ashe ma bashi da wahalar sha'ani kamar yadda kullum Fareeda take cewa

"Ke ƙyale ni, Mukhtar murɗaɗɗen mutum ne. Lallaɓawa nake yi ina haƙuri don mu zauna lafiya."

Tunanin Fareeda a wannan gaɓar da tunanin irin maganganun da suke yi a lokuta mabanbanta yasa ta jan tsaki ƙasa-ƙasa.

"Ƙawata lafiya kuwa?"

Ramlah ta tambayeta.

"Ba komai ƙawata. Wani banzan tunani ne ya faɗo min arai. Ki jira ni anan pls in sallami Aban Twince, idan ya tafi sai in baki cikon kuɗin."

Ta miƙe da hanzari ta fara sabunta kwalliyarta, a fuska kaɗai za'a kalli Fatima asan tana cikin matsanancin farin ciki.

Cikin lokaci kaɗan ta rambaɗa wani ubansun kwalliya, kamar wacce za ta je gasar fitar da sarauniyar kyau ta jihar kaduna. Ta ɗauko wani ɗan ubansun leshi da aka yi mata ɗinkin doguwar riga, daga sama ya kamata tsam, daga gurin gwuiwarta zuwa ƙasa sai rigar ta baje. Ta ɗauko wani siririn gyale da zai shiga da leshin ta rataya a kafaɗa, ta yi kyau sosai.

Ƙawarta Ramlah sai zabga mata kirari take yi ita kuma kanta yana ƙara kumbura. Daga bisani ta fice daga ɗakin da salon tafiyar za tayi baza tayi ba, tana wani rangaji kamar reshen bishiya a iskar damina, hannunta riƙe da wannan turare wanda Ramlah ta karɓo mata.

A ƙofar shiga cikin falon ta tsaya ta buɗe turaren ta zuba fiye da rabi a jikinta, nan take gurin ya ɗume da wani irin ƙamshi mai tafe da ƙauri-ƙauri.

Ita kanta ƙamshin baiyi mata ba, amma kasancewar turaren magani ta san dole za'a ji haka, wataƙila a hancin wanda aka siya turaren dominsa tattausan ƙamshi mai matuƙar kwantar da hankali zai shaƙa.

Tunanin hakan ya sa ta sakin murmushi. Ta maƙale muryarta ƙasa sosai da wani irin salo na jan hankali tayi masa sallama, ta jira ya amsa sannan ta yaye labulen ta sa kanta ciki.

Suna haɗa idanu a tare su biyun suka sakarma juna wani lallausan murmushi, ta ƙarasa a hankali da wannan salon tafiyar nata har zuwa kusa da inda yake zaune, kan kujera mazaunin mutum uku.

A maimakon ta zauna kan ɗaya daga cikin kujerun da suka zagaye falon, sai ta tsuguna a ƙasa, cikin ladabi da ƙanƙan da kai ta sauke idanunta ƙasa kamar baiwa a gaban ubangidanta.

"Haske nah, ina maka barka da zuwa akurkin muhallina a karon farko. Na ji daɗi matuƙa gaya, yau ɗin ta kasance rana mai matuƙar muhimmanci a cikin tarihin rayuwata. Barka da zuwa, ya hanya? ina fatan ka iso lafiya?"

Duk waɗannan maganganun da take yi tana yi ne da wani irin salo na jan hankali, ga miji mai matuƙar son girma da biyayya na ƙarshe irin Mukhtar.

"Mace mai ladabi duniya ce Alaji."

Mukhtar ya faɗa a zuciyarsa. Daƙyar ya iya mazewa don kar ya bada kanshi a karon farko ya amsa gaisuwarta.

Umarni yayi mata kan ta tashi ta hau kan kujera, buɗar bakinta sai cewa

"Miji fa tamkar Ubangida yake a gurin mace mai wayau. Taya zan iya hawa saman kan kujera in goga kafaɗa da kai alhalin kana saman kujerar? A ganina babu ladabi ko kaɗan a cikin haka. Ka barni haka Aban Twince, nan ɗin ma ya isa."

Sai ta ɗan muskuta ta gyara zama a kan kafet nan gabanshi, ta tsura mishi idanu tana kallon tsantsar kwarjini da zatin da Allah ya zuba a fuskar wannan bawan Allah.

Tunanin ko ruwa bata gabatar mishi ba yasa ta nemi afuwarsa a marairaice.

"Yi haƙuri Haske nah! kallon kyakkyawar fuskarka na neman shagaltar da ni in gabatar maka da ababen motsa bakin da na shafe tsawon yini guda ina shiryawa musamman domin kai Mijina. Ina sake neman afuwa a karo na biyu."

Lallausan murmushi kawai ya sakar mata, shi fa ya ma kasa magana. Babu abinda yake hasasowa a zuciyarsa sai irin kyakkyawan zamantakewar da za suyi shi da Fatima. Lallai wannan ita ce abokiyar burminsa.

Sai bin ta da kallo yake yi tana jera wasu ƙayatattun kulolin cin abinci a gabansa, bayan ta janyo wani ɗan madaidaicin teburin da ake ɗora abinci a tsakiyar falo idan ba'a sha'awar zuwa dining table.

Sai da ta kwaso kayan abincin tas, da wani jug ɗin gilashi mai cike taf da kakkauran zoɓo da yasha kayan ƙamshi.

"Haske nah! Ka yi min izinin in zuba maka abincin?"

Ta tambayeshi a ladabce.

A wannan karon ma ya kasa magana, sai kai ya iya ɗaga mata alamar yayi mata izini.

Martanin lallausan murmushi ta fara sakar masa, kafin ta fara buɗe kular miya tana satar kallonshi.

Daddaɗan ƙamshin miyan agushin da ya daki hancinshi yasa shi buɗe hanci sosai ya shaƙi ƙamshin, ya lumshe idanunsa. Kafin daga bisani ya buɗe idanu ya sauke kan kayan abincin, a daidai lokacin da ta ɗauko malmala ɗaya na sakwarar da ya daku luƙwui-luƙwui ta saka masa a faranti.

A wannan gaɓar kam ya kasa shiru, sai da ya ce

"Fatina? ya aka yi kika san abincin da na fi so a rayuwata?"

Ya tambayeta yana mamaki.

Far tayi masa da idanu, ta rausayar da kanta gefe guda. Muryarta ƙasa-ƙasa da rangwaɗa ta gilla mishi ƙarya da cewa

"Haske nah! Sakwara da miyar agushi nima shi ne abincin da na fi so a rayuwata. Kawai zuciyata ce ta raya min, idan da gaske so ya kai so tsakanina da kai tabbas zai kasance abinda nake matuƙar so kaima kana son sa. Abinda nake ƙi kaima za ka ƙi shi Aban Twince, kasancewar hakan shi ne cikar soyayya."

A zahirin gaskiya a gurin Fareeda taji yana matuƙar son sakwara da miyar agushi. Idan ta je gidan a mabanbantan lokuta tana tarar da ita tana daka sakwara. Ita kuma Fatima abinda bai dameta ba kenan, idan ta fara ƙorafi ita ko wahalar daka ba ta ji kai tsaye take faɗa mata Mukhtar na tsananin son sakwara, ko laifi tayi masa idan tana so ya huce da sauri to tayi masa sakwara miyar agushi da busasshen kifi ko kuma da naman rago. Ta yi amfani da haka ne don ƙara saye zuciyarsa.

Shi kuwa tsananin farin ciki da jin daɗi ba kunya ya tare hannunsa a baki ya sumbata, sannan ya hura mata a cikin iska.

Lumshe idanunta tayi tana dariya ta ɗan rufe gefen fuska irin alamun ta ji kunyar nan, me ta tuna kuma oho! sai ta buɗe fuskar da sauri ta saka idanunta cikin nashi. A tare suka sakarwa juna murmushi.

Sosai ta zuba mishi miyar agushin da ta ji naman rago ya dahu luguf a gefen sakwarar.

Ko kafin ta miƙa mishi har miyan bakinshi ya gama tsinkewa. Don haka bai ɓata lokaci ba yayi bismillah ya fara ci a nutse, yana yaba ɗanɗanon girkin a fili da zuciyarsa.

Tagumi ta buga da hannu biyu ta gyara zama a ƙasa nan gabansa tana sake ƙare masa kallo.

'Wato lallai Allah Al-musawwiru ne. Ashe akwai rabon yin aure wataƙila ma har da yara tsakaninta da Mukhtar? Ba tun yanzu ba yake bala'in burgeta. Auranta na farko dattijo ta aura, wanda ya auri wata matar kafin ita ta haifa masa yaya uku duk mata sai Allah yayi mata rasuwa. Ko da ya aureta ya aura ne da sa ran za ta riƙe masa marayun yayansa, da farko kuma rigiɗi-rigiɗi kamar zaman zaiyi daɗi a tsakaninsu. Daga bisani ta tasa su gaba da makirci da bita da ƙulli rikici ya ɓalle tsakaninta da manyan yaran biyu. Duk sa ido irin na mijin kuma ya rasa gane mare gaskiya a tsakaninsu.

Daga ƙarshe dai dole a zaman yayan ya koma gaban yayar mijinta Hajiya Zainab, wacce ko ƙanƙani babu shiri tsakaninta da Fatima. Aure da rabo kuma wata goma sha ɗaya ta sunkuto yarta mace, aka saka mata sunan marigayiya uwar mijinta, Sa'adiyya, sai suke kiranta da Ummee. Wata shekarar na zagayowa ta sake haifo ya mace. Wannan haihuwa biyu da tayi a jere shi ya kawo sauƙin ƙiyayyar da Yar mijin ke mata, har sukan zauna inuwa ɗaya ba tare da ta caccaɓa mata baƙaƙen maganganu ba.

_A gefe guda kuma duk da waɗannan yayan biyun da ta haifa shaiɗaniyar zuciyarta bata daina bugawa duk sa'adda za tayi tozali da Mukhtar mijin Fareeda ba. A wani lokacin har baiken kanta take gani, tana ga kamar tayi sauri wajen zaɓin mijin aure. Tunda ita ta fara aure da shekara ɗaya da rabi kafin Fareeda tayi. Wata ƙil da bata

yi gaugawa ba, ita Mukhtar zai gani ya ce yana so ba Fareeda ba, tun da duk inda ɗaya za taje tare take da ɗayan._

Kwatsam kuma sai ga rasuwar mijinta bayan ta haifa masa yaya huɗu. Idan ta ce bata ji rasuwar mijinta uban yayanta ba ta yi ƙarya. Amma bayan kwaranyewar komai ta ci gaba da rayuwarta cikin walwala tare da ƙannenta biyu waɗanda ta ɗauko daga gida don su tayata zama. Da yayanta huɗu, tunda kafin rasuwar mijin ya bar wasiyar ta riƙe mishi yayanshi a gidanshi, idan za tayi aure ta ba Yayarsa Hajiya Zainab yaran ta haɗa da na hannunta ta riƙe har zuwa aurensu.

Bayan shekara guda da rasuwar mijinta sai wannan shaiɗaniyar zuciyar ta sake yunƙurowa ka'in da na'in take ƙawata mata Mukhtar. Duk sa'adda taje gidan Fareeda ta gan shi ta dinga kwainane kenan da sunƙe-sunƙe na neman samun shiga, shi kuwa a lokacin ko kallo bata ishe shi ba.

Ashe ba tare da sanin su biyun ba ƙaddarar aure zai iya shiga tsakaninsu a lokacin da basu taɓa tsammani ba. Lallai Allah da girma yake...

"Tunanin me kike yi?"

Ya tambayeta da kulawa bayan ya gama cin abincin, ƙaramin kofin da ya tsiyayi zoɓo ne a hannunsa yana kurɓa a hankali yana lumshe idanu.

"Ikon Allah kawai nake tunani Aban Twince. Ummm nace ba? Ka faɗa ma Aunty Fareeda za ka aure ni?"

"Ke tsaya, wai Fareedar ce kike ce mata Aunty?"

Ya tambayeta yana dariya.

"Uhmmm ba dole in ce mata Aunty ba? Ko da na ɗan girme mata da ƙananun watanni kuma Aminiyata ce ai gaba take da ni a gidan miji, ka ga girma dole in bata a matsayinta na uwargidan farin cikin zuciyata.

Ni dai don Allah Aban twince"

Tayi ƙasa da idanunta ta haɗe hannayenta biyu alamun roƙo.

"Duk da na san ƙawata akwaita da bala'in taurin kai, duk abinda ta so kuma zuciyarta ta kitsa mata ko ba daidai bane shi take aikatawa. Na san za ka ga tashin hankali da masifarta idan ka faɗa mata maganar aurennan, don Allah kar ka biye mata.

Ka bi ta a sannu, idan tayi haƙuri ni ba da tashin hankali zan shiga gidanta ba. Alkhairi da albarka nake so mu haɗu mu gina bisa jagorancinka Haske nah! Kayi haƙuri da haukarta pls"

Lallai bahaushe yayi gaskiya, duk girma da shekarun namiji ƙaramin yaro yake zama a gaban mace. Duk tsauri da taurin Mukhtar sai ga shi salon da Fatima tayi amfani da shi ta bala'in tafiya da shi.

Bai bar gidan ba sai misalin ƙarfe tara da rabi na dare, ko sallar isha'i bai halarta ba. Ya tafi ne bayan sun gama tsara za suyi aure nan da sati uku! in dai sun samu yadda suke so babu daɗi ba ƙari.

******

Ido a buɗe Hajiya Aisha take kallon babban ɗan nata da mamaki, bayan gama sauraren duk irin maganganun da ya taho mata dasu a wannan dare. Daƙyar ta iya buɗe baki ta ce

"Aure nan da sati huɗu Malam? (Haka take kiranshi saboda kasancewarsa ɗan fari.) To wace yarinya za ka aura a cikin wannan taƙaitaccen lokacin?"

"Fatima, Fatima zan aura Hajiya. Don Allah ki saka albarka kar ki ce min a'a."

Ya ƙarasa maganar a marairaice, da damuwa sosai a fuskarsa.

"Wata Fatima kenan?"

Ta tambayeshi ba tare da damuwa da yanayin fuskarsa ba. Ita zancen auren ne ke ta bata mamaki, to wani rikici ke tsakaninshi da Fareedar da ita basu faɗa mata ba?

"Za ki santa ma yarinyar, Fatima ƙawar Fareeda. Wacce mijinta ya rasu kwanakin baya can..."

"Fatima dai Yaya? amma kam ta tabbata gagarumar munafuka kuma maciya amana ta ƙarshen zamani."

Ƙanwarsa Zubaida da tayi luf akan kujera kamar tana barci ta faɗi haka bayan ta wuntsulo daga kan kujerar ta faɗo ƙasa saboda yadda maganar ta jijjigata.

Idanu ya zazzaro mata yana galla mata harara

"Wa ya kasa da ke a wannan maganar yɗar sa'ido? Ɓace min daga nan kafin in tattaka ki."

"Yarinyar da auranta za ka taka ta Malam?"

Hajiyarsu ta tambayeshi tana jinjina kai alamun ƙarin mamaki. Sai kuma ta mayar da kallonta wajen Zubaida da ta daskare a zaune tana kallon Mukhtar.

"Shiga cikin ɗaki ki jira ni."

Tsam ta miƙe tsaye bayan ta ɗauki wayarta da ke ajiye a hannun kujera. Kamar baza ta sake cewa komai ba, sai da ta kusa shiga ɗaki ta jiyo ta kalli Mukhtar, da ɗaurarriyar fuska ta ce

"Yaya, gaskiya baka yi ba. Amma fa ka sani, duk wanda yaci amana ko ba jima ko ba daɗe tabbas amana sai ta ci shi. Fatan alkhairi."

Da saurin gaske ta shige cikin ɗaki ta banko ƙofar ganin ya miƙe a zafafe yana muzurai.

"Hajiya kina ganin Zubaida..."

"Zauna."

Uwar ta bashi umarni fuskarta a ɗaure.

A sanyaye ya koma inda ya tashi ya zauna, ya saukar da kanshi ƙasa, zuciyarsa cike da addu'ar Allah yasa dai kar Hajiyarsa ta hana shi auran Fatima, don gaskiya ba ya jin zai iya bin umarninta a wannan karon.

"Me Fareeda tayi maka?"

"Ba komai."

Ya amsa kai tsaye.

Girgiza kai tayi, kafin ta sake cewa

"To me yasa za ka auro mata ƙawarta ko in ce aminiya a matsayin kishiyarta?"

"Hajiyaaaa.... wannan auren fa ba haramun bane. Banzar magana ce kawai ta Malam bahaushe da yake wani cewa ana barin halas ko don kunya. A matsayina na namiji mijin mata huɗu na ga Fatima tayi min, ina niyyar auranta. Kuma na faɗa ma Fareeda bata tayar da hankalinta ba, har tayi min fatan alkhairi. To don Allah Hajiya menene kuma na wani damuwa ko ƙananun maganganu?"

"Babu! Fatan alkhairi Malam. Hmmm! Allah ya jiƙan Alhaji (Mahaifinsu Mukhtar da ya rasu shekaru shida baya tun Fareeda na amarya) Idan ka bar nan sai kaje gurin ƙanin mahaifinka yayi maka jagora."

Ta faɗa har lokacin babu walwala a fuskarta.

Ya buɗe baki zaiyi magana ta ɗaga mishi hannu alamar dakatarwa.

"Maganar da ka zo don muyi mun gama ta, kana iya tafiya. Dare yayi, kwanciya zanyi. Allah ya bamu alkhairi."

"Ameen."

Ya amsa jikinsa a sanyaye, yana ta kallonta amma ta hana shi sake magana. A dole ba don yana so ba ya miƙe ya kama hanyar fita daga falon.

"Malam"

Ta kira sunanshi.

Ya juyo da sauri zai dawo ta sake dakatar da shi.

"Ka tsarkake zuciyarka, kayi komai don Allah. Idan ba haka ba tabbas ƙarshen ko wace gaugawa da-na sani ce da cizon yatsa, don daga shaiɗan take. Ka gaida Fareeda, sati mai zuwa ina nemanta."

A dai dinga yi ana siyan data a guri na😘😘😘❤□□

*_Aminci + Ƙarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*11*_

Sosai kanshi ya ɗauki zafi, ɓacin ran Hajiyarsa ba abu bane da zai murje fuskarsa ya shanye kamar babu komai.

Daga yadda ta amsa mishi ya san ta dai amince ne kawai, don ba ta da yadda za tayi. To amma shi ya zaiyi ne? zancen gaskiya bai fara neman auren Fatima don ya fasa ba.

Shi sai yau da suka yi ido biyu maganganu suka shiga tsakaninsu ya ji tabbas aurenta wajibi ne a gare shi. Aurenta shi ne zai zamo babbar maslaha tsakaninshi da Fareeda.

Kawai dai zai kwantar da kanshi ya cigaba da lallaɓa Hajiya yana bata haƙuri, ita ba mace bace mai tsananin riƙo, ya san cikin ƙanƙanin lokaci za ta haƙura ta yafe mishi.

Ganin dare ya fara yi sai bai yi yunƙurin zuwa gurin ƙanin mahaifinsa ba, kai tsaye ya nufi gida. Gajiya ke nuƙurƙusarsa yana mazewa, da yake ya sa maganar auren a ranshi yana so ayi komai da zafi-zafi, yadda ya shawo doguwar tafiyarnan ai da babu abinda zai fitar da shi a yau dai sai zuwa masallaci, ko kuma larura wacce ba'a fatan samuwarta.

Ganin wutan falon a kashe shi ya alamta mishi Fareeda ta kwanta, ya taɓe baki, ko kaɗan bai ji ba daɗi ba yadda yake ji a baya idan yana gari ya fita ya dawo ya tarar ta kwanta bata jira shi ba.

Kai tsaye ɗakinsa ya nufa, yayi tunanin zai tarar da ita ciki sai yaga saɓanin haka.

"Ma sha Allah"

Ya furta a fili cikin jin daɗi.

Ya gaji ƙwarai, hutu yake buƙata. Kuma a yadda yasan halin Fareeda kamar yunwar cikinsa shirun da tayi masa ɗazu yasan akwai rikici da bala'in tashin hankalin da zai biyo baya, duk masifa irin tasa sam ba ta tsoronsa a wasu lokuta, kuma bakinta bai cika mutuwa akan ko ma menene ba, sai dai kawai tayi shiru ba don ta rasa abin cewa ba.

Ya shirya mata, bai jin tsoron komai, duk wani rikici da za ta girgizo dai-dai yake da ita. Ita tasan a faɗa da masifa ya dame ta ya shanye.

A darennan ne dai yake buƙatar hutu, gara da ta bashi iska sa haɗu da safe, in yaso suyi duk wacce za suyi, ko ta ware ko ta warwaraye, ya shirya ma ko wanne a cikin abu biyun.

A shekarunsa na tashen ƙuruciya bazai sake yarda ya ɗauki wani zafin taurin kai da rashin jin maganar Fareeda ba. Ya kai maƙura, iya haƙuri da kawar da kai yayi, yanzu lokacinsa ne na ɗaukar matakin da yaga ya dace.

A gurguje yayi wanka, ya canza kayansa zuwa na barci, ya bi lafiyar gado. Yana kwanciya kiran Fatima na shigowa cikin wayarsa, da mamaki a fuskarsa yake kallon kiran.

Ya rasa dalilin da yasa shi jin babu daɗi a ransa, me kuma take nema bayan ɗazunnan suka rabu?

Ƙasa-ƙasa ya ja tsaki, ya danna maɓallin rage ƙara ya juya ma wayar baya. Addu'ar kwanciya barci yayi ya shafe jikinsa gaba ɗaya, yana runtse idanu babu ɓata lokaci nannauyan barci yayi awon gaba da shi.

Tun da ya shigo da mota cikin gidan tana jin shi, a wannan lokacin tana zaune ne kan darduma tana jan casbaha, bayan ta idar da shafa'i da wuturi.

Buɗe ƙofar falon da yayi yayi daidai da wani irin bugawa da ƙirjinta yayi, da sauri tasa hannun hagu ta dafe saitin zuciyarta tana jan Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un.

Sai wani bahagon tambaya ya shigo cikin zuciyarta.

"Yanzu fa Mukhtar ɗinta daga gurin Fatima yake ko?"

"Uhmmm!"

Ta faɗa a fili, zuciyarta na sake tuna mata tsakaninta da Fatima. Aminiyarta ta ƙud da ƙud!

Fatiman da a baya babu jituwa ko na kwabo tsakaninsu da Mukhtar, wai ita ce yanzu har suka ƙulla za suyi aure...

Numfashi ta fara ja tana saukewa sama-sama cikin sauri saboda wani irin bala'in zafin kishi da takaicin cin amanar da suka yi mata.

Ta lumshe manyan idanunta da daga yammacin nan zuwa dare suka kumbura sosai, ga wani irin nauyi da suke mata saboda yawan kukan da tayi.

Ita ba jahila bace, ta sani babu haramci a cikin aurensu. Amma tsakani da Allah sun ci amanarta, ta yarda da su biyun sosai da sosai, aure tsakaninsu biyun abu ne da ko a mugun mafarki bata taɓa hasashen zai iya faruwa ba.

Wasu zafafan hawayen suka sake silalowa daga idanunta. Zuciyarta cike da saƙe-saƙen tunanika da tambayoyi mabanbanta.

"To wai shin, ta yaya aka haihu a ragaya? ko dai daman tuntuni akwai kyakkyawar mu'amala a tsakaninsu ita ce suke ninke ta a baibai saboda sun maishe ta sakarya?

Inaaa... Za ta iya rantswa Babu ! Duk da Fatima gwana ce gurin ɓoye-ɓoye, da iya yima ƙarya kwaskwarima don ta zama gaskiya.

Shi Mukhtar ba mutum bane mai fuska biyu, ya sha ce mata shi fa ya tsani Fatiman nan, ruwan munafukai gare ta. Kuma yadda yake maganar a kallo ɗaya za'ayi masa asan daga zuciyarsa ne, iya zallar gaskiyar abinda ke ransa yake faɗa.

Ko rantsuwa tayi babu kaffara a baya babu wata dangantakar arziki a tsakaninsu, a cikin kwanakin nan ne dai suka ƙulla dangantakar da har ta miƙa za suyi aure.

Saboda rashin jin maganarta ne Mukhtar zai auro ƙawarta don ya girgiza duniyar nutsuwa da kwanciyar hankalinta? Tayi wani murmushi mai ciwo, tabbas ya ci galaba a kanta.

Wani ƙaƙƙarfar kuka da ya ƙwace mata yasa da sauri ta cukwuikwuiye hijabinta ta cusa a bakinta, don kar sautin kukan ya fita har ya jiyota daga ɗakinsa.

"Yʻar'uwa, yanzu ba lokacin da za ki zauna kina ɓata lokacinki akan kuka bane. Ki tashi tsaye da ibada, ki ninka ki ƙara ninkawa a cikin nafilfilin da kike yi. Allah da ya halicce ki ya halicce su biyun shi za ki fuskanta ki kaiwa kukanki, idan akwai zalunci a ciki da gaugawa zai saka miki, domin shi Allah SWT mai saurin karɓar addu'ar wanda aka zalunta ne."

Maganganun da yʻar'uwarta Baby tayi mata ɗazu gab da za su bar gidan suka dawo mata raɗau a cikin kunnuwanta kamar a lokacin take faɗa mata.

"Fareeda shalelen ƙanwata, ki kwantar mana da hankalinki don girman Allah. Kishiya ko? Anyi ma dubu bata kashe su ba ke ma baza ta kashe ki ba.

Idan matsananciyar damuwa ta turnuƙo ki ki tuna mu yʻan'uwanki da muke tsananin ƙaunarki, idan kika bari wani mummunan ciwo ya kama ki mu muke da asara ba Mukhtar ba.

Ki yawaita istigfari domin Allah ya yafe miki kura-kuranki, wataƙil laifin da kika aikata ne yasa Allah ya jarrabeki da wannan lamari ko za ki hankalta ki dawo cikin hayyacinki. Ki tuba ma Allah, domin shi ɗin mai karɓar tuban bayinsa ne ako wane lokaci.

Ki dinga faɗin Hasbiyallahu wa ni'imal wakeel. Ki ta maimaita Lahaula walaa ƙuwwata illa billah. Kiyi kuka a gaban Ubangijinki Fareeda, ki kira shi da tsarkakan sunayensa waɗanda idan an kira shi da su yake amsawa. Ki roƙe shi da kyawawan sunayensa waɗanda idan an roƙe shi da su yake bayarwa. Ki yawaita maimaita Ya

Allah ka jiɓanci lamurana, ka zama gata na, ka shirye ni shiriya madaidaiciya, ka kawo daidaito tsakanina da mijina. Ya hayyu ya ƙayyumu ka kawar da shaiɗan ko shaiɗaniyar da take tsakaninmu."

Shawarwarin Aunty Murja gareta kafin su bar gidan.

Shi kuwa Mustapha murmushin ƙwarara gwuiwa yayi mata, ya riƙo hannunta na dama ya riƙe a cikin nasa.

"Fareeda, mu maza muna so idan za muyi aure matayenmu na gida su dinga hauka da nuna mana tsananin kishinsu, hakan yana sa muyi ta jin daɗi muna ƙara manna musu hauka. Duk zafin da za kiji a zuciyarki kar ki kuskura ki nuna ma Mukhtar kin ji ko?"

Daƙyar ta iya ɗaga mishi kai.

"Na san fa ƙanwata Fareeda za ta iya, don ita ɗin mai aji ce. Duk tsananin son abu da take yi idan ya bata haushi tana aje shi gefe ɗaya ta cigaba da harkokinta lafiya kamar wannan abu bai dameta ba. Ko ta canza daga wannan halin?"

A dole ta saki murmushin yaƙe ga hawaye kaca-kaca da fuskarta. Ta girgiza kai alamar bata canza ba.

"Yauwa Luvly Sister. To yanzu amfanin wannan halin ya zo, ki yi mishi biyayya, amma ki kawar da kai a lamarinsa kin ji ko? Akwai addu'o'in da zan tura miki ta whatsapp, ki dage ki tayi, mu ma za mu taya ki. Idan kika fuskanci Ubangiji tabbas zai fuskance ki Fareeda."

Tunanin kyawawan maganganu da shawarwarin da yan'uwanta suka ba ta ɗazu kafin ficewarsu daga gidan yasa ɗif ta ɗauke kukanta.

A nutse ta miƙe tsaye, hijabin jikinta ta cire ta ajiye a gefen gado. Banɗaki ta koma ta sake ɗauro alwala.

A wannan dare, kusan kwana Fareeda tayi tana sallah, idan ta gaji, sai ta zauna tayi ta istigfari, hailala, tasbihi, salatin Annabi, sai ta cigaba addu'o'i cikin kuka take roƙon Allah ya daidaita mata al'amuranta.

Ƙarfe uku da minti biyar wani nannauyan barci yayi awon gaba da ita nan kan darduma. Barcin da ya zo mata da wani irin nutsuwa, kwanciyar hankalin da bata taɓa tsammanin samunsa a cikin ƙanƙanin lokaci haka ba. Lallai da gaske ne duk wanda ya dogara ga Allah ya isar masa.

Ƙarfe huɗu da minti arba'in daidai ta farka da salati a bakinta, idanunta na sauka kan agogo tayi saurin miƙewa zuwa banɗaki ta sabunta alwalarta.

Malamin islamiyarsu ya taɓa faɗa musu lokacin ketowar alfijir lokaci ne na karɓar addu'ar bayi.

Da nutsuwa ta cigaba da nafilfili tana addu'o'i a cikin sujada har aka kira sallar farko. Ta miƙe tayi raka'atanul fijr, aka kira sallar asubah ta gabatar da ita. Tana cikin yin azkhar ɗin safe wani nannauyan barci ya dinga fisgarta, daƙyar ta iya ƙarasawa tayi addu'a tabi lafiyar gado. Tana jin zuciyarta sakayau, kaso tamanin cikin ɗari na tashin hankalinta Allah ya yaye mata.

******

Tana idar da sallar asubahi ko addu'a bata tsaya yi ba ta tafi ɗakin da ƙannenta suke kwana.

Ta tarar da su kan dadduma ne, suna Azkhar, tsananin zaƙuwar da tayi suyi maganar da ke tafe da ita ta kasa jira su gama, umarnin katse Azkhar ɗin tayi musu, ta ce magana za suyi.

Hankali tashe suka yi addu'a a gurguje, suka tattara nutsuwa da hankalinsu kaf zuwa gareta.

Cikin hikima da yi ma zance kwaskwarima ta faɗa musu maganar za tayi aure, kuma Mukhtar za ta aura. Ƙure su da kallo tayi tana jira taga yanayin da za su nuna da irin maganganun da za su furta.

Sai taga gaba ɗaya su biyun shiru suka yi suna kallonta da matsananciyar al'ajabi da mamaki a fuskokinsu, kamar sun ga wata sabuwar halitta, bakunansu a buɗe.

Haushin yadda suka tsaya kallonta bayan tsawon daƙiƙun da ta ɓata tana faɗa musu maganar aurenta kawai sai ta ja wani dogon tsaki, ta daka musu tsawa cikin fushi ta ce

"Wani irin iskanci ne za ku tasa ni gaba da kallo kamar baku sanni ba?"

A tare ƙannen nata suka yi firgigit kamar masu barcin da aka sheƙa ma ruwan sanyi, sai kuma wannan ta kalli wancan wancan ta kalli wannan, aka rasa wacce za ta fara cewa komai.

Cikin hargagi da masifa ta cigaba da cewa

"Wallahi tallahi idan baku ce wani abu ba sai na ci mutuncinku da asubahinnan..."

"Kiyi haƙuri Aunty."

Suka haɗa baki gurin faɗin haka da damuwa a fuskokinsu.

Jiddah ce ta ɗan motsa tana jin yadda mazaunanta suka yi wani irin tauri kamar wacce ta shafe awoyi a zaune, ta kalli Fatima da take ta huci na ɓacin ran da suka guma mata, da sanyi a muryarta ta ce

"Aunty Fatee, Ni fa wallahi na yi shiru ne ina warware maganganunki, kamar ban fahimci me kike magana akai ba.

Wai kina nufin Yaya Mukhtar mijin Aunty Fareeda aminiyarki shi za ki aura nan da ƙanƙanin lokaci?"

Kafin ta amsa sai da ta ƙara haɗe gabas da yamma ta murtuke fuska don kar su kawo mata wargi, kar ma dai Jiddah ta ji labari. Gara Salma tana nuna jin tsoronta a wasu lokutan.

"Eh! ƙwarai! Mukhtar zan aura, shi ne yazo gidannan jiya da daddare..."

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Me ya shiga cikin hankalinki Aunty? Wannan wane irin mummunar saɓo ne kike ƙoƙarin aikatawa?"

Jiddah ta jefa mata tambayoyin fuskarta na ƙara bayyana matsanancin mamaki da firgici.

Kallon ƙasa da sama ta watsa mata, ta san halin Jiddah sarai, idan bata yi mata na mahaukata ba baza ta ƙyaleta salin-alin ta aikata hidimar gabanta cikin nutsuwa da kwanciyar hankali ba.

"Ubanki ne ya shiga cikin hankalina, Jiddah na ce Babanki ne ya shiga cikin hankalina. Ina ruwanki da rayuwata? Da kike cewa zan aikata saɓo uwar me muka haɗa da Fareedar da ya wuce ƙawance da zaman unguwa ɗaya? Ina haramci a cikin aurena da mijinta? Wallahi akan maganar nan na shirya ja da ko uban wanene, duk wanda yasan bazaiyi fatan alkhairi ba ya rufe min ɗoɗɗoyan bakinshi, idan ba haka ba kuwa za mu hau sama mu faɗo da ko wane ɗan iska. A duniyar nan kakaf ban cire miki hula ba babu wanda ko wacce ta isa haramta min abinda yake halas a gurina..."

"Kiyi haƙuri Aunty, Allah ya sanya alkhairi."

Salma ta faɗi haka cikin sanyin murya, zuciyarta cike da tsoro da mamakin Yayar tasu.

Ita kuwa Jiddah tun da ta hangame baki ta ɗora hannu akai bata sauke ba har Fatima taja musu wani dogon tsaki ta fice daga ɗakin cikin fushi kamar za ta tashi sama.

"Amma dai wallahi ke banza ce Salma. Ina wani alkhairi a lamarin cin amana da har za ki ce mata Allah ya sanya alkhairi..."

"To me kike so in ce Jiddah? kina ganin yadda ta ɗauki zafinnan tsaf za ta iya rufe mu da duka. Kin ji dai ta ce ta shirya ja da uban kowa a duniyar nan. Ba gara da na faɗa mata hakan ta fice ba tare da tashin hankalin ya fi haka ba? Taje can da yawarta, kila rabon fige kazar wahala ke kiranta ga auren mijin Aunty Fareeda."

"Ai Wallahi ƙarya take yi, maganganunta a cika baki da zancen banza na ɗauke su. Inna zan kira yanzunnan in faɗa mata halin da ake ciki, baza mu zuba idanu ta janyo mana zagi da tsinuwa a cikin gari ba."

Jiddah tayi maganganun cikin ɓacin rai tare da janyo wayarta, ta buɗe wayar kenan buf Fatima ta dawo cikin ɗakin kamar an jefo ta.

Kai tsaye gurin Jiddah ta nufa a gaggauce ta fisge wayar hannunta, ta soke a haɓar zani sannan ta riƙe ƙugu tana kallonsu cikin wani irin fushi da basu taɓa ganin tayi irinshi ba.

"Ashe daman ku ɗin yan iskan yara ne matsiyata ban sani ba nake zaune da ku ina taimaka muku?"

Taja wani ƙaƙƙarfan ƙwafa, ta cigaba da cewa

"To duk maganganun da kuka yi ina laɓe a bakin ƙofa ina saurarenku.

Har da ke Salma da nake miki kallon mutumiyar kirki ashe tsohuwar munafukace ke? To ku jira ni, duk sai na ci ubanku ɗaya bayan ɗaya.

Bari in gama da Inna zan dawo ta kanku don ubanku."

Wayar Salma da yake maƙale a caji ta cire a fusace ta fice da wayoyin a hannunta fuuuuu kamar kububuwa.

*****

Ba ita ta farka ba sai ƙarfe tara da rabi na safiya. Ganin lokaci ya tafi yasa ta bubbuɗe idanunta da mamaki.

A gurguje ta faɗa banɗaki tayi wanka. Wani abu da ya saka ta cikin farin ciki shi ne, ko da ta tsaya gaban madubi tana kallon fuskarta kumburin da idanunta suka yi duk sun saɓe, saura kaɗan.

Taƙaitaccen murmushi tayi, ta ƙara gode ma Allah kwanciyar hankali da nutsuwar da ya saukar mata. Bayan ta shafa mai da powder sai ta bi idanun da kwalli ɗan kaɗan, sauran kumburin sai ya ƙarasa ɓacewa.

Bata tsaya ɓata lokaci gurin daidaita girarta ba, ɗan tacewa kawai tayi sama sama, sai suka yi wani irin gazar-gazar, su basu kwanta ba basu miƙe a hargitse ba. Ta goga man baki kaɗan a laɓɓanta.

Wata doguwar rigar roba roba mai sauƙin kuɗi da ta siya a gurin maƙwafciyarsu ta saka a jikinta, rigar ta bi jikinta ta lafe, tudun mazaunanta suka taso sosai ta bayan rigar.

Hular rigar ta saka a kanta, shi bai rufe gashinta da bata cika son kitsa shi gaba ɗaya kuma bai bar suman da yawa a waje ba, sai tayi wani irin sanyin kyau sosai, irin yadda rigar ya zauna a jikinta idan ba sani aka yi ba sai a zaci mai bala'in tsada ne.

Kai tsaye kicin ta nufa ba tare da ta kalli ko ƙofar ɗakinsa ba. Dankalin hausa tayi sha'awar soyawa ta sha da lipton, idan shi ma Mukhtar yana ra'ayi za ta aje masa don fita hakki.

Tana da pure man ƙuli mai kyau, wanda idan ta soya dankali da shi ba ƙaramin ɗanɗano yake ƙara yi ba.

Ba tare da ɓata lokaci ba ta ɗebi dankalin iya yadda zai ishe su ta wanke, ta fara ferewa cikin hanzari, tana jin yadda yunwa ke sakaɗarta.

Sai a lokacin ta tuna jiya ko abincin dare bata iya ci ba saboda tashin hankali, ƙasa-ƙasa taja tsaki ta cigaba da aikin da yake gabanta.

A ɓangaren Mukhtar shi ma barci yayi wadatacce, ko da ya dawo sallar asubah kwanciya ya sake yi. Bai farka ba sai ƙarfe goma na safe, tun dare da ya juya ma wayarsa baya sai a lokacin ya waiwayeta.

Kiran da aka rasa ya gani da yawa, amma na Fatima su ne guda goma sha ɗaya. Da sauri yabi bayan kiran yana jin damuwa da rashin ɗaukar wayoyinta da baiyi ba, tun asubah ya kamata ya kira yaji yadda ta tashi a matsayinta na wacce take niyyar zama iyalinsa nan da lokaci ƙanƙani.

Ya kira sau biyu bata ɗauka ba, sai ya tura mata saƙon ban haƙuri da zafafan kalaman soyayya ya ajiye wayar ya shiga wanka.

A mintuna goma sha biyar ya gama shiryawa cikin ƙananun kaya. Ya ɗauki wayarsa ya nufi falo, yanzu kam ya shirya tsaf don tarbar duk wani tashin hankali daga matar gidan, shi yasa ko fuskarsa kadaran kadahan take.

Ba ta a falo, amma ya jiyo motsinta a kicin ga kuma ƙamshin man gyaɗa da yake tashi alamun tana soya wani abu.

Ba tare da fargabar komai ba ya nufi kicin ɗin. Ya ɗauki tsawon daƙiƙu ashirin yana ƙare ma bayanta kallo, ya haɗiyi wani kakkauran miyau, ya ɗaure fuska yayi sallama a daƙile.

"Ameen wa'alaikas salaam."

Ta amsa da wani irin sanyi da yanga a muryarta.

A nutse ta juyo tana kallonshi, fuskarta a sake yake sosai, idan ba gizo idanunsa ke masa ba sai yaga kamar ma wani kwantaccen murmushi take yi.

Duk ƙwaƙwarsa ya kasa gano ɓacin rai ko kaɗan a fuskarta, ga wani irin annuri da kwarjini da fuskarta ke fitarwa.

"Ranka ya daɗe, barka da asubah! Ina kwanah"

Ta katse mishi tunani da gaisuwa, har tana wani ɗan duƙawa kaɗan cikin salo alamun girmamawa.

"Lafiya ƙalau."

Ya amsa daƙyar bayan yayi ƙumajin daidaita kansa daga mayataccen kallon da yake bin ta da shi, zuciyarsa cike da maɗaukakin mamakinta, sai kallon yadda tayi wani irin kwalliya na ɗaukar hankali kamar wacce ba ta a cikin wata damuwa.

Bai dawo hayyacinsa ba ta sake shayar da shi wani mamakin ta hanyar cewa.

"Ranka ya daɗe, ina neman afuwa. Yau ɗin wani daɗin barci ne ya kwashe ni har na makara, minti biyar za ka bani kacal in kammala haɗa maka abin karyawa. Afuwa plsssssss"

Ta ja kalmar "Pls" ɗin da wani irin salon shagwaɓa da ya kusan kifar da shi a ƙasa yayi saurin dafe ƙofar kicin ɗin.

Kamar bata ga abinda ya faru ba, ta dallare fuskarsa da kyakkyawan murmushinta, ta ƙara tura tsukakken bakinta gaba tana mommotsa shi kamar za tayi sumba, ta ƙale mishi idanu ɗaya, ta ƙarke da sakar mishi Fari da idanun da ya saka shi ficewa da baya da baya daga cikin kicin ɗin baki hangame yana kallonta.

Tunani ɗaya ne a ransa.

'Ko dai ta zaci wasa yake mata maganar aurenshi da Fatima? lallai kuwa idan haka ne ta yaudari kanta, zai kuma tunasar da ita yanzunnan.'

*_Aminci + Ƙarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*12*_

Yana ɓacewa daga idanunta ta gallawa bayansa harara, taja tsaki ƙasa-ƙasa ta cigaba da aikinta cikin nutsuwa.

Kamar yadda ta buƙata, bata ɗara daga mintuna biyar ɗin da ta nema ba.

Bayan ta shimfiɗa ɗan madaidaicin ledar cin abinci nan gabansa ta shirya mishi komai, kamar yadda ya buƙata.

Ta ɗan sauke ƙwayoyin idanunta ƙasa-ƙasa tana satar kallon gefensa, da wani irin sanyi na kwarkwasa a muryarta wanda ta ƙara akan nata na da ta ce

"Ranka ya daɗe. Da yake ni ina ra'ayin shan lipton ne, ko in kawo maka kayan tea?"

"A'a! wannan ɗin ma ya isa."

Ya amsa yana ta ƙara bin ta da kallon mamaki.

"To ma sha Allah"

Har ta yunƙura za ta tashi daga gurin ya dakatar da ita ta hanyar cewa

"Ina za ki kuma?"

"Da yake ban gama ba, zan koma in ƙarasa suyar ne."

"Ok!"

Har ta fara tafiya ya sake cewa.

"Idan kin ƙarasa ina jiranki, yanzu fa. Don fita zanyi ina gama karyawa."

"Toh!"

Ta amsa a sanyaye.

Ko da ta shiga kicin ɗin kusa da cabinet ta tsaya ta lumshe idanunta, ƙirjinta banda luguden daka babu abinda yake yi.

Tunda ya ce yana jiranta ta tabbata wata maganar zai sake takalo mata.

'Menene irin haka kuma don Allah? Me yasa bazai barta ta ji da abinda yake damunta ba? Wasu mazan dai ba sa son a zauna lafiya.'

Hannayenta ta ɗaga sama ta fara addu'a a fili, idanunta ciccike da hawaye.

"Ya rabbi, ba ni da ƙarfi kai ne mai ƙarfi. Ina roƙonka ka kawo min ɗauki tako wane ɓangare a wannan lamari. Allah ka ƙara min juriya da jarumtar ɓoye duk

ƙunan da zan ji a zuciyata a gaban Mukhtar da Fatima da duk sauran masu burin ganin kasawata."

Ta shafa addu'ar ne tare da saukar wasu ƙananun ƙwallah daga idanunta. Da saurin gaske ta share ƙwallan, a hankali cikin dabara yadda bazai ɓata kwalliyarta ba.

Duk yadda tayi burin yi ma dankalinnan cin marmari haka kawai ta ji ya fice daga ranta. Cikinta ya cunkushe gaba ɗaya, tana gama kwashe kaskon ƙarshe ta kashe gas ɗin, ta rufe komai ta nufi falo gurinsa. A zuciyarta babu abinda take maimaitawa sai

"Hasbunallahu wani'imal wakeel."

"Ina naki abin karin?"

Ya tambayeta idanunsa na kanta, kamar mai karantar halin da take ciki.

Kamar ba ita ce ta gama ƙwallah a kicin ba wani lallausan murmushi ne ya suɓuce a fuskarta. Gefenshi ta nemi guri ta zauna, ta buɗe kulan dankalin ta ƙara masa kaɗan a cikin faranti don ganin ya kusa cinye wanda yake cikin farantin.

"Da yake na ji ka ce kana jira na ne, ka ga bai kamata in ɓata maka lokaci sosai ba Ranka ya daɗe. Akwai abinda kake buƙata in kawo ko inyi maka ne?"

"A'a! Magana ce nake so muyi."

'Ya hayyu ya ƙayyumu birahmatika astageethu, aslihlee sha'anee kullah, walaa takilnee ila nafsee ɗarfata ain."

Tayi saurin karanta wannan addu'ar a zuciya, a fili kuma sai ta gyara zama haɗe da cewa

"Ina jin ka Ranka ya daɗe."

"Ummmm dangane da maganar da muka yi jiya da yamma ne kafin in fita."

"Wacce kenan Oga? Jiya da yamma bayan dawowarka idan ba na manta ba munyi maganganu masu yawa. Ɗan tunamin don Allah..."

Ta ƙarasa roƙon da murmushi haɗe da kashe mishi ido ɗaya.

"Maganar auren da na ce miki zan ƙara..."

"Auhooo..! Wai maganar aurenka ? wanda ka ce min za ka auri Fatima da kake kira mai siffar munafukai a baya? To ya ake ciki? an saka lokacin bikin ne ko kuma ka bugo Invitation card ne kake son bani in fara raba ma mutane na?"

Baki buɗe yake kallonta, wani mugun mamaki ke neman kifar da shi a zaune. Ya ƙifta ido ya buɗe ya sake ƙiftawa, sai kuma ya ɗaure fuska tamau, kamar wanda bai taɓa sanin me ake kira da wata aba dariya ba.

Ita dai har lokacin tana kallonsa, kuma wani abin mamaki zuciyarta a tsaye take, da gaske fa babu wani tsoro a tare da ita. Daman Fareedar jaruma ce tun da can, in dai ɓangaren faɗan gaskiya ne duk yɑn'uwanta sun santa kan wannan halayar. Duk girman mutum ba ta shayin kallon ƙwayar idanunsa ta faɗa masa gaskiya komai ɗacinta, wasu tana burge su a wannan halin nata, wasu kam cewa suke bata iya magana ba.

"Miye haka kike ƙoƙarin faɗe? wannan wane irin banzar magana ce mare daɗin sauraro?"

"Au! Au!! To Allah ya baka haƙuri Habeebeen zuciyar Fareeda."

Ta ƙara marairaice fuska da muryarta ta cigaba da cewa

"Ban ɗauka don na faɗi abinda kai da bakinka kake yawan faɗe a baya zai ɓata maka rai ba. A yafe min don mai sama."

"Ai sai kiyi Fareeda. Na ce ai sai kiyi. Ki sani wallahi tallahi duk wani kushe da hassada da za kiyi akan wannan lamari babu abinda zai hana ni auren Fatima sai wani ikon Allah..."

"To ni dan Allah me nace? Tun jiya ba na ce Allah ya tabbatar da alkhairi ba? To yanzu ma bari in sake cewa, Allah yasa alkhairi Ranka ya daɗe."

Ta ƙarasa cikin wani irin dariya da tun ɗazu yake taso mata tana dannewa.

Yadda yake ta wani huci yana hura hanci cikin fushi don an taɓa abin son shi shi ne abinda yake ta bata dariya.

Kallonta kawai yake yi ta tasa shi gaba tana dariyar raini, zuciyarsa sai ƙara tafarfasa yake yi. Ga abin duka babu sanda, tunanin abinda zai faɗa ya ƙona mata zuciya a take yake yi amma ya rasa. Sai kawai ya ce

"Da siffar munafuncin Fatima da duk wasu munanan halaye da take da su a soyayyar da muka gudanar na kwanaki goma sha biyar ta shayar da ni farin cikin da ya goge duk wani baƙin ciki da kika daɗe kina ƙunsa min. Babu wasu munanan halayya nata da matsananciyar soyayyar da take min bazai sa ta canza su ba. Ta yi min alƙawarin tsundumani a kogin farin cikin da ɗan ƙaramin saninki bai taɓa sa kin kaini ko da kusa da gurin ba, sai canza halayenta da basu da kyau ne zai gagare ni...?"

"Allah ko Mukhtar?"

Ta tambayeshi da wani irin yanayi da a fili yake nuna tana kokawa da ɓacin ranta ne.

Duk da har lokacin murmushin fuskarta bai ɓace gaba ɗaya ba, idanunta ciccike suke da ƙwallah. Abinda yake cutarta kenan a rayuwarta saurin kuka, ko tana da gaskiya bata cika jurar daɗewa a cacan baki ba.

Cikin dauriya da ƙarfin gwuiwa ta cigaba da magana cikin sanyin murya,

"Me kake ci na baka na zuba Mukhtar? Ba dai Fatima bace? Ga ka ga ta nan! Allah ya baku sa'ar cikar burinku duk ku biyun. Amma abinda zai faru a rayuwar auren, Allah ne kawai masanin gaibu. Zan iya tafiya?"

"A'a! Ban gama da ke ba."

Ƙarar shigowar saƙo cikin wayarsa yasa shi mayar da hankali kanta, yana buɗe saƙon ya fara sakin wani fitinannen murmushi, daga Fatima ne.

Zafafan kalamai ta turo masa masu matuƙar zaƙi da garɗi a zuciyar irinsa da yake tsaka da shauƙin son ta.

Tana kallonshi, tana kallon yanayinshi, nan take zuciyarta ta kitsa mata daga gurin wacce saƙon ya fito. Kasancewar hankalinsa ya koma kan waya gaba ɗaya sai kawai ta ba hawayen idanunta damar kwaranyowa, da bala'in saurin gaske da zafin nama ta sharce hawayen tun kafin ya gani, bayan sharewar sai ta lumshe idanunta, ta jingina bayanta sosai da kujera ta kishingiɗa.

A zuciyarta take ta jan

'La'ilaha illa anta subhanaka innee kuntu minaz-zalimeen.'

Domin ta sha jin ana cewa tana maganance baƙin cikin azzalumai.

A ganinta tabbas Mukhtar da Fatima sun zalunceta, zalunci mai girma. Ba ta da wanda zau mata sakayya sai Allah da ya halicceta kuma ya haliccesu.

"Yauwa ina jin ki, me kike cewa?"

Ya tambayeta da rashin damuwa a fuskarsa, bayan ya dawo da hankalinshi kanta.

A hankali ta buɗe idanunta, ta ɗan muskuta ta ƙara gyara zamanta.

"Ban ce komai ba fa, kai nake jira kayi min izinin tafiya. Har yanzu ban samu sararin karya kumallo ba."

"Zancen aurena da Fatima dai shi zan ƙara jaddada miki. Ba fashi, ba gudu ba ja da baya. Kuma ni da ita duk a shirye muke, a yadda muka tsara ma bikin bazai wuce nan da sati uku ba..."

"Sati uku dai?"

Ta tambaye shi da ƙarin mamakinsa sosai a fuskarta.

"Kwarai kuwa. Me ya faru da sati ukun?"

Yayi mata tambayar yana wani zazzaro mata idanu kamar zai taso mata.

Mele baki tayi gefe ɗaya.

"Babu abinda ya faru, mamaki dai nake yi. Yadda alamu suka nuna kai da ita kuna kan gwuiwa ai na zaci bayan sallar isha'in yau za'a ɗaura auren."

"Ɗaura auren dare kamar na wasu tsofaffi?"

"Yo menene banbanci? Shekarunka talatin da takwas cikin da tara. Fatima duk yadda take ɓoyewa talatin da takwas take ciki. Ta taɓa aure, haihuwarta huɗu rigis a wani gida, na biyar ɗin ma ta haife shi wata takwas yazo babu rai. To me ya banbantaku da tsofaffi?"

Irin yadda take kishingiɗe a hakince take zaƙulo maganganun za'a iya rantsewa da Allah zuciyarta wasai take. Amma fa a haƙiƙanin gaskiya wutar kishi da mamakin lamarin ne ke ci da wuta bal! bal!! bal!!! a cikin zuciyar.

A hargitse da wani irin masifa ya miƙe tsaye yana faɗin

"Fareeda ku fita daga ido na in rufe, duk bala'in da kike ji ina jin..."

"Allah ya raba mu da bala'i. Allah ya baka haƙuri Angon Fatima. Ni kaga tafiyata, idan da sauran maganar da za muyi don Allah don Annabi kayi min alfarma zuwa anjima. Yanzu kam yunwa nake ji ba kaɗan ba, kayi min uzuri in ci abinci kar in kamu da cutar Ulcer yan'uwana su shiga uku!"

Ko kafin yayi yunƙurin cewa komai har ta wuce daga gurin, kicin ta nufa da sassarfa, tana shiga ta danna ƙofar ta rufe ta murza key ta ciki.

Jikin ƙofar ta jingina bayanta, ta haɗe hannuwa a ƙirji, ta lumshe idanunta wasu zafafan hawaye suka gangaro mata.

Tana wannan kukan ta ji alamun ficewarsa bayan ya buga mata ƙofar falo da ƙarfi saboda ɓacin rai da tafarfasar zuciyar da maganganunta suka haifar masa.

Fuskarta kaca-kaca da hawaye ta buɗe ƙwayoyin idanunta ta kalli sama

"Ya Allah... kana ji kana gani..."

Abinda ta iya cewa kenan ta kifa kanta saman cabinet ta cigaba da rusa kuka, sai jan numfashi take yi sama-sama kamar wacce za ta shiɗe.

'Ashe haka zafin kishi yake? irin yanayin da take ji a zuciyarta yanayi ne da bazai taɓa faɗuwa ko fasaltuwa ba. Lallai duk wacce bata taɓa shiga cikin yanayin ba ta gode Allah, kada ma tayi fatan shiga, ko kuma ta dinga ganin baiken matan da suke hauka a irin wannan lokacin. Wani irin azabtaccen yanayi ne da matan da suka san shi ne kawai za su iya ƙaraswa. Kamar naƙuda ce, wacce ta taɓa yi ne kawai za ta san yadda azaba da raɗaɗin yake.

Tuwo labarin wuta yake ji tsire shi yaga zahiri.'

******

Tun da ta gama sauraren bayanin da ke tafe da babbar ɗiyar tata ta kife kai a hannun kujera tana rusa kuka. Kamar ba babbar mace ba.

Duk yadda Fatima take cikin matsanancin ɗoki da zakwaɗin lamarin, da ganin babu uban da ya isa hanata aikata abinda Allah ya halasta mata sai da jikinta ya ɗanyi sanyi kaɗan, kukan da Innan take yi kuka ne da rabon da taga tayi irinsa tun rasuwar mahaifinsu.

"Inna, Don Allah don Annabi kiyi haƙuri. Ni fa ban ce miki zan auri mijin Fareeda don in ƙuntata mata ko..."

"Ke dallah rufe min baki banza kawai sakarya."

Inna ta katse ta cikin kuka. Ta ɗago idanunta da suka yi jaaa saboda kukan da ta ɗauki lokaci tana yi, ta sauke su akan Fatima.

Cikin ɓacin rai da matsanancin tashin hankali ta ce

"Idan kin manta bari in tuna miki. A sadda muka zo unguwarnan kuna ƙanana ke da ƙannenki amma na tabbata kina da wayan da baza ki manta lokacin ba.

Mahaifinki ba shi da komai sai rufin asiri kawai na ubangiji. Marigayiya Hajiya Hajara Mahaifiyar Fareeda da ta kasance mai hannun kyauta ita ce ta sakawa kanta aiko mana da abincin rana kullu yaumin ba tare da ina mata wani aiki ba, watarana ma har da abincin dare.

Ita mahaifiyar Fareeda ita ce ta nuna ma Marigayi mahaifin Fareeda irin matsanancin halin da muke ciki, hakan yasa ya dinga taimaka mana akai akai.

Fareeda ita tayi ma Mahaifinta magana ya saka ku a makaranta mai tsada boko da islamiya wanda su ƴayƴansa suke zuwa saboda ƙaunar da take miki.

Hatta da ɗinkin sallah a gidansu Fareeda iyayenta suke haɗawa da ku suyi saboda sun san matsanancin halin da muke ciki.

Wannan ɗakin da muke rayuwa a ciki cikin kwanciyar hankali Mahaifin Fareeda shi ya fitar da zakkah ya damƙa mahaifinki, a cikin kuɗinne aka yi cinikin ɗakinnan ya

biya, sauran kuɗaɗen ya fara sayar da kayan miya a bakin layi har ƙarshen rayuwarsa.

Haba Batula. Yanzu waɗanda suka yi mana wannan alkhairin ne kike ƙoƙarin sakawa ta hanyar aure mijin yʼarsu? Karki manta ana barin halas don kunya..."

"Inna... Inna don Allah duk me ya kawo waɗannan maganganun? Taimakon da suka yi mana don Allah sukai ba don wani abu ba. Kuma auren mijin Fareeda ni fa ba da wani mugun nufi zanyi ba, to da ya auro mata wacce bata sani ba ba gara ni da ta sani mu taru mu zauna lafiya mu rufa ma juna asiri ba. In da za ki kalli wannan lamarin da fuska mai kyau babu abinda zai haifar sai ƙara danƙon zumunci..."

"Zumunci dai Batula? Zumunci? A lamarin kishi har da wani zumunci ne? to wallahi ki sani, wannan al'amarin babu hannuna. Na barranta da abinda kike so a wannan karon. Duk zafin da kika ɗeɓo ke za ki ƙona bakinki, kar ki kuskura ki nufo ni da wata magana ta tsiya ko ta arziki.

Ki tura shi gurin dangin mahaifinki, idan batun kawo kaya ya zo ki tura su gidan ƙanwata Rabi. Allah ya baki sa'a kan abinda kika sa gaba."

Duk yadda Fatima ta so samun daidaito da mahaifiyarta a wannan rana abin dai ya gagara. Abinda ta guda shi ne ya faru, tayi gudun ƙannenta su fara zuwa da maganar gidansu ne don kar Innan ta ƙi fahimtarta.

Sai ga shi da iya maganarta da komai Innan ta ƙi saurarenta. Sun rabu dutse da hannun riga, ta fice a gidan tana gungunin aure ne dai kamar ta yi ta gama.

Sunnar ma'aiki SAW za ta raya, duk ma mai hangen mummunan abu zai faru in sha Allah ita dai alkhairi za ta gani. Aure ta ce za suyi ba dadiro ba.

A wannan rana, mahaifiyar Fatima Inna Laure kwana tayi tana kuka. Tunanin halaccin da iyayen Fareeda da ita kanta Fareedar suka yi musu ne kwance malala a ranta.

Yanzu da iyayen Fareeda za su dawo duniya da wane ido za ta kalle su? me za ta ce musu?

*_Aminci + Kʼarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daƌe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuƌin tsarin datar da kike so a wannan acc ƌin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*13*_

"Kin gansu nan?"

Ta buɗe jakarta ta ciro wasu robobin magunguna guda uku, ta ɗauko wasu kwalaben turare yɗan ƙanana guda biyu ta miƙa ma Fareeda.

Ita kuma ta karɓa jikinta a sanyaye, zuciyarta cike da mamakin yadda tun bayan fasuwar zancen ƙarin auren da mijinta zaiyi ake ta nufo ta da irin waɗannan abubuwa.

Ƙuri tayi tana ƙare ma yɗan ƙananan robobi da kwalaben turaren kallo. Roba ɗaya a cikin garin maganin sak ararraɓi, amma dai bata ce ba, sai ta mayar da hankalinta kan Ramlah don jin ƙarin bayani.

"Duka biyar ɗin ki bada dubu arba'in. Wallahi Dubu hamsin ne ma amma saboda hidindimun da suke gabanki ki bayar da arba'in, sai in cika miki dubu goma. Kin wuce komai a gurina Fareeda, bazan manta lokacin da muke secondry irin kyaututtukan da kike yi mana mu ƙawayenki ba, don na cika miki kuɗin magani banyi miki komai ba."

Da saurin gaske Fareeda ta miƙa ma Ramlah magungunan tana cewa

"Kin ganni Ramlah? Wallahi tallahi ba ni da kuɗi. Ni a yanzu da kike ganina ko dubu biyar ba na magani. Na gode da ƙaunar da kika nuna min, ki mayar ma da Hajiyar maganinta kema ki riƙe dubu goman ki. Allah yabar zumunci."

Baki buɗe Ramlah take kallonta. Ta ɗan muskuta, zuciyarta cike da addu'ar Allah yasa kar Fareeda taƙi siyan maganin.

Daga fara harkar karɓo ma Fatima magani ba ƙananun kuɗaɗe take samu a ɓangarenta ba. Tunanin cin riba biyu a duka ɓangarorin biyu tunda duk ƙawayenta ne yasa ta kawo ma Fareeda, idan Allah yasa ta siya dubu sha biyar ne ribarta a ciki.

"Amma Fareeda kin fahimci maganganun da na gama karanta miki a matsayin sharar fage kuwa?

Wallahi kin ji na rantse da girman Allah babban burin Fatima idan aka yi aurennan ki wulaƙanta a gidannan. Daga ƙarshe baƙin ciki da takaicin yadda za ki ga tana juya mijinki ya zama ajalinki.

Magunguna take amfani da su kala-kala, wanda suka dace da waɗanda basu dace ba, ba ta jin ƙyashin kashe ko dubu nawa aka faɗa mata kuɗin magani matuƙar aka tabbatar mata da ingancinsa..."

"Uhmmm! Taje tai tayi wallahi, Ramlah ƙyaleta taje tai tayi. Ni Allah ya sani tun farkon tarayyarmu ba Fatima kaɗai ba, da zuciya ɗaya nake zaune da kowa. Ko da suka ƙullah za suyi aure ni ba na mata fatan ta wulaƙanta, Aniyar kowa ta bi shi tsakaninmu."

Duk yadda Ramlah taso juyar da tunaninta don ta sayi maganinnan ko bashi ne bayan biki ta biya ƙin karɓa tayi. A ƙarshe dai haka suka rabu dutse a hannun riga, zuciyar Ramlah cike da takaicin buƙulun da Fareeda tayi mata, ta fice a gidan tana jan tsaki.

Bayan fitarta Fareeda ta daƈe zaune a gurin, hannayenta biyu tallabe da kunci, damuwar zuciyarta na ƙara ninikuwa.

Daga fara maganar aurennan zuwa yanzu matan da suka zo takanas ta kano har cikin gidanta da kuma waɗanda suka kira ta a waya da maganganu na ɗaga hankali baza ta iya ƙayyade yawansu ba.

Kaso biyu da rabi cikin uku na masu yi mata jaje da bata shawarwari ce mata suke yi

"Fareeda sai kin tashi tsaye, wallahi idan baki tashi tsaye ba kina ji kina gani gidan mijinki zai gagareki."

To don Allah ita ya suke so tayi da rayuwarta? A matsayinta na marainiya babu uwa ba uba ta tashi tsaye taje ina? Ita ba kuɗi take da shi ba, kuma ko tana da kuɗin tana roƙon kar Allah ya nuna mata ranar da za taje gurin wani ko wata don neman taimako akan Mijinta.

Tana neman taimako ne a gurin Allah kaɗai, kuma tana da tabbacin shi zai kareta daga duk wani sharri ko bita da ƙulli da zai sameta, ba ma akan al'amarin auren Mukhtar ba, aduk wasu lamura na rayuwarta a duniya.

Idan ta ce maganar da Ramlah ta faɗa mata kan Fatima bai tsaya a zuciyarta ba tayi ƙarya. Amma babu komai, ita dai tana ta cigaba da addu'a har a gama rugu-rugun bikinnan kar Allah yasa imaninta ya raunana kan ɗa namiji.

Ɗa namijin da bashi da tabbas, tun zamanin kakanninmu da iyayenmu har yau maza sun kasa mallakuwa. Ko a tarihi da labarun hikaya bata taɓa jin wata shahararriyar mace da ta samu nasarar mallake ɗa namiji ya mallaku mata har abada ba.

To me zai kaita ta kashe ɣan kuɗaɗenta sannan ta ɓata lokacinta a banza? Ba dai Mukhtar bane? Tana ta ƙara dagewa da Addu'a Allah ya cire mata damuwa da al'amarinsa a ranta.

Za tayi masa biyayya, za ta bi umarninsa kamar yadda addini ya umarta. Amma idan ya aje ta gefe Wallahi ita ma za ta aje shi ne, idan ya zaɓi Fatima ya ce ita Fareeda zai wulaƙanta za ta rabu da shi, rabuwa ta har abada.

Ta rasa uwa da uba a duniya tayi haƙuri ballantana wani ɗa namiji? Miji goma ba uba goma bane, za ta cigaba da zama ne kawai idan ya riƙe ta da darajarta. Allah bai wulaƙantata ba babu wani mahaluki da ya isa ya wulaƙanta ta.

Fatima kuwa in dai Mukhtar ne ga ta ga shi nan, Allah ya basu sa'a.

*****

"Mukhtar wai don Allah da gaske kake wannan maganar?"

Abokinsa Ibrahim ya tambayeshi, da fuskarsa mai ɗauke da matsananciyar mamaki.

"Au! wai kai baka yarda ba? Wallahi da gaske nake yi."

Ya rantse don ƙara tabbatar masa da gaskiyar maganar ƙarin aurensa, ya cigaba da cewa

"Yanzu haka ma na kai komai da ake buƙata, saura kwana takwas ɗaurin aure. Kaga tunda bazawara ce babu wani amfanin ɓata lokaci..."

"Amma gaskiya ka bani mamaki, anya kuwa wannan busasshiyar haka ta barka? Kai da kake da mace kamar Fareeda wani kuskure ko rashin rabo ne zai kai ka ga auro Fatima? Matar da a fuska kawai za ka gane duk bula ce, idan bata girma maka ba ba na jin kai za ka girme mata.

Ni a ture ma zancen Fatima Aminiyar Fareeda ce, tunda aurenku ba haramun bane duk mai hankali bazai tsaya ja'inja ba.

Amma don Allah me ya shiga cikin hankalinka? Kai da na sanka mutum mai bala'in tsantsenin bazawara? A cikin ƙungiyar abokanmu kowa ya sanka kan wannan aƙidar ta cewa baza ka iya mu'amala da wacce wani namijin ya rigaka mu'amala da ita ba, ko da kuwa sakin wawa ce.

Sai ga shi ba ma sakin wawa za ka kwaso ba wacce ta haife yaye rututu, ina wani abin sha'awa ko burgewa a tattare da ita don Allah?

Ko ka manta falsafarka da kake cewa duk wanda zai ƙara aure ya tabbatar wacce zai auro ta fi matarsa ta gida da abu uku.

Tafi ta kyau

Tafi ta asali

Tafi ta ƙuruciya.

A cikin abu ukunnan wannene Fatima ta fi Fareeda?

Ka manta..."

"Ka ga don Allah saurara Ibrahim, tunano tsofaffin maganganun da nake yi a baya tun kafin in waye da rayuwar duniya ya isa haka."

Ya katse abokin fuskarsa na bayyana matsanancin ɓacin rai. Cikin zafin zuciya ya cigaba da cewa

"A ɓangaren zaɓin abokiyar rayuwa ni nake da yancin yin haka ba wani ba. Kuma duk waɗannan maganganun da kake yi a baya ne na furta su, a yanzu ina kan wani mataki ne na nemawa kaina mafita da hanyar ɓullewa cikin salama ba tare da baƙin ciki ya kashe ni tun lokacina baiyi ba.

Fatima dai ita ce zaɓina, ita nayi ra'ayin aure a matsayin mata ta biyu. Idan kuma akwai wanda yake da iko da rayuwata sai ya canza min ko kuma a hana ni ƙara aure gaba ɗaya."

Daga haka bai sake cewa komai ba ya shige ɗaya daga cikin ɗakuna uku da ke cikin ginin yana sake duba irin gyaran da ma'aikan sukai masa.

Lokaci bayan lokaci shi kaɗai yake jan tsaki. Ya rasa dalilin da yasa duk wanda ya ji labarin zai ƙara aure da kuma wacce zai aura sai ayi ta kushe lamarin, bakin mutane bai taɓa furta alkhairi kan lamarin.

Da yawan mutane nuna masa suke lallai ya tafka kuskure a gurin zaɓinsa. To ina ruwan jama'a da ra'ayinsa?

A wannan lamari shi ne mai ruwa da tsaki, kuma ga wacce yake ga tayi daidai da irin ra'ayinsa. Me yasa mutane baza suyi koyi da Hadithin nan da yake cewa a faɗi alkhairi ko ayi shiru ba?

Bai san Ibrahim ya fice daga gidan ba sai da ya fito daga cikin ɗakin. Ko da ya leƙa ƙofar gida bai tarar da motarsa a gurin ba.

Ko a jikinsa ya sake jan tsaki tare da komawa cikin gida bayan ya janyo ƙofar apartment ɗin da aka gama gyara ya kulle. Gyaran yayi kyau sosai da sosai, angama komai.

Sai dai duk tattalin arzikinsa ya kusa shigewa a wannan gyaran, maƙudan kuɗaɗe ya saki sosai aka gyara gurin don kawai ya faranta zuciyar Fatima.

Tunda ta bashi tabbacin kayan gado da kujeru masu bala'in tsada za ta siya ta zuba a ɓangarenta, shi yasa yayi gyaran da baza ta taɓa ji a ranta tayi asarar kashe kuɗinta ba.

Da sallama a bakinsa ya shiga ɗakin Fareeda.

A hankali ta ɗaga kanta daga kan wayar da take dannawa ta kalle shi tana amsa sallamarsa.

Cikin ɗakin ya shigo, ya nemi guri kan katifarta ya zauna, idanunshi a kanta. Cikin kwanaki goma sha huɗu da ɓullar maganar auren ta yi wani sanyi gaba ɗaya kamar ba ita ba, sam ba ta da karsashi.

Har wata yʻar ƙwarya-ƙwaryar rama tayi a fuska, hancinta ya ƙara tsawo. Amma fa ko ya ƙi Allah ya san tana cikin nutsuwarta.

Babu abinda ta fasa masa na dangane da hidimar gidan, sai dai gaba ɗaya ta janye jikinta daga gare shi. Kuma babu wani ɓacin rai a fuskarta balle ya ce haukar kishi ke damunta.

Jingine shi tayi a gefe ɗaya, magana idan ba dole ba bata cika son yana shiga tsakaninsu ba, ko ɗakinsa ta daina zuwa, shi kuma ko sau ɗaya bai taɓa yi mata ƙorafi kan haka ba.

Ya zuba mata idanu ne yaga iya gudun ruwanta. Aure ne dai, bazai fasa ba.

"Biki saura kwana takwas"

Ya karya shirun da ke tsakaninsu da faɗin haka.

"Allah yasa muna da rabon gani."

Tayi maganar cikin rashin damuwa.

Wayar hannunta ta ajiye a gefenta, ta kalle shi cikin idanu, sai da taja addu'ar ya hayyu ya ƙayyumu kafin tayi ƙarfin halin cewa

"Ina neman alfarmar don Allah ka barni in koma wancan apartment ɗin da aka gama gyarawa..."

"Amma dai wasa kike ko?"

Ya katse ta da tambayar, yana aika mata da wani irin kallo mai kama da na lallai ba ki da hankali.

"Wasa dai? Uhmmm! Me zaisa inyi maka wasa a daidai wannan gaɓar? Da gaske nake yi. Idan ka bani dama zan koma wancan apartment ɗin in bar ma amarya wannan, ya ishe ta, tunda ba ta da yaya.

Idan baka manta ba wancan part ɗin ɗakuna uku ne, nan ɗin kuma biyu ne. Kuma wancan shi ne a farkon gida, nan kuma a baya.

A matsayina ta uwargidanka kuma uwar yayanka can ɗin ne ya dace da ni ba Amarya ba..."

"Fareeda. In dai ba tashin hankali kike nema da ni a tsakar ranar nan ba ki bar wannan maganar. Nan ɗin dai shi ne naki, can na gyara da sunan Fatee ne, ita za ta shiga ciki. Idan kina so zan iya sakawa ayi miki fentin nan ɗin, shi ma ya koma kamar sabo.

Amma can na Amarya ne, ita kanta ta sani, har na faɗa mata yanayin ginin domin siyo labulayen da zai isa. Ki bar ma wannan maganar."

Bai sake bata damar cewa komai ba ya fice daga ɗakin.

Ta bi bayanshi da kallo, zuciyarta na wani irin tafarfasa, a hankali ta lumshe idanunta tana maimaita

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Lahaula walaa ƙuwwata illah billah"

Su tayi ta maimaitawa tana ji ɓacin ranta na raguwa da kaɗan kaɗan, sai ta zame ta jingina da jikin gado, ba'a ɗauki lokaci sosai ba nannauyan barci ya kwasheta.

*****

"Hmmm! Fatima kenan, sai muka na samu labari a bakin Ummee wai za kiyi aure."

Wani mugun kallo ta juya ta aika ma Ummee, wacce duk cikin yaran nata ita ce mai bala'in surutu kamar aku.

Daƙyar ta iya ƙaƙalo dariyar yaƙe ta mannawa fuskarta, ta kalli Yar mijin nata a ɗarare, da alamun rashin gaskiya ta fara kalaman kare kanta.

"Kiyi haƙuri Yaya, wallahi daman ina shirin zuwa in faɗa miki da kaina... kawai dai..."

"A'a! riƙe kawai dai ɗinki. Ina fatan baki manta wasiyyar marigayi ba?"

Kiƙƙifta idanu ta fara yi, da alamun ta manta wane wasiyya ne tsohon mijinta uban yayanta ya bar mata? A yanzu Mukhtar da soyayyarsa ce kawai a zahirinta da baɗini, ta daɗe da manta duk wasu abubuwa da suka shuɗe. Gaba da abinda za ta haifar kawai take hange.

"Uhmm! YarAdam butulu. To bari in tuna miki, a gabanki da mu yan'uwan mijinki kafin rasuwarsa ya ce idan za kiyi aure in karɓi yayansa."

Wani ƙatoton ajiyar zuciya ta sauke a fili, wani murmushin farin ciki ya bayyana a fuskarta. Dama ina za ta iya kayan yaya ita da take burin yin ƙara'i na sosai a fannin soyayya.

Ta buɗe baki za ta tambayi a haɗo kayan yʻayʻan ne Yar mijin ta faɗi maganar da yasa ta ɗauke wuta na wucin gadi.

"To kinga tunda aure za kiyi, baza mu taɓa barinki da dukiyar marayun yʻayʻanmu a hannunki ba. Duk abinda kika san na Yaya ne ya siya a gidannan ki tattaro su guri ɗaya, daman already Mujittaba ya gama haɗo duk wasu takardun kadarorin da Yaya ya mallaka.

Za'a raba gado in Allah ya yarda gobe da yamma, za'a fitar miki da tumunin takaba a baki abinki. Su kuma yara za'a cigaba da juya musu dukiyarsu har zuwa sadda za su mallaki hankalin kansu. Na barki lafiya."

Ko bayan ficewarta Fatima ta daɗe zaune a gurin kamar mutum mutumi, ita yanzu idan aka raba gado aka ƙwace kason yʻayʻanta a hannunta ya za tayi da batun kayan ɗaki na garari?

*****

Daf da kiran sallar magrib Mukhtar da Fareeda suka karɓi baƙuncin Hajiyarmu. Da yʻan rakiyarta Shaheed da Sayyid (Yʻan biyun Fareeda), da ƙanwar Mukhtar Zubaida wacce har lokacin bata koma gidan mijinta a lagos ba.

"Ko bakuyi murnar ganinmu bane mu koma?"

Hajiyarmu ta faɗa ganin yadda suka ƙame guri ɗaya fuskokinsu cike da mamakin wannan ziyara ta bazata.

A tare suka ƙarasa da sassarfa suna yi mata sannu da zuwa.

Zubaida da yake akwai shaƙuwa sosai a tsakaninta da Fareeda hannu ta bata suka kashe suna musayar murmushi.

Yʻan biyu da gudu suka ruƙunƙume mahaifiyarsu, kowa na ƙoƙarin bata labari da hausarsu da bai gama fita ba.

Daƙyar Mukhtar ya janye su ita kuma ta fara jelar kawo ma Hajiya ruwa da abinci, cikin mintuna ƙalilan ta haɗa ma Hajiya kayan tarbar baƙi a mutunce.

"Mummyn Twince, akwai wata matsala ce?"

Hajiyarmu ta tambayi Fareeda cikin kulawa, tana kallon yadda ta rame a fuska ba kamar zuwanta gurinta satin da ya wuce ba.

"Wallahi ba komai, me kika gani Hajiya?"

Mukhtar yayi saurin amsawa kamar shi ne Fareeda.

Wani mugun kallo ta watsa mishi, ba shiri ya sunkuyar da kai yana ba ta haƙuri.

"Daman zuwan takanas don kai nayi ta. An gama gyaran wancan ɓangaren ko? To tunda dai ɗakunanshi uku ne nan kuma biyu gobe in Allah ya kaimu Fareeda ki kira yʻan'uwanki su taya ki tattare kaya ki koma can.

Nan ki bar ma Amarya. Nan da kwanaki uku za'a dawo da su Alhassan, a cikin ɗakuna ukun sai a ware musu ɗaya a shirya musu kayayyakinsu. Ka riƙe ɗaki ɗaya, itama ta riƙe ɗaya.

Nan ɗakuna biyu, falo, bayi, kicin sun isa amarya ko yʻar gidan uban wanene. Ina fatan ka ji abinda na ce?"

"Na ji Hajiya. Haka za'ayi in Allah ya yarda."

Ya amsa daƙyar kamar mai ciwo a maƙogwaro.

"Madallah! Zubaida tashi mu tafi..."

"Ayya mana Hajiyarmu wayyo, tunda kika shigo fa ko ruwa baki sha ba, don Allah ki bari ku gama cin abinci sai ku tafi."

Fareeda ta katse ta da yar damuwar rashin zamansu Hajiyar a fuskarta.

Amma fa zuciyarta Rai fes sunan wata zani. Haƙiƙa da gaske ne duk wanda ya dogara ga Allah ya isar masa. Ita ta fara mishi zancen komawarta can ɓangaren, ya ce bazai yiwu ba, sai ga shi cikin sauƙi wacce za ta bashi umarni ba tare da ya musa ba ta zo ta yanke hukunci, kuma ba tare da ta kira Hajiyar ta faɗa mata ga yadda suka yi ba. Allah mai girma.

Mukhtar dai tunda ya duƙar da kanshi ƙasa har su Hajiyarmu suka fice ganin sabon gini bai iya ɗaga kanshi ba. Daga can kuwa sallama suka yi ma Fareeda direban Hajiya yaja suka bar gidan.

*_Aminci + Kwarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*14*_

Ta daɗe tsaye a tsakar gidan bayan tafiyarsu. Tunanin Mukhtar zai iya zargin ita ta kira Hajiyarmu ta faɗa mata wannan maganar yasa duk jikinta yayi sanyi. Lokaci ɗaya ta nemi matsanancin farin cikin da ya lulluɓe zuciyarta ta rasa.

Da taga dai tsayuwar bazai mata ba sai ta fara takawa a hankali zuwa cikin falon, hankalinta a tashe, zuciyarta a ɗugunzume.

Ko da tayi sallama bai amsa mata ba, yana zaune a inda suka barshi, har lokacin kanshi a ƙasa.

Saɗaf saɗaf ta kama hanyar shigewa ɗakinta.

"Fareeda"

Ya kira ta da wani irin murya da bata taɓa jin ya kira ta da irinsa ba.

Lokaci ɗaya idanunta suka cicciko da hawaye, daƙyar ta iya juyowa tana kallonsa, wani dunƙulallen abu da ya tokare mata a maƙoshi yasa ta kasa amsa kiran da bakinta.

Bai damu da rashin amsawar da bata yi ba. Ya miƙe tsaye da wani irin fusata kamar bajimin zaki, ya naɗe hannuwansa a baya. Fuska a ɗaure tamau kamar bai taɓa sanin wata aba wai ita dariya ba.

"Saboda na ce baza ki koma can ɓangaren bane kika haɗa ni da mahaifiyata? Yaushe muka fara haka a tsakaninmu?"

Kafin ta ce komai hawayen idanunta ne suka samu damar gangarowa, saukar hawayen da yayi daidai da ɗan matsawar wannan malolon da ya tokare mata maƙoshi. Ta haɗiyi wani kakkauran miyau, da rawar murya ta fara magana

"Wallahi, Tallahi, na Rantse da girm..."

"Akan ƙarya za ki rantse min?"

Ya katse a zafafe yana matsowa kusa da ita kamar zai kikkifa mata mari.

Da saurin gaske taja da baya, zuciyarta cike da wani irin bala'in tsoronsa. Tunda suka yi aure duk bala'insa bai taɓa dukanta ba, ba ta fatan ya fara daga yau.

"Saurareni ki ji da kyau! Don kin samu goyon bayan Hajiyarmu ta amincewa komawarki wancan ɓangaren ba shi zai sa in fasa auren Fatima ba.

Zan auro Fatima a matsayin matar aure na. Aminyarki ta ƙud da ƙud, wacce duk wani sirrinki na fili da ɓoyo a tafin hannunta yake.

Bari in faɗa miki abinda tun fara neman auren nan nawa ban faɗa miki ba.

Zan auro Fatima ne don kawai inga faɗuwarki Fareeda. Kin daɗe kina guma min takaici, kin daɗe kina ƙunsa min baƙin ciki, kin ɗauki lokaci mai tsawo kina gasa min ɗanyar gyaɗa a hannu ta hanyar ƙona min zuciya kina tsallake umarnina a matakai mabanbanta.

A yanzu lokacina ne. Lokacin da a sannu a hankali zan ɗauki fansar duk irin abubuwan da kika daɗe kina yi min. Kina ji kina gani wacce take zuga ki ta mayar da ke sakarya tana ƙara izaki wajen ƙetare umarnin mijinki.

Za ta shigo gidanki a matsayin matar mijinki. Za ta yi masa biyayya akan abinda ke kika kasa dannar zuciyarki wajen yi ma mijinki biyayya.

Za tayi amfani da sirrukanki da ta sani wajen rugurguza tubalin da kika daɗe kina ginawa..."

"Mukhtar !!! Ta katse shi ta hanyar ƙwalla kiran sunanshi. Mugayen baƙaƙen maganganunsa nema suke su saka zuciyarta mummunar bugawa.

Tunda ya fara maganganun wasu zafafan hawaye suke tsere a fuskarta. Idanunta sun kaɗa sunyi jajur, lokaci ɗaya fuskarta ta damalmale ta canja kamanni.

Ta ja shesshekar kuka mai ƙarfi, ta sanya hannu biyu ta fara goge hawayen fuskarta da sauri, amma sam sun ƙi daina zubowa.

Ita da kanta ta bada tazara tsakaninta da shi, a yanzu da kanta ta fara haɗe tazarar da yake tsakaninta da shi, tana kallonsa da manyan idanunta da suke ta wani irin rawa rawa saboda kuka, sai wani irin numfarfashi take ja mai tafe da shesshekar kuka sauri-sauri. Laɓɓan bakinta sai rawa suke yi, gwanin ban tausayi.

"Fatima ko Mukhtar? Ina sake maimaita maka ga ta ga ka nan! Ni Fareeda Allah ya sani, kuma yana ganin zuciyata, duk ku biyun da zuciya ɗaya nake zaune da ku.

Kuma ko da kuke shirin yin aure dai dai da sakan ɗaya ban taɓa yi muku wani fata saɓanin ta alkhairi ba.

Amma na lura duk ku biyun nema kuke ku hallakani. To ina so ku sani, wannan saƙo ne zan faɗa maka ka isar ma ita gimbiyar taka.

Ni Fareeda in Allah ya yarda ba dai mutum ba sai dai Allah. Alhaji Abdullahi Bawa kafin rasuwarsa hannayen mu yayansa gaba ɗaya ya dafa ya ce yayana, in Allah ya yarda a duniya baza ku taɓa taɓewa ba.

Hajiya Hajara Usman tana gargarar mutuwa da alƙur'ani a hannuna ina karanta mata suratul Yaseen, ta shafo kumatuna da tattausan murmushi a fuskarta ta ce Fareeda, idan anyi duniya don Manzon Allah SAW maƙiya sai dai su bi bayanki. Maƙiya su bi bayan Fareeda, Ya Allah ga Fareeda, ina roƙon maƙiya su bi bayanta.

Ta ƙara da cewa Ubangiji duk wanda zai so ganin bayan Fareeda da yan'uwanta Allah kasa sai dai su suga bayanshi. Ina damƙe da Alƙur'ani a hannun dama, hannuna na hagu na cikin nata na dama. Daga wannan maganar numfashi biyar ta ƙara ja mala'ikan mutuwa ya zare ranta.

Da waɗannan kyawawan addu'o'in na iyaye da hadithi ingantacce ya tabbatar da cewa yardarsu tana tare da yardar Allah kake tunanin za ku iya cin galaba a kaina?"

Sai ta saki wani tattausam murmushi da ya fito tun daga ƙarƙashin zuciyarta. Tana kallon yadda ya tsaya wani sagalau da baki yana kallonta, da wani irin yanayi mai kama da na mamakin ƙarfin halinta. Bata damu ba ta cigaba da cewa

"Mukhtar tunda ba don Allah kake shirin auren Fatima ba, ba baki zanyi maka ba. Amma idan baka tsarkake niyyarka ba ko rantsuwa nayi babu kaffara tafiyar taku babu nisan da za tayi, idan kuma za tayi nisan za tayi ne duk ku biyun kuna cikin fige kazar wahalar da Rabbi zai yanka muku.

Amma har yanzu kana da sauran dama, lokaci bai ƙure maka ba. Ka koma ka gyara Tubalin ginin ƙarin aurenka, idan ka cigaba da tafiya kan wannan TUBALIN tokar lallai... Hmmm! Allah ya kiyaye."

Da sassarfa ta shige ɗaki ta barshi tsaye a gurin.

Wani dogon tsaki yaja, duk waɗannan dogayen maganganun nata sam ko kaɗan basu girgiza zuciyarsa ba. Sai ma wani dogon tsaki yaja zuciyarsa cike da takaicin wannan girman kai da jiji dakai da bala'in bakin na Fareeda.

Ita a rayuwarta babu wani magana da zai saka jikinta yayi sanyi? Duk bala'insa ba ta tsoronsa, wai idan yana magana bakinta ya mutu? A'a ba dai Fareeda ba.

Idan tayi mishi shiru ya san tayi shiru ne kawai ba don tsoro ko bata da abin cewa ba. Yayi ƙwafa mai ƙarfi yana cije gefen baki, ya girgiza kai yana fitar da wani zazzafan huci daga bakinsa.

"Hmmm! Na san maganinki Fareeda. Za kiyi laushi, dolenki za kiyi laushi. A sannu zan dafa ki ki dahu luguf, ba dai mace kike ba? Za ki gane duk zafin kanki dole kiyi laushi ƙarƙashin ɗa namiji."

A fusace ya banke ƙofar ɗakinsa ya faɗa ciki, banɗaki ya nufa kai tsaye ya fara watsa ruwa a gurguje. Dole yaje gurin Fatima a darennan, ya kamata ya sanar da

ita an samu canjin tsari, tun kafin ta lodo kayyakin gadon ɗakuna uku cif gara ya faɗa mata ta sai na ɗakuna biyu ne.

Ba tare da tunanin a banɗaki yake ba a karo na barkatai ya sake jan tsaki. Tun kwanaki sun gama tsarawa ɗakuna ukun ɗaya nashi ne, ɗaya nata, ɗaya kuma na yaryan da za su haifa.

Har kimanin kuɗaɗen gadajen da za ta siya ta sanar da shi, wani abu kuma da ya ƙara faranta mishi rai shi ne, gadon da za ta saka mishi a ɗakinshi ya fi nata da na yaryansu masu zuwa tsada.

"Ina son ki Fateena"

Ya faɗa a fili cikin wani irin shauƙi na soyayya, har yana lumshe idanunsa.

****

"Aban twince saurara don Allah! Ban... fahimce ka ba? Wai kana so ka ce min ginin da ka gama gyara min har aka auna yawan labulai shi ne yanzu Fareeda za ta koma ciki? Ita kuma ta bar min tsohon apartment ɗinta wanda ta gama zama ta mata shi da ƙazantarta na tsawon shekaru?"

Ta katse shi da faɗin haka cikin gatsali da ɓacin rai, bayan tsawon lokacin da ya ɗauka yana kwararo mata bayanin hukuncin da Hajiyarmu ta yanke.

A hankali ya ɗaga idanunsa ya kalleta, yau babu ma wannan ladabin da take masa na zama a ƙasa. Tana zaune akan kujerar da ke fuskantarsa fuskarta a ɗaure tamau.

Sai karkaɗa ƙafafu take yi irin na rainin nan, daman a muryarta ya fahimci babu tausasawa da girmamawa ko misƙala zarratin.

Ranshi ne ya soma ɓaci, da sauri ya danni kansa da cewa

"Yi mata uzuri Mukhtar, dole ranta ya ɓaci. Ta saka ran a matsayinta na amarya ita ce da sabon gini sai kuma yanzu ace ba haka ba? Ya zama dole ka lallaɓata.'

Lumshe idanu yayi yana ƙara tattaro nutsuwa da kwanciyar hankali jikinsa. Ya haɗe yatsun hannayensa guri ɗaya yana ɗan matsawa.

Lallausan murmushi ya sakar mata wanda a kwanakin baya idan yayi mata lumshe idanu take yi alamun matsanancin jin daɗi, sai ta ɗan rufe fuska tana satar kallonsa irin alamun ƙara nutsewa a kogin soyayyar nan.

Wani abin mamaki yau sai yaga ta ƙara ɗaure fuska, ta kawar da kanta gefe ɗaya, ta tura baki gaba, idan ba kunnensa ne ma yaji gari ba sai yake jin kamar ƙaramin tsaki taja masa.

"Tsaki kika yi ne?"

Yayi mata tambayar don share tantama.

"A'a gyara zama nayi."

Ta amsa da shaguɓe.

Bai ɗauka gatse tayi mishi ba. Ya kwantar da murya sosai alamun rarrashi da ban haƙuri.

Abinda bai sani ba a darennan Fatima kan dokin zuciya take. Abinda yayar mijinta ta ƙudurce yi mata wulaƙanci da tozarci ne na ƙarshe da bata taɓa tsammani ba a daidai wannan gaɓar.

Ga shi yan kuɗaɗenta dubu ɗari uku da take ajiyewa daga cikin kuɗin hidimomin yara duk ta gama ɓarnatar da su a wajen gyaran jikinta da siyan magungunan mallaka da maganin mata waɗanda Ramlah take amso mata.

Tsananin baƙin cikin fallasa za tayi aure da Ummee tayi bayan tafiyar Hajiya Babba rufe ɗaki tayi tama yaran tsinannen duka, kamar tana dukan manyan yaya.

Ga ƙannenta biyu duk sun gudu gurin Innarsu, daga ita sai yaran a gida. Babu mai ceto sai Allah da kanta ta gaji ta ƙyalesu bayan ta lallasu ligis, yanzu haka wahala ce tasa su barci.

Bata yi sallar magriba ba balle isha'i. Tana kan wannan tsinin ne yazo gidan.

"Fateena, kiyi haƙuri. Don Allah ki kwantar da hankalinki. Kamar yadda na faɗa miki, wallahi in banda umarnin Hajiyarmu ne wannan babu yanda za'ayi in ba Fareeda sabon gini..."

"Dakata Aban twince, don Allah saurara. Ka daina wani kwana-kwana, ko umarnin Hajiyarku ne ai kaine mai gidan. Kawai ka ce Fareeda ta mallakeka..."

Wani uban tsawa da ya daka mata saboda tsananin tsorata bata san sa'adda ta durgo ƙasa daga kan kujera ba.

A zafafe ya miƙe tsaye, duk wani ɓacin rai da yake dannewa tun daga wanda Fareeda ta kuntuka mishi lokaci ɗaya yayi fitar burtsu. Da yatsa manuniya ya nunata yana magana da wani irin ɓacin rai da bata taɓa sanin zai iya nuna mata ba.

"Ki tsaya iya matsayinki. Kar kiyi kuskuren sakin linzamin bakinki wajen faɗa min maganar banza. Ki sani, dalili ne zai sa in aure ki. Ko yanzu da zan samu tabbacin kwaranyewar wancan dalilin na aurenki wallahi tallahi bazan aure ki ba..."

Tsananin tashin hankali da firgicin kalamansa Fatima bata san sa'adda ta rarrafa ta damƙe ƙafafunsa ba.

"Na tuba, na bi Allah na bi ka. Don girman Allah kayi haƙuri, ka rufa min asiri. Ka yafe min, dan Allah kar ka fasa aure na Hasken zuciyata."

Zuciyar maza ta riga ta motsa. Fincike ƙafafunsa yayi ya fice daga falon a fusace. Bai ɓata lokaci a tsakar gidan ba ya shige motarsa ya fice a fusace.

Ƙaƙƙarfan kuka ta fashe da shi bayan ta ɗora hannu biyu akai, sai kuma a haukace ta janyo wayarta ta fara jera mishi kalaman neman afuwa da ban haƙuri.

Ko kafin ya isa gida ta aika mishi saƙonni ashirin da ɗaya...

Kuna buƙatar ayi muku Cover mai kyau da ɗaukar hankali na littafi ko kayan sana'arku? Ku tuntuɓi wannan lambar domin samun naku akan farashi mai rahusa 09160286737

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*15*_

Tun fara maganar neman aurensa ta rage barcin dare. Alarm ƙarfe huɗu saura kwata ta saka a wayarta, kullum a daidai wannan lokacin take tashi ta ɗauro kyakkyawar alwala.

Ta shimfiɗa dadduma ta fuskanci gabas ta cigaba da kai kukanta ga Rabbil izzah, Alƙawarinsa ne idan ka kusance shi da taku goma zai kusanto bawa da taku ɗari.

Kusanci sosai take nema ga Ubangijinta. Babban buri da kuma fatanta ya zame mata ja gaba aduk al'amarinta.

Saboda bala'in ƙuncin da zuciyarta take ciki a dalilin sa'insar da suka yi da shi ƙarfe uku na dare ta mayar da alarm ɗin, lokacin tana zaune a gefen gado tana karatun Alƙur'ani mai girma don samun sauƙin zuciyarta, tun tara na dare ta fara karatun, har zuwa ƙarfe goma sha ɗaya na dare.

Barcin da ya fara fisgarta yasa ta ajiye Alƙur'anin kan durowar jikin gado, tayi addu'o'i sosai sannan ta kwanta, tana jin yadda nauyin zuciyarta ya ragu sosai. Tabbas a cikin karatun Alƙur'ani mai girma akwai waraka da rage ƙuncin zuciya.

A cikin kwanakin da suka gabata duk addu'o'inta sun fi tafiya ne akan Allah ya tabbatar da alkhairin da ke cikin wannan aure, ya kare su daga sharrin da yake ciki.

Yau sai ta canza yanayin addu'o'inta gaba ɗaya, tana cikin sujadarta na ƙarshe, bayan ta gama jera ma Allah SWT kirari da sunayensa kyawawa tsarkaka. Sai ta cigaba da cewa

"Ya Allah! Gani baiwarka Fareeda, ba ni da kowa ba ni da komai. Ban dogara da kowa ba ban dogara da komai ba sai kai ya Allah. Ina roƙonka don darajar Fiyayyen Halitta SAW ka kare gaba da bayana daga dukkan sharri.

Duk masu nufina da sharri a faɗin duniyar nan mutum, aljan, dabbobi ka kare ni daga sharrinsu.

Ya Allah ga Mijina Mukhtar Abubakar Labaran. Allah kai ka halicce shi, ka san me ke zuciyarsa game da ni matarsa Fareeda Abdullahi Bawa. Ya Allah ina roƙonka, don tsarkin mulkinka, idan yana da wani mugun nufi akaina Allah ka tarwatsa wannan mummunar nufi tasa, ka mayar masa da Aniyarsa.

Ya Hayyu ya ƙayyum! Ga Fatima Ibrahim kabiru, ita ce wacce mijina yake niyyar aurowa ya kawota cikin gidannan a matsayin abokiyar zama ta. Allah ina roƙonka don tsarkin mulkinka, duk wani kissa, kisisina, munafurci, maganin mata, asiri, sharri, zamba cikin aminci, ƙarya, kalaman yaudara da Fatima Ibrahim Kabeeru za tayi amfani da su domin ta ci galaba a kaina, ko akan mijina, ko akan yʻayʻana, ko akan dangin mijina, Allah ina roƙonka kada ka taɓa bata nasara. Duk mugun nufin da ta ƙullo a kaina ka mayar mata da munanan aniyarta kanta ya Allah.

Ba don munanan halayena ba, ba don rashin jin maganata ba, ba don ƙetara umarnin mijina da nayi tayi a baya ba.

Ka shirye ni Ya Allah, Allah ka shiryeni da yʻayʻana da mijina kan hanya madaidaiciya. Ya Allah ka kawar da shaiɗan a cikin rayuwar aurena, ka kawo daidaito da zaman lafiya tsakanina da mijina.

Ya Allah, duk burin da mijina Mukhtar da Fatima suke ƙoƙarin cimmawa a wannan aure don su nuna min iyakata Allah kada ka taɓa cika musu burikansu. Ka mayar musu da aniyarsu kansu."

Haka Fareeda ta shafe awoyi cikin kuka tana kiran cikakken sunan Fatima da cikakken sunan Mukhtar tana kai ƙararsu gaban wanda ya haliccesu ya halicceta.

Bata tsagaita ba sai da tayi sallar asubah, tayi azhkar har zuwa wayewan gari.

A maimakon ta kwanta barci sai ta faɗa banɗaki ta tsallo wanka. Ta cancaɗa kwalliya sosai kamar mai shirin zuwa gidan biki. Babu wanda zai ganta yace tana da damuwa a cikin ranta ko ƙanƙani. Ta ɗauko turarenta mai sauƙin kuɗi ta feffesa a sassan jikinta.

Ta fice daga ɗakinta ta nufi na Mukhtar tana taku ɗaiɗai, kamar wata sarauniya.

Har lokacin yana kwance bai samu sararin tashi ba, sai juyi yake yi kamar mare lafiya, shi kaɗai yake ta jan tsaki ƙasa-ƙasa, zuciyarsa a ƙuntace.

Sallamarta yasa ya ɗaga kansa yana kallonta, bayan ya amsa a ciki-ciki. Lokaci ɗaya ya ƙara ɗaure fuska yana kallonta har ta ƙarasa gefen gadon ta ɗan durƙusa.

"Ranka ya daɗe Mukhtar mijin Fareeda. Barka da asubah, ina fatan ka tashi cikin aminci da kwanciyar hankali?"

Ta gaishe shi a tausashe, fuskarta ɗauke da yalwataccen murmushi.

Kallonta yake ta yi tsawon wasu daƙiƙu, ya san a halayenta dama can ita ba mace mai riƙe abu a zuciya bane. In dai ta samu ta fitar da abinda ke zuciyarta ta hanyar furta ko da mare daɗi ce in sha Allahu zuwa anjima kaɗan za ta saki ranta.

Amma irin acting ɗin da take yi a waɗannan kwanakin tana bashi mamaki ƙwarai da gaske. Ko kusa ta ƙi kaiwa kusa da matakin da yake tunanin za ta kai saboda matsanancin kishin da ya santa da shi, sai ga shi tana ta shayar da shi mamakin wasu sabbin halaye da ko kusa a zamansu na baya bai san tana da su ba.

"Lafiya na tashi. Menene?"

Ya amsa a gundure haɗe da tambayarta, bayan yayi ƙoƙarin katse tunaninshi.

Ƙasa ta ƙara sunkuyar da kanta, sai wani mutsu-mutsu take yi tana haɗe hannayenta da murmushi a fuskarta. Kamar sabuwar amaryar da take kunyar faɗawa angonta maganar da ya shafi ɓangaren auratayya.

"Kin ga Fareeda ba na son fi'ili. Idan baki shirya furta abinda ke tafe da ke ba don Allah ki barni inyi abinda ke gabana. Kunyar furta magana yayi ɓangaren dama ne kinyi ɓangaren hagu, sam bai ma dace da ke ba..."

Sassanyar dariyar da ta saki yasa shi tsayawa da maganar yana kallonta, da idanun mamaki. Ko miye abin dariya a maganganunsa?

"Ranka ya daɗe. Don Allah ina neman izinin zuwa gidan Aunty Binto, anjima zuwa sha biyu, idan ka amince..."

"Ban amince ba."

Ya katseta yana ƙara haɗe fuskarsa. Me ya tuna kuma sai ya ce

"Ko da yake me zai sa ma in hana k fita? kije kawai, duk inda kike son zuwa kije Fareeda nayi miki izini.

A yanzu da nake gaf da samun wacce za ta bi umarnina ko zuciyarta baya so ba sai kin wahalar da kanki wurin satar fita ba. Kije kawai..."

"Na gode Ranka ya daɗe. Tuntuni da ka bani izinin zuwa duk inda nake ganin ya dace da babu abinda zai saka in ƙetare umarninka. Ina sake godiya da wannan umarni ba tare da takurawa ba. A huta gajiya Ranka ya daɗe"

Ta ƙarasa maganganun tana ƙara faɗaɗa murmushinta.

Ya yunƙura zai tashi zaune tayi gaugawar ficewa daga ɗakin tana cewa

"Ji da kanka Malam! Ban shirya kurɓar ruwan ɓacin rai da safennan ba."

Kicin ta wuce kai tsaye, ruwan shayi ta dafa da kayan ƙamshi ta zuba a flask. Nan cikin kicin ta haɗa tea tasha da biredi.

Kan teburin cin abinci ta jera mishi nashi kayan karin sannan ta fara gyaran gidan cikin zafin nama.

Gidan Aunty Binto za ta yini in sha Allahu, tunda yayi mata izini baƙar maganarsa bazai sa ta zauna ba.

Tana gyaran ɗakinta sai tashin motarsa taji, ta taɓe baki cikin rashin damuwa. A fili ta ce

"Allah ya tsare, Umma ta gaida ashsha."

Tana gaf da kammala gyaran gaba ɗaya kiran Auntyn ya shigo cikin wayarta. Da mamaki ta ɗaga wayar tana cewa

"Allah yaja da ran babbar Yaya mahaifiya, kamar kin san yanzu nake shirin ƙarasa aiki in kira ki."

"To madallah Fareedarmu, Allah yasa dai lafiya?"

"Lafiya ƙalau Aunty. Ya kwanan Baby Nu'aim? (Jaririn da Auntyn ta haifa. Sunanshi Abdurrahman inkiyarsa ce Nu'aim.)"

"Lafiyarsa ƙalau Fareedarmu. Ya aka yi? na ji kin ce za ki kira na kira ki? Allah yasa dai lafiya?"

"Ƙalau ne fa, zan shigo gidan zuwa anjima in sha Allah..."

"Kin tambayi Mukhtar ya barki?"

Sai da tayi dariya sannan ta amsa da

"Ya barni Aunty."

"Kin ga Fareeda, kiyi zamanki a gida. Zuwa ƙarfe biyu za mu taho gaba ɗayanmu gidanki, daman tun shekaran jiya mukayi shirin haka."

"To shi kenan Aunty, Allah ya kawo ku lafiya."

Ta amsa cikin farin ciki. A zuciyarta take ayyana idan sun zo gaba ɗaya shi kenan ma sai su taya ta kwashe kayanta zuwa can ɓangaren.

***

Aka ce sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi, cikin awanni biyu da rabi da zuwansu gidan har sun gama kwashe kayanta gaba ɗaya zuwa can ɓangaren.

Sun gyara mata gurin yayi kyau sosai. Da yake ita ɗin mai tsafta ce, kayayyakinta ba wani datti suka yi ba, waɗanda suka ɗanyi ƙura aka sake gogewa.

Ƙofar ɗakin yara da windonsu ne kawai basu samu labule ba, tunda babu su a acan ɓangaren.

Bayan sun zauna hutawa ne suke faɗa mata abinda yake tafe da su.

Allah sarki, yɗan'uwa masu daɗi. Al'ada ce da mafiyawa daga cikin mata muka ɗaukawa kawunanmu, idan miji zai ƙara aure in da hali mu canza kayan ɗakunanmu.

To ita ma Fareeda shawarar da suka taho mata da shi kenan. Gudummuwa suka harhaɗa mata a tsakaninsu naira dubu ɗari da hamsin.

Sai suka bata zaɓi idan tana so ayi amfani da dubu ɗari wajen cikawa a canza mata kujerunta, duk da tsofaffinma basuyi komai ba.

Dubu hamsin kuma sai ta siyo abubuwan da take buƙata na kayan kicin.

"Kinga ko kuloli biyu kika siya da sabbin farantai za su taimaka miki, baza kiga ayi ta kaima miji abinci a sabbin mazubi ke kuma kiyi ta safa da marwa da tsofaffi ba."

Nannauyan ajiyar zuciya ta sauke da ta fuskanci Aunty ta gama magana.

"Na gode yaan'uwana. Allah ya saka da alkhairi, Allah yabar zumunci."

Tayi musu godiya idanunta ciccike da hawaye, sai jujjuya kuɗaɗen take yi a hannunta, zuciyarta cike da farinciki. Bata taɓa tsammanin don za'a yiwa mace kishiya har sai anyi mata gudumuwa ba.

"Ameen ya Allah"

Suka amsa gaba ɗaya.

"Bangaren canza kujeru da kayan kicin, ina da damar faɗin ra'ayina ko kuwa kun gama yanke shawara dole za'ayi hakan?"

Ta tambayesu da murmushi a fuskarta.

"A'a! kina da ikon zartar da abinda kike so. Gudumuwa ce dai mun haɗa miki saboda Allah da zumunci."

Ya Mustapha ya faɗi haka yana mayar mata da martanin murmushi.

"Ni dai a ra'ayina, Allah ya sani a yanzu don kawai za'a auro Fatima cikin gidannan ba ni da ra'ayin canza komai na kayan ɗakina. A hakan Alhamdulillah, rayuwar duniya dai ba ta ƙiyama ba in ba ƙarya zan saka ma kaina ba ɗakina a hakan Tubarkallah.

Idan Fatima ta so tazo da kayan ɗaki na biliyoyin kuɗaɗe, Wallahi ko ɓangarenmu ɗaya ne ba na jin hakan zai dame ni ballantana ɓangarenta daban nawa daban.

Babbar damuwata a yanzu rashin sana'a ne. Ya kamata in nemi sana'ar da zan dinga yi wanda zai ɗauke min hankali daga damuwa da ƙananun abubuwan da bai kamata in kai hankalina kai ba.

Kunga a maimakon in kashe kuɗaɗennan a gyaran ɗaki me zai hana ku nema min wani ƙwaƙƙwaran sana'a da zai taimaka min wurin samun na kashewa?

Ni a ganina in dai da yɐan kuɗaɗe a hannuna to in Allah ya yarda zan samu sauƙin abubuwa da dama, balle ma yanzu da zai zama ba ni kaɗai ba ce..."

"Wannan kuma gaskiya ne. To amma ke wani sana'a kike ganin za kiyi? kin dai san halin Mukhtar, bazai barki zurga-zurgar zuwa kasuwa saro kayan sayarwa ba."

"Kuma kin san shi ya tsani shige da ficen mata barkatai a cikin gidanshi. Shi kuwa sana'a yana buƙatar cuɗanya da jama'a, ko baki je ba za'a zo gidanki."

Bayan ɗaukar tsawon lokaci suna tattake guri sun yanke shawarar sana'ar da za'ayi mata da kuɗin. Aunty Binto a gidanta tana da wadataccen gurin da take kiwon kajin turawa, za'a fara siyan jarirai ko guda hamsin ne a gwada kiwata ma Fareeda, idan an sayar duk abinda aka samu za'a raba biyu, rabi a ƙara a cikin jari, rabi kuma a bata ta samu na kashewa.

Suna zaune mijin Aunty ya turo mata dubu talatin cikin acc wai gudumuwarsa, ta sayi abinda take so.

Saboda tsananin farin ciki bata san sa'adda ta miƙe ta fara taka rawa ba. Yɐan'uwan sai dariya suke mata, zukatansu cike da farin cikin ganinta cikin walwala.

Wannan dubu talatin ɗin yasa suka canza shawara, tunda faufau ta ƙi canjin kujeru da sayen kayan kicin.

Dubu ashirin aka ɗauko a cikin ɗari da hamsin ɗinnan, jarin kaji suka koma ɗari da talatin.

"Wannan dubu hamsin ɗin kasuwa zan shiga gobe da wuri in sayo miki kayan da za kiyi fitar biki..."

"Aunty Murja ni fa bazanyi wani taro ba. Babu wacce zan gayyata, balle a ishe ni da gulma da tsegumi."

Tayi maganar tana ɗaure fuska.

"Taɓɗijan! Ai wallahi ko baki gayyata ba wasu sai sunzo gayyar soɗi. Kuma ɓangarenki idan ba'a zo ba za kiga yadda dangin Fatima za su cika gidannan dam! Ba gara danginki su zo su ɗan rage miki zafi ba?

Ke ko ma baza'a taru ba kiyi ɗinkinki yadda bayan biki amarya zata yi shigar sababbi kema ki shiga sababbi. Tunda dai banga alamun yana da niyyar yi miki kayan faɗan kishiya ba..."

"Ko yayi ko kar yayi ba abinda ya dame mu bane, tunda al'ada ce kawai ba addini ba. Yanzu dai ki bari a sayi kayan fitar bikin, ni zan sayi kayan ɗinki mu ɗinka miki a gurguje, tunda bikin saura kwana bakwai ko?"

Eh! Yau saura kwana bakwai Bro. Don Allah ka yaryaɗa min ɗinki na gani a faɗa..."

"Ke da kika ce bakya son kayan?"

"Ai ɗazu ne, a yanzu kuma ina so."

Dariya suka fashe da shi gaba ɗayansu.

Basu bar gidanta ba sai yamma liƙis. Sun rabu zukatansu cike da farin ciki, Yadda suka tarar da ita cikin walwala abin yayi musu daɗi.

Itama ta ji daɗin zuwansu ba kaɗan ba, har zuwa dare da ta juya sai ta ce

"Oh yan'uwa masu daɗi. Allah ka ƙara mana zumunci da ƙaunar juna."

*****

"Kayi haƙuri, don Allah ka yafe min Haskena... wallahi tallahi jiya ko na minti ɗaya barci bai samu nasarar ɗauka ta ba saboda damuwar na saka ka cikin ɓacin rai..."

"Ba na ce miki na haƙura ba?"

Yayi maganar cikin basarwa yana ɗan kallonta a fisge. Da gaske tsakanin daren jiya zuwa yau har wani ƙwarya-ƙwaryar rama tayi a fuskarta. Idanunta duk sun zurma ciki, sai duk ta wani tsofe a idanunsa.

"Ki daina damuwa Fatina, kin san ina son ki ko?"

A sakalce da wani irin shagwaɓa da yayi mata banbaraƙwai saboda bata saba ba ta ɗaga kai, alamar ta sani. Sai matsar ƙwallah take yi tana jan hanci.

"To ki kwantar da hankalinki. Ni ɗin saurin faɗa nake da amma ina da saurin sauka. Kawai dai kiyi ƙoƙarin kiyayewa, bana son ana faɗa min magana gatsau ba tare da an tauna ba. Idan kika kiyaye wannan za'a daɗe ba'a ji kanmu ba..."

"Zan kiyaye, na ma kiyaye Haskena. Daga jiya irin haka baza ta sake faruwa ba."

Ta bashi tabbaci fuskarta na bayyana matsanancin farin ciki. Sai ajiyar zuciya take saukewa na samun nutsuwa da kwanciyar hankali.

Jiya ta tsorata ba kaɗan ba, tuni ta nemi tashin hankalin da take ciki na raba gadon tsohon mijinta ta rasa. Tsoronta Allah tsoronta Mukhtar ya ce ya fasa aurenta, da ina za ta saka kanta da wannan ƙatoton abin kunya?

Duk ta gama yaɗawa cikin ƙawayensu Mukhtar ɗin bin ta yake tun shekarar da ta gabata da kalmar soyayya amma ta ƙi amince mishi sai yanzu da ta samu goyon bayan Fareeda.

Da wannan maganar ta samu hankalin ƙawayen ya rabu biyu, wasu suna ganin ƙarya take yi, wasu na ganin hakan zai iya yiwuwa.

Wasu masu ƙoƙarin kuma kai tsaye kiran Fareeda suke yi da tambayar wai da gaske ne? Da yake bata son maimaita dogon magana sai take ta bin su da Eh! Da amincewarta...

Katse mata tunani yayi da cewa

"Ni fa tafiya zanyi, akwai saƙon da zan amso gidan abokina. Lefenki sun iso..."

Da saurin gaske ta rufe fuska tana murmushin jin kunya, kamar budurwar ƙauye.

Murmushi yayi, yanayin jin kunyarta na masifar ƙayatar da shi.

"Yanzu dai faɗa min, Zuwa yaushe kike so a kawo kayan?"

"Ko zuwa jibi Haske nah"

Ta amsa kanta a ƙasa, zuciyarta sai azalzalarta take yi kan ta tambayeshi akwatuna nawa ne?

Kamar ya san tunanin da take yi sai ya rage murya ya ce

"Sai dai za ki min haƙuri. Tanadina gaba ɗaya sun tafi a gyaran wancan ginin ne, duk abinda kika gani ki karɓa da haƙuri, gaba ta fi baya yawa."

"Babu komai Haskenah"

Ta amsa daƙyar tana ƙoƙarin danne ɓacin ranta. Ta zaci wasu ubansun kaya ne zai haɗa mata, tunda bata samu sabon gini ba. Amma don rainin hankali shi ne zai wani ce ta karɓa da haƙuri?

"Aban Twince, ina fatan itama Auntyn tawa ka yi mata kayan faɗan kishiya...?"

"Addini ne?"

"A'a! Daman dai kyautatawa ce kawai. Idan baka yi mata ba ko a cikin nawa ne ka ɗebi wasu abubuwan ka bata, za ta ji daɗi."

Tayi maganar da zallan salon munafurci da neman gindin zama. Zuciyarta cike da fatan Allah yasa kar ya amince da maganarta.

"Ina son ki Fatina. Na gode da wannan alfarmar taki. Amma ni bazan taɓa miki kayanki ba, zan siyo mata ko babu yawa, tunda kin saka baki."

*****

Akwatuna uku yayi ma Fatima. Zannuwan ciki duka guda goma ne, Atamfa huɗu, leshi uku, shadda guda biyu sai material guda ɗaya.

Duk da kayan ciki basu da yawa amma ya kashe kuɗi gurin siyo masu ɗan tsada babu laifi. Domin shi a tsarinsa bai taɓa siya ma Fareeda zanen da ya haura dubu goma ba, kayan Fatima kuwa har da na dubu ashirin da biyar.

Sai rugunan barci guda huɗu, gyale biyu, hijabi biyu, yɑn kunne da sarƙa masu sauƙin kuɗi set uku. Takalmi da jaka set biyu, da kayan shafa.

A sannu ta girgiza kai

"Na gani. Kaya sunyi kyau! Allah yasa albarka."

"Ameen ya Allah. Na gode Hajiya."

Ya amsa cikin matsanancin farin ciki, bakinsa kamar zai yage don murmushi.

"Na ga kayan amarya, ina kayan Fareeda matsayinta na uwargida?"

Da wani irin karsashi ya janyo ledar Viva da take ajiye gefensa ya aje ma Hajiyar.

Da mamaki ta fara ciro kayan cikin ledar, Atamfofi ne yɑn dubu bakwai guda uku, sai mayafi guda ɗaya, shi ma dai mai bala'in sauƙin kuɗi ne.

"Ina sauran?"

"Su kenan Hajiya. Gyaran ɓangaren da ta koma duk ya lashe min tattalin arzikina. Ni wlh da banyi niyyar yi mata ba ma tunda ba addini bane, sai Fatima ce ta roƙi alfarmar in ɗiba a cikin nata in ba Fareeda. Shi yasa dai na siyo mata waɗannan."

Ya ƙarasa maganar babu damuwa ko kunya ko kaɗan a tattare da shi, shi bai ga wani aibu a cikin faɗin Fatima ce ta roƙi yayi ma Fareeda kaya sannan yayi ba.

A zabure da wani irin masifaffen ɓacin rai Zubaida ta buɗe baki za tayi magana da sauri Hajiya ta ɗaga mata hannu.

"Madallah! Babu laifi. An gode. Kana iya kwasar akwatunan ka tafi..."

"Hajiya in tafi da su ina? Ai na kawo ne idan kun gama gani gobe ko jibi a tara mata yan'uwa da abokan arziki sukai kayan can gidansu Fatima, yadda ake yi a al'adance "

"Waye zai maka gayyar matan yan'uwa? ko da yake ai ka san gidajensu, wasu kuma kana da lambobinsu. Ka ga tun kafin raina ya ɓaci ka kwashi akwatunanka sawu a likkafa ka fice min a gida.

Yo tsohuwar bazawara ma har sai an wani wahalar da mata gurin kai mata akwatuna? Ai yadda ta karɓi sadaki a hannunka akwatunanma ka kai mata ta karɓi abinta.

Na Fareeda dai ni da kaina zan kai mata ko zuwa jibi in Allah ya yarda."

Haka ya kwashi akwatuna ya fice a gidan jikinsa a saɓule. Ɗan murnar da ya fara yi saboda saka albarkar da tayi tuni ya koma ciki.

Yana fita Hajiya ta miƙe da kanta ta ɗauko wasu sabbin Atamfofi da lesussuka kusan kala takwas masu bala'in tsada da bata ɗinka ba. Ta kalli Zubaida ta ce

"Zubaida, kinga a cikin kayannan ɗiba ma Fareeda guda huɗu, ki tabbatar kin zaɓa mata kalar matasa waɗanda za su dace da jikinta."

Da wani irin matsanancin farinciki Zubaida ta ƙwalla ihun murna sannan ta ruƙunƙume Hajiyar tana godiya.

Allah ya sani tana ƙaunar Fareeda. Shaƙuwa mai girma ke tsakaninsu, Fareeda tana da bala'in kirki da hannun kyautan da in dai ba butulci irin namu na yayan Adam ba masu manta alkhairi babu yadda za'ayi ki hanata abin hannunki.

Duk kuɗi da gatar da kike ciki Fareeda bata damu tayi miki kyauta komai ƙanƙantarta ba. Balle idan kika je muhallinta, ta ringa kyarma kenan tana ina aka saka ina aka aje da ke.

Duk abinda take da shi a lokacin za ta mallaka miki. Fiye da sau goma Fareeda tana buɗe mata set ɗin akwatunan aurenta tace ta ɗebi iya abinda take so. Baza ta taɓa manta alkhairan Fareeda gare ta ba, kuma ba ita kaɗai da take ƙanwar mijinta ba, ga kowa haka halayen Fareeda suke.

Bayan ta zaɓi kayan aka haɗa da wanda Mukhtar ya saya, ta kira telanta da yake mata ɗinki tun kafin tayi aure ta sakar mishi maƙudan kuɗaɗe, yayi mata alƙawarin jibi zai kawo kayan. Da yake yanayin jikinsu ɗaya da Fareeda shi yasa basu sami damuwar gwajinta ba.

Da yake mijin da take aure mai bala'in kuɗi ne, suturunta masu tsada ne, nan cikin kayanta da ta zo dasu ta ware mata sababbi kala bakwai, ko wanne da mayafi da takalminshi.

Hajiya ta bata kuɗi ta ƙara da nata washe gari da wuri ta shiga kasuwa gurin yan sari ta lodo ma Fareeda yan kunnaye masu kyau sosai, waɗanda duk girman taro za ta iya sakawa ta shiga ba tare da anyi mata kallon ƙasƙanci ba.

*****

Mukhtar bai ƙara tabbatar da kyawawan halayen Fareeda sun gama zagaye ko ina a cikin danginsu ba sai da yakai kayan akwatinan Fatima gidan ƙanwar mahaifiyarsa Hajiya Rabi.

Lokaci na farko da ya ji jikinsa ya ɗanyi sanyi kaɗan da ƙarin auren, tausayin Fatima ya lulluɓe zuciyarsa. Nan take ya fara tunanin anya za ta sami karɓuwa a cikin yan'uwansa kuwa?

Daƙyar ta karɓi kayan bayan tayi masa Wankin babban bargo. Ta tunasar da shi ɗumbin alkhairan Fareeda a gare shi da su danginsa.

Ta tunasar da shi sa'adda yake neman auren Fareeda yadda ta zaɓe shi talaka a cikin samarinta masu kuɗi sosai. Har da ɗan mataimakin gwamnan jihar kaduna.

"Yarinyar nan duk ta tsallakesu ta ce sai kai Mukhtar! A lokacin ɗan arzikin naka bai taka kara ya karya ba."

Ta ankarar da shi girman tabon da ya yima zuciyar Fareeda, na zaɓo aminiyarta ya ce zai auro saboda bala'in cin amana irin na su biyun.

"Ga saƙo kuma ka faɗawa wannan busasshiyar da za ka auro ma kanka. Ko ta shigo gidanka ta tsaya a matsayinta, gamu danginka ba ta da wani fuska da za tayi mana kwarjini."

Haka ya bar gidan jiki a sanyaye, gwuiyawu a sake, kamar wanda ya kwana ya yini yana amai da gudawa.

***** ***** *****

Rana ba ta ƙarya, sai dai uwar ɗiya ta ji kunya. Yau asabar, da misalin ƙarfe biyu da rabi na rana, aka ɗaura auren Mukhtar da Fatima a bisa sadaki naira dubu ɗari, lakadan ba ajalan ba.

Ɗaura auren da ya samu halartar mutane ƙididdigaggu, saboda ta ɓangaren Amarya da Ango duk basu saki jiki sunyi wani gayyata ba.

Ana ɗaura aure babu wani ɗoki sai ma sanyi da jikinsa ya ƙara yi kamar mai zazzaɓi, daƙyar ya iya shigewa cikin motar abokinsa Idrees yaja suka bar gurin.

"Ina muka nufa ne Ango? ko gurin Amarya za muje ku ɗanyi rungumar farko na samun yɞancin..."

Dogon tsakin da yaja yasa Idrees dafe bakinsa yana dariya.

"Kaina ciwo yake, kaini gida kawai."

Ya faɗa daƙyar, bakinsa na wani irin ɗaci kamar ya kurkuri maɗaci.

Acan ɓangaren Amarya Fatima kuwa ba haka abin yake ba. Tana cikin wani irin matsanancin farin ciki ne da za ta iya rantsewa da girman Allah tun da uwarta ta haifeta bata taɓa shiga cikin makamancinsa ba.

Tana tsakiyar ƙawayenta suna tiƙar rawa, fuskar nan tasha make'up ta canza kamanni gaba ɗaya. Gidan ƙanwar Innarsu ya cika damƙam da mata, mafiyawa daga cikinsu sa'ido ne ya kai su, wasu kuma gayyar soɗi.

Tana cikin rawa kamar wacce aka raɗa mata a kunnuwanta sai ta janye hannun manyan aminanta uku suka fice daga filin. Tana rangwaɗa da farfar da idanu kamar wacce za ta tayar da aljannu ta ce

"Kun ji bari in kira Hubby in samu tabbacin an ɗaura aure daga bakinsa..."

Ramlah ce tasa hannu a hanci ta rangaɗa ƙaƙƙarfan guɗa sauran ƙawayen suka mara mata baya. Sai kuma suka haɗa idanu suka kwashe da dariya, da idanu suke zunɗen Fatima da ta danna kiran lambar Mukhtar ta kara a kunnenta tana doka murmushi.

Zuciyarta na bata tabbacin yana can cikin matsanancin farin ciki kamar yadda take ciki, ta san ma yadda suka zaƙu a ɗaura aurennan daga can gurin ɗaura auren idan ya gama sallamar baƙi gurinta zai nufo.

Zafafan hotuna take so su ɗauka a gaban mutane da yawa, don dai su ƙara tabbatarwa a yanzu ita Fatima, mallakin Mukhtar ce.

Hotunan da take so ta fara amfani da su a matakin farko wajen tarwatsa zuciyar Fareeda, suna gama ɗauka za ta tura mata gaba ɗaya ta whatsapp.

Idan yaso ta haɗiyi zuciya ta mace, ko kuma tayi bindiga buummm! saboda tsananin baƙin ciki, a yanzu babu wani fifiko ko gani-gani a tsakaninsu, matsayinsu ɗaya a gurinshi.

Abinda Fareeda take taƙama da shi itama za ta bugi ƙirji gaban ko uban waye tayi tutiyar mallakinta ne.

*Makaranta labarin Rabon Ayi, ina godiya kuma ina ƙaunarku duk inda kuke a faɗin duniya. Kuzo ku sayi data a gurina don ƙara samun kusanci tsakanina da ku😍😍😍□□ *

*_Aminci + Ƙarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*16*_

Gaf da za su isa gida kiran Fatima ya shigo cikin wayarsa. A suɓutar baki kawai tsaki ya ƙwace masa, da saurin gaske ya katse kiran. Yana ji a ransa ko ya ɗaga ba shi da abinda zai ce mata a daidai wannan lokaci.

Da wannan dalilin yasa kafin wani kiran ya sake shigowa yayi saurin kashe wayar gaba ɗaya.

Irin yawan matan da ya gani sun cika gidan danƙam shi ne abinda ya bashi mamaki. Ya kasa shiru, cikin al'ajabi ya kalli Idrees haƌe da cewa

"Hmm! Lallai Fareeda, ita da tace babu gayyar da za tayi a sha'anin kishiya shi ne mata suka cika gida..."

Da sauri Idrees ya katse shi yana cewa

"Kai Fareeda fa ko bata yi gayya ba dole mata su cika gidannan! Ka san a duniyarnan babu abinda yakai zama da mutane lafiya daƌi.

Halin kirkinta da faram-faram da jama'a su zasu saka duk abinda ya sameta na farin ciki ko akasinsa ayi tururuwan zuwa yi mata murna ko jaje.

Ka ga duk yadda abokanmu suka ƙi zuwa maka ƌaurin aure? Jiya ina kwance naji Abeeda(matarsa) tana waya za su haƌu gaba ƌaya matan abokanmu a gidan Kareema(matar Ibrahim) su zo ma Fareeda dannar ƙirji.

Kuma ina ji tana cewa baza su tafi ba sai an kawo amarya, saboda ko da yɗan kawo amarya za su zo da wani rawar kai su saita musu zama."

Nannauyar ajiyar zuciya ya sauke bayan ya gama sauraren kalaman Idrees. A farkon gidan akwai wani ƙaramin ƌaki da aka yi shi kaman na maigadi, sun zuba komai na kwanciya da kujerar zama mazaunin mutum biyu a ciki saboda ko da wata rana za suyi baƙi maza su nemi kwana a gidan. Nan suka shige shi da Idrees.

A gefen katifa ya zauna ya lumshe idanunsa, yana jin yadda kansa yake ƙara ƌaukar wani irin nauyi ta ɓangare ƌaya.

Waya ya ƌauka ya kira Fareeda, har ya gama ringing ya ƙara kira sau biyu bata ƌaga ba. Sai ya kira ƙanwarsa Zubaida, yana da tabbacin tana cikin gidan.

"Ango Ango..!"

Ta fara faɗa tana ɗaga wayar da wani irin dariyar shaƙiyanci.

"Ina Fareeda?"

Ya tambaya ba tare da ya bi takan wasar da take mishi ba.

"Ga ta nan! Au tana cikin ɗakinta da mutane..."

"Ke kuma kina ina?"

"Ni ma ina falo da mutane."

Tsaki yaja ƙasa-ƙasa.

"Ki ce mata ta haɗo mana abinci, ga mu a ɗakin baƙi maza."

Bai jira abinda za ta ce ba ya katse wayar.

Minti goma tsakani suka ji sallama daga bakin ƙofa, ko da suka amsa haɗe da bada umarnin shigowa ya zaci Zubaida ce tayi sallama Fareeda na tsaye a gefenta, sai yaga Masrura ce ƙanwar Fareeda ta riƙo ma Zubaida wasu kulolin.

"Ah! Yaya ku biyu ne kawai? Ina sauran abokan naku? Kalolin abincin da muka ware maka ko mutane talatin ne za suci su ƙoshi Alhamdulillah..."

"Ina Fareeda?"

Ya katse ta da wani irin jin haushin bala'in surutunta.

"Yaya tana can cikin abokan arziki suna hotuna. Don abinci kawai naga ko ni zan iya kawo maka ba sai na katse mata harkokinta ba. Yaya Idrees ina yini?"

Tun kafin ya amsa gaisuwar taja hannun Masrura suka fice da sauri. Mukhtar ya bi su da kallo yana jin wani sabon ɓacin rai na lulluɓe shi.

Idrees yana gama cin abinci bai ƙara zaman minti ashirin ba yayi mishi sallama ya fice.

Ɗan kaɗan ya tsattsakuri abincin, ya kwanta a kan katifa kansa a kulle, zuciyarsa a ƙuntace. Ya ma rasa wane kalar tunani ya kamata yayi, a haka har wani marayan barci ya fara kwasarsa.

"Mai halin dattako kin wuce kinyi nisa tun basu farga ba. Ji Fareeda uwar mata ja da ke kwarankwatsa bazai yiwu ba. Duk yawan taron mata na faɗa baza suyi tamkar Fareeda ba. Sunkuye na ce kuma masgaye Allah ƙara taya ma Uwargida."

Kalaman da ya jiyo kenan cikin sautin waƙa da wata zazzaƙar murya mai bala'in karaɗin tsiya tana rerawa da baki amma kamar ta sa amsa kuwwa saboda amon muryarta.

Lokaci ɗaya yaji mata da yawa sun saka shewa. Sai yake jin kamar taron matan a daidai jikin get ɗin gidan. Da saiɓin jiki ya taso a hankali ya ɗan yaye labule ya leƙa karaf idanunsa suka yi kyakkyawan gani.

Fareeda ya hango tsaye matan abokansu sun zagayeta. Irin kwalliyar da tayi mai aji ne, baki ma bazai iya furtawa ba. Ta yi wani irin bala'in kyau da kwarjini a idanunsa fiye ma da ranar aurensu.

Wani uban leshi da yake jikinta ya kallah ya ƙara kallah. Wohoho! Fareeda tayi kyau, ta yi kyau, wallahi ta yi kyau a idanunsa. Sai wani irin murmushinta na ƙasaita take saukewa kamar wata gimbiya. Bakinnan a tsuke ta ɗan tura laɓɓan ƙasa gaba kaɗan, sai ta zama kamar wata zahrah a cikin taurari.

A inda yake raɓe jikin labule yana leƙe ya hangi wayoyi fiye da goma suna ɗaukarta Hotuna da Vidio ana rera mata waƙar nan da ya tashe sa tana wani irin juyi cikin gayu da ƙasaita kamar yar gidan sarkin saudiyya.

Da hanzari ya fara gyara riga yana ɗan kakkaɓewa, babbar rigarsa da ya aje hannun kujera ya ɗauka ya fara ƙoƙarin sakawa. Sauri yake ya fita waje su ɗauki hotuna tare, irin wannan kyau da tayi abin alfahari ne a ɗauke su hotuna tare matsayinshi na mijinta.

Kafa hularnan yayi ta zauna tsaf, ya fito a ango sosai. Tun daga nan cikin ɗakin ya fara rehazal ɗin irin murmushin da zai dinga saki idan ya fita gurinta. Har ya kama labule zai buɗe ya fita wani tunani da ya gilma mishi a cikin ransa ya saka shi sakin labulen da sauri ya zauna daɓas kan kujera.

"Yanzu fa duk taron matannan sun san aure mai kama da na cin amana yayi? Ya auro aminyar matarsa ta ƙud da ƙud!"

Ko basu faɗa a fili ba ya san a zukatansu za su dinga mishi wani irin kallo. Jiki a saɓule ya cire hula da babbar rigar ya kwanta nan kan kujera.

*****

"Kar kiyi min haka! Hajiya Asabe Dillaliya don girman Allah kar kiyi min haka. Kinga mun gama magana da ke, wallahi tallahi ina shiga gidannan yau zuwa gobe da yamma zan ciko miki dubu ɗarin ki..."

"Fatima sai dai fa kiyi haƙuri. Bazan ɓoye miki ba kayannan wasu na samu suka siya kuɗi hannu har da ƙarin dubu arba'in kan yadda kika siya..."

"Ki bani zan ƙara miko dubu arba'in ɗin."

Ta faɗa bakinta na rawa, hankalinta na ƙara ɗugunzuma.

"Ai sai dai fa kiyi haƙuri. Masu kayannan har sun kwashe. Yanzu dai ga set ɗin shadow nan ana sake miki feshi, kujeru kuma tun safe na saka aka fara aikin canza musu yadi, ƙafafuwa kawai suka rage a saka. Kuma baki ga yadda suka yi kyau ba. In dai ba ƙarya kika saka ma ranki ba waɗannan sun ishe ki bagu da bubbuɗawa. Allah na tuba zawarawa nawa ke aure babu kayan ɗaki? Adireshin da kika bayar can za su kai miki kayan?"

"Eh..!"

Ta amsa a raunane! kalmar eh ɗin ta fito ne haɗe da saukar wasu zafafan hawaye a idanunta.

Hajiya Asabe Dillaliya ta gama yi mata wulaƙanci na ƙarshe. Amma babu komai, kwanaki uku na amarcinta sun isa ta saka Mukhtar a loko ta kalamamme shi ya bata ko dubu ɗari biyu ne ta sayar da waɗannan kayan ta cika ta sayi masu ɗan kyau.

Saboda tana so a kawo kayan kan idanunta. Lambar Mukhtar ta cigaba da kira kamfani na faɗa mata wayar a kashe take.

Habawa!! Ba sai kukanta ya ƙara ƙarfi ba.

Ƙawayenta na zazzaune a falo ita tana ƙuryar ɗaki suka fara jiyo shesshekar kukanta.

Nan take suka dabaibayeta da tambayar me ke faruwa. Cikin kuka ta sanar da su ango ta kira wayarshi a kashe, kuma za'a kai kaya bata so akai babu idanun mutanenta acan gidan, don kar yan baƙin cikin auren suyi mata ɓarna.

"Eh kuma kina da gaskiya. To ke ko lambar ɗaya daga cikin abokansa ba ki da ita?"

Da saurin gaske ta lalubo lambar Idrees ta kira, sun je gurinta shi da Mukhtar ana jibi ɗaurin aure. Har za su tafi ta ce ya bata lambarsa saboda ko ƙawayenta za su nemi wani abu sai su kira shi, ashe ita lambar zai yima amfani ba ƙawayenta ba.

Bai daɗe yana ringing ba daga can ɓangaren ya ɗaga. Yadda ya fara da tambayar wa ke magana shi ya bata tabbacin ko da suka yi musayar lamba shi bai adana nata ba.

Ta ɗan ji babu daɗi. Amma damuwar da take ciki ya hana tayi mishi ƙorafi. Ko da ta faɗa mishi sun gama shiryawa motocin ɗaukar amarya suke jira mamaki ne ya hana shi magana.

Lura da katoɓarar da tayi yasa ta saurin cewa

"Kayi haƙuri. Ba wai mun zaƙu bane, amma da yake bamu yi jere kafin biki ba. Yanzu ne motocin kayan suka tafi shi ne yɗan'uwana suke so a tafi da wuri a gama gyaran ɗaki kafin dare yayi su koma gidajensu."

"To na gane. Nan gidan da muka zo shekaran jiya za'a turo motocin?"

"Eh!"

Ta amsa tana sauke ajiyar zuciyar samun kwanciyar hankali.

Ƙit! ya katse wayar daga can ɓangaren.

Abokansu ya fara kira ɗaya bayan ɗaya, amma wani abun mamaki duk sai zillewa suke yi. Kowa da raunataccen uzurin da zai ba shi wanda zai hana shi zuwa ɗaukar amarya da motarsa.

Ibrahim ne kawai ya fito kai tsaye ya ce

"Idee, bazan iya ba. Mukhtar baiyi auren da zan iya ɗauko mishi amarya da motata ba. Kai ma in zaka ji shawarata ka zille kawai ka barshi ya ƙarata da

yawarsa, idan kuma baza ka iya ba ka nema musu hayar yan ƙumbula a kasuwar barci." (Kun san yar ƙumbula? wannan motar mai kama da napep amma ta fi napep girma, kuma ba Bus bace. Idan ba na manta ba kamar tana ɗaukar mutane goma duk guda ɗaya.)

A ƙarshe dai shawarar Ibrahim yayi amfani da shi. Akwai wani yaro a layinshi da yake da taxi mai kyau ta haya, shi ya kira, ya umarce shi ya ɗauki yar ƙumbula guda biyu da shi na uku su je su ɗauki Fatima da ƙawayenta.

"Habib a motarka ka ɗauki Amarya da ƙawayenta. Sauran kuma su kwashi jama'a, iya yadda kuka ɗiba sauran su san yadda za suyi."

Hum! humm! Hummm! Ƙawayenta da abokan arziki suke tayi ganin motocin da aka turo ɗaukar amarya amma ita ko a jikinta.

Shatar napep tasa aka samo mata ta loda yan kayayyakin kicin ɗin da ta siya waɗanda basu taka kara sun karya ba. Da kanta take shiga da fita tana ɗaukar duk wani abu da ta san nata ne, ƙawayenta na gefe suna yi da ita.

A ƙarshe tayi lulluɓi ta shige bayan taxi ita da ƙawayenta biyu bayan tayi tayi da Innarta tayi mata rakiya ta ce baza ta iya ba.

"Kiyi haƙuri Fatima. Kije kawai, ina miki fatan alkhairi. Bazan iya haɗa idanu da Fareeda na kaiki gidanta a matsayin kishiya ba. Zan zo bayan kwana biyu."

Ramlah ce ta shige gaban taxi, Habib yaja a guje suka bar unguwar.

"Kan ubancan kayyasa!!! Jama'a ku kunga kayan amarya? Rugwagwa... sunan wata mota. Saboda tsananin rashin ƙwarin kujeru tun gurin sauke kayan a mota hannun biyu daga ciki sun ɓalle."

Kareema matar Ibrahim da ta dawo daga tsakar gida ta faɗi maganganun tana tuntsira dariya.

Kun san mata da tsegumi, da saurin gaske kusan duk mazauna falon suka tashi zuwa ƙofar falon Fareeda suna hangen yadda ake sauke kayan amarya Fatima, kayan da tun a ido in dai mutum ya san kayan gado da kujeru zai gane sai dai tayi maneji kawai.

A daidai lokacin motar amarya ta iso cikin gidan.

Fareeda da yɗan'uwa da wasu cikin abokan arzikinta suna cikin ɗaki sai sauƙar zaƙaƙan guɗa daga hancina mabanbanta suka ji a kunnuwansu.

Wani irin luguden daka ƙirjinta yayi, duhu mai tsanani ya ratsa ta cikin idanuwanta da sauri ta rufe idanu. Wani ƙaƙƙarfan jiri ya kawo mata farmaki, ta tafi taga-taga za ta faɗi. A fili kuma da ɗan ƙarfi ta ce

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Allahumma ajirnee feemusibati, wa akhlifnee khairan minha."

Da wani irin bala'in sauri Baby da Zubaida da suke tsaye kusa da ita suka tallafeta, hakan shi ya hana ta zubewa ƙasa warwas!!!

"Subhanallahi! Fareeda menene? Lafiya kuwa?"

Aunty Binto da Aunty Murja da suke zaune gefen gado suka taso cikin sauri suna tambayarta fuskokinsu na bayyana tashin hankali.

Har lokacin bata buɗe idanunta ba, bata amsa musu ba. Addu'o'in da duk yazo cikin kanta take karantawa don samun sauƙin tashin hankalin da wani masifaffen fargaba da tsoron da ya lulluɓeta lokaci ɗaya.

*_(Kishi bala'i ne yɗan'uwa□□□ Ya Allah ka sauƙaƙa mana, ka bamu ikon komawa gare ka aduk lokacin da mazajenmu suka yi yunƙurin ƙaro mana abukkan zama□□)_*

Daga addu'o'in da take yi ta samu sauƙin firgicin da ta shiga. Amma lokaci ɗaya kanta ya fara wani irin ciwo, duk yadda ta so daurewa ta kasa. Ko da ta shiga banɗaki da niyyar alwalar sallar magrib sai da ta ɓata lokaci tana sharɓen hawaye.

Zuciyarta na wani irin ƙuna da zugi. Damuwar komai ya dawo mata sabo fil a ranta.

'Yanzu shi kenan? Mukhtar ba nata bane ita kaɗai? ya zama mallakinsu su biyu?'

Daƙyar ta iya tsayar da hawayenta tayi alwala ta fito bayan ta ji Zubaida tana ƙwanƙwasa mata ƙofa, haɗe da kiran sunanta a tausashe.

Jikinta a sanyaye tayi sallah, nan kan darduma ta zauna tana lazumi, hannunta ɗaya dafe da ƙunci, ɗaya riƙe da casbaha.

Aunty Binto ne ta haɗo mata tea mai kauri a kofi ta bata umarnin ta shanye. A hankali take kurɓa har ta shanye gaba ɗaya.

Paracetamol ta bata guda biyu tasha. Ta zauna nan gefenta ta ci gaba da yi mata nasiha a tausashe, har ta ɗan samu nutsuwa da kwanciyar hankali.

Ƙarfe takwas da rabi na dare ɓangaren Fareeda babu kowa. Daga ita sai yayanta biyu. Ƴan'uwa da abokan arziki duk sunyi mata sallama da ƙarin nasiha sun koma gidajensu.

Ɓangaren Fatima ma babu kowa. Sun gama jere sun tattara ina-su ina-su sun wuce. Tayi tayi ƙawayenta su tsaya su karɓi kuɗin sallama suka ƙi, ko da ta nuna rashin jin daɗinta ɗaya daga cikinsu mai suna Hadiza Uwar gayu cewa tayi

"Fatima idan kika ɓata ranki kin so ne. Wannan biki naki dai ko kin so ko kin ƙi duk mun gane yana da rangwamen armashi daga ɓangaren ango. Ki duba irin wulaƙancin da suka yi miki gurin turo motocin ɗaukar amarya mana? Wace za ta zauna ta kwasar ma kanta takaici?

Mu dai tafiya za muyi, amma Idan sunzo abokan mun baki sallahu ki karɓa mana kuɗin sallama. Idan basu bayar ba daman bamu saka rai ba."

Uffan ta kasa cewa don kariyan kai. Tana ji tana gani suka fice, ta zauna tsuru tana yɗan tunane-tunane. Daga bisani kuma sai ta miƙe ta shige ɗakinta tana kallon mutattun kayan gadon da Asabe dillaliya ta bata a matsayin kuɗinta.

Ɗakin Mukhtar bata samu sararin siya mishi ko tsinke ba. To ita ma nata gado da kujerun da ya suka samu balle ta sai mishi na ɗakinshi?

Takaici da baƙin cikinta bai ninku ba sai da taje falo tana sake ƙare ma kujerunta kallo. Bayan ɓalla hannu biyu da aka yi da kallon yadin kujerun za'a gane yɗan ɗari uku duk yadi ɗaya ne.

Kwal-ƙwal tayi za ta fara hawaye sai kuma ta haɗiye kukan da sauri.

"Na san halin Aban Twince, zaiyi min uzuri. Da mun kwana ɗaya yau yaji zan-zan zai sakar min bakin aljihunshi, watakila ma gobe yasa a kwashe waɗannan a zuba min wasu sabbi haɗaɗɗu.'

Ta ƙarasa tunanin ne da sakin lallausan murmushi.

******

Tun da ya fita a gidan lokacin sallar magriba bai dawo ba sai ƙarfe goma saura kwata na dare.

Buɗe get da shigowar motarsa shi ya alamta ma Uwargida da Amarya mai gidan fa ya dawo.

Fareeda tana zaune a gefen gado ne tana shafa bayan Shaheed da tun ɗazu yaƙi barci yana yɼan rigingimu, sai yanzu ta samu yayi barcin, shi ne take ɗan lallaɓa shi barcin yayi nauyi.

Sayyid yayi barci tun sa'adda tayi musu wanka ta saka musu kayan barci. Lumshe idanu tayi tana jan Hasbunallahu wani'imal wakeel a zuciyarta.

A ɓangaren Fatima da sassarfa ta shige uwarɗakinta, pose ɗinta ta lalubo cikin kaya ta ɗauko kwallin _Idonka idona masoyi_ ta zizara a idanunta, sai wani turare _Na sha gaban kishiya_ ta shafa a fuskarta gaba ɗaya.

Kan gado ta haye taja mayafi ya sauka har goshinta, ita kaɗai take ta sakin murmushi tana cije laɓɓanta na ƙasa, zuciyarta cike da tunanin irin salo-salon da za tayi amfani da shi ta haukata Mukhtar a wannan dare.

Za ta tabbatar mishi lallai ya ɗauko bazawara wacce tasan hannunta. Za ta gigita shi, za ta birkita shi, za ta tabbatar a wannan dare ta ƙarasa shafe duk wani ɗan ragowar soyayyar Fareeda a zuciyarsa.

*_Aminci + Kɼarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*17*_

Har zai nufi ɓangaren Fareeda, hango ɓangaren Amarya Fatima da wuta ga kuma alamun labulaye yana kallo ta window yasa shi buɗe baki yana mamaki.

"Fatina sunyi jere kenan?"

Ya tambayi kansa a fili. Domin share duk wata tantama sai kawai ya nufi ɓangaren.

Shigarsa yayi daidai da fitowarta daga uwarɗaki, fuskarta a ɗaure, ta fito ne don ta leƙa ta windo ta gani ko ya wuce ɓangaren Fareeda ne.

"Ai wallahi da tun a darennan za'a fara kwasar bala'i a gidannan"

Tayi maganar a fili haɗe da jan tsaki mai ƙarfi. Wannan dalilin yasa ta fito sai suka yi kiciɓis!

Kallon kallo suka yi na daƙiƙu biyu a tsakaninsu. Shi fuskarsa na bayyana mamaki ita kuma nata fuskar na bayyana shauƙi da bege.

Shi ya fara katse shirun da cewa

"Fatina? Ke ce anan? Ta yaya akai haka?"

Sansarai tayi a tsaye, jikinta ya ɗanyi sanyi kaɗan, da ɓacin ran kalamansa a fuskarta ta ce

"Baka yi murnar ganina bane...?"

"Ah haba dai! Kawai dai na ɗanyi mamakin ganinki ne anan. Na ga tunda aka ɗaura aure ko a waya bamu yi magana ba, balle muyi zancen tarewa in tura da motocin ɗaukar amarya. Ganinki anan ai kinga dole inyi mamaki, amma nayi murna ƙwarai. Barka da zuwa gidan Haskenki Amaryataaaa..."

Ta buɗe baki za tayi magana ya kai mata wata wawuyar runguma, a dole ta haɗiye abinda tayi niyyar cewa, ya riƙe ta ƙamƙam a jikinsa yana shaƙar wani irin ƙamshi da take yi mai bala'in hawa kai kamar na koron aljanu.

Bata ɓata lokaci ba gurin mayar masa da martanin rungumarsa, itama ta ƙanƙameshi, sai ajiyar zuciya take saukewa sauri-sauri kamar jaririyar da ta kwana ta yini ba tare da mahaifiyarta ba.

"Bari in leƙa Fareeda, idan bata yi barci ba sai in haɗa ku inyi muku nasiha. Haka ake yi a irin wannan daren ko Fatina?"

Ya tambayeta da murya ƙasa-ƙasa.

"Haskenah, dare yayi fa. Ni barci nake ji, baza a iya barin nasihar sai da safe ba?"

Tayi maganar a hankali tana ƙara lafewa a jikinsa, zuciyarta cike fal da farin ciki.

'Waiyo duniya gidan daɗi. Idan baka mutu ba za ka sha kallo. Wai yau ita Fatima ce rungume a ƙirjin gayen nan? kuma a matsayinshi na mijinta. Mutumin da a baya ko gaisuwarta daƙyar yake amsawa, a wasu lokutanma fuskewa yake ya wuce kamar bai ji ba.

Lallai mahaƙurci mawadaci. Ita kam ta ga gurin zama, kwance-kwance za tayi ta ƙara fahimtar abinda yake so da wanda ba ya so ta bi shi sawu da ƙafa. Wannan ne zai sa ta ƙara riƙe shi ƙaƙam sai yadda ta juya shi.'

"Kinga, kiyi haƙuri. Na san wannan daren naki ne. Bazanyi gangacin cinye miki shi gurin nasiha ba. Yʼan mintuna kaɗan za ki ara min inyi muku nasiha inyi mata sai da safe. Kin amince Fatina?"

"Na amince."

Ta faɗa ba don zuciyarta na so ba. Sai don gudun kar yayi mata lambar musu tun a darensu na farko.

Yana ƙoƙarin ɓamɓareta a ƙirjinsa ta shagwaggwaɓe fuska kamar za ta saka ihu ta ce

"Ƙalb na zaci tare za muje? Tunda ka ce nasiha za kayi mana mu tafi tare mana? Ka ga ka huta zuwa da dawowa kai kaɗai."

"Haka ne kuma fa! Daɗina da amaryar tawa akwai hangen nesa."

Murmushin jin daɗi ta saki cikin kissa da jan hankali. Tana riƙe a ɓangaren kafaɗarsa sai firirita da lanƙwasa take yi ita ga Amarya har suka isa ƙofar falon Fareeda.

Ko kafin yayi yunƙurin buɗe ƙofar har Fatima ta sa hannunta ta buɗe ƙofar, da sauri ta sake shigewa jikinsa tana sussunne kai a ƙirjinsa, da wani irin salon makirci don a ɗaga hankalin abokiyar zama sai ta fara saka hannunta tana shasshafa shi, har inda ma bai kamata ace hannunta ya kai ba a wannan lokacin da babu wani abu da ya taɓa shiga tsakaninsu.

Fareeda tana tsaye a tsakar falon, a hannunta ɗaya riƙe da kofin tea tana kurɓa a hankali, ɗaya hannun kuma riƙe da wayarta tana dannawa taga an buɗe mata ƙofar falo.

Karaf idanunta suka faɗa kan Fatima da Mukhtar suna maƙalƙale da juna. Duk da faɗuwar da gabanta yayi bai sa tayi gaugawar kawar da idanunta daga kansu ba.

Daƙiƙu goma ta ɗauka wajen ƙare musu kallo, ganin yadda Fatima tayi wata tsugul a jikin Mukhtar ɗin yasa ta saki wani malalacin murmushi, ta kawar da kanta daga gare su.

Da tafiyar nutsuwa mai bayyana isa da taƙama ta juya ta ƙarasa kan kujera ta zauna. A ɗan tafiyar da tayi mazaunanta sai juyi suke yi cikin riga da wandon kayan barcin da suke jikinta.

"Ranka ya daɗe, idan za ku shigo bismillah, idan baku shirya shigowa ba don Allah ku koma, sannan ku rufe min ƙofa. Daman shigo min kuka yi kai tsaye ba tare da neman izinina ba, wanda ko a addinance hakan haramun ne."

Ta faɗi hakan idanunta cikin na Mukhtar, ganin yadda su biyun suka ƙame a bakin ƙofa suna kallonta.

Mukhtar ne kaɗai yayi sallama bayan ta ankarar da su, yaja hannun Fatima suka ƙarasa ciki ya zaunar da ita kan kujerar da yake fuskantar Fareeda, shima ya zauna a gefenta.

Tsabar takaici da baƙin ciki kamar zuciyarta za tayi bindiga. Abinda taso bata samu ba, so tayi daga ganinsu riƙe da juna Fareeda ta ɗora hannu akai ta fashe da ihun kuka, amma abin mamaki ko gezau bata yi ba.

Wannan baƙin ciki da takaicin yasa hankalinta yayi gaba, duk yɗan nasihohin zama lafiya da kiyaye haƙƙoƙin juna da Mukhtar ya ɓata lokaci wurin yi musu ita ko kaɗan bata ji ba.

Ta dawo hayyacinta ne ta ji shi yana cewa

"Tunda Fatima bazawara ce kwanaki uku addini ya bani damar yi a ɗakinta. Haka ne ko Fareeda?"

"Oga ni kuma ina zan sani tunda ba taɓa zawarcinnan nayi na sake wani auren ba."

Tayi maganar cikin rashin damuwa, har lokacin kurɓar tea ɗinta take yi a hankali.

Maganar ta buge su, inji malam bahaushe ya ce kowa yayi zagi a kasuwa...

"Fareeda me kuma ya kawo wannan maganar?"

Ya tambayeta fuskarsa a ɗaure.

"Magana? Wacce kenan?"

"Humm! Shi kenan!"

Ya mayar da hankalinsa kan Fatima. A tausashe ya ce

"Fatina, kwanakin da addini ya bani damar yi a ɗakinki uku ne. Bayan na gama yin su sai ku fara kwana bibiyu ke da Fareeda."

Hannunshi ɗaya ta riƙo a cikin nata tana ɗan murzawa cikin salo, ta kashe mishi idanu ɗaya, ta rage murya amma yadda Fareeda za ta iya jin abinda take cewa ta fara yi mishi magana cikin shagwaɓa da salon iya duniyanci.

"Haskenah! Wasu iyayen gidan fa cikin adalcinsu suna ƙara ma amare kwanaki. Ka tambayi Aunty Fareeda ko za ta ƙara mana, plssssss! Kwanaki uku sunyi min kaɗan ni dai, me muka ci a cikin yan waɗannan kwanakin?"

Maganar ta bugi Fareeda ƙwarai, har sai da ta tsaya ƙyam riƙe da kofin tea ɗinta tana kallon Fatima cikin idanu. Ita kuwa ta kashe mata ido ɗaya haɗe da sakin wani irin shegen murmushi.

Cikin dabara Fatiman ta ɗaga mata yatsunta tayi mata alamar anyi 1-1. Wato ta rama maganar zawarci da ta yaɓa mata.

Mukhtar da bai gane dawan garin ba sai yayi dariya, sosai jikinsa ke karɓar saƙon da Fatima take aika mishi da shi ta hanyar murza mishi tafin hannu. Ya kalli Fareeda ya ce

"To ke kin ji, tana buƙatar ƙarin kwanakin cin amarci..."

"Ranka ya daɗe, addini ne yazo da zancen in ƙara mata kwanakin?"

Ta tambayeshi fuskarta na bayyana mamakin yadda ya iya maimaita mata zancen da Fatiman tayi, bayan yana da tabbacin ta ji abinda ta ce. Lallai namiji...

"A'a ba addini bane. Ai kin ji itama cewa tayi cikin adalcin wasu iyayen gidan..."

"To ni kam banyi niyya ba. Sai da safenku! idan kun fice ku ja min ƙofa"

Daga haka bata sake cewa komai ba ta shige ciki ta barsu sake da baki. Mukhtar har ya miƙe zai bi ta da sauri Fatima ta riƙe hannunsa. Ta kwaɓe fuska kamar za ta fashe da kuka.

"Haskenah ina za ka ? kishi ne fa ya rufe mata idanu. Kai baka lura sadda take magana idanunta ciccike da hawaye ba?

Hmmm! To ya za'ayi? Ya muka iya da abinda Allah ya ƙaddara tun fil-azal? Sai dai duk muyi haƙuri kawai, mu rungumi juna da mijinmu mu zauna lafiya.

Za ta huce fa. A yanzu dai naga alamar tana buƙatar mu bata fili ne, muje kawai. Gobe idan ta huce sai kazo ka rarrashe ta."

Haka ya biye mata zugwui-zugwui suka fice daga falon.

Farin ciki fal ranta, a zuciyarta take cewa

'Sakarya, baki ga komai ba in dai ni ce. Taya wacce ta riga ki kwana baza ta riga ki tashi ba? Mu zuba mu gani Fareeda, na fiki iya duniya.'

Ko da suka koma ɓangarenta kai tsaye Mukhtar bayi ya shige. Ita kuma ta zauna a gefen gado tana jiran fitowarsa.

Cikinta in banda ƙugi babu abinda cikinta ke yi, gara ya fito ya ɗauko mata kaza da madarar amarcinta ko ta rage zafi, yinin yau gaba ɗaya bata nutsu ta abinci ba.

"Haskenah, ni fa yunwa nake ji"

Ta faɗa a shagwaɓe tana ɓata fuska.

"Yunwa dai Fatima? baki ci abinci bane?"

"Eh!"

Ta amsa kai tsaye.

"Ikon Allah! Wai yaushe kika shigo gidannan ne? Ba'a kawo muku abincin tarbar amarya ba?'

Ya tambayeta fuskarsa na bayyana mamaki.

"Haba Aban Twince. Ni da take baƙin cikin aurenmu taya za ta aiko mana da abinci? Haka nan na ba jama'ata haƙuri suka tafi da yunwarsu ransu a ɓace. Yanzu dai ko kazar amarci na ne kawai ka ɗauko min inci, na san ma ka haɗo da madara. Ko su kaɗai na ci za su ishe ni zuwa safe..."

"Kazar amarci?"

Ya tambayeta, kamar ta faɗi wani mummunan abu. Sai kuma ya kalli agogo. Ƙarfe sha ɗaya na dare saura minti biyu.

"Kiyi haƙuri Fatina. Wannan kazar yau dai don Allah a bi ni bashi. Wallahi na gaji, bazan iya fita a yanzu dai in nemo miki kaza ba.

Ni fa gaba ɗaya yinin yau tun bayan ɗaura aure lissafina ya ƙwace. Ko da na dawo ban taɓa tsammanin zan tarar da ke a gidannan ba sai ga ki, kin ga ban san kina nan ba balle inyi tunanin siyo kaza.

Kiyi haƙuri. Bari in tambayi Fareeda ko tana da ragowar abinci sai ki ci. Ko kuma in haɗo miki tea kisha da biredi?"

Saboda ɓacin ran rashin ɗaukarta da muhimmancin da taga ƙiri-ƙiri yana yi yasa ta kasa magana. Sai kai ta iya ɗaga masa, fuskarta a damalmale kamar za ta ɗora hannu akai tai ta rusa ihu.

Da sassarfa ya fice zuwa can ɓangaren Fareeda. Amma sai ya tarar da ƙofar a kulle da makulli, ya ɓata tsawon mintuna huɗu yana ƙwanƙwasawa, tana jinsa ta ƙi buɗewa.

Haka yaja sanyayan ƙafafunsa ya nufi ɓangaren Fatima. Har ya kama hannun ƙofa zai buɗe sai ya tuna ai ɗazu kafin ya fita ya bar abinci a ɗakin baƙi, Allah yasa ba'a fitar da kulolin ba.

Da sauri ya juya zuwa can ɗakin, sai ya tarar abincin na nan yadda ya barshi.

Ajiyar zuciya ya sauke na jin daɗin samun mafita. Ya ɗauki kular sinasir da miyar taushe ya fice mata da su.

Haka dai ba don ranta ya so ba ta ɗibi sinasir ɗin tana cusawa cikin takaici da baƙin ciki. Da gaske yunwa take ji, idan bata ci ba sai dai ta kwana da yunwa.

Tunda babu komai a ɗakinta, ko yar cincin da dubulan da ake ma amare ita bata sami sararin yi ba saboda rashin kuɗi.

A daidai lokacin Mukhtar ya fito daga ɗakinta ya buɗe ƙofar ɗakinsa ya shiga. Kirjinta ne ya buga daram, bata sami zarafin yin wani tunani ba ta ji ya fara ƙwalla mata kira a haukace.

Jikinta na rawa ta ƙarasa cikinta ɗakin. Ko kaɗan Ta kasa haɗa ido da shi, sai ta sunkuyar da kanta ƙasa ta raɓe a bakin ƙofa.

"Haskenah, ga ni..."

"Fatima? Me zan gani haka? ya naga babu komai a cikin ɗakina? ina kayan gadon da kika siya na ɗakinnan?"

Mirgina kai ta fara yi tana muimui da baki cikin rashin abin cewa.

"Kayi haƙuri"

Ta fisgo kalmomin biyu daƙyar!

"Hmmm! Allah ya kyauta."

Ta gefenta ya raɓa ya fice, ko kallonta baiyi ba.

A falo ya tsaya ya gama ƙare ms kujerun kallo, ɗaki a ɗaiɗaice kamar na tsohuwa. Daga kujeru sai wasu zaga-zagan labulaye. Ko arzikin kafet ɗin tsakar ɗaki ba ta da shi balle akai ga su dining table da kayan kallo.

Hannaye biyu na kujeru da ya gani a ɓalle ya sa shi haɗiye wani kakkauran miyau mai bala'in ɗacin tsiya. A fusace ya shige cikin ɗakinta.

Kayan barci da duk siturunsa suna can ɓangaren Fareeda. Haka nan ya kwanta daga shi sai singileti da gajeren wando.

****

Hannunsa na sauka a kafaɗunta yayi shiru cikin tunani, sai kuma dai ya ƙara miƙa hannuwansa ya laluba dakyau ya shafo har ƙirjinta.

Sulum ɗin da yaji kamar babu komai yasa shi ɗan zaro idanu waje, sai kuma dai ya sake lalubawa da kyau.

Wasu yʻan ababe ya kamo ƙananu ga su sun kwanta sharaf kamar suɗaɗɗen silipas. Yʻan ƙananun kawunan da ke jikinsu da kuma tushen mazauninsu da ya shafo ya bashi tabbacin eh lallai fa abinda yake nema ne suke kwance sharaf haka.

Ya runtse idanu da ƙarfi, ƙirjinsa sai bugawa yake fafafat! Haka dai ya daure ya cigaba da lalubawa.

Wani abu da ya bashi tsoro shi ne duk inda ya taɓa da tunanin zai ji taushi da tsokar nama tuɓus sai dai ya ji hannunsa na karo da ƙasusuwa, yʻar tsokar namar bata taka kara ta karya ba.

Bai sake shiga cikin firgici, tsoro, da tashin hankali ba sai da ya damƙo mazaunanta, inda yake kallonsu ta cikin kaya a ciccike dam sun cikr shape ɗin siket ko doguwar rigar da ke jikinta.

Tsoka-tsoka ƙwamemen ƙashin da hannunsa ya damƙo yasa shi sakin mazaunan a firgice. Kamar wanda aka sokawa allura ba tare da ya shirya ba a zabure ya miƙe zaune.

Jikinshi na rawa yakai hannu ya kunna ƙwan lantarki mai haske sosai. Ya kalleta tsurarta a kan gado, wata yʻar ficika da ita saboda tsabar ƙanƙantar jikinta.

"Keh Fatima! Miƙe tsaye in gani."

Ya bata umarnin cikin tsawa da ɗaga murya, kamar ya manta an doshi ƙarfe ɗaya na dare.

A tsorace ta sauka daga kan gadon ta tsaya a tsaye haihuwar uwarta.

"Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un"

Yayi salatin a tsorace, idan ya kalleta da sauri sai kuma ya kawar da kansa.

Fatima irin siraran matannan ne na sosai, waɗanda sirantarsu ta wuce duk yadda ake tsammani. Kʻirjinnan ba su da girma amma gaba ɗaya sun tsiyaye sun kwanta lakaf.

Cikinta a ɗame, a ɗame sosai kamar ba ta cin abinci. Yʼan cinyoyinta kuwa ko rantsuwa yayi babu kaffara damtsen ƙafarsa ta fi cinyarta kauri.

Ya juya gabas da yamma kudu da arewa kamar mai faretin zagaye, sai ya tafi da baya baya ya zube da ƙarfi a gefen gadon.

Take shimfiɗar gadon ɓarayin ƙafa biyu daga cikin huɗu suka durƙushe, ji kuke ƙaƙaƙas!

Bai damu da karyewar katakon gadon ba, ya kalleta, idanunsa sunyi ja sosai ya ce

"Fatima da nake ganinki dumurmur a cikin kaya da me kike cikon gaba da baya?"

A kunyace ta kwaso mishi biyu daga cikin wanduna da bireziya mai uban soso da take kwalliya da su.

Ya kasa magana, ya kasa cewa komai. Gaba ɗaya Fatima ta goge mishi hadda.

Shi mutum ne mai son kakkauran mace, ya fi so duk inda ya damƙa ya ji tsoka dumus! Amma sai ga shi da busasshiyar mace irin Fatima?

Daman bai saka ran zai same ta kamar Fareeda ba. Amma ya tsammaci sai sameta da ƙiba yʼar daidai ita, kamar dai yadda yake ganinta a cikin kaya.

"Fatima, kin ha'ince ni."

Ya faɗa daƙyar, a haukace ya miƙe tsaye. Inda take ya ƙarasa a fusace ya kai mata wani wawan damƙa a allon kafaɗa, saboda azabar ya damƙi ƙashinta sai da ta saki ihu.

Ko a jikinsa ya hurga ta kan gadon. Ya bi bayanta ya danne.

A wannan dare... wani irin azabtaccen zuwa yayi mata, shi a wahale ita a wahale. Haka ta wage baki kamar ƙaramar yarinya ta dinga kwarara ihu a tsakiyar dare.

Bakin gurin ta sa wata nurse tayi mata kankara anyi mishi ɗinki na bala'i. Ko da aka bata zaɓin a tsuke ya zama kamar ta yʼar ashirin da biyar ko ashirin cewa tayi a tsuke kamar ta yʼar sha biyar.

Wannan ɗinki shi ne abinda yasa yayi mata fata-fata.

Shi kuwa Oga Mukhtar abinda ya wahalar da shi ba wannan bane. Ga dai bakin gurin a tsuke, amma can cikin a bushe yake ƙayau mayau, irin bushewar da ya dinga ji kamar ana yayyanka shi.

Amma saboda bala'in haushinta ya ƙi haƙura, sai da ya sauke a wahala, ya fice daƙyar, yana ja mata wani dogon tsaki...

Ya ke yʼar'uwata budurwa da matar aure? Zo kiji wani daddaɗan labari😘□□□□ Ko kin taɓa amfani da maganin infection ɗin da Zainab Maman Mujaheed take saidawa? Maganinta garanti trust ne in sha Allah! Ina tabbatar muku ya sha banban da duk wani maganin sanyi da kika taɓa amfani da shi. Ki gwada yʼar'uwata, za ki ji daɗinsa, za ki gode min, har ma ki shi min albarka. Domin siyan maganin cikin farashi mai rahusa a tuntuɓeta a wannan lambar □□ 0 816 285 9027

*_Aminci + Kʼarko Data Services_*

Kina/kana buƙatar Datar MTN, AIRTEL, GLO, 9MOBILE mai matuƙar aminci da ƙarko? Wanda za ki daɗe kina sauke abubuwa da kallace-kallace ba tare da yayi saurin ƙarewa ba?

Ga farashin datarmu a sauƙaƙe□□ ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai a tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online a kira ni ta 09077591726.

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Hallau muna tura katin waya, katin startimes, go.tv, e.t.c□□

Namu ba irin nasu bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*18*_

Daƙyar ya iya yin wanka saboda wani irin zafi da zuciyarsa ke masa. Yana fitowa ya zura kayansa, a gaggauce ya fice daga ɗakin.

Bai tsaya a falon ba, buɗe ƙofa yayi ya fice daga apartment ɗin ba tare da damuwar tsalawar da dare yayi ba. Lokacin ƙarfe uku da minti biyu na dare.

Duk da yana da tabbacin Fareeda ta daɗe da yin barci ɓangarenta ya nufa, ya murɗa hannun ƙofar ya ji ta a kulle. Ƙwanƙwasawa yayi a hankali sau biyu, a zuciyarsa yake jin rashin kyautawa, bai kamata ya tasar da ita a wannan lokacin ba.

To amma ya zaiyi ne? a wannan lokacin da ita kaɗai yake so yayi tozali ko zai ji sauƙin damuwarsa. Zai so ya rungumeta a ƙirjinsa, a hankali sai ya ja ta su zauna kan kujera ya cusa kanshi a ƙirjinta, ya dinga sauke ajiyar zuciya akai-akai. Idan yayi hakan yana da tabbacin zai samu sauƙi da rangwamen halin da yake ciki.

Tun yana ƙwanƙwasawa a hankali har ya fara bugawa da ƙarfi, amma ko kaɗan bai ji alamun za'a buɗe daga ciki ba.

Ga sanyi-sanyi a wajen na alamun ketowar alfijir, ga wasu bala'yʻayʻyʻun sauro da suka taso shi gaba da cizo haɗe da kuka wiiiii kamar an kunna jiniyar yʻan sanda.

Haka nan yaja sanyayan gwuiyawunsa irinna rashin samun abinda zuciya taso ya wuce ɗakin baƙi.

Duk abinda yake yi har ya fice daga Fatima tana jin sa, tana kwance inda ya barta, kuka take yi ƙasa-ƙasa na zallar baƙin ciki da takaici. Amma saboda rashin tausayi haka yasa ƙafa ya fice ya barta ba tare da ya bi ta kanta ba.

'Wannan wane irin mummunan baƙin dare ne yau take gani a idanuwanta? Idan ta tuno daki-daki yadda abin ya faru kawai sai ta ji hawaye sun sake ɓalle mata.

Bata taɓa tsammani ba, abu ne da bata taɓa tunanin zai faru ba. Tun shigowarta gidan duk abinda ta tsammaci faruwarsa na matsanancin farin ciki akasinsa ne ya faru.

Me yake faruwa ne haka? A ina ta kuskure a matakan da tabi tun fara neman aurenta har zuwa yau da ya kasance mummunan daren farko a gurinta?

Laifi ne don ta fi mayar da hankali kan gyaran ƙasarta a bisa gyara suɗaɗɗun mamanta? Laifi ne don ta kashe maƙudan kuɗaɗe domin amfani da magunguna da turarukan da za su taimaka mata wajen mallake Mukhtar da zuciyarsa?

Ganin tsanar ramarta ko tsanar yadda nonuwanta suka kwanta abu ne da bai taɓa faruwa tsakaninta da tsohon mijinta ba. A ko da yaushe lallaɓata yake yana gwada mata soyayya, suɗaɗɗun nan haka yake tattarosu ya damuƙa da hannayensa cikin rawar jiki da shauƙi, kuma daga yadda jikinsa ke ƙara ɗaukar harama a lokacin da yake taɓa ta za ta iya rantsewa da girman Allah duniyar shauƙi da jin daɗi ya faɗa ba akasinsa ba.

To me yasa bata ga irin wannan daga Mukhtar ba?

'Ke ma dai Fatima da wani zance, maza ai kala-kala ne. Wani namijin duk ramar mace ba ya damunsa, wani kuwa ko a ƙafa aka bashi ramammiya zai tsinke ya gudu.'

Amsa daga can cikin zuciyarta.

Ta ja shesshekar kuka sau uku, a fili ta ce

"Allah ya isa tsakanina da ke Ramlah! Babu yadda banyi da ke in sayi zumar ƙiba da naga ana talle a group na whatsapp kika hana ni.

Babu yadda ban nemi shawararki kan in sayi garin Sabaya da ake talle ba kika hana ni. Na nemi shawararki kan in fara dama kunun alkama da kunun gyaɗa ina sha tunda an ce suna taimakawa jiki ya murmure kika ce a'a!

Kika ce hakan da nake na fi kyawun kallo a matsayin abar sha'awa da burgewa, kuma ɗan zama na lokaci kaɗan za muyi Fareeda ta ragwaɓe ni kuwa ina nan ƙyam abar sha'awa. To ai ga irin ɗanyen madarar wulaƙancin da kika janyo min nan. Allah ya isa, wallahi Allah ya isa, muguwa kawai."

Sai ta sake fashewa da matsanancin kuka kamar wata ƙaramar yarinya.

Bata gane Mukhtar yagalgalata yayi ba sai da ta nemi miƙewa zuwa banɗaki. Saboda tsananin zafi da azaba bata san sa'adda ta buɗe baki da ƙarfi ta ƙwalla ihu ba.

Wani irin mugun azaba da raɗaɗi take ji, irin azabar da ko a daren farkonta bata ji shi ba. Ga yadda take jin gurin da yake a tsuke tunda aka yi mata ɗinkin ƴar sha biyar yanzu ya buɗe hayam shi ne abinda yake ƙara ba ta tsoro.

Fitsarin da ya matseta har tana jin kamar za ta sake shi kan gadon yasa dole ta ƙara motsawa da ƙarfi

"Wasssshhhhh! Wayyo Allah na zafiiiii.."

Ta ja kalmar zafin ta sauke shi da wani irin huci mai ƙarfi da gurgani kamar matar da naƙuda fara kankama mata.

Izuwa yanzu kukan ma ya ƙi zuwa, sai zare ido take yi kamar ƙwai a ledar biredi, lokaci ɗaya kuma tana haɗawa da cije laɓɓa saboda tsananin raɗaɗin da take ji, duk da fankar sama na ɗakin a kunne yake ta haɗa zufa tai kashirɓin.

Babu yadda ta iya, tana ƙarasawa gefen gadon da ta kasa sauka da ƙafafunta sai kawai tayi shahadar ƙuda ta faɗa ƙasa, daɓas haka tayi zaman ƴan bori.

Kasusuwan mazaunanta suka daki dandaryar tiles, wani marayan ihu ta ƙara sakewa a karo na ba adadi.

Ta ɗauki sakanni tana sauke numfashi sannan ta lallaɓa a hankali da rarrafe ɗaya biyu har Allah ya taimaketa ta ƙarasa banɗaki. Sai a lokacin magana mai harshen damon da nurse ɗin da tayi mata ɗinki ya dawo mata daram a zuciyarta, kamar a lokacin take faɗa mata.

"Kika ce inyi miki ɗinki ki koma kamar yarinya yar sha biyar?"

Sai da ta kaɗa idanu tayi fari da yalwataccen murmushi a fuskarta ta amsa da eh!

"Shi kenan! Tunda kin biya ni wadataccen kuɗi zanyi miki aiki har ma fiye da yadda kike tsammani. Amma fa ki sani, shi tsukewar gaban mace ya koma kamar ta budurwa idan tantanin budurci ya tafi a karo na farko ya tafi kenan har abada.

Ban ce baza ki tsuke ba, za ki tsuke tsam, don fatar ciki da ta waje duk zan haɗa in ɗinke miki tsaf! Amma kar ki ce ban faɗa miki ba, duk sadda Oga ya kawo kai zai shige gurin ba ƙaramin azaba za ki ɗanɗana ba.

Amma idan Allah ya taimake ki kika sami mai haƙuri zai ta lallaɓawa yana bi a hankali har ya samu nasarar shiga, duk da haka dai za ki sha wahala, amma ba sosai ba.

Idan kuwa kika samu jarumin maza mara haƙuri... Hmmm! Wallahi sai ya miki fata-fata, duk wani ɗinki da muka yi miki zai kekketa shi..."

"Aunty Nurse, kar ki wani damu. Ke dai kiyi aikinki yadda na ce. Daman a cikin yaƙin ƙwato ma kai daraja ta musamman dole sai an sha wahala. A mai haƙuri ko mare haƙuri na tarar da Aban twince zan jure ƙwarai don in ƙara samun tambarin jarumar mata a zuciyarsa.

Idan komai ya kammala nasan ba ƙaramin tarairaya da gata zan gani a wannan dare ba, saboda ya tarar da ni a yadda bai taɓa tsammani ba"

Wasu zafafan hawaye ne suka sake silalo mata da zuwa ƙarshen tunaninta.

Kamar wacce ta haihu, haka tai ta tara ruwa mai zafin gaske tana shiga ciki, duk azaba haka ta jure.

Fiye da sau takwas tana canza ruwan ƙafin Allah yasa ta fara jin dama-dama. Ta gwada miƙewA tsaye taga ta miƙe, ta gwada tafiya taga tana yi a hankali, duk da ƙafafunta a tattale suke kamar ta ɗan shayi ai babu laifi, matar da a ɗazu ta kasa tafiya, yanzu da take yi ko a bobbotsere ne ai ta gode Allah.

Balle ma tana saka ran yinin da za tayi yau tana shiga ruwan zafi zuwa dare komai na jikinta zai koma yadda yake. Idan yaso ma a sake zagaye na biyu.

Yo miye a ciki? Wannan ai shi ne auren. Gara ta lallaɓa ta koyi juriya, so take su gogu ita da Aban Twince, su murzu sosai a cikin kwanaki ukunta na amarci. Tunda wancan yar buƙulun ta ƙi ƙara musu kwanaki.

***

Lamo yayi akan katifa kamar mai zazzaɓi, saboda tsabar damuwa da tunanin da yayi masa yawa ya kasa janyo filo a gefensa ya ɗora kai. Hannayensa biyu yayi matashin kai da su, ƙwayoyin idanunsa na kallon sama, a kallon farko sai ayi tsammanin ƙirga layin PPC da aka sa a saman ɗakin yake yi, amma ba haka bane, tsananin nisa a cikin tunani ne.

Surar jikin Fatima kamar hoton da aka maƙala a duk inda ya juya idanunsa, sam ta ƙi ɓace masa a cikinsu.

Mamaki yake yi, mamaki mai tsanani ƙwarai. Wai don Allah me ya shiga cikin nutsuwa, hankali, da idanunsa har ya kasa gano ramar Fatima? Yadda yake gogagge kuma wayayyen matashi ai ya kamata ko a ido ya iya banbance kayan kanti da na shago.

Bazai manta wani abokinshi Sunusi da yayi aure shekaru uku baya ba. Ya auro wata yarinya a ƙauye ramammiya sosai, saboda ramewarta shi yayi tsammanin sikila ce.

Tunda Sunusin ya tabbatar mishi ba sikila bace haka yanayin jikinta yake ya tasa shi gaba da tsokana da dariyar mugunta.

Minti ɗaya biyu sai ya kalli Sunusin yana ƙyalƙyala dariya ya ce

"Kai kuwa Sunusi don Allah me ka gani a jikin wannan lamba One ɗin? Kana ganin mace ko a cikin kaya ba tsoka ba alamar tsoka ina ga ta tsaya zir a gabanka? Kƙarmanjola kenan"

Sai ya sake kwashewa da mahaukaciyar dariya ya cigaba da nuna Sunusin da yatsa, a lokuta da dama har ƙwalla yake yi saboda dariyar mugunta.

Ashe shi ma yana da rabon auren irin wannan matar a rayuwarsa? Ku gane Shi fa ba ramammiyar mace ne ba ya so ba, amma a gaskiya ba ya son macen da ramarta ya cika yawa sosai ɗinnan.

"Fatima kin ha'ince ni."

Ya sake faɗa a karo na biyu zuciyarsa na ƙara ƙuntata.

Wani abu ne ya faru a yanzu da ko a cikin tarihinsa na baya bazai ce da wayonsa ga sadda abin ya faru ba, wannan abu ba komai bane face fitowar wasu yan ƙananun ƙwallah a idanunsa.

Ya runtse idanunsa da ƙarfi, ƙwallar suka gangara gefe da gefe har cikin kunnuwansa, zuciyarsa cike da addu'ar Allah yasa barci ya ɗauke shi ko zai samu sauƙin tunanin da yake yi, barcin bai zo ba ya ji ladanin unguwarsu ya kwaɗa kiran sallar farko.

****

Ko da ake cewa ba'a iya barci a daren da aka tabbatar miji yana can zai haɗa shimfiɗa da wata macen ita kam yau an samu akasin lissafi a kanta.

Tunda suka fice da zantukan rainin wayonsu suka barta cikin ƙunci, tai takwa-takwa da fuska za ta fara hawaye da sauri ta haɗiye kukan.

'Kukan me za kiyi kuma Fareeda? Bayan aikin gama ya riga ya gama?'

Ƙoƙarin tattare tunaninsu tayi ta ajiye a gefe ɗaya. Taje ta rufe ƙofar falonta, ta dawo ta faɗa banɗaki ta ɗauro alwala, tana ji ya dawo yana ƙwanƙwasa ƙofa taba banza ajiyarshi. Ta shimfiɗa dadduma tayi shafa'i da wutiri.

Ya ke yar'uwa mai karatun wannan labari, ina baki shawarar ki saki kowa ki kama Allah. Kar ki kuskura ki manta da Allah a lokacin farin ciki ko ƙunci. Shi fa Ubangiji ako da yaushe ƙofofin rahamarsa a buɗe yake, jira yake kawai bawa ya roƙa da ikhlasi ya amsa masa. A duk sa'adda kika dogara da Allah mafificin dogaro na haƙiƙa kuma da zuciya ɗaya tsarkakakkiya tabbas addu'arki za ta dinga amsuwa kamar yankar wuƙa. Idan kuma ba abin alkairi bane kike roƙa Allah zai sanyaya miki zuciya, ya cire miki damuwa da son ganin biyan buƙatar da gaugawa, a sannu a hankali sai ya canza miki da mafi alkhairi. Ko da duk duniya maƙiyanki ne aduk lokacin da suka nufo ki da yaƙi Ubangiji shi zai tare miki. Ko ba'a so ana ji ana gani za kiyi ta cigaba, a rasa ta yadda aka yi duk wani mugun abu baya samunki. Dogaro ga Allah yayi yan'uwa, ku gwada za kuga alkhairi.

A wannan dare bayan ta idar da shafa'i da wuturi, ta ɗauki lokaci tana istigfari, hailala, tasbihi da godiya ga Allah kan ni'imomin da yayi mata.

Abu uku ta daɗe tana roƙa, abu na farko ta samu nannauyan barci a wannan dare, na biyu Allah ya cire mata damuwar Mukhtar na can kwance da tare da Fatima. Na uku ta roƙi Allah yasa duk ni'imar da Mukhtar zai ɗanɗana a jikin Fatima kar ya ɗanɗani ko kwatan wanda yake ɗanɗana a jikinta.

Bayan ta gama addu'o'in ta bi lafiyar gado, ta kwanta ta tasa yaya anta a gaba ta rungume su. Tana hammar barci ta janyo wayarta ta kunna ƙira'ar Sudais cikin suratul Baƙara, ta daidaita ƙarar wayar baiyi yawa ba baiyi kaɗan ba ta aje wayar, ta lumshe idanunta tana sauke numfashi cikin nutsuwa.

Wani nannauyan barci ne yayi awon gaba da ita irin wanda ta daɗe rabon da tayi irinsa. Fitsari bai tashe ta ba, yaya anta biyu da Hajiya ta ce ta dinga saka su fitsari cikin dare basu tashe ta ba, kuma basuyi fitsarin kwancen ba. Duk ƙara irinna alarm ɗin wayarta da yake bugawa ƙarfe huɗu na dare sam bata farka ba. Ta farka ne a daidai lokacin da Ladan ya tada iƙamar sallar asubah.

Cikin nutsuwa ta farka da salati a bakinta, da farko kamar a mafarki take ji an tayar da sallah, sai da ta ƙara saurarawa sosai sai taji da gaske fa sallah ake yi.

Sai ta miƙe a firgice tana taɓa wandunan yaran, ko da taji basu tsula ba ajiyar zuciya ta sauke. Ta ɗauke su ɗaya bayan ɗaya takai su bayi suka yi fitsari, bayan ta sake kwantar da su ta koma bayi ta ɗauro alwala.

Zuciyarta sakayau, babu nauyi balle damuwa ko kaɗan, ta ma manta da Mukhtar balle wata Fatima karan kaɗa miya.

Cikin nutsuwa ta gabatar da sallar raka'a tanilfijr sannan ta gabatar da sallar asubah! Bayan gama tasbihi tayi azkhar, ta ɗauki lokaci mai tsawo tana karatun Alƙur'ani mai girma, har gari yayi haske sosai bata kammala ba, kwatsam taji ana ƙwanƙwasa mata ƙofar falo.

Sai da ta kai aya sannan ta miƙe a nutse da hijabin jikinta taje ta buɗe ƙofar.

Yana shigowa da wani irin zafin nama ya kai mata wawuyar runguma.

Kasancewar tana ankare da shi, matuƙar ƙoƙari tayi gurin gocewa ya rungumi iska. Cikin wayancewa da ƙwarewa a iya basarwa ta ja da baya a tsorace, ta zazzaro idanu waje, hannayenta biyu dafe da ƙirji ta ce

"Oga Lafiya?"

"Lafiya ƙalau"

Ya amsa da wata shaƙaƙƙiyar murya. Kafin ta ce komai ya sake cewa

"Miye haka? ina ƙoƙarin riƙe ki kin wani zille"

"Da alwata ta."

Ta faɗa kai tsaye.

"Me ya haɗa riƙe kin da zanyi da alwalarki...?"

"Oga mana, ka san kai ɗin fa ba dama ne. Alwalata zai iya karyewa daga riƙon da kake mishi kallon ba wani abu bane"

Ta ƙarasa haɗe da kashe mishi ido ɗaya.

"Ina kwana Angon Fatima? Ina fatan ka tashi cikin ƙoshin lafiya kai da amaryarka?"

Da murmushi sosai a fuskarta ta gaishe shi, har tana ɗan duƙawa a ƙasa.

Ya buɗe baki zaiyi magana buff aka buɗo ƙofar falon, a tare su biyun suka kai idanunsu kan ƙofa, wa za su gani?

Fatima ce tsaye ta riƙe ƙugunta da hannu biyu. Ta sha kwalliya sosai, ta fito a amaryar turawa sak! Domin kuwa ta tsuke ne cikin wani matsattsan wando wanda da kaɗan ya ɗara gwuiwarta da yar fingilar riga.

Ta yi amfani da kayayyakin cikonta gaban da bayan sun taso ɗam-ɗam gwanin ban sha'awa.

Lokaci ɗaya Mukhtar ya fara harhaɗe girar sama da ƙasa zai ɓalle tsiya, daman kwana yayi da masifaffen haushinta a ransa.

Lura da hakan da tayi cikin kissa da iya ƙwarewa a ladabi ba don Allah ba sai don tura ma wata haushi da saurin gaske ta zube a gabansa gwuiyawunta a ƙasa.

Kamar an buɗe famfo sai ga hawaye shar! shar!! Bakinta na rawa ta ce

"Allah ya baka haƙuri Haskenah. Don Allah don Annabi kayi haƙuri, Allah ya huci zuciyarka. Yunwa, yunwa ce ta fito da ni har linzamin tunanina ya ƙwace na faɗo muku kai tsaye ba tare da sallama ba. Haskenah, ɗan abinda na ci jiya da daddare duk ya gama tsiyayewa..."

"Ke dallah saurara min kina ta wani zuba shaaaa kamar kanyar da ba zaƙi. Kije ɓangarenki ki dafa ruwan zafi, zan taho miki da kayan tea da biredi."

Yayi maganar a gundure, fuskarnan a ɗaure tamau.

Cikin nutsuwa Fareeda ta juya zuwa cikin ɗakinta, kwatsam ta tsinkayi muryar Fatima a raunane tana cewa

"Ko za ka yi ma Aunty Fareeda magana ta sammin ruwan zafi..."

"Saboda me? ita ɗin baiwarki ce?"

Ya jefa mata tambayoyin cikin tsawa.

Sai da ta sunkuyar da kanta ƙasa, a yanayi na muzanci da jin kunya ta ce

"Dama... dama... dama... ba ni da gas ne. Ban samu sararin sayen gas ba, abin girki da gawayi na zo da shi kuma babu gawayi."

Mukhtar da ya tsani tsaki a yanzu ƙarfi da yaji yawan tsakin na nema ya aure shi. Wani dogon tsaki yaja ya galla mata harara, ko kaɗan kwalliyarta bata burge shi ba, domin ya ga gaskiyar abinda ake rufewa wannan kwalliya duk bula ce.

Fareeda na gaf da shigewa cikin ɗakinta ya kira sunanta a tausashe.

A hankali ta juyo ta zuba manyan idanunta cikin nasa.

Ƙoƙarin tausasa maganar da zaiyi yayi, ba don komai ba sai don kar Fareeda ta ji babu daɗi.

"Ko kina da ruwan zafi a flask ki sammata? kin ji ba ta da gas sai abin girkin gawayi..."

"Idan ka fita ƙofar gida, nan ɓangarenmu gida na huɗu a hannunka na hagu suna sayar da gawayi. Suna ƙulla na hamsin da ɗari, kwatan buhu, rabin buhu, buhu guda zuwa buhu ashirin duk suna sayarwa.

Ka siyo mata gawayin kawai. Ni wallahi shigowarka ce ta fito da ni falo, karatun Alƙur'ani nake yi. Don Allah kar ka tilastani ba ta ruwan zafi alhalin ba hakkina bane."

Cikin ɗakinta ta shige ta barsu a gurin.

Mukhtar da Fatima suka rakata da idanu har ta ɓace ma ganinsu.

Fareeda ce tayi maganar, amma Allah ya sani haushin Fatima ya ƙara ji a zuciyarsa. Tana tsugunen nan yayi mata wata muguwar damƙa a kafaɗarta ɗaya ya miƙar da ita tsaye, kafin ta gama daidaita tsayuwa ya finciketa da ƙarfi suka fice daga falon, tana wash-wash saboda ciwon da yaji mata amma bai saurara mata ba sai da suke je falonta, ya watangarar da ita ta tafi taga-taga za ta ci da baki da saurin gaske ta dafe hannun kujera, idanunta a warwaje saboda bala'in tsoron da ta ji.

Zee Maman Mujaheed mai sayar da ingantaccen maganin sanyi za ta sauƙaƙa kuɗin sayen maganin don faranta zukatan kwastomominta□□

Promo! Promo!! Promo!!! A baya tana sayar da maganin 4k ne. A yanzu ta sauƙaƙa shi zuwa 2k. Za ta rufe wannan garaɓasar ne a cikin sati ɗaya kacal! Yʻar'uwa me kike jira? Maganin nata ya samu shaidar aiki ingantacce kuma da gaugawa ake ganin biyan buƙata in sha Allah. Idan kina fama da ɗaya daga cikin waɗannan matsalolin ina mai baki shawara kiyi gaugawar siyan maganin Zee Maman Mujaheed□□

Ciwon gabobi, ciwon mara, fitar farin ruwa, kaikayi gaba, rashin Sha'awa, rashin kuzari gare ki ko ga namiji, rashin ni'ima, rashin haihuwa, kurajen jiki ko na gaba, jin Zafi yayin saduwa. Maganinta cikin sauƙi kuma a gaggauce yake magance duk waɗannan matsalolin. Ki tura kudin

maganin ta wannan account ɗin da ke ƙasa, sai ki tura mata shaidar biya da garin da kike ta lambar wayarta□□0 816 285 9027 Ga kuma acc ɗinta□□

3968303018

Zainab Shu aibu

Fcmb

Jinjina ga makaranta labarin Rabon Ayi aduk inda kuke a faɗin duniya□□□ ina maraba da gyara, sharhi, ƙorafi ko shawarwari ta whatsapp a lambar wayata□□ 07039080978. Masu sayen data ma su tuntuɓeni ta kan lambar, idan kuma ba ni a online ku kira ni kai tsaye ta wannan lambar 09077591726. Son ƙauna😘😘😘😘

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*19*_

Ya daɗe tsaye yana sauke zafafan numfashi a tsakiyar falon. Idan ya kalleta, sai ya kalli cikin falon ya sake kallon irin kujeru da labulayen da ta zuba, waɗanda ko makaho ya laluba ya san ba masu tsada bane.

Da sassarfa ya taka ya shige kicin ɗin, wani jiri da ya nemi kayar da shi da saurin gaske ya rirriƙe Cabinet da hannu bibiyu, yana ta sauke numfashi sama-sama.

Yʻan kayayyakin kicin ɗin da ta zo dasu duka-duka ga su nan babu yawa, idan aka tattara su duka baza su cika buhun suger ba, idan kuwa sun cika baza su taɓa fin buhun suger ba.

Kuloli masu sauƙin kuɗi guda biyu, sai farantan cin abinci dozen ɗaya, kwandon kifa wanke wanke, kwandon tsane shinkafa, tukwanen tower guda uku, jug da ƙananun kofunansa, tarkacen cokula da ludaya, bahon wanka babba da ƙarami, bokiti guda biyu, sai wasu manya kofuna na ɗidan ruwa, ga abin girkin gawayi nan babba da ƙarami ajiye a gefe guda. Ko flask Allah baisa idanunshi sunyi katarin hangowa ba.

Da wani irin sanyin jiki da na gwuiwa ya fice daga kicin ɗin ya koma falo. Tana tsugune a inda ya barta, irin yadda take zare idanu ya tabbatar mishi a balaʻin tsorace take, kamar ya ce kyat! ta zura da gudu.

Kujerar da ke kusa da ita ya laluna ya zauna a hankali, yayi tagumi da hannu bibiyu yana kallonta. Can dai ya buɗe baki daƙyar, muryarsa na fita a hankali ya ce

"Fatima!!! me yasa kika yi min ƙarya?"

"Banyi maka ƙarya ba! Wallahi banyi maka ƙarya ba!! Na rantse da Allah banyi maka ƙarya ba!!! Haskenah don girman Allah kayi haƙuri..."

Ta jero maganganun cikin sauri tare da saukar wasu zafafan hawaye a idanunta. Laɓɓan bakinta sai rawa suke yi saboda tsananin tashin hankali.

Kallonta yake yi, mamakinta yake yi da har ta iya rantsewa da girman Allah bata yi mishi ƙarya ba.

Ya sauke ajiyar zuciya, ya gyara zama ta hanyar miƙar da ƙafafunsa, ya kalleta, ko kaɗan kukan da take yi bata bashi tausayi ba.

"Satin da ya wuce, ina gurin aiki kika kira ni da zancen ga ki a kasuwan barci. Da na tambaye ki me kika je yi kika ce min dubu ɗari uku ne kika je rage siyayyar kayan kicin, ga shi kinyi siyayyar kuɗin hannunki sun ƙare gaba ɗaya babu kuɗin da za ki biya me motar da zai ɗaukar miki kaya. A take na tura miki da dubu goma kuɗin mota. Anyi haka ko ba'a yi ba?"

Hawayenta ne suka ƙara ƙarfin sauka, a kasalance ta zame daga tsugune ta zauna a ƙasa. Ta saukar da idanunta ƙasa sosai ta amsa da

"Anyi haka! Kayi hakuri, dubu hamsin ne naje siyayyar da su ba dubu ɗari uku ba. Tabbas anan na faɗa maka ba daidai ba..."

"Kin kuma yi min ƙarya ta hanyar kwaɗaita min za ki sai mana kayan ɗaki masu ƙoluluwar tsada. Tsakani da Allah ni kuma na saka rai, saboda ɗabi'a ce irinta ɗanAdam duk sa'adda aka ce za'a yi mishi wani abu dole ya saka rai.

Sai yanzu kawai na ganki da waɗannan sakarkarun kayayyakin da a kallonsu kawai za'a gane na hannu ne. Saboda Allah Kin san ba ki da kuɗin sayen kaya masu tsada me yasa kika ce min za ki siya?"

Lallai baki shi ke yanka wuya, a wannan gaɓar ta kasa magana, ina ma ƙasa za ta tsage ta shige don kunya?. A zuciyarta ta tsine ma yar mijinta da ta sa aka raba gado kuma aka hana ta kason yayanta ya fi sau ashirin.

Da ta rasa abinda za ta ce don kare kanta sai kawai ta ƙara ƙarfin kukanta, daga sharƃen hawaye zuwa jan shessheƙa da jiniyar kuka ƙasa ƙasa.

"Kinga, Fatima ni ba na son ƙarya. A rayuwata na tsani ƙarya, na tsani maƙaryaci. Sam Fareeda ba ta min ƙarya, za ta faɗa min gaskiya ko da ɗacin gaskiyar zai sa in kwana in yini in ɗauki tsawon sati biyu ina mata masifa.

Haka kuma na tsani yaudara da munafunci. Waɗannan munanan halayen guda uku wallahi na tsane su, na tsani masu yin su.

Kin ga daga fara tafiyarmu da har yau bamu yi wata biyu ba, kinyi min ƙarya ta hanyar kayan ɗaki, abinda kika ce za ki zo da su ba su na gani ba.

Kin yaudare ni ta hanyar yin ciko na abubuwan da ko kusa ba ki da su. Fisabilillahi me yasa za kiyi haka? Da kika ga da gaske aure za muyi me yasa ko sau uku ne baki fito babu kayan ciko don in ɗan fahimci yadda kike kamar 1 a cikin riga ba?

Bazan ƃoye miki ba. Wallahi raina yayi bala'in ƃaci kan wannan yaudarar da kika yi min. Ki auna lamarin ke a karan kanki, da ace ni ne nayi miki ƙaryar ina da wani abu sai da muka yi aure kika tarar ba haka ba fa?

Wannan yaudarar da kika yi min da zan kai zancen kotu tsaf alƙali zai raba aurenmu, saboda nayi hidimar mallakar wayar Samsung ne na tsinci waya rakani banɗaki a cikin kwalin Samsung ɗin da aka bani. Alƙali zai tilasta ki duk da wani abu ya shiga tsakaninmu zai sa ki biyani kaf abinda na kashe na hidimar auren ki..."

"Kayi hakuri! Don Allah kayi haƙuri. Kar ka kai ni kotu, don Allah kar ka bayar da dama a raba aurenmu. Mukhtar wallahi tallahi ina son ka, irin tsananin soyayyar da babu wata yɑ mace da ta taƃa gwada maka irinsa, ka bani dama ko ɗan yaya ne, wallahi zan yi maka biyayya kamar baiwa da ubangidanta! Duk abinda kake so zan so shi ko da zuciyata ba ta so.

Don Allah kar ka sake ni. Bazan sake yi maka ƙarya ko yaudara ba, nayi maka alƙawarin wannan."

Ta ƙarasa maganganun tana rusa kuka gwanin ban tausayi, zuciyarta sai wani irin bugawa take yi fafafat!

Kalmar rabuwa tsakaninta da Mukhtar kalma ce da ko a mugun mafarki ba ta fatan ya taɓa wanzuwa. Idan ya sake ta ina za ta jefa kanta? Magauta za suyi mata dararraku ba dariya ba. Ko a gurin Fareeda da mutanenta ai ta shiga uku, ƙaryarta ta ƙare.

"Hmmm! Allah yasa hakan! Ni dai na faɗa miki ki kiyaye. Kin ganni nan ba ni da haƙuri ko ƙanƙani, ɓarna dubu gyara dubu. Kamar kunama nake a taɓa ni ko da kuskure ne aji ɗau! Idan kina son zamanmu ya ɗore lafiya ki kiyaye duk abinda zai janyo mana saɓani."

Yana gama faɗin haka ya miƙe tsam ya nufi hanyar fita daga cikin ɗakin, har ya kusa bakin ƙofar sai ya dawo ya tsaya daidai ƙafafunta, ya nuna mazaunanta da ƙirjinta da yatsarsa manuniya.

"Sannan cikon da kike yi anan da can kar ki kuskura ki ƙara yi min amfani da su a gidannan. Ki tsaya a iya halittar da Allah ya baki.

Kashaidi na ƙarshe da zanyi miki akan ciko kenan. Na hana daga yanzu, ba na so, ruwanki ne ki nemi magungunan da za su sa ki ɗanyi kumari, ruwanki ne ki tsaya a bushe. Ciko dai na hana daga yanzu. Ke ni ko sha ka fashe za ki nema can matsalarki, ni dai kar ki kuskura ki ƙara yi min kwalliya da kayan da ba naki ba. Na faɗa miki!!"

Bai jira ko za ta ce wani abu ba ya fice daga ɗakin.

Ya so yaje ɗakinshi na ɓangaren Fareeda yayi wanka, amma haka nan ya haƙura. Ya shiga motarshi ya fice daga gidan.

Yʻan kuɗaɗen da suka rage masa a cikin acc ya cire ya shiga kasuwa, dangin kayan abinci ya loda babu laifi, duk wani abu da yasan mace za ta nema wajen yin girki ya saye shi.

Sai da ya gama siyayya tsaf sannan ya sai ma Fatima ƙaramin gas, 6kg. Ya sai mata ƙaramin flask, yaja motarsa zuwa gida.

Bayan ya ajiye motar ɓangaren Fareeda ya wuce. Ya tarar da ita cikin yʻayʻanta sun sha kwalliya gwanin ban shaʻawa. Suna zaune akan teburin cin abinci suna karyawa, dankalin turawa ne da soyayyen ƙwai, ga kofin tea a gaban ko wannensu.

A gefe guda kuma ga faranti nan shaƙe da dubulan da alkali, irin yadda suka yi kyau a ido kawai sun isa bayyana irin daɗin da za suyi a baki.

Da sauri yaran suka tashi suna mishi Oyoyo. Har ƙasa ya durƙusa ya rungume su yana shaƙar daddaɗan ƙamshin turaren da suke fitarwa a jikinsu.

"Abee ina kwanna"

Suka haɗa baki gurin gaishe shi da muryarsu na yarinta.

Cikin jin daɗi ya amsa musu sannan ya ja su zuwa kan teburin.

"Iyyeee! Madam irin wannan kayan daɗi haka babu ko tayi?"

Ya faɗi haka idanunsa cikin na Fareeda, fuskarsa taf da murmushi. A zuciyarsa yake yaba irin kyawun da tayi cikin doguwar rigar atamfar da ke jikinta.

Sai da tayi faree da idanu da murmushi a fuskarta ta amsa mishi

"Haba Oga! Kai da ke da Amarya ai kayan daɗi sai dai a gani a gurinku. Mu kam abinda ya samu ne kawai muke ɗan lasawa don mu kauda tsamin baki."

Idanunsa idon alkaki sam ba ya wuce tayi, a yanzu ma hannu ya miƙa ya ɗauki guda ɗaya yakai baki ya gutsura. Lumshe idanu yayi yana jin wani irin garɗi da daɗi da ya ratsa bakinshi gaba ɗaya,

"Ummmn! Gaskiya duk wacce tayi alkakinnan ta cancanci a bata tukwuici. Ba ƙarya ta iya."

"Kai dai santi kawai kake yi Oga, bari in saka maka waigi..."

"Da gaske nake fa."

Yana gama cin na hannunsa ya sake ɗaukar wani. Sannan ya fara faɗa mata abinda ya kawo shi.

"Kayan abinci ne na siyo, ina so a ɗiba ma Fatima ta ajiye a gurinta, sauran sai ki ajiye anan! Tunda yanzu ga yara na san cin abincin zai ƙaru sosai akan na da."

"Haka ne! Allah ya ƙara buɗi da arziki mai albarka."

"Idan kin gama muje ki gani mana."

Bata gama ba, amma saboda ba ta son ya cika daɗe mata a gurinta sai ta miƙe tsaye.

Su Shahid ma suka miƙe da sauri ganin iyayen za su fita su barsu su kaɗai.

"Abee"

Sayyid ya faɗa yana ɓata fuska alamun zai saka kuka.

Da sauri ya dawo ya ɗauke shi, ya riƙe hannun Shahid suka nufi ƙofar fita daga falon.

Suna fita suka tsaya jirab fitowar Fareeda, tana fitowa suka jera, tafiya suke cikin nutsuwa zuwa gurin motarsa.

Sayyid da aka ɗauka sai surutu yake yi yana ba uban labari, iyayen fuskokinsu cike taf da murmushi, a kallonsu kawai za'a gane kyakkyawan iyali ne da suke cike da farin ciki.

Fatima tana tsaye kan kujera tana gyara ƙarfen labulenta na gurin window, ɗan lanƙwashewa yayi kamar zai karye. Shi ne ta taka kujera ta hau tana ƙoƙarin gyarawa, kamar ance ta kalli harabar gidan, kwatsam idanunta suka yi kyakkyawan gani.

Saboda tsananin firgici da baƙin cikin da lokaci ɗaya ya turnuƙe zuciyarta ƙiris ya rage ta faɗo ƙasa, Allah ya taimaketa tayi saurin faɗawa kan kujera.

A maimakon kuma ta nema ma kanta salama ta hanyar wucewa daga gurin ta daina kallon abinda ke ƙona mata zuciya, sai taja ta tsaya. Ta buɗe labulen sosai tana kallonsu, zuciyarta sai tafarfasa take yi da kishi da baƙin cikin Fareeda.

Ta kalli yadda tayi kyau cikin doguwar rigar jikinta, fuskarta babu kwalliya sosai amma ko maƙiyinta bazai ce bata yi kyau ba.

A daidai lokacin Shahid ya ɗauki wani abu da bata san ko menene ba a cikin boot ɗin motar Mukhtar ya ruga da gudu, a yangace Fareeda ta bishi da ɗan gudu-gudu da niyyar ta kamo shi, a fili take kallon yadda mazaunanta sai saɓar saɓar suke a cikin riga.

Ƙanƙance idanu tayi sosai ranta yana ƙara ɓaci, a hankali ta miƙa hannu ta shafo nata shafaffun mazaunan, sai taja tsaki.

Ganin yadda Mukhtar yayi wani dagalo yana bin Fareeda da kallo yadda suke ta zagaye motar ita da ɗan, shi yaƙi tsayawa, ita kuma ta ƙi daina bin shi. Sayyid da Mukhtar sai dariya suke musu.

Ita kuma Fareeda sai tura baki take yi a shagwaɓe tana bin yaron tana maganar da sam ba ta jin me take cewa.

"Sakarya kawai wawuya."

Ta faɗa cikin jin haushi. A zuciyarta ji take kamar ta janyo Fareedan ta zauna a ruwan cikinta tai ta ɗibga saboda baƙin cikinta da takaicinta.

Caraf taga Mukhtar ya cafke yaron, ya amshi abin hannunsa ya miƙa ma Fareeda, ta karɓa tana ƙara tura baki haɗe da ɓata fuska.

Tana ganin yadda Mukhtar da yʻayʻan suka haɗa hannuwa alamun bata haƙuri suke yi.

Ita kuma ta ɗan kama kumatun yʻayʻan biyu ta ja, ta aika ma Mukhtar hararan wasa sannan ta saki murmushi. Hannun yʻayʻan ta kama suka ja da baya.

Mukhtar ya fara fito da kayayyakin abinci daga cikin boot ɗin. Tana tsaye tana ganin yadda Fareeda take nuna mishi yana ajiyewa guri daban daban har ya gama fitar da kayan boot ɗin gaba ɗaya.

Ya buɗe kujerun baya ya fito da gas da kwalin ƙaramin flask ɗin. Kusa da Fareeda ya matsa da su ya ce

"Kiyi haƙuri Madam! Na san yanzu haƙƙoƙin duk ku biyun ya rataya a wuyana ne. Amma ni a ganina babu laifi don ka sai ma wacce ba ta da abu wani abin da bai taka kara ya karya ba.

Kamar yadda kema wata rana zan siyo miki abinda kike buƙata ba tare da na sai mata ba. A ganina wannan shi ne adalci. Babu laifi ko?"

Murmushi tayi, kuma ko kaɗan bata ji ba daɗi a ranta ba. A ganinta yadda ya faɗa ɗin shi ne adalci na gaskiya, tabbas itama wani lokacin za ta buƙaci abinda zai sai mata ba tare da ya haɗa da Fatima ba.

"Babu komai Oga. Allah ya ƙara arziki."

Martanin murmushinta ya mayar mata sannan ya ajiye Gas da flask ɗin a gurin kayan abincin da ba shi da yawa.

Izuwa wannan lokacin ɓacin rai da baƙin cikin Fatima ya kai ƙololuwa, ta kasa daure ma zuciyarta. A fusace ta ɗauki tsintsiya da abin kwashe shara ta buɗe ƙofar falonta ta fita waje, cikin hikima ta fara yɗan kakkaɓe kakkaɓen dattin gurin, alamun dai shara za tayi.

Mukhtar na juyawa zai fara kwasar kayan abinci mai yawa zuwa ɓangaren Fareeda sai ya hangi Fatima tana shara.

"Fatima, Fatima, Ke Fatima"

Ba tare da wani yanayin ƙauna ko girmamawa ba ya buɗe murya ya dinga ƙwala mata kira.

Bata amsa ba, sai ɗagowa da tayi a fusace ta zuba mishi ido.

Hannu yasa ya yafito ta, ya ƙara da cewa

"Zo nan"

Tsintsiya da abin kwashe sharar ta ajiye gefe ɗaya, ta fara tafiya a ɗan tattale ta nufi gurinsu tana wani nannarke idanu.

Kallo ɗaya Fareeda tayi mata ta kawar da idanunta daga kanta.

Yanzu ta canza kayan jikinta, daga na turawa zuwa leshin akwatinta da ta ɗinka tayi fitar biki. A cikin kayan turawa babu cikon da Mukhtar ya hana ta sakawa sosai ramarta ke fitowa, shi yasa ta yi ma kanta ƙiyamullaili ta canja kayan, ko babu komai kaurin leshi zai hana ramar armashi a idanun mai kallonta.

Akan kayan abincin da suke rabe ta fara sauke idanunta, cikin ladabi ta ɗan duƙa ƙasa ta ce

"Haskenah barka da dawowa. Ga ni."

Bai amsa ba sai nuna mata kayan abincin da bai da yawa yayi ya ce

"Ki ɗauki abinda za ki iya cikin kayayyakinnan kije da su ɓangarenki. Idan na shigar da waɗannan zan shigo miki da ragowar."

Kafin ta amsa sai da ta sauke idanunta akan wancan kayan mai yawa da yake ajiye gefen Fareeda, ta haɗiye wani maƙwallato na ɓacin rai.

Ta ƙaƙalo murmushi ta sakar ma Mukhtar, ta durƙusa har ƙasa ta ce

"Na gode Haskenah. Allah ya saka da alkhairi. Allah ya ƙara buɗi, Allah ya jiƙan Babanmu ya ƙara ma Hajiyarmu Lafiya, Allah ya..."

"Ameen! Ameen!! Ameen!!!"

Ya katse ta da sauri. Umarnin miƙewa tsaye yayi mata.

Har ya sunkuci buhun shinkafa a kayan da zai kai ɓangaren Fareeda kamar wanda aka matsa bakinshi sai ya kalli Fatima ya ce

"Daga yau kar ki sake durƙusa min gwuiyawunki a ƙasa. Malamai da yawa sun haramta haka, kuma ko ba haramun bane ni ba na so!!"

A tare mata biyun suka bi shi da kallo. Fatima kallo ne take mishi na rauni da kunya haɗe da takaicin gwasaleta da ya tsiri yi yau a gaban Fareeda. Ɗazu yayi mata, yanzu ma ya ƙara wani, idanunta ne suka cicciko da hawaye.

Ita kuwa Fareeda kallo ne take mishi na yadda a wasu lokutan ba ya iya tauna magana, sakinsu yake kamar ya ci kashi. Fisabillahi ina daɗin irin wannan? Tunanin ba abinda ya shafeta bane yasa ta watsar da abin a ranta ta kawar da kanta gefe ɗaya.

Itama Fatima ba yadda ta iya haka ta mutsuke idanunta, ta ɗauki ƙananun ledojin da suke cikin cefanenta taja ma Fareeda dogon tsaki ta wuce tana karkaɗa yʼan ƙananun mazaunanta. Ko ta manta babu ciko ne oho mata!!

Ita Fareeda abin ma dariya ya bata, ta bi Fatiman da kallo tana jinjina ƙarfin halinta. Ita ta rasa gane wannan al'amari, ita ce ya kamata tayi mahakacin kishi da Fatiman da bata duba sanayya ba ta aure mata miji ko kuwa ita Fatiman ce ya kamata tayi mahaukacin kishi da ita?

Ko da ta ƙara kallon bayan Fatiman taga yʼan ɗuwaiwakan da take kaɗawa ta kasa hana kanta darawa.

"Ke kuma da wa kike dariya?"

Mukhtar da ya isa gurin hannunshi riƙe da alƙaki yana taunawa ya tambayeta.

"Kai dai Oga kana da son jin magana. To Ni da matar mijina ne"

A tare ita da shi suka sake kallon Fatima da take gaf da isa ɓangarenta, har lokacin kuma bata canza yanayin tafiyarta ba.

Da ɗan ƙarfi Fareeda ta ƙyalƙyale da dariya, shi kuma yaja tsaki ƙasa-ƙasa.

Bai sake cewa komai ba ya cigaba da jidar kayan abinci har ya gama kaima Fareeda nata. A lokacin taja yʼayʼanta bayan tayi mishi sannu da aiki suka shige ɓangarenta.

Tsaf ya kwashe na Fatima ita ma ya loda mata a store ɗinta. Bai ganta a falo ba, bai nemeta ba ya fice zuwa ɓangaren Fareeda.

Tashar da ake karatun yara ya tarar ta kunna ma su Sayyid, ita kuma tana kicin tana wanke-wanke.

Ɗakinsa ya wuce kai tsaye, suturunsa masu ɗan yawa ya ɗiba ya fice da su zuwa ɓangaren Fatima. Sai a lokacin ya tarar da ita cikin falon, tana zaune kan kujera tayi tagumi, idanunta sun kaɗa sunyi jaaa.

"Haɗa min ruwan wanka."

Ya bata umarni ba tare da ya bi takan yanayin damuwar da yake gani kwance male-male kan idanunta ba.

Cikin ɗakinta ya shige, ya zuba kayan akan gado. Ita kuma ta wuce bayi ta haɗa mishi ruwan wankan, tana fitowa kafin ta ce ta haɗa ya kalle ta da yanayin rashin jin daɗi ya ce

"Ke gadon ma ko arzikin sif baki samu ba, yanzu a ina zan zuba kayan sakawa na?"

"Kayi haƙuri. Bari in kwashe kayan babban akwatin can sai ka zuba kayanka a ciki."

Kallo ɗaya yayi mata ya shige banɗaki.

Ita kuma ta janyo akwatunan da yayi mata na aure ta kwashe kayan cikin babban akwatin ta loda a ƙananan da babban ghana must go ɗin da ta zubo tsofaffin kayan sakawarta.

Tana kwashe kayan zuciyarta cike da tunanin inda za ta samu kuɗi da gaggawa ta sayi sif ta biya a gyara mata katakon shimfiɗar gadon da ya ɓalle da hannayen kujerun da suka ɓalle.

Ya fito bandakin ya tarar da ita har ta gama shirya mishi kayanshi a cikin akwatin. Gaban madubi ya wuce yana goge gashin kansa zuwa wuyansa da tawul. Da murmushi a fuskarsa yana kallonta ta cikin madubi ya ce

"Na ci alkali mai dadi a gurin Fareeda. Ni fa mayen alkaki ne, gara ki hana ni nama da kiyi min rowar alkaki. Ina nawa?"

"Alkaki?"

Ta tambaye shi da mamaki a fuskarta.

"Eh! Ba ke kika bata ba?"

"Ni wallahi ban bata wani alkaki ba. Kila dai a wani guri ta samo."

Ta amsa da dukkan gaskiyarta.

A dofane ya dora mazaunansa gefen gadon, bai manta karyewar da yaji bangaren da ya zauna da karfi yayi jiya da daddare ba. Ya juyo da fuskarsa yana kallonta ya ce

"Alkaki fa nake nufi irin na kayan gara da amare suke zuwa gidan miji da shi. Ba ke kika bata ba?"

"Eh!"

Ta amsa a raunane, sai kuma ta saukar da kwayoyin idanunta kasa tana murza yatsun hannunta na dama cikin na hagu. Domin kawo karshen duk wasu tambayoyinsa ma sai ta ce

"Kayi hakuri. Ba ni da kudi ban samu yin komai na ciye-ciye ba. Rabon gadon su Ummee aka yi kuma yan'uwan babansu duk sun rike komai. Shi yasa komai ya zo min a hagugunce..."

"Au! Wai daman da kudin gadon yayanki kika so ki kayata min gida?"

Bakinsa a buɗe yayi mata tambayar.

Kamar wacce aka ɗinke mata baki. Kai kawai ta iya ɗaga masa alamar haka ne.

Shi ma dai ba shi da zaɓin da ya wuce yayi shiru. Amma a zahirin gaskiya Fatima ta sane masa, lamarinta a birkice yazo mishi, irin yadda ko a mummunan hasashe bai taɓa tunanin lamarin zai zo musu ita da shi a haka ba.

****

A bala'in maneji ko in ce a daddafe Mukhtar ya gama kwanaki ukunsa a ɓangaren Fatima. Lamarin dai ga shi nan... Ƙarerayin da tayi mishi ya rusa armashin komai.

Har Fareeda ta lura da babu wani rawar kai ko girigiɗishin amarci daga duka ɓangarorin biyu. Ita dai nata idanu, su ta kawo ta zuba musu ta cigaba da harkokinta da ƴaƴanta hankali kwance.

A yammacin da zai koma ɓangaren Fareeda jikinsa har rawa yake yi. Sosai murnarsa ta gaza ɓoyuwa, har Fatima ta lura da haka, wannan yasa jikinta ya ƙara sanyi, zuciyarta ya ƙara cika da tumbatsa da tsanar Fareeda.

A karo na biyu ya sake haɗa su a falonta Fareeda matsayinta na uwargida. Nasihar a zauna lafiya yayi musu, sannan ya faɗa musu shi ba ya sha'awar matanshi su raba girki.

"Girkin karin safe ne kawai na yarje ma kowa tayi a ɓangarenta. Amma girkin rana da dare duk mai girki idan tayi ta ɗiba ma wacce bata da girki a wadace yadda zai ishe ta.

Da za ku haɗa kanku ma ta hanyar yin girki tare da cin abinci tare ba ƙaramin farin ciki da jin daɗi zanyi ba. Kuma zan samu nagartaccen kwanciyar hankali da nutsuwa a zuciyata."

'Ashe kuwa baza ka taɓa samu ba Mukhtar'

Fareeda ta faɗi haka a zuciyarta. A fili kuwa fuskarta cike taf da murmushi.

"Fatima kin gama kwanakinki uku da addini ya baki. Yau da yamma zan koma ɗakin..."

"Oga minti biyu don Allah! Zan iya magana?"

Fareeda ta katse shi, daa muryarta a sanyaye kuma cikin ladabi.

"Ina jin ki"

Ya amsa yana tsatsareta da idanu.

Itama Fatima kai ta ɗaga ta kalleta, a sace ta gallah mata harara.

Karaf a idanun Fareeda. Murmushi ta saki cikin rashin damuwa. Idanunta ta mayar cikin na Mukhtar, da dakiya a muryarta ta ce

"Oganah, rannan kai da amarya Fatima kun nemi alfarmar in ƙara muku kwanaki. To nima dai daga baya nayi tunanin inyi ƙoƙarin kasancewa cikin uwaren gida masu adalcin da ta ambata kai kuma ka maimaita min.

Don haka na ƙara muku wata uku, sati goma sha biyu, kwanaki casa'in. Waɗanda addini ya basu kwanaki uku na ninninka muku uku sau talatin ai na ɗan kyautata ko...?"

"Kan'uba!!! Fareeda Wallahi baki isa ba!!!"

Mukhtar ya katse ta cikin fushi haɗe da miƙewa tsaye a fusace...

Kuyi min uzuri masu karatu. Satinnan muna da biki. Daga gobe da safe za mu fara hidindimu, ina mai baku haƙurin cewa bazan samu lokacin zama yin typing ba. Ko kun ganni online na hau in duba saƙonni ne kawai ko kuma zancen masu sayen data. Sabon posting zai zo komai dare ranar lahadi in sha Allahu. Kuyi hakuri. Ina tunasar da ku ku kira ni a wannan lambar don siyen data 09077591726. Ku kira Maman Mujahid ku sayi maganin sanyi, maganinta babu da na sani in Allah ya yarda, duk wacce ta siya baza ta ciji yatsa ba□□

Zee Maman Mujaheed mai sayar da ingantaccen maganin sanyi za ta sauƙaƙa kuɗin sayen maganin don faranta zukatan kwastomominta□□

Promo! Promo!! Promo!!! A baya tana sayar da maganin 4k ne. A yanzu ta sauƙaƙa shi zuwa 2k. Za ta rufe wannan garaɓasar ne a cikin sati ɗaya kacal! Ƴar'uwa me kike jira? Maganin nata ya samu shaidar aiki ingantacce kuma da gaugawa ake ganin biyan buƙata in sha Allah. Idan kina fama da ɗaya daga cikin waɗannan matsalolin ina mai baki shawara kiyi gaugawar siyan maganin Zee Maman Mujaheed□□

Ciwon gabobi, ciwon mara, fitar farin ruwa, kaikayi gaba, rashin Sha'awa, rashin kuzari gare ki ko ga namiji, rashin ni'ima, rashin haihuwa, kurajen jiki ko na gaba, jin Zafi yayin saduwa. Maganinta cikin sauƙi kuma a gaggauce yake magance duk waɗannan matsalolin. Ki tura kudin maganin ta wannan account ɗin da ke ƙasa, sai ki tura mata shaidar biya da garin da kike ta lambar wayarta□□0 816 285 9027 Ga kuma acc ɗinta□□

3968303018

Zainab Shu aibu

Fcmb

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*20*_

Cikin nutsuwa taja da baya ta ƙara shigewa cikin kujeran da take zaune. Da wani irin salo ta ɗaga ƙafa ɗaya ta ɗora kan ɗaya, ta ɗaga hannu guda ta tallabe kumatunta. Ta ƙure shi da kallo tana wani irin narai narai da fuska kamar za ta saki kuka.

Tunani take yi

'Saboda Allah a maganganunta ina abin ashar da fusatarwa? Shi fa Mukhtar haka yake! Idan tsiyarshi ta motsa da abin faɗa da ba na faɗa ba duk faɗa yake yi, kamar mai aljanu ne, idan ba jirgewa suka yi ba sam ba'a samun sauƙi. Ita kam gaskiya ba ta jin za ta iya biye mishi ya ɓata mata rai a wannan lokaci da take jin zuciyarta sakayau babu wata damuwa.'

Muktar dai har lokacin yana tsaye yana huci kamar wani bijimin sa.

Yana so yayi magana, amma ya san idan ya buɗe baki domin yin magana mai daɗi baza ta taɓa fitowa daga bakinshi ba, don haka ya zaɓi yin shiru yana ƙoƙarin rage ƙarfin fusatar da yayi.

Fareeda da bata san dawan garin ba a hankali ta sake kallonshi, ta mayar da idanunta kan Fatima da take zaune tsamoo kamar kazar da aka tsamo a cikin ruwan zafi. Ta ƙura ma kan kafet idanu, ko tunanin me take yi oho!

Idanunta ta dawo da su kan Mukhtar ta ƙara rage muryarta ta ce

"Idan akwai abinda ya fusatar da kai a maganganu na Allah ya huci zuciyarka Abee"

Ta kira shi da yadda su Sayyid suke kiranshi, bata bashi damar cewa wani abu ba ta cigaba da magana.

"Idan kuma Kwana casa'in ɗin da na ƙara muku sunyi kaɗan ne to na ƙara muku wasu kwana casa'in ɗin, kaga wata shida kenan. Idan su ɗin ma sun muku kaɗan ba laifi ku ƙara wasu kwana casa'in ɗin akai, daga haka..."

Wani irin wawan damƙa da ya kai ma kafaɗarta na hagu yasa ta katse maganar da take haɗe da cewa

"Ahhhhhhh! Wayyo Allah Hannuna... Wash za ka murƙusa ni."

Sai ga wasu zafafan hawaye sun silalo daga idanuwanta.

A gaggauce ya sake ta haɗe da ja baya. Cikin fushi ya nuna ta da yatsarsa manuniya

"Ki kiyaye ni Fareeda. Ni ba sa'an wasanki bane, kar ki kuskura ki ce za kiyi wasa da ni ko kuma ki nemi raina min hankali. Wallahi tallahi baki isa ba, ba'a son kwanakin. Saboda Allah da Annabi ni ne kike kyauta da ni kamar wani tsohon kaya Fareeda? Ni? Ni kike ma haka?"

Yayi mata tambayoyin bakinsa na ɗan rawa-rawa.

Ya ƙara murtuke fuska yana sake ɗaga murya cikin bala'i da masifa ya cigaba da cewa

"Ke in banda rashin hankali da ƙuruciya ina kika taɓa jin an ƙara ma miji da kishiya kwana casa'in? Na yi magana kuma kin sake ƙara mana wasu casa'in ɗin, ke gwana har da sake ƙara wasu kwana casa'in ɗin. Haba Fareeda? Ba kya so na ne? Ko kuwa kishi na ne ba kya yi?"

Yai mata tambayoyin yana zazzaro idanu waje don tsananin ɓacin rai da takaicin da ƙari kwanakin suka cusa masa.

Ita dai har lokacin hawaye take yi, Allah ya sani sosai ta ji zafin riƙon da yayi mata. Ita ba ta son irin wannan, ita ƙashinta ba irin ƙauƙau ɗinnan bane da take jure wahala. Har yanzu zafi take ji a inda ya riƙe mata.

A hankali ta ɗago fuskarta da sukai kace kace da hawaye ta ce

"Ni ce ba ni da hankali ko Mukhtar? Ni ɗin ce dai mare hankali don na yi muku abinda kuka nema. Na gode Mukhtar, ga mai hankali nan a kusa da kai ka tattara ta ku fice min daga ɗaki. Ke kuma"

Ta mayar da idanunta kan Fatima, ta nuna ta da yatsa manuniya, cikin ɓacin rai ta cigaba da cewa

"Ba dai Mukhtar bane? Ga ki ga shi nan! Kin dai ji da kunnenki na ƙara muku kwana casa'in kan casa'in bisa wasu casa'in ɗin ko? To don Allah ki tarkata shi ki riƙe a gurinki. Amarcin da kika ce me kukai a cikin kwanaki uku ina so kije kiyi ta sharɓan romonsa har nan da shekara guda mu ga tsiyar da za ki tsinta a cikinshi..."

"Fareeda"

Mukhtar ya katse ta da kiran sunanta a haukace cikin tsawa.

Idanunsa sun kaɗa sunyi jajur ya fara kora mata kashaidi bayan ya shata rantsuwa

"Wallahi Tallahi in kika sake cewa kin bada kwanakinki ga Fatima sai nayi mugun saɓa miki anan gurin.

Ke daga yau ma na soke batun wani kyautar kwana ko me zai je ya zo a gidannan. Babu wata mace da ta isa ta ce za tayi kyauta da kwanakinta ga abokiyar zamanta.

Ni ne maigida, sai na so za'a aikata min duk irin waɗannan abubuwan a gidannan! To ba na so!! Na ce ba na so!!!"

Ya ƙarasa cikin tsawa da tartsatsi.

A fusace ya ja musu tsaki ya kaɗa kai ya shige cikin ɗakinsa na nan ɓangaren Fareeda.

Fatima ta raka shi da idanu. Zuciyarta damƙam da mamaki da tsoro. Abin har ya kai a ƙara musu irin waɗannan magagan kwanaki masu yawa ya ƙi karɓa? To saboda me? Bayan duk irin maƙudan kuɗaɗen da ta kashe gurin magungunan mata da magungunan mallaka a ina ne aka samu matsala? Lallai ya kamata ta koma baya a hankali tayi karatun ta nutsu ta gano inda ta kuskure tayi gaggawar gyarawa...'

Dogon tsakin da taji saukarsa a kunnuwanta yasa tayi gaggawar dawowa cikin hayyacinta, sai ganin Fareeda tayi ta balla mata harara da manyan idanunta ta wuce tana gaf da shigewa cikin ɗakinta.

Ita kuwa tana zaune, kamar wacce aka dasa ta a gurin, ta kasa motsawa balle har ta tashi ta fice zuwa ɓangarenta. A madadin zaman banza da tunani ma sai ta fara ƙare ma falon kallo.

Lallai dole Mukhtar ya raina mata ajawali. Ba wasu sababbin kaya Fareeda ta zuba a falon ba fa, amma saboda tun farkon sayen kayan an zuba manyan kuɗaɗe ne ba tare da ƙyashi ba an sai na gari don mayar da kuɗi gida shi yasa har yanzu kayan ƙal suke.

Ga Fareeda kamar mayya take gurin tsafta, duk iya hangenta bata hangi wani ɗan datti da za taga cikashin falon ba.

"Gaskiya da sake! Ya zama dole in shiga in fita in nemo kuɗaɗe in gyara ɗakunana."

Tayi maganar a fili, zuciyarta cike da ƙyashin kyawun ɓangaren Fareeda.

Kwatsam sai ga Mukhtar ya fito daga ɗakinsa zuwa cikin falon kamar wanda aka jefo shi. Ganin Fatima a zaune kuma babu Farida yasa shi yin turus yana kallonta da mamaki.

"Zaman me kike yi anan?"

Sai da tayi fari da idanunta sannan ta ƙanƙance murya ta ce

"Ai na zaci ka shiga ciki ka fito mu tafi ne? Haskenah ko ka ƙi karɓar mana kwanakin da ta ƙara mana har yanzu magrib da zan fita a girki baiyi ba. Gurina ya kamata a ce..."

"Girko! Fatima na ce Girko!! Za ki ɓace min da gani ko sai na ja ki a wulaƙance na fitar da ke?"

Ai a saba'in Fatima ta fice daga falon. Zuciyarta cike da mamakin wannan irin murɗaɗɗen hali na Mukhtar!

Shi kaɗai ya tsaya a tsakiyar falon yana ta safa da marwa. Zuciyarsa sai wani irin tuƙuƙi take yi na ɓacin ran maganganun da Fareeda tayi mishi waɗanda ƙarara suke nuna mishi bata damu da shi da lamuransa ba.

Lallai zai nuna mata bata isa ba, son da yake mata ba shi zai ba ta lasisin da za ta fara wasarere da al'amarinshi ba.

Kuma zai tabbatar mata har yanzu yana nan a zazzafan Mukhtar ɗinnan da ta sani, auren Fatima da ya ƙaro bai sa yayi laushi ba.

A fusace yaje ƙofar ɗakinta ya murɗa hannun ƙofar domin suyi duk wacce za suyi sai ya tarar da kofar a rufe.

Dogon tsaki yaja, ya shafa aljihunsa yaji makullin motarsa na ciki don haka ya fice daga falon. Motarsa ya hau ya fice daga gidan ba tare da ya koma ɓangaren Fatima

da take tsaye jikin window tana kallon harabar gidan ta ɓangaren Fareeda ba, a zuciyarta take lissafin mintunan da ya ɗauka bayan fitarta, tare da shan alwashin ko ana ha maza ha mata sai ta rama wannan abu a ranar girkin Fareeda.

Ko da ya fita daga gida kai tsaye unguwar dosa ya nufa gidan mahaifiyarsa. Bai tarar da ita a falo ba, sai ya zauna kan kujera yasa hannaye biyu ya tallabe ƙeyarsa, ya ƙura ma guri ɗaya ido cikin zuzzurfan tunani.

"Lafiya? Tunanin me kake yi haka ina ta sallama baka ji ba?"

Hajiya ta tambaye shi da kulawa.

Nannauyar ajiyar zuciya ya sauke. A hankali ya ɗan zame zuwa ƙasa ya fara gaisheta a ladabce.

"Ya Fareeda da mazajena? Allah yasa dai lafiya suke?"

Ta tambayeshi bayan ta amsa gaisuwarsa.

"Lafiyarsu ƙalau Hajiya..."

"To tunanin me kake yi?"

"Babu komai"

Ya amsa a kasalance.

Kure shi tayi da kallo tana ganin yadda ya ɗab faɗa a idanunta. Shi kam ko irin kumarinnan na angwanci baiyi ba.

Tsakanin ɗa da uwa sai Allah. Karo na farko da taji tausayinsa ya ɗan ratsa ta tun bayan da ya fara rugu-rugun neman aurensa.

Nasiha mai ratsa jiki ta fara yi masa a tausashe, cikin hikima irinta manya da balagar iya magana. A fakaice tana ƙara nunar mishi da muhimmancin adalci a cikin iyali. Da kuma hanyoyin da zai bi wajen gujewa zama munafuki a tsakanin matan nashi guda biyu.

Sosai ya samu nutsuwa, shi da yaje gidan zuciyarsa danƙare da ƙunci sai ga shi ya samu nutsuwa da walwala.

A masallacin ƙofar gidan yayi sallar magriba da isha'i, sannan yayi mata sallama ya kama hanyar komawa gida.

A Taraba suya ya tsaya ya sayi kaza, guda ɗaya daban sai kuma ya sayi rabi itama aka naɗe ta daban. Exotic ya siya babba da ƙarami ya shige cikin motarsa ya bar gurin.

Ko da ya isa gida, kai tsaye ɓangaren Fatima ya nufa. Da ledojin biyu riƙe a hannayensa. Sallama yayi ya shige cikin falon, fuskarsa yalwace da fara'a.

Tana zaune akan kujera tayi kwalliya daidai gwargwado. Jikinta sanye da kayan barci, wayarta ce riƙe a hannunta tana dannawa.

Ganin fuskarsa a sake yasa ta cewa

"Oyoyo Hasken zuciyar Fatimah"

"Amarya yar shagali, amarya ba kya laifi ko kin kashe ɗan masu gida. Hutawa ake yi ne?"

Yayi maganar da salon tsokana yana yar dariya. Ya nemi guri a gefen ƙafafunta ya zauna.

Da sauri ta janye ƙafafun ta saukar zuwa ƙasa, da murmushi a fuskarta ta ce

"Amare dai suna can inda suke! Mu kam maneji muke yi..."

"Maneji? Me yasa kika ce haka?"

Ya tambayeta da mamaki.

"Maneji mana Haskenah! Wace irin amarya ce har yanzu Ango bai biya bashin kazar ta na amarci da yayi alƙawarin biya ba?"

Ta faɗi maganar a wasan dare tana ƙara buɗe hancinta sosai tana sake shaƙar ƙamshin gasasshiyar kazar da take ji tun bayan shigowarsa.

Dariya ya ƙyalƙyale da ita, a zuciyarsa yake yaba girman rainin wayau irin nata. Wato duk kwanaki ukun da yayi a ɗakinta bata san tayi ƙorafin kaza ba sai yanzu da ta ji ƙanshin ya taho da kaza.

Har da yayi niyyar mutsuke fuska ya hanata kazar yaga in tana da yadda za tayi da shi. Sai kuma ya tuna girman hakki da ɗazunnan Hajiya ta gama tunasar da shi, ledar da aka ƙunshe rabin kaza da ƙaramin lemun exotic ɗin ya miƙa mata.

"To ki kwantar da hankalinki. In dai kaza ce tasa kike ganinki a amaryar maneji ga ta na kawo miki, kici ki more, ke kaɗai ba tare da Ango ya miki giɓi ba."

"Hmmm! To na gode."

Ta faɗa da fuska ba yabo ba fallasa. Ledar da ya bata ta karɓa ta kalla dakyau, sai kuma ta kalli ɗayar ledar da take ajiye a gefensa taga ai nadin ya fi girma.

Ba tare da wani tunanin ya kamata taje kicin ta ɗauko faranti ba ko kuma ta bari ya fita kawai sai ta warware nadin kazar tun a nan gabansa.

Kallo ɗaya tayi ma naman ta gane rabin kaza ce. A raunane ta ɗaga idanu ta kalle shi

" Haskenah? Kana nufin a matsayina na amarya ban ci arzikin da za ka sayo min gudar kaza ba sai rabi?"

"Ikon Allah"

Ya faɗa da mamaki, bai bata damar cewa komau ba ya cigaba da cewa.

"Haba Fatima, ki dinga jin tsoron Allah mana. Fisabilillahi tunda dai kazar nan ba addini bace ya kamata ki karɓi abinda ya samu. Kuma in ba neman tayar da zaune tsaye ba duk kwanaki ukun da nayi anan baki tuna da wata kaza ba sai yanzu da kika ji ƙamshin na shigo da kaza?"

Shiru tayi mishi, ta duƙar da kanta zuciyarta na tuƙuƙin ɓacin rai. Duk yadda kazar nan take ta tururi da nasha-nashan mai ga uban kayan haɗin da aka zuba wajen gasuwarta ji tayi sam bata burgeta ba.

Saboda Allah da Annabi ita da Fareeda wacece ta cancanci gudar kaza? Da ganin waccan babban ledar kaza guda ce ko kuma ɗaya da rabi, sai ita ne saboda ya raina ajinta zai kawo mata rabi?

Ganin yadda take ta cika tana batsewa yasa shi ɗaukar ɗaya ledar ya miƙe tsaye tsam! So take ta ɓata mishi rai a darennan shi kuwa gaskiya bai shirya ma hakan ba.

Nasihar Hajiya yayi tasiri ƙwarai a zuciyarsa. Tunda ya tara mata biyu to dole sai ya ninninka haƙurin da yake da shi.

"Allah ya huci zuciyarki Fatima. Kiyi haƙuri, ki daure ki ci rabin kazar. Gani nayi ke kaɗai ce anan shi yasa na siyo miki rabin kaza.

Ita kuma Fareeda ga ta, ga yara, ga kuma ni da zan kwana a gurinta. Kuma ma dai gurin sayen kazar nan wallahi ko kusa ban tuna da kina bi na bashin kazar amarci ba, amma ki ci rabin, ki yi haƙuri ki sake biyo ni bashin rabin. In Allah ya yarda in girki ya zagayo kanki zan biya wannan bashin.

Sai da safe."

"Hmm! Ba komai, Allah ya tashe mu lafiya."

Ta amsa a cuccushe.

Har ya nufi ƙofar fita daga falon sai kuma ya koma ciki. Nasihar mahaifiyarsa ya tuna, ɗazu ta jaddada mishi lallai haƙƙi ne da ya rataya a wuyanshi in dai yana da yadda zaiyi yayi ƙoƙarin saka ko wace mace a cikin su biyu cikin farin ciki.

Ledar hannunsa ya ajiye kan hannun kujera ya karasa kusa da ita ya durƙusa a gabanta.

Hannayensa biyu ya ɗora kan gwuiyawunta yana kallon fuskarta, ɗan girgiza kai yayi, sai ya sakar mata lallausan murmushi.

Ya tausasa murya sosai kamar saurayi a gaban budurwar da yake mutuwar so ya ce

"Haba Fatina, Haba Fatin Haskenta. Haba Amaryata yar shagali na. So kike in tafi can in kasa barci saboda barinki da nayi cikin ƙunci? Don Allah ki ɗan yi min murmushi mana ko na tafi da hoton kyakkyawar fuskarki a zuciyata."

Tun kafin ya rufe baki ta sakar mishi faffaɗan murmushi kamar bakinta zai yage.

Ledar naman hannunta ya karɓa ya ajiye a gefe, ya miƙar da ita tsaye, a slow motion da salo irinna indiyawa ya janyota jikinsa ya rungume. Wani abu da tun ranar farko da ta shigo gidan bai sake bari ya shiga tsakaninsu ba

Luf tayi a ƙirjinsa tana jin wani irin sanyin daɗi da nutsuwa yana kwarara a zuciyarta. Tana son Mukhtar, Allah ya sani tana son shi. Duk irin ɓacin ran da ya cusa mata a cikin kwanakinnan yan waɗannan kalaman da rungumar nan duk sun share wani fushi da take yi da shi. Lallai da gaskiyar bahaushe da ya ce

"So hana ganin laifi."

Tsawon wasu daƙiƙu yana rungume da ita sannan ya sake yi mata sallama. Ya sumbaceta a laɓɓa ta mayar mishi da martani cikin rawar jiki.

Ya ɗauki ledarsa ya fice suka rabu tana farin ciki, bayan ta raka shi har bakin ƙofar falonta.

Yana fita ta kulle ƙofar, kamar yar tsuntsuwa ta fara daka tsalle a tsakiyar falon tana ɗebo shoki tana watsawa, zuciyarta cike da farin cikin irin rabuwar da suka yi ita da Haskenta Mukhtar a wannan dare.

Ko da yaje ɓangaren Fareeda, wani abin mamaki sai ya tarar da ƙwayayen lantarkin falon duk a kashe, sai wani mai duhu guda ɗaya da ta bari a kunne.

Kan teburin cin abinci ya hanga idanunsa. Sai yaga sabbin kuloli masu bala'in kyau da tsada ajiye akan teburin. Da saurin gaske ya ƙarasa gurin, ledar hannunsa ya ajiye a gefe ya buɗe babban kular abincin.

Farar shinkafa ce da aka dafa ta tayi wara wara da koren wake da karas, yana buɗe kular miyar ƙamshin soyayyar miyar stew ya daki hancinshi. A gefe guda kuma ga yankakken kabeji nan da albasa a cikin wani ɗan madaidaicin kwanon tangaras mai murfi.

Muƙut ya haɗiye miyau. Duk yunwar da yake ji bai tsaya cin abinci ba ya nufi ɗakinsa, a tunaninsa zai tarar da ita a ciki ta yi ƙayataccen kwalliyar barci tana jiran dawowarsa, sai yaga wayam.

Ga dai gadonshi nan lafe da sabon zanin gadon da bai taɓa ganinshi ba. Amma ya duba ko ina ba ta a cikin ɗakinshi.

Da sassarfa ya fita zuwa ɗakinta, wani abu da ya bashi mamaki kuma ya kashe mishi jiki shi ne ƙofar ɗakin Fareeda kulle yake gam da makulli.

A hankali ya fara ƙwanƙwasawa, amma har ya kwashe mintuna uku yana ƙwanƙwasawa ko motsinta bai ji ba balle ya saka ran za ta buɗe mishi.

Hakanan ba don ransa ya so ba yaja sanyayar ƙafafunsa ya koma wurin teburin cin abincin, zuciyarsa cike da tunanin ko me yasa Fareeda ta kulle ɗakinta? Shi har ga Allah ya ma manta a yadda suka rabu da ita ɗazu...

Promo! Promo!! Promo!!! A baya tana sayar da maganin 4k ne. A yanzu ta sauƙaƙa shi zuwa 2k. Za ta rufe wannan garaɓasar ne a cikin sati ɗaya kacal! Ƴar'uwa me kike jira? Maganin nata ya samu shaidar aiki ingantacce kuma da gaugawa ake ganin biyan buƙata in sha Allah. Idan kina fama da ɗaya daga cikin waɗannan matsalolin ina mai baki shawara kiyi gaugawar siyan maganin Zee Maman Mujaheed□□

Ciwon gabobi, ciwon mara, fitar farin ruwa, kaikayi gaba, rashin Sha'awa, rashin kuzari gare ki ko ga namiji, rashin ni'ima, rashin haihuwa, kurajen jiki ko na gaba, jin Zafi yayin saduwa. Maganinta cikin sauƙi kuma a gaggauce yake magance duk waɗannan matsalolin. Ki tura kudin maganin ta wannan account ɗin da ke ƙasa, sai ki tura mata shaidar biya da garin da kike ta lambar wayarta□□0 816 285 9027 Ga kuma acc ɗinta□□

3968303018

Zainab Shu aibu

Fcmb

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*Littafin TUBALIN TOKA ya zama complete Document. Ga duk wacce take buƙata akan N400 ta tura kuɗin ta 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ta tura shaidar biya ta lambata 07039080978*

_*21*_

Duk da matsananciyar yunwar da yake ji, ɗan kaɗan ya tsakuri abincin ya kora da ruwa. Duk ƙamshin da naman yake baɗawa ko buɗe ledar baiyi ba balle ya ɗanɗana.

Abu ɗaya da ya iya yi shi ne saka ledar naman a cikin firij, saboda kar ya canza ɗanɗano zuwa safe tunda akwai kayan haɗi a ciki.

Yana gama cin abinci ya shige cikin ɗakinsa. Hanci ya buɗe sosai ya shaki wani ƙamshi mai bala'in daɗi na turaren wuta, wanda a ɗazu sa'adda ya shiga duba Fareeda hankalinshi yayi gaba, sam bai ji ƙamshin ba.

"Hmmm! Fareeda ba dai son ƙamshi ba."

Ya faɗa a fili sa'adda ya buɗe banɗakin nasa ya ji ƙamshin turaren wutan ya daki hancinshi.

Yana gama biyan buƙatarsa bai ɓata lokaci wajen yin shirin barci ba, ya gama komai ya canza ƙwan lantarki zuwa mai duhu ya bi lafiyar gado.

Jikinsa a saɓule, wayarsa ya janyo ya danna mata kira, nan take kamfani suka faɗa mishi wayar a kashe take. A dole ya haƙura ya kwanta ba don ransa ya so hakan ba.

Allah ya sani yau ya saka ran jin ɗumin jikinta, yayi kewarta, irin sosai ɗinnan. Sai a lokacin ma yake tunawa ashe rabonshi da ita tun dawowar da yayi ya zo mata da zancen zai auri Fatima.

Tun lokacin ta raba musu makwanci. Shi kuma duk ƙulafucinta da yake yi bai taɓa nuna mata ya damu da raba makwancin ba.

A sannu ya runtse idanunsa, yana jin yadda wani matsanancin kewa da sha'awarta ke ƙara lulluɓe shi. Zuciyarsa cike da fatan nannauyan barci yazo yayi awon gaba da shi.

Bayan tsawon lokaci yana juye-juye daƙyar ya samu barci ya ɗauke shi a wahalce.

****

Motsin da ya ji a kicin yasa shi ƙarasawa da sassarfa. Ita ya gani, tana tsaye gaban cabinet tana fasa ƙwai a cikin roba.

A firgice ta juya jin anyi ma ƙugunta wani wawan damƙa. Ganinshi yasa ta sauke ajiyar zuciya, ta kwaɓe fuska, tayi narai-narai da idanunta ta ɗan tura baki gaba

"Ashe kai ne, ka tsorata ni..."

Cikin salo ya juyo da ita suna fuskantar juna. A sannu a hankali yana riƙe da ita ya dinga matsawa da fuskarsa zuwa tata, ita kuma ta dinga ja da kanta baya har sai da ta kusa kwantar da kanta kan Cabinet ɗin

"Abee ka bari mana don Allah, za ka sa inyi ɓari fa."

Tayi maganar tana zazzaro idanu ƙirjinta na bugawa. Bata san me yasa ba sam ba ta son ya sumbace ta.

Hannayensa ya ɗaga daga ƙugunta zuwa bayanta ya tallabota dakyau, a hankali ya janyota ya matso da ita tsakiyar kicin ɗin, har lokacin yana riƙe da ita.

Murmushi ya sakar mata. Ita kuma ta ƙara daidaita yanayin fuskarta zuwa ba yabo ba fallasa.

"Jiya, na zaci zan tarar kin shirya min kyakkyawan tarba? Me yasa kika ƙi zuwa ɗaki na? Kuma nai ta ƙwanƙwasa ƙofarki kina ji na kika ƙi buɗewa"

Idanunta ta wulƙita kamar tana harara, kamar kuma tana kallon gefe da gefe.

"Abincinka, da duk wani abu da na san za ka buƙata na ajiye maka. Ɗakinka duk da ko wane lokaci a gyare yake sai da na sake ƙalƙale shi. Me kuma kake buƙata bayan waɗannan Habeebee?"

"Ke"

Ya amsa kai tsaye.

"Ke nake buƙata Fareeda! Allah ya sani ina kewarki..."

Katse shi tayi ta hanyar sakin wata irin dariya a sakalce.

"Dariya kike yi...?"

"Eh to ai dole inyi dariya Habeebee! Ni da tun kafin amarya ta zo aka tattarani aka aje gefe ɗaya? Ai kaje ka ji da Amaryarka kawai, babu komai, zan baku lokaci sosai har fiye da yadda kuke buƙat..."

A bazata ya haɗe bakinsu guri ɗaya. Ya fara aika mata da wani irin zazzafan sumbata, duk yadda ta so ƙwacewa ta kasa, sai kawai ta mishi kakim shi kaɗai yake kiɗansa yake rawarsa.

Hakan bai dame shi ba. Daga bisani ma ɗaga ta yayi cak suka nufi ɗakinsa. Duk yadda take ƙoƙarin zillewa bai sauke ta ba sai da ya kaita har kan gadonsa.

Ko kafin tayi yunƙurin sauka ƙasa har ya mata rumfa ta yadda baza ta iya sauka ƙasa ba sai ya bata dama. Daman har lokacin kayan barci ne a jikinta, don haka bai sha wahala wajen zame mata da cillar da su ba.

Da wani irin zafi-zafi da rawar jiki kamar wanda ake ingiza shi yake aikata komai. Sosai jikinsa ke karɓar duk wani abu da yake yi.

Duk da a ɓangarenta babu wani armashi ko tallafi a hakan dai ba ƙaramin samun yadda yake so yayi ba.

Sai da ya gama taɓo duk wani guri da zai motsa shi yana gyarata da nufin ayi mai gaba ɗaya ba zato ba tsammani gaba ɗaya kuzarinshi ya tafi. Ya wani kwanta lakaf kamar ba shi ne yai tsaye ƙiƙam yana zakwaɗin samun biyan buƙatarsa ba.

Hannunsa yakai gurin, a tsorace ya janye hannu ya kai idanunsa jin kamar ya taɓo lagwani don sanyin da yayi.

Ya ɗago idanu a tsorace ya kalli Fareeda da take kwance da ɗaurarriyar fuska, ya sake mayar da idanu jikinshi yasa hannu ya ɗan taɓo bakinshi na rawa ya ce ma Fareeda

"Lllllla...fiya.. kuwa...? Kin ga... yadda...na zama?"

A lalace ta ɗaga idanu ta kalli inda yake nuna mata. Ganin yadda yayi lakaf kamar wanda ya gama aikata komai yana buƙatar hutawa sai ta kawar da kanta gefe ɗaya.

A bazata wani irin faɗuwar gaba ya sameta.

'Mukhtar lafiyayye kuma jarumin namiji ne da ko bai gani ba bai taɓa ba haka kawai yake miƙewa saboda tsananin lafiya da jarumtarsa. Amma yanzu ace ya kwanta ligif tun ba'ayi komai ba? Lallai an gogu da Amarsu ta Ango mai zaƙin miya."

Da sanyin jiki sosai ta zame ƙafafunta ta mirgina gefe ɗaya, ajiyar zuciya take saukewa a hankali kuma akai-akai.

Tunanin kwanciyar me za ta cigaba da yi tunda ba halin yin abinda yasa shi ɗaukota sai ta yunƙura za ta tashi.

Da sauri Mukhtar ya riƙota ya sake komar da ita kan gadon.

A hankali ya fara yamutsata jikinsa na rawa, ƙoƙari yake ya taɓa duk inda ya san zai tayar da kanshi da gaggawa.

A yanzu ɗin wani irin salon soyayya yake gabatar mata wanda ba shi kaɗai ba, ita kanta duk ɗaurewarta da kawar da kai sai da ya samu nasarar kunnata. Da armashi sosai ta juyo tana mayar mishi da martanin wasanninshi, sai a lokacin ita kanta tasan ta yi kewar mijinta.

Wani abin mamaki da ban tsoro ga su biyun kamar ɗazu dai haka ne ya sake faruwa. Duk yadda Goga Mukhtar ya miƙe tsaye ƙiƙam kwanciya ya sake yi lakaf sa'adda ya zo zai ratsa gonar da ta daɗe da zama halaliyarsa.

Ruƙunƙumeta yayi da ƙarfi a ƙirjinsa yai shiru, zuciyarsa na bugawa fafafat! Hankalinsa a bala'in tashe.

'Me yake faruwa ne haka?'

Tana kwance a jikinsa wani irin tashin zuciya ya fara zuwar mata bagagatan, amai take jin yi, duk da cikinta babu komai da ta ci a safiyar nan sosai amai ke taso mata.

Jin miyaun bakinta ya tsinke sosai alamun ko wane lokaci aman na iya ƙwace mata yasa ta fara ƙoƙarin ƙwace jikinta.

Mukhtar bai lura da halin da take ciki ba. Hankalinsa yayi nisa gurin tunanin inda matsalar take, sai ya ji ta fara ƙoƙarin ƙwacewa daga riƙon da yayi mata.

Jajayen idanunsa ya ɗago ya zuba mata sai yaga yunƙurin da take yi da yadda take kai hannu tana tare bakinta.

"Lafiya...?"

"Amai"

Ta amsa daƙyar sannan ta sauka a guje zuwa banɗaki.

Wani irin ƙaƙƙarfan amai ne take yi kamar za ta amayar da yan cikinta. Jin yunƙurin ya ƙi ƙarewa dole ya taso zuwa bayin yana jera mata sannu.

Hankalinsa ne ya ƙara tashi ganin yadda cikin ƙanƙanin lokaci ta galabaita. Ta gama aman kumallo yanzu kuma yunƙurin aman take yi babu abinda ke fitowa. Kuma ta kasa daina yunƙurin.

Sosai ya riƙe ta a jikinsa ganin tana ƙoƙarin zubewa ƙasa saboda rashin ƙarfin jiki. Hankalinsa a ɗugunzume. Sannu kuwa ya jera mata ya fi baki ɗari.

Bayan tsawon lokaci suna cikin banɗakin daƙyar yunƙurin da take yi ya ragu. Ruwa ya tara mai zafin gaske cikin kulawa da tarairaya ya salleta soso da sabulu.

Cikin rashin ƙarfin jiki ita kuma ta lallaɓa tayi na tsarki, duk da ruwan zafi take amfani da shi tana yi jikinta na kyarma-kyarma.

Babban tawul ya rufa mata yana riƙe da ita a gefen kafaɗarsa ya kaita gefen gado ya zaunar da ita, sannan shi ma ya faɗa wanka.

Ko kafin ya fito daga wanka ta kwanta, bayan ta janyo bargo ta lulluɓe jikinta har saman kai. Wani irin rawan sanyi take yi sosai yadda ko daga waje ne ana kallon yadda take jijjiga a cikin bargo.

Ko mai be shafa ba ya zura kaya a gaggauce yana yi yana kallonta. A daidai lokacin kuma daga can falo ya ji muryar su Sayyid suna ƙwala kiran Ammee, da raunin murya mai nuni da alamun ko wane lokaci za su iya fashewa da kuka.

Da sauri ya fita falo gurinsu. Ganinshi yasa suka taho da ɗan gudu gudu suka rungume shi suna gaishe shi cikin harshen nasara.

"Ammee ba ta da lafiya. Me kuke so?"

Ya tambaye su da kulawa bayan ya amsa gausuwarsu.

"Abee, yunwa muna ji."

Suka amsa da gwaranci a muryoyinsu.

Ganin kayan barci ne a jikinsu ya bashi tabbacin yanzu suka tashi. Sai yaja hannayensu zuwa banɗaki ya goge musu baki, yayi musu alwala. Ya shimfiɗa musu sallaya ya durƙusa a gabansu ya ce

"Kuyi sallah, idan kun idar yanzu zan kawo muku kayan break fast. Kun ji?"

Kawunansu suka ɗaga.

Sai ya wuce kicin da sauri, wani ƙwan ya sake fasawa ya soya musu, saboda wancan da Fareeda ta fasa a buɗe suka bar shi.

Ya haɗa musu tea a yɞan kofunansu ya ɗauki biredi da ƙwan da ya soya ya kai musu.

Gurin kayanta ya nufa, bayan ya ɗauki Inner wears sai ya ɗaukar mata doguwar rigar atamfa mai faɗi, ya ɗauki babban hijabi mai kauri ya koma gurinta a ɗakinsa.

Yanzu ta rage jijjigar da take yi, barci take, amma irin wahalallen barcin nan mai tafe da zazzafan zazzaɓi. Ko da ya taɓa jikinta zafi sosai.

A hankali ya ɗaga ta ya saka mata kaya, ya sa mata hijabin ya sake kwantar da ita ya lulluɓa mata bargo.

******

"Barr. Ka taimaka min, don girman Allah ka taimaka min. Wallahi tallahi ina cikin wani matsanancin hali ne da idan ban samu kuɗaɗen ayau ɗinnan ba rayuwata za ta ƙara shiga cikin garari..."

"Hajiya Fatima wai saurin me kike yi ne? Idan kinyi haƙuri, wata huɗu ya rage su sake biyan kuɗin hayar nan. Da yau da nan da wata huɗu ai kaman gobe ne in dai muna raye..."

Jin da tayi yana neman yi mata yawo da hankali alhali yana da ikon taimaka mata kawai sai ta sakar mishi kuka. Shi kaɗai ne hope ɗinta na ƙarshe da take tunanin za ta iya samun rancen kuɗi a gurinshi kafin ƙarshen shekara a biya kuɗin hayar shagon da take da kaso a ciki.

Dubu ɗari biyu da hamsin ake biya duk shekara, to ita a rabon gadon da aka yi duk sa'adda aka biya kuɗin tana da dubu saba'in da biyar a ciki.

Wani abun armashi shi ne, masu biyan kuɗin hayar shagon idan sun tashi biya suna bada na shekara biyu ne. A lissafi tana da dubu ɗari da hamsin kenan.

Yanzu saura wata huɗu kenan a biya kuɗin. Jiya da daddare ta yanke shawarar kiran lauyan da yake tsaye akan kadarorin yʻayʻan mijinta ta roƙe shi ya taimaka ya bata kasonta tun kafin lokacin biyan kuɗin yayi.

Shi ne yake ta mata yawo da hankali, sai yayi kamar zai taimaka mata sai ya zille, ga ɗari biyar ɗin da ta ci bashi a wayarta kuɗin na tafiya a iska babu biyan buƙata.

Jin kukanta ya ɗan karya mishi zuciya, da sauri ya dakatar da ita ta hanyar cewa

"Tsaya, tsaya, saurara Hajiya Fatima. Ai abin duk bai kai na kuka ba. Kin dai san yanzu lokaci ya canza gwamnati ta hana aikin da babu riba ko?"

"Eh!

Ta amsa da rawar murya.

"Zan taimaka miki, amma bisa sharaɗi ɗaya idan kin amince. Kuɗinki na shekara biyu dubu ɗari da hamsin ne, idan kin amince zan cire dubu talatin, yanzu in baki ɗari da ashirin ni kuma idan sun biya in riƙe ɗari da hamsin ɗin. Kin amince?"

Shiru tayi cikin tunani, ya za ta yi? Ba ta da wani hanyar samun kuɗi da ya wuce wannan. A baya al'mubazzaranci kawai tai tayi da kuɗaɗe ba tare da tunanin irin wannan lokacin zai iya zuwa ba.

"Na amince"

Ta amsa a raunane.

Ko minti biyar ba'ayi ba da yake yana acc ɗinta taji wayarta yayi ƙaran shigowar saƙo, tana dubawa taga ɗari da ashirin ɗin ne ya turo mata.

Tsananin farin ciki yasa ita kaɗai ta fara ƙyalƙyala dariya, kamar wata sabuwar kamu. Tana wannan dariyar taji kamar ana ƙwanƙwasa mata ƙofar falo.

Ajiye wayar tayi a kusa da ita ta ƙara saurarawa da kyau, sai taji tabbas ƙwanƙwasawar ake yi. Agogon fuskar wayar ta kallah taga ƙarfe takwas da minti arba'in da bakwai na safe.

Hijabi ne a jikinta, sai ƙarfe takwas ta samu sararin gabatar da sallar asubah tun da ta idar shi ne bata cire ba ta zauna kiran lauya.

Har za ta fita sai tayi tunanin idan ba Mukhtar ba wa zai ƙwanƙwasa mata ƙofa da safennan? Hijabin ta cire ta aje a gefen gado, ta cire zanin da ta ɗora kan rigar barcin jikinta tayi sallah ta ajiye.

Ta sake kallon rigar barcin jikinta, shara shara take ana ganin komai na jikinta. Murmushi ta saki ta nufi ƙofar falon ta buɗe tana ta wani gantsare - gantsare.

Suna haɗa idanu ta sakar mishi lallausan murmushi, da wani irin salon rangwaɗa ta gantsare sannan ta duƙa a gabanshi kamar za tayi ruku'u, yʼan mamunanta suka fito sosai ta gaban rigarta ta ƙale mishi idanu ɗaya haɗe da cewa

"Haskenah! Barka da asubah hasken zuciyar Fatima. Ina fatan ka tashi cikin aminci da ƙoshin lafiya?"

Yʼayʼansa da ke tsaye gefensa yayi saurin mayar da su baya haɗe da cewa

"Miye haka kike yi? Dallah ki miƙe tsaye bakya ganina tare da yara ne?"

Ya ƙarasa maganar haɗe da ɗaure fuska tamau.

A saɓule ta miƙe tsaye tana tura baki.

"Fareeda ba ta da lafiya. Za mu tafi asibiti yanzu..."

"Allah ya sauwaƙe"

Ta katse shi tare da mayar da ƙofar falon za ta rufe.

Hannunshi ɗaya yasa ya danne ƙofar

"Za mu bar yara a hannunki ne..."

"Yara kuma?"

Tayi mishi tambayar tana yamutsa fuska. Allah ya sani ta tsani wahalar yʻayʻa, nata yʻayʻan ma ƙannenta ke ɗawainiya da su, shi yasa babu wani shaƙuwa mai girma tsakaninta da yaran har aka raba su.

Ganin wani mugun kallo da ya aika mata yasa tayi saurin cewa

"Shi kenan! Ba damuwa. Kai kuzo mu shiga ciki"

Ta miƙa hannu da nufin janyo Shahid da tun ɗazu take kallon yadda yake leƙota daga bayan Uban.

Aikuwa a tsorace yaron ya fashe da ihun kuka yana ƙamƙame ƙafafun uban. Sayyid ganin ɗan'uwanshi na kuka shi ma ya fashe da kuka yana rirriƙe ɗan'uwansa.

"Daman ba kiyi niyyar riƙe su ba."

Yayi ƙwafa, sannan yaja hannun yʻayʻansa a fusace suka bar gurin.

Cikin rashin damuwa ta mayar da ƙofar ta kulle.

"Ai kam dai banyi niyya ba. Haka kawai ina zaƙin amarcina na samu an raba ni da nawa yaran za ka fara haɗa ni da wata wahalar? Bazan ɗauka ba. Ba ni na ɗora mata ciwo ba don haka ko za ta mutu taji da yʻayʻanta."

Taja dogon tsaki sannan ta shige cikin ɗakinta.

Wayarta ta ɗauka ta duba lafiyar kuɗinta tana sakin murmushi. Nan gefen gado ta zauna ta fara kasafta yadda za ta bi da kuɗin daki-daki gurin magance matsalolin da take ganin su suka sa Mukhtar yake mata gani-gani.

Mintuna goma tsakani taji ficewar motar Mukhtar. Cikin gyatsine ta ce

"A gayas, Umma ta gaida Assha."

*****

Ko da suka isa asibiti babu ɓata lokaci aka bata gado saboda yadda ta galabaita sosai. Bayan duk wasu gwaje-gwaje, Likita ya tabbatar musu tana da ƙaramin ciki na wata biyu, sai kuma tyohoid ɗan kaɗan a jikinta.

Saboda tsananin murnar jin tana da ciki bakin Mukhtar ya ƙi rufuwa. Sai rungume su Shahid yake yi kamar wasu manyan yara yana basu labarin Ammee za ta haifa musu ƙani. Suna so?

Ɗaga kai suka yi suna dariya ganin yadda yake dariya amma ba don sun fahimci abinda yake nufi ba.

Su da suka bar gida tun safe ba'a sallamesu sai da yamma liƙis. Ruwa leda biyu aka ƙara mata, kuma likita ya ce a barta ta huta ta hanyar samun wadataccen barci cikin nutsuwa.

Ita kuma Fatima wannan yinin asibiti da suka yi abin yayi mata daidai. Akwai wani yaro a maƙwaftansu da ta sani kafinta ne, tun safen ta kira shi yaje gidanta.

Ko da ta nuna mishi kujeru da shimfiɗar gadonta tana tambayarshi nawa za ta kashe gurin gyara su zama lafiyayyu? Domin kujerun har yadinsu take so a canza.

Kasancewar yaron yana da tsoron Allah kuma akwai zaman amana kai tsaye ya ce mata in dai za ta ji shawararshi ta canza kujerun kawai, saboda ruɓaɓɓun katakai ne aka lulluɓe su da katifa da yadi.

"Aunty Fatima ko kin gyara waɗannan sake ɓallewa za suyi. Amma idan za'a sami dubu tamanin a hannunki akwai wasu lafiyayyun kujeru a ƙasa da sai a kwashe waɗannan a kawo miki waɗancan."

Nannauyan ajiyar zuciya ta sauke tana jinjina shawarar da ya bata. Ta marairaice sosai tana kallon yaron mai suna Khalipha ta ce

"Wannan harka taimaka min za kayi Khalipha. Ka ga waɗannan ruɓaɓɓun kujerun wallahi a dubu tamanin da biyar suke a hannuna. Asabe Dillaliya cutata tayi, Allah zai min sakayya tsakanina da ita. Ka taimaka don girman Allah in baka cikon dubu hamsin ka kwashe wannan ka kawo min waɗancan..."

"Ina.. Ai hamsin baza ta yi ba Aunty Fati."

Taja yaja dai daƙyar ya karɓi dubu saba'in. Ta bashi dubu biyar kuɗin wasu sabbin shimfiɗun gado da zai kawo mata. Sai dubu biyar kuɗin motar da za'a kwaso kayan.

Yana fita bai ci awa biyu ba sai ga sababbin kujeru masu kyau daidai gwargwado ya kawo mata.

Cikin ƙanƙanin lokaci aka kwashe tsoffin kujerun da shimfiɗun gadon aka zuba mata sababbi. Sai ga guri ya fara fitowa tsaf.

Bakin Fatima har kunne saboda tsananin farin ciki da jin daɗi, ita kaɗai sai safa da marwa take yi tsakanin uwarɗaki da falo tana ƙyalƙyala dariya. Idan ta gaji da zurga-zurgar sai ta daka tsalle ta haye kan kujera tana sauke ajiyar zuciya, kujeru daƙauƙau, duk tsallen da tai tayi a kansu ko motsi basu yi ba.

"Saura labulaye."

Ta faɗa a fili tana kallon yadda ko kusa kalar kujerun basu shiga da labulayen ba.

Cikin ɗaki ta shige da sauri ta ɗauko wayarta, lambar wata tsohuwar ƙawarta Jamila da take aure kusa da kasuwar barci ta lalubo ta danna mata kira.

Sun taɓa magana da Jamilar ta tabbatar mata ana samun labulai masu kyau kuma cikin sauƙi a gwanjo, waɗanda idan ba ke kika faɗi cewa gwanjo bane za'a rantse da Allah sababbi ne.

Bayan gaisuwa Jamilar ta tabbatar mata in dai da kuɗi a ƙasa to akwai kaya. Nan take ta ɗauki hotunan kalar kujerun ta tura mata, ta tura mata kuɗi dubu ashirin.

Itama nan Jamilar bata ɓata cikakkun awa uku ba sai gata niƙi-niƙi da labulai. Kuma babu ƙarya sunyi kyau, sunyi kalar kujerunta. Sai dai a yamutse suke sosai.

Dubu biyu ta ba Jamilar da take kamar mayya gurin son kuɗi jikinta na rawa ta koma gida ta goge labulayen tas ta sake kawo mata.

Kafin ta bar gidan sai da ta taimaka suka maƙala labulayen. Sai ga guri ya sake fitowa gwanin ban kyau, ɗakin Amarya ya fito shar!

Saboda tsananin Murna ita kaɗai sai wani hura hanci take yi tana jin kanta a sama. Duk da ɗakin Fareeda ya fi nata kyau amma itama baza a raina mata ba.

"Hmmm! Wai dan ma babu kafet, dining table, da kayan kallo kenan. Ai wallahi da ɗakina sai ya yaga ma nata a kyau! Amma babu damuwa kan tafe kan isa dai."

Ta faɗa a fili tana sake hango yadda tsarin falon Fareeda yake a idanuwanta. Sai kuma taja tsaki, lokaci ɗaya ƙunci ya mamaye farin cikin da take yi tunano har yanzu fa Fareeda ta kere mata.

*****

"Amma dai kin tabbatar yanzu bakya jin ciwon komai?"

Ya tambayeta cikin kulawa a hanyarsu ta komawa gida. Hannunsa ɗaya na kan sikiyari yana tuƙi, ɗayan hannun kuma na riƙe da nata yana ɗan murzawa a hankali.

Kafin ta amsa sai da tayi murmushi, zuciyarta cike da jin daɗin wani kulawa ta musamman da ya ƙara ninka ma wanda yake mata a baya da jin zancen tana da juna biyu.

"Alhamdulillah! Ba na jin ciwon komai Habeebee. Na ji sauƙi sosai."

"Madallah! Haka nake son ji. Bari mu biya in muku takeaway, yadda baki da lafiyar nan bai kamata da mun je gida ki shiga kicin ba..."

"A'a! Don Allah ka barshi. Akwai ragowar abincin jiya babu abinda yayi. Kuma na ga ka aje nama a firij sai in haɗa in ɗunɗuma, zai ishe mu a wadace. Amarya ce dai ina roƙon alfarma ka ce mata tayi girkinta na dare, gobe da rana idan na dafa sabo sai in bata."

"Ba damuwa, Allah ya ƙara miki lafiya."

"Ameen"

Su Sayyid suka haɗa baki gurin amsa addu'ar! A tare iyayen suka saki murmushi.

Suna isa gida bayan ya taimaka mata zuwa ɓangarenta kai tsaye ya fice zuwa gurin Fatima.

Ko da ya shiga falon ko kusa hankalinshi bai kai kan gagarumin canjin da aka samu a kayan ɗakin ba.

"Kin ji mu shiru ko? Jikin nata ne sai a hankali..."

"Allah sarki! Sannunku da dawowa."

Ta faɗa da wani irin yanayi da ƙarara yake nuna mishi rashin damuwarta kan ciwon Fareeda.

Sai yayi turus a tsaye ya dafa hannun kujera yana kallonta, ta ci kwalliya sosai cikin wata doguwar riga yar kanti.

"Muje ki duba jikinta ko...?"

"Kwance take ranga-ranga ne? Ina kallonku ta window fa da ƙafafunta ta shige ɓangarenta. Tunda jikin ba tsanani yayi ba ko zuwa sati mai zuwa ne idan bata warke ba sai in leƙa ta."

Saboda tsananin takaici da baƙin ciki, tsawon minti biyu yana kallon ƙasa. Ya ma kasa kallonta, ya kasa buɗe baki yayi magana. Idan ya buɗe baki a yadda yake jin zuciyarsa lallai zai iya ɗuɗɗura mata ashar.

Sai kawai ya kaɗa kai ya juya zai fice daga cikin ɗakin.

"Haskenah, baka ga na yi canjin kayan ɗaki bane?"

Ta faɗa ganin yana gaf da ficewa ba tare da ya yaba ƙoƙarin da tayi gurin kashe maƙudan kuɗaɗe a gyaran ɗakin ba.

A ɗaiɗaice ya kalleta yana taɓe baki, ta wani tsuke cikin kayan da ya ƙara bayyana ramarta a fili tunda babu ciko. Ya kalli falon nata a wulaƙance, ya sake taɓe baki don ya cusa mata haushi

"Ummm na gani. Ba laifi. Duk da haka dai da kaɗan kwaɗo ya ɗara gaya. Ni dai har yanzu ko kusa banga royal chairs da gadajen da aka yi ƙaryar za'a cika min ɗakuna da su ba."

Ya fice yana jin sauƙi-sauƙin takaicin maganar da ta yaɓa masa kan ciwon Fareeda. Ko babu komai dai ya ɗan rama.

*****

A wannan dare, haka dai aka sake maimaita abin yau da safe. Sai bayan gama zafafan wasanni a tsakaninsu da ya yi yunƙurin shiga gonarsa sai ta kwanta likif, izuwa yanzu lamarin ya daina ba shi mamaki. Sai dai tsoro.

Ita kuwa Fareeda kawar da damuwar komai tayi tasha barcinta hankali kwance. Shi kuwa yana rungume da ita a ƙirjinsa yana karanta wasiƙar jaki.

Yʻar'uwa me kike jira? Na ce kin siya kuwa? Jibi ne fa idan Allah ya kaimu ranar Alhamis Promon maganin infection na Zee Maman Mujaheed zai zo ƙarshe. Idan baki mallaki naki ba ina tabbatar miki kiyi gaugawar taɓo ta ta whatsapp kiyi odar naki. Maganin zai kawar miki da duk wata damuwa ne ya ƙara armashin harka tsakaninki da Maigida ran gida. Zai kankaro miki mutunci da daraja fiye da yadda kike tsammani😍😍😍😘□□

Promo! Promo!! Promo!!! A baya tana sayar da maganin 4k ne. A yanzu ta sauƙaƙa shi zuwa 2k. Za ta rufe wannan garaɓasar ne a cikin sati ɗaya kacal! Yʻar'uwa me kike jira? Maganin nata ya samu shaidar aiki ingantacce kuma da gaugawa ake ganin biyan buƙata in sha Allah. Idan kina fama da ɗaya daga cikin waɗannan matsalolin ina mai baki shawara kiyi gaugawar siyan maganin Zee Maman Mujaheed□□

Ciwon gabobi, ciwon mara, fitar farin ruwa, kaikayi gaba, rashin Sha'awa, rashin kuzari gare ki ko ga namiji, rashin ni'ima, rashin haihuwa, kurajen jiki ko na gaba, jin Zafi yayin saduwa. Maganinta cikin sauƙi kuma a gaggauce yake magance duk

waɗannan matsalolin. Ki tura kudin maganin ta wannan account ɗin da ke ƙasa, sai ki tura mata shaidar biya da garin da kike ta lambar wayarta□□0 816 285 9027 Ga kuma acc ɗinta□□

3968303018

Zainab Shu aibu

Fcmb

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

_*22*_

Ku zo ku sayi data a gurina sai ku cigaba da karatu□□□□□□😘😘

Ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ki tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online ki kira ni ta 09077591726. In sha Allah cikin daƙiƙu ƙalilan datar da kika siya zai sauka a wayarki□□

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

10GB□□ N2500

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Na mu ba irin na su bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

Washe gari Fareeda ta tashi lafiya ƙalau, babu wani ciwo ko ƙanƙani da take ji a jikinta.

Amma saboda ɗoki da zakwaɗin cikin jikinta da Mukhtar yake yi haka ya dinga tarairayarta, duk inda ta saka ƙafa yana biye da ita. Duk aikin da ta kamo haka yake saka hannu ya tayata suyi su gama.

Ba yadda baiyi da ita ba kan ta zauna ta huta ta ce a'a! Ita baza ta iya kwanciya ba tare da ta gyara ɗakunanta ba.

Ya ce ta barshi yayi aikin, nan ma ta ce a'a! Baza ta iya zama tana kallonshi shi kaɗai yana aiki ba.

Wannan shi ne dalilin da yasa ya saka sauƙaƙan kaya marasa nauyi ya dinga taimaka mata. A yinin wannan rana, sun sabunta soyayyarsu fiye da yadda ake zato.

Minti ɗaya biyu zai kalleta da faffaɗan murmushi a fuskarsa ya ce

"Ina son ki Fareeda."

Idan ya faɗi haka wani irin girma kanta yake yi kamar zai fi ƙarfin gangar jikinta, zuciyarta ta cika ta tumbata da matsanancin farin ciki, har takan manta yanzu ba ita kaɗai ce da shi ba.

A yangace cike da ƙasaita take mayar mishi da martanin murmushinsa.

"Nima ina son ka Uban yaya-na."

"Allah ya barmu tare"

"Ameen thumma Ameen"

Suke haɗa baki su biyun gurin amsa kyakkyawar addu'ar da yayi musu. Sai su ƙara musayar murmushi sannan su cigaba da aikin da yake gabansu.

Irin kalaman soyayyar da ya dinga faɗa mata a wannan rana, kamar lokacin da ta samu cikin farko ne, tana Amarya.

Suna bala'in mararin juna tun gishiri bai fara sauka daga kan kaza ba.

Da an ɗauki yan mintuna zai riƙo ta zuwa jikinsa, cikin salon soyayya yake shafa lafaffen cikinta da in banda likita ya tabbatar tana da ciki babu wanda zai ce akwai ajiyar ɗa a ciki saboda shafewarsa.

"Baki gaji ba Matata? Ba na so ku wahala ke da Babys ɗina..."

Ta zazzaro idanu a tsorace ta ce

"Babys ɗin har guda nawa Habeebee?"

"Uku mana! Wancan karon kin bani biyu rayayyu kuma lafiyayyu yanzu ba sai ki bani uku ba?"

Ya raɗa mata a kunne, har lokacin yana shafa cikinta.

"Ban yarda ba, ni dai gaskiya ban yarda ba Habeebee. Haihuwa wahala, ko ɗaya Allah ya bani Allah ya saka mishi ko mata albarka."

Kukan shagwaɓa ta sakar mishi bayan gama maganar tana bubbuga ƙafafunta a ƙasa.

Ƙara riƙeta yayi sosai a jikinsa yana dariya yayi sama da hannayensa yana lalubeta kamar yana mata cakulkuli. Daƙyar ta iya ƙwace jikinta ta matsa gefe itama tana dariya.

Ko da ta gama abinci ta zuba na Fatima wadatacce a kula shi da kansa ya ɗauka ya miƙa mata.

Ya tarar da ita bakinnan a gaba don har lokacin bata manta maganar da ya yaɓa mata jiya ba. Kuma da safe ko sararin leƙawa ya duba yadda ta tashi baiyi ba, ta leƙa ta window fiye da sau talatin da tunanin ko ya fita ne sai taga motarsa na ajiye a tsakar gida.

Saboda wannan baƙin cikin da ƙyar ta iya buɗe baki ta gaishe shi.

Ya amsa hankalinshi kwance ba tare da ya bi ta kan ɗaure fuskar da take yi ba. Ya kai mazaunai zai zauna kenan kan ɗaya daga cikin kujerunta ta kalle shi da salon saƙa magana ta ce

"Ai na zaci ba ka lafiya ne. Tun safe nayi ta zuba idon ka shigo mu gaisa baka shigo ba, har na fara tunanin ko idan ba ranar girkin mace bane baza ka dinga leƙawa da safe kaga lafiyarta ba"

Zaman da yayi niyyar yi ne ya fasa, ya tsaya a tsaye.

"Amma dai kin san Fareeda ba ta da lafiya?"

Yayi mata tambayar idanunshi na cikin nata.

"Haka ka ce min dai."

Ta amsa bayan ta kawar da idanunta daga gare shi.

Da mamaki sosai a fuskarsa ya ce

"Haka na ce miki? Ƙarya nayi kenan?"

Shiru tayi bata amsa ba, sai ƙara tamke fuska da tayi tana hararar inda take kallo.

Shirunta shi ya fara fusata shi, da ɓacin rai ya kira sunanta.

"Fatima?"

"Na'am"

Ta amsa a ɗaiɗaice bayan ta taɓe baki.

"Wai me kike nema da ni ne tun jiya a gidannan?"

Yayi mata tambayar cikin tsawa-tsawa.

Runtse idanu tayi tana ƙoƙarin danne ɓacin ranta. Ta buɗe idanun bayan ta kalato hawaye ƙarfi da yaji ta kalle shi a raunane, da rawar murya ta ce

"Kayi haƙuri Haskenah! Allah ya huci zuciyarka. Ni ba nufi na in ɓata maka rai ba."

Kaɗa kai kawai yayi ya fice daga ɗakin, zuciyarsa cike da baƙin ciki. Ƙoƙarin watsar da tunanin komai yayi gaf da zai shiga ɓangaren Fareeda don kar ta karanci damuwa a fuskarsa itama ta shiga damuwa.

Cikin walwala da farin ciki suka ci abinci su da ɣayɣansu. Kamar a film, haka sukai ta ba juna da salon ƙauna har suka ƙoshi. Shi da yaran suka tattara farantan abincin zuwa kicin ita kuma tana zaune kan kujera a falo tana hutawa.

Ko da Magrib tayi sun rabu ne cikin farin ciki. Ita da yaran sai bye bye suke mishi kamar wanda zaiyi tafiya. Duk da bata furta ba, yana hango kewa mai girma a cikin idanunta.

Har ya fita sai ya dawo, kai tsaye inda take ya ƙarasa yaɗan riƙo ta kaɗan saboda idanun yaran ya ce.

"Ko in zauna sai zuwa anjima? sai in bata uzurin baki da lafiya..."

Da sauri ta katse shi da cewar

"A'a! Haba dai! Abinda bazan so ayi min ba bazan taɓa ba da damar ayi ma wata ba. Je ka Habeebee, Allah ya bamu alkhairi. Bayan ma kamar anjima ne kwanaki biyun za suzo su wuce..."

"Ai zan ma dinga shigowa duba lafiyarki da ta yara."

"To babu damuwa! Sai da safe."

Ta sakar mishi murmushi ta riƙe hannunshi cikin nata ta raka shi har ƙofar falon.

Fuskarta ya riƙe cikin hannayensa ya sumbace a laɓɓa. Ya shafo cikinta, ya tsugunar da fuskarsa saitin cikin ya sumbaceta, ya riƙo hannunta na dama ya sumbaceta.

Ya sake mata sallama ya nufi ɓangaren Fatima zuciyarsa tumbatse da kewar Fareeda da komai nata. A kasalance yake yafiya, yana yi yana tsayawa sai ya waiga ya kalli Fareeda da har lokacin take tsaye tana kallonsa, fuskarta da murmushi, hannunta ɗaya a sama alamar bye.

Duk wannan abu da yake faruwa kan idanun Fatima da tun da ya rage sha biyar a kira Magrib take ta safa da marwa tsakanin window da tsakar falon.

Ta sha kwalliya sosai kamar wacce take shirin zuwa dinner. Leƙe take yi taga ta ina Mukhtar ɗin zai fito, kuma da wani yanayi zai fito, farin ciki ko akasin haka?

Idan ta gaji da tsayuwa a window sai taja dogon tsaki, ta sake kallon agogo zuciyarta cike da matsanancin baƙin ciki da ɓacin rai.

A fili take surutan cewa

"Tun yanzu shegiyar nan za ta fara gwada min bariki ta hanyar mini ƙwangen lokacin barin miji ya dawo gurina? Wallahi sai na ci ubanta, zan nuna mata bata isa ba. Wato za ta nuna min ta fi ni sanin daɗin miji ko? Ni rannan ai ba haka na mata ba, tun la'asar ma da ya bar nan bai dawo ba sai da daddare da ya kawo min wata wulaƙantacciyar kaza."

Tayi ƙwafa mai ƙarfi, ta cije gefen laɓɓa tana girgiza kai.

"Daga ke har Mukhtar ɗin zan nuna muku ku ƙananun ƙwari ne. Na fi ku sanin duniya da ajujuwan cikinta na kissa da makirci"

A haukace ta shige uwarɗakinta ta ƙara janyo jarkar da aka cika mata shi taf da tsumin yar gata, ta ɗaɗɗaka sosai kafin ta mayar da jarkar inda ta ɗauko.

Kicin ta wuce ta ɗauko kofi da madara ta sake dama kalolin magungunan mata masu yawa ta shanye. Gyatsa mai ƙarfi ta saki saboda yadda cikinta ya cika sosai da magungunan da tun ukun rana take sha.

Ta sha alwashin yau sai ta saka Mukhtar ihu a kan gado, sai ga shi yana neman ɓata mata lissafin da ta yini tana yi a ƙwaƙwalwarta.

Ko da ta koma falon a wannan karon ba a window ta tsaya ba, ƙofar falon ta buɗe tana leƙen ɓangaren Fareeda kwatsam sai taga fitowarsu, kamar wacce aka dasa tana tsaye ta kasa motsawa daga gurin har Mukhtar ya gama sumbace sumbacensa ya kamo hanyar ɓangarenta.

"Auchhhhh"

Ta faɗa tana dafe goshinta bayan ya turo ƙofar ba tare da sanin tana tsaye a gurin ba ya buga mata a goshi.

"Subhanallahi, na buge ki ko? Me kike yi a bakin ƙofa?"

Ya tambayeta cikin kulawa bayan ya janyo ta jikinsa yana mulmula mata goshin.

"Na zo rufe ƙofar ne."

Ta amsa daƙyar cikin jin zafi, sosai ta bugu a goshin, hankalinta yayi nisa sosai har bata san ya iso bakin ƙofar ba da tuni ta kauce.

"Yi haƙuri. Sannu! Hankalina yayi gaba ban lura da ke a gurin ba."

Sosai ya mulmula mata goshin yana jera mata sannu kafin ya sake ta ya shige banɗaki don ɗauro alwalar sallar magrib.

Ita kuma kicin ta shige ta fara fito mishi da kayan abinci tana jerawa a tsakar ɗakin.

Har yayi mata sallama zai fita masallaci ta nuna mishi kular da Fareeda ta zuba mata abincin rana ta ce

"Ga abincin yan can ɓangaren fa. Ko za ka miƙa musu kafin ka wuce?"

"Ok!"

Ya amsa a taƙaice.

Har ya ɗauka zai fita jin kular babu nauyi sosai sai ya buɗe. Ƙanƙance idanu yayi yana kallonta bayan ya ga abincin can ƙasa, shinkafa ce da miya tayi, kuma miyar yar ɗugul akan shinkafar

"Miye haka Fatima? Wannan abincin ai ko su Sayyid bazai ƙosar ba balle ace har da mamansu. Kuma saboda Allah sai ki zuba musu miyar akan shinkafa? Idan ba yanzu za su ci ba fa?"

Narai narai tayi da fuskarta cikin sallamawa ta ce

"Ayya Haskenah, don Allah kayi haƙuri. Na san Fareeda bata cika cin abinci da yawa ba shi yasa ban cika musu ba, kuma daman yaɗan kaɗan na dafa saboda kar inyi ɓarna. Amma zan kiyaye gaba in sha Allahu. Kayi haƙuri."

Bai ce komai ba. Inda ta jera nasu abincin ya nufa ya, ko da ya buɗe babbar kular sai yaga ta shaƙe musu taf da farar shinkafa. Ta miyar ma ta zuba a wadace ga mai nan nasha-nasha a sama.

Ajiye wanda ta zuba ma Fareeda yayi ya ɗauki wanda ta zuba musu ya nufi ƙofa zai fita da su.

"Zan kai musu wannan. Ke sai ki ci wancan, ko ban samu ba babu damuwa sai in sha tea."

Ya fice da kulolin a hannunsa, ya barta daskare akan kujera baki buɗe. Ranta a ɓace, zuciyarta a ƙuntace. Tsabar baƙin ciki da takaici bata san sa'adda ta lailayo wani ƙatoton ashariya ta maka ma Fareeda da yayanta ba.

Daƙyar ta iya danne zuciyarta ta shige banɗaki tayi alwala. A gurguje tai salla ta sabunta kwalliyarta ta ƙame akan kujera tana jiran dawowarsa.

Yau ranarta ce, lokacin gaba ɗaya nata ne. Ko kaɗan ba ta son tayi abinda zai janyo ɓacin rai tsakaninta da Haskenta.

Ko da ya dawo daga masallaci bai shiga gurinta ba, sai tashin motarsa taji alamun zai fita daga gidan. Da gudu ta leƙa ta window sai bayan motarsa ta gani yana gaf da fita.

Turus tayi a tsaye, zuciyarta cike da tunanin ina kuma za shi a wannan lokacin da ya kamata ace tana zaune a cinyarsa suna ciyayyar abinci a tsakaninsu?

A sanyaye taja ƙafafunta ta koma kan kujera ta zauna, ta zuba tagumi da hannu bibiyu, zuciyarta danƙare da saƙe-saƙe mabanbanta.

Minti talatin da fitarsa ya dawo gidan. Ko da ya shiga har lokacin tana zaune inda take, ta amsa sallamar da yayi a sanyaye.

"Barka da zuwa"

"Yauwa!"

Ya amsa haɗe da miƙa mata ledar hannunsa. Ya ƙara da cewa

"Ga alƙawarinki na cika. Rabin kazar amarcin da kike bi na..."

"Haba Haskenah, wallahi da ma baka wahal da kanka gurin siyowa ba. Ai ka fi ƙarfin kaza a guri na."

Ta ƙarasa maganar haɗe da kaɗa ƙwayoyin idanunta cikin salo tayi wani farrrr da su.

Sai da yayi dariya sosai sannan ya ce

"Kar ki damu. Ki ci kawai, hakkinki ne a al'adance matsayinki na Amarya. Ina dai ƙara roƙon afuwa kan jinkirin da nayi gurin cika wannan al'ada."

Martanin dariyarsa ta mayar mishi sannan ta shige kicin ledar na riƙe a hannunta.

A faranti ɗaya ta juye naman kazar, ta sako cokula masu yatsu guda biyu ta fito tana rangwaɗa ta ƙarasa kusa da shi ta zauna a kujerar da ke gefensa.

"Bismillah Haskenah! Jin daɗin cin kazar amarci a ci shi tare da ango, daga nan ko me zai biyo baya zai taho ne a marmarce kuma cike da armashi. Ko ba haka ba Aban Twince nawa?"

"Wannan haka yake Amaryata"

Ya amsa yana dariya.

Tare suka ci naman kamar yadda ta buƙata, ta zubo musu abinci a faranti ɗaya suka ci tare. Duk da ɗarewa kan cinyarsa bai samu ba soisai ta ji daɗin yanayin da suka kasance ita da shi.

Saboda tsananin shauƙi har bai san ji sadda aka kira sallar isha'i ba, sai ji yayi ana raka'ar ƙarshe. Ko kafin yayi alwala ya fice har an idar da sallar. Anan cikin falonta yayi sallar yana jin babu daɗi na rashin jam'in da bai samu ba.

****

Bai manta yadda ya tarar da Fatima a darensu na farko ba. Amma saboda yana so ya share ma kanshi tantamar ko ba shi da lafiya ne shi yasa tana fara tayawa ya amshi gayyatarta da gaggawa.

Wani irin salo ne taje mishi da shi cikin ƙanƙanin lokaci ta birkita shi, sosai jikinsa yake karɓar saƙonnin da take aika mishi.

Wani abin ban mamaki a gare shi, wani abin tsoro da firgici, wani abin tunani a gare shi shi ne yadda ya iya ratsa gonar Fatima ba tare da fuskantar matsala makamanciyar wacce ya fuskanta tsakaninshi da Fareeda ba.

Bayan kammaluwar komai gefe ya matsa a wahalce yana sassauke ajiyar zuciya. Ita dai Fatima har yanzu matsalar jiya na nan a jikinta, bai saba jin irin haka a jikin Fareeda ba, gaskiya bazai iya ba. Gara tun da wuri ya sanar da ita idan ma wani

magani take amfani da shi da yake sakata bushewa ta daina, shi ba ya jin daɗi, ko kusa ba ya jin wani armashi a karo biyun da suka yi. Har ta fara barci ya tashe ta.

"Haskenah? Ya aka yi? Akwai wata matsala ce?"

Ta tambayeshi tana mutsutsuke idanunta.

"Fatima, in faɗa miki gaskiya ko in ƙyale ki cikin duhu?"

"Faɗa min Haskenah, don Allah faɗa min. Allah yasa dai ba wani laifi nayi maka ba. Idan nayi laifi ne don girman Allah kayi haƙuri ka yafe min, da alkhairai nake nufinka a zamanmu ba na so muna yawan samun saɓanin fahimta..."

"Dakata Fatima. Ni ban ce kinyi min laifi ba."

Ya katse ta. Sai kuma yayi shiru ya haɗiye miyau sau ɗaya.

"Fatima. Ni fa gaskiya a yadda nake tarar da ke ɗinnan ba na jin daɗi."

Ba tare da wani alkunya ko karantawa ba ya faɗa mata yadda yake jin ta a bushe ƙamas.

"Don haka idan ma wani magani kike amfani da shi da ya mayar da ke haka ina baki shawarar ki daina. Don wallahi ni bazan iya jurewa ba, shi yasa kika ga ko a wancan kwanakin na amarci tun daga sau ɗaya ban ƙara yunƙurin cewa zan wani taɓa ki ba."

Yana gama maganar ya faɗa banɗaki, ba tare da ya saurari ko za ta mishi wani ƙarin bayani ba.

Hankalin Fatima a tashe ta saka kuka ƙasa-ƙasa, wani iri take jin jikinta gaba ɗaya, irin a muzancen nan. Anya a duniya akwai abinda ya fi wannan ban takaici da baƙin ciki? miji ya ƙeƙashe idanunsa ba tare da jin kunya ko karantawa ba ya faɗa ma matarsa ba ya jin daɗinta a ɓangaren auratayya?

A wannan dare ta ci kuka har ta gode Allah! Barcinta raba da rabi ne, zuciyarta cike da tunanin hanyar da za ta bi don magance wannan matsalar da gaggawa. Ashe shi

yasa ko irin ɗokinnan na amare Mukhtar ba ya nuna mata? To menene amfani duk magungunan da ta siya ta hannun Ramlah da sauran masu magungunan mata? Duk sun tashi a banza kenan? Yaudararta suka yi ta ɓarnata dubban kuɗaɗenta a banza ko kuwa ita ce magungunan basuyi aiki a jikinta ba.

Shi dai Mukhtar juya mata baya yayi yashaa barcinsa hankali kwance, cikin nutsuwa. Domin ya gama sakankancewa a zuciyarsa tunda ya samu nasarar ratsawa ta gonar Fatima, tabbas babu wani abu da zai hana shi samun kyakkyawan mu'amala tsakaninshi da Fareeda.

Washe gari da wuri ya shirya ya fice, a gurguje ya leƙa Fareeda ya duba lafiyarta da yara sannan ya fice daga gidan. Gurin aikinsa ya nufa, hutun sati ɗaya aka bashi don cin amarci. Tun jiya Ogansu ya kira shi ya jaddada mishi lallai yau ya zo Ofis akwai wasu takardu da ake buƙatar ya duba ya saka musu hannu, da gaggawa ake buƙatarsu bazai yiwu a jira zuwanshi jibi da hutunsa zai ƙare ba.

Ko wanka bata yi ba ta ɗaga waya hankalinta a tashe ta kira wata makwafciyarta da suka yi zaman mutunci da amana mai suna Aunty Ladidi.

Aunty Ladidi irin matannan ne masu tsage gaskiya komai ɗacinta. Duk yadda take aminci da ke ko take ƙaruwa da ke ba ta jin kunya ko tsoron ta wanke ki tas idan taga kina neman kauce hanya.

Ko a batun aurenta da Mukhtar har gida Aunty Ladidi ta bi ta tayi mata wankin babban bargo, ƙal tayi mata sannan ta bar gidan. Ko a yanzu ta yanke shawarar neman Aunty Ladidin ne saboda ta san ita ɗin idon gari ne, tana da mutane sosai. Kuma tana sana'ar haɗa magungunan mata ingantattu waɗanda take haɗawa da hannunta, dangin kayayyakin ciye-ciyenmu da ganyayyaki masu amfani a jikinmu mata

Yau ne fa da misalin ƙarfe goma sha biyu daidai na dare Zee Maman Mujaheed za ta rufe garaɓasar siyan maganin a sauƙaƙe. Kin siya kuwa? A baya tana sayar da maganin 4k ne. A yanzu ta sauƙaƙa shi zuwa 2k. Ƴar'uwa me kike jira? Maganin nata ya samu shaidar aiki ingantacce kuma da gaugawa ake ganin biyan buƙata in sha Allah. Idan kina fama da ɗaya daga cikin waɗannan matsalolin ina mai baki shawara kiyi gaugawar siyan maganin Zee Maman Mujaheed□□

Ciwon gabobi, ciwon mara, fitar farin ruwa, kaikayi gaba, rashin Sha'awa, rashin kuzari gare ki ko ga namiji, rashin ni'ima, rashin haihuwa, kurajen jiki ko na gaba, jin Zafi yayin saduwa. Maganinta cikin sauƙi kuma a gaggauce yake magance duk waɗannan matsalolin. Ki tura kudin maganin ta wannan account ɗin da ke ƙasa, sai ki tura mata shaidar biya da garin da kike ta lambar wayarta□□0 816 285 9027 Ga kuma acc ɗinta□□

3968303018

Zainab Shu aibu

Fcmb

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

_*23*_

Ku zo ku sayi data a gurina sai ku cigaba da karatu□□□□□□😘😘

Ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ki tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online ki kira ni ta 09077591726. In sha Allah cikin daƙiƙu ƙalilan datar da kika siya zai sauka a wayarki□□

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

10GB□□ N2500

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Na mu ba irin na su bane shi yasa farashin daban yake da nasu😊😊

Cikin kuka mai bayyana tana cikin masifar tashin hankali take roƙon Aunty Ladidi a waya don girman Allah ta taimaka mata, tazo gidanta da gaggawa a safiyarnan, tana cikin wani gagarumin bala'i ne da idan ba Aunty Ladidin ba babu wacce za ta iya fitar da ita a cikin wannan halin.

"Allah ya raba mu da bala'i"

Aunty Ladidi ta faɗa cikin rashin damuwa da irin kukan da Fatima take yi.

Daƙyar Fatima ta iya tsagaita kukan ta amsa da

"Ameen"

Ladidi ta gyara zama ta cigaba da cewa

"Maman Ummee (Inkiyar da suke ma Fatima da sunan yarta ta farko) a halin yanzu gaskiya bazan iya sakin ayyukan da nake yi in taho gidanki ba. Ah toh iya zallar gaskiyar magana kenan, bazan yi ƙarya don ki so ni ba.

Amma idan kin ga matsalar za ta faɗu ta waya ki faɗa min, ina saurarenki. Idan kuma baza ta faɗu ba to ki jira ko zuwa nan da sati mai zuwa, kila in samu sararin leƙowa."

Katse kiran tayi ta saka katin dubu ɗaya ta banki cikin ragowar kuɗin da suka rage mata, sannan ta sake kiran lambar Aunty Ladidi. Ba tare da ɓata lokaci ba ta zayyane mata irin matsalolin da take ciki ita da Mukhtar, tana maganar tana kuka. Idan ta tuna yadda ƙeƙe da ƙeƙe cikin dare ya iya sanar da ita yadda take sai taji zafafan hawaye sun sake ɓalle mata, zuciyarta sai wani irin suya da ƙuna take mata kamar ana babbakata ta ciki.

"Ashsha! Eh lallai Maman Ummee dole kiyi kuka. Miji ya fito ɓaro-ɓaro ya faɗa miki irin wannan magana dole hankalinki ya tashi afujajan ki fara neman mafita.

Amma na ce ba? Kin sha magungunan sanyi kafin ayi biki kuwa? Kin san shi ne babban ciwon da ke janyo matsala makamantan naki da wasu waɗanda suka fi naki. Kamar su ƙaiƙayin gaba, rashin sha'awa, jin zafi lokacin mu'amalar auratayya, rashin kuzari, ke ciwon sanyi har hana haihuwa yake yi. Kin sha maganin sanyi?"

"A'a!"

Ta amsa muryarta na fita da ƙyar! Ta ƙara da cewa

"Amma magungunan mata babu kalar wanda ban sha ba..."

"Shirme kika yi kenan! Ta yaya ga sanyi danƙare a jikinki za ki tsaya ɓarnata kuɗaɗenki a magungunan mata? Baza su taɓa yi miki aiki ba, dama maganin sanyin kika yi ko baki sha maganin mata ba in dai kin dace da maganin sanyi mai kyau ni'imarki da Allah ya halicceki da ita za ta dawo taf! Maganin mata ana sha ne kawai don bahaushe ya ce ko kana da kyau ka ƙara da wanka..."

"Yanzu ya zanyi Aunty? Don Allah ki taimaka min."

Tayi maganar cikin marairaita da rawar murya.

"Eh to akwai yadda za kiyi mana. Amma fa in kina da kuɗi. Shi ciwon sanyi da kike gani balayꞏayꞏyꞏen ciwo ne da idan ba dace kika yi da magani ba sai dai kiyi ta wahala. Kuma an fi dacewa da maganinsa a ɓangaren magungunan gargajiya, na asibiti sai tsananin sa'a za ki rabu da ciwon gaba ɗaya. Amma na gargajiya idan Allah ya taimakeki kika yi dace da ingantaccen magani kamar na Zee Maman Mujaheed cikin ƙanƙanin lokaci za kiga biyan buƙata..."

"Wacece ita? Aunty Ladidi ina son maganin, a ina take? Nawa ne kuɗin maganin? Wallahi ko nawa ne zan siya in dai zan samu waraka daga wannan matsala."

"Don waraka fa za ki samu da yaddar Allah! Mata da ɗunbin yawa sunyi amfani da maganinta kuma sun ga biyan buƙata. Kuma wani abin armashin shi ne sam maganinta babu tsada, galan dubu huɗu ne. Nima ba ta hannuna za ki sayi maganin ba, akwai wata ƙawar ƙanwata da take sayar da ingantaccen haɗin gyaran nono da cikowarsa ita naga ana kawo ma maganin masu siye anan kaduna suna karɓa a gurinta. Ita Zee Maman Mujaheed ɗin a katsina take, amma duk sa'adda kika yi magana kina son maganinta a cikin yinin ko washe gari saƙonki zai iske ki har garin da kike zaune."

"Maganin cikowar nono?"

Fatima ta tambaya cikin zakwaɗi, zuciyarta cike da tunanin yadda a fili Mukhtar yake tattaro suɗaɗɗun silifas ɗinta yana yamutsawa babu shauƙi ko kaɗan a tare da shi.

"Shi ma maganin nonon ina so. Nawa take sayarwa?"

"Dubu biyu da ɗari biyar ne ɗan ƙaramin bokiti. Kuma wallahi ina mai baki tabbacin maganin nonon da za ki siya gurin Farida ba nono kaɗai zai gyara miki ba, har ni'ima yana ƙara ma mace saboda nagartaccen haɗi take yi ba irin na yꞏan kuci ku bamu ba. Bayan ni'ima zai sa jikinki yayi kyau, ki murmure, fatarki tayi ta sheƙi saboda kunun da kike sha na maganin..."

Jikinta a sanyaye jin sunan mai maganin ta ce

"Sunan mai maganin Farida? A ina take ?"

"Kinkinau, ta gurin masallacin musabaƙa."

Kamar baza ta siya ba, jin sunan mai maganin ɗaya da na kishiyarta da ta tsaya mata a ƙahon zuci. Sai kuma wata zuciyar ta umarceta da ta siya, ai ba gurin kishiyar bace balle a ce tayi abin kunya. Kuma Fareeda nawa ne a duniyarnan?

"Ina son maganin Infection ɗin galan biyu. Shi ma maganin nono ina son roba biyu. Amma zan samu da wuri ko Aunty? Idan da so samu ne a kawo min tun yau in fara amfani da su."

"Kar ki damu. In dai kina da kuɗi a ƙasa za ki samu magunguna akan lokaci. Bari in kira Farida in ji yadda za kuyi."

Bayan minti goma sha biyar Aunty Ladidi ta tura mata lambobin waya guda biyu, da bayani kamar haka.

"Ga lambobin masu sayar da magungunan ki kira su, za su baki acc no ki tura musu kuɗi za su faɗa miki lokacin da saƙo zai iske ki 09077591726□□Farida Maganin nono. 0816 285 9027□□ Zee maganin infection."

Akan gwuiwa take, don haka babu ɓata lokaci ta kira lambobin. Sosai ta saki jiki ta faɗa ma matan biyu halin da take ciki, saboda Farida da Zainab mata ne da suka iya kasuwanci, sun iya tafi da jama'a cikin haba-haba da fara'a.

Shawarwari sosai suka bata na yadda ko bayan tayi amfani da magungunan za ta kiyaye kamuwa da makamantan matsalolin in dai ba wata muguwar ƙaddara ba da ba'a fata. Sannan suka faɗa mata yadda za tayi amfani da maganin, kuma sai washe gari za'a kai mata maganin. Ita za ta biya kuɗin delivery.

Acc no suka tura mata ta saka musu kuɗaɗen siyayyar da za tayi. Yinin wannan rana haka ta ƙarasa shi cikin ƙunci da damuwa. Ko abincin rana sai gaf da la'asar ta samu ta dafa jallof ɗin taliya.

Bata ji kashaidin da Mukhtar yayi mata jiya ba, haka ta sake zuba ɗan cukul a kula tana zubawa tana ƙunci, ita wannan tsarin na yin girki ɗaya sam baiyi mata ba. Don dai kawai ba ta da yadda za tayi ne.

Tun safe ko wanka bata samu sararin yi ba, a taƙaice ma babu aikin da tayi a ɓangarenta. Tana kwance tana tufka da warwara, wani lokacin kuma ta cigaba da saƙa da mugun zare kamar yadda ta saba.

Gyale ta ɗauka ta yafa kan kayan barcin jikinta ta fice da kular abincin a hannunta, fuskarnan a ɗaure tamau. Ta nufi ɓangaren Fareeda tana tafiyar laƙaiƙaita za tayi baza tayi ba.

Tun daga nesa ta hangi Fareeda zaune akan kujeran roba a ƙofarta, daga ɗan nesa kaɗan kuma almajirin da yake yi mata wanki ne, ga kaya nan a gabanshi ya duƙa yana wankewa.

Ko da ta isa ƙofar Fareeda maimakon a mutunce tayi mata sallama, ko baza su gaisa ba ta ajiye mata abincin, sai kawai ta ƙarasa gurin almajirin kai tsaye. Sunan yaron Yusuf, ta san shi yake yi ma Fareeda wanki tun da daɗewa, a wasu lokutanma har ita tana kwaso kayan wanki daga gidanta ta kawo ma Yusuf ɗin ya wanke mata anan gidan Fareeda.

A fili ta kalli Fareeda ta galla mata harara. Irin yadda Fareedar tayi kyau cikin sakakken doguwar rigar jikinta shi ne abinda ya ƙara ƙuntata zuciyarta. Har baiken kanta ta gani, me yasa bata tsaya tayi wanka ta sha uban kwalliya kafin ta fito kawo abincin ba?

Taja dogon tsaki kamar bakinta zai taɓi ƙasa. Ta kalli almajirin ta ce

"Yusuf sannu da aiki. Karɓi wannan abincin ka miƙa ma wancan matar."

Ta ƙarasa maganar tana nuna Fareeda a wulaƙance da yatsarta manuniya.

Tun isarta gurin, Fareeda tana kallonta. Tana kallon yadda take ta wani kallon komai a wulakance, tana kallon yadda ta galla mata harara, amma sai tayi kamar bata gani ba.

Tana jin yadda ta ja mata tsaki amma duk ta basar, kamar bata san da wanzuwar Fatima a gurin ba. Fuskarta yana kan wayarta da take dannawa a hankali, lokaci bayan lokaci ita kaɗai sai ta saki murmushi.

Karaf maganar da Fatima tayi ya faɗa cikin kunnenta, wani ƙayataccen murmushi ta sake yi. Ta ƙasan idanunta take kallon yadda almajirin ya duƙa har ƙasa ya gaishe da Fatiman, sannan ya karɓi kular abincin ya nufo gurinta da shi.

"Yusuf ka faɗa mata ta sake abincin yanzunnan ta baka kular ka miƙo min. Sannan sabbin kulolina na jiya da Haskenah ya kai mata abinci ta baka ka kawo min, tunda ba uwar mace ta siya min ba."

Fatima ta faɗa cikin tsiwa da masifa.

Duk da ranta ya ɓaci da jin zagin da tayi mata a fakaice, ko kaɗan bata nuna a fuskarta ba. Kanta yana ƙasa tana cigaba da shafa fuskar wayarta, duk da izuwa lokacin ta daina fahimtar rubutun da take karantawa a fuskar wayar.

Idan akwai wani abu da Fareeda tayi matuƙar ƙwarewa akai shi ne ɓoye ɓacin ranta. Bata iya riƙe baƙin ciki a zuciyarta ba, amma idan ba ita ta so ba duk yadda za ka so ka ɓata mata rai ko ta ji haushi baza ta taɓa nuna maka ba.

Har wannan lokacin murmushin fuskarta duk da ya koma na yaƙe ne bata bari ya ɓace ba.

Yusuf na isa gurinta ya duƙa har ƙasa ya ajiye kular a gabanta, kusa da ƙafafunta, a ladafce ya ce

"Aunty wai ga shi, ki sake ki bata kular da kulolin jiya."

Irin yadda Fareeda ta janye ƙafafunta a ƙyamace daga jikin kular abincin da almajirin ya ajiye shi ne abinda ya fara dukan zuciyar Fatima. Bata gama farfaɗewa daga wannan takaicin ba ta ji Fareeda ta kira Yusuf da har ya miƙe zai koma kan aikin da yake yi.

"Buɗe kular mu ga jagwalgwalon da ke ciki."

Fareeda ta umarci Yusuf.

Babu musu kuwa ya tsuguna da hannunsa duk kumfa ya kama murza murfin kular, daƙyar ya buɗe saboda santsin hannayensa.

Taliya ce dafa duka ta manja, da yake a gurguje aka dafa ta sai bata wani ji kayan haɗi ba, kuma sa'adda ta gama dafawar ba'a lokacin aka kawo ba sai ta wani irin sanƙarewa a cikin kular babu ko armashin kallo a idanu.

Fatima tana kallon yadda Fareeda ta kawar da kanta da sauri daga kan abincin, ta mele baki gefe ɗaya.

"Yusuf za ka iya ci? idan baza ta ciwu maka ba ɗauko robarka ka sake a ciki, idan ka koma makaranta sai ka ba waɗanda basu samu abinci ba. Wata ƙil su su iya cin wannan busasshiyar taliyar mai kama da ta yʻan fursuna. Idan ka sake ka miƙa mata kular..."

"Aunty sauran kulolin da ta ce ki bata fa?"

"Yusuf ka faɗa mata wanda ya kawo abincin jiya, idan ya dawo shi zai shiga kicin ɗina ya ɗauko ya kai mata."

Tana gama faɗin haka a ƙasaice ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya, ta ɗan zamo gaba kaɗan a kan kujerar da take zaune ta ɗaga wayarta ta cigaba da dannawa.

Fatima tana tsaye ita kaɗai sai huci take kamar kububuwa. Lallai wannan shi ne baki idan ya san abinda zai faɗa bai san abinda za'a mayar mishi ba. Tana kallon

yadda almajiri Yusuf ya ɗauko robarsa ya kara saman robar daidai kan sabon kularta da ko Mukhtar bai taɓa cin abinci a ciki ba.

Ya dinga buga kular kan robar saboda taliyar ta fara sanƙarewa, shi kuma so yake ya kifa abincin cikin robarsa ba tare da ya saka hannu a ciki ba, zai iya kai bayan magrib bai koma makaranta ba, baya so ta fara saki.

A ƙoshe yake, tun ɗaya da rabi na rana Fareeda ta shaƙo mishi faranti da indomie da dankalin turawa, an zuba busasshen kifi wadatacce a ciki, duk loma ɗaya biyu sai ya ci karo da kifi. Da ya gama ya kora da ruwan pure water guda biyu, kun san indomie tana da riƙe ciki har yanzu dam yake jin sa.

Daƙyar abincin ya saku kirif a cikin robarsa, bayan kular ta gama shan buguwa da wujijjiga. Bakin kular jage-jage da manja ya rufe da murfin ya ƙarasa ya miƙa ma Fatima.

"Ga shi, an gode Allah ya karɓa."

Ta kasa karɓan kular saboda ɓacin rai, ta kasa amsa addu'arsa don ba tayi niyyar sadaka ba.

Shi kuwa ya ajiye mata nan gabanta a ƙasa ya koma kan aikinsa.

Fatima da ta rasa abinda za tayi ma Fareeda ta huce sai kawai ta cire gyalen da ta rufa da shi taci ɗamara, idanunnan sunyi jajur don ɓacin rai.

Ta buɗe baki za ta fara zuba zallar madaran rashin mutunci na bala'i sai ga Mukhtar ya shigo cikin gidan. Da manyan ledoji biyu riƙe a hannayensa.

"Oyoyo Abee! Da fatan ka dawo lafiya?"

Fareeda ta faɗa tana kallonshi da yalwataccen murmushi a fuskarta.

Martanin murmushinta ya mayar mata. Ya amsa gaisuwarta da kulawa yana tambayarta ya jiki?

Idanunsa na faɗawa cikin na Fatima ya ce

"Ke kuma lafiya kuwa?"

Ganin rigar barcin jikinta shara-shara ga almajiri na tsugune yana wanki a gurin ya saka shi ƙanƙance idanunsa.

"Menene haka? Wani wawancin shiga ne wannan?"

Ya sake mayar da idanunsa kan Fareeda ya ce

"Me yake faruwa anan? Kamar akwai abinda ba daidai ba.."

"Komai lafiya kalau Oga. A huta gajiya. Ni daman zan shiga ciki ne."

Tana gama faɗin haka tsam ta miƙe tsaye, ta nufi ciki hannunta riƙe da wayarta.

Bayanta Mukhtar ya bi. Itama Fatima a fusace ta bi bayanshi zuwa falon Fareeda.

Suna shiga ciki ta zube ƙasa gaban Mukhtar ta saka kuka.

"Haskenah! Menene laifina don na aure ka? Na zaci Aunty Fareeda za tayi haƙuri ta rungumi ƙaddara mu zauna cikin aminci kamar yadda muke a baya..."

"Don Allah saurara! Me yake faruwa?"

Yayi maganar yana kallonta. Sai kuma ya mayar da idanunsa kan Fareeda da taja ta tsaya a tsakiyar falon, ta harɗe hannayenta a ƙirji tana kallon Fatima da wani irin yanayi mai wuyar fassarawa.

A hankali ta sassauta kukan da take yi, ta gyara zama idanunta cikin na Mukhtar, har lokacin hawaye basu daina tsiyaya a idanunta ba.

"Haskenah kai ka saka dokar abincin rana da dare wacce take da girki ita za ta zuba ma mare girki. Yau tun safe yini nayi a kwance ba ni da lafiya, ban samu sauƙin shiga kicin ba sai ɗazu. Kuma ba don kowa na ƙuƙuta nayi girkin ba sai don ita da yaranmu. Kawai ina kawo mata abincin ko buɗewa bata yi ba ta fara saƙa min baƙaƙen maganganu, har tana cewa wa zai iya cin ƙazantaccen jagwalgwalon abinci na? Don ƙarin wulaƙanci a gaba na ko taɓa kular bata yi ba ta ce almajirinta ya sake a robarsa..."

"Me yasa haka Fareeda?"

Ya tambayeta fuskarsa na nuna ko kusa bai ji daɗin abinda Fatima ta faɗa mishi ba.

Ita kuwa Fareeda mamakin ƙarya da munafurcin Fatima ke neman kifar da ita a tsaye. Har wani jiri jiri ne taji yana ƙoƙarin kayar da ita. Daƙyar ta iya ɗaga yatsarta manuniya ta nuna masa agogo, ƙarfe huɗu da minti goma.

"Ni da yara baza mu iya jure har ƙarfe huɗu bamu ci abincin rana ba. Tun da naga ɗaya ta wuce na dafa mana indomie muka ci, ko na karɓi taliyar da ta kawo min ba ci zamu yi ba, shi yasa na ba almajiri. Ka faɗa mata, daga yau girkin rana idan ya wuce ƙarfe biyu ta dafa ita kaɗai kawai, bazan rasa yan dabarun da zanyi mu ci ni da yayana ba."

Bata ƙara tsayuwan minti ɗaya ba ta shige cikin ɗakinta, ta barsu a gurin suna kallon-kallo.

"Yanzu saboda Allah da Annabi ke ko kunyar fitowa a haka baki ji ba? Dube ki fa? Dubi jikinki? a madadin ki saka ƙaton hijabi da zai rufa ma ƙasusuwanki asiri sai ki fito haka ƙozai-ƙozai kamar bulala? Kuma wannan ɗamarar da kika ci ta menene? Dambe kike shirin yi da ita?"

Da sauri ta fara warware ɗamarar da tayi ba tare da ta ce komai ba. Sosai ranta ya ƙara ɓaci, so tayi reshe ya juye da mujiya Mukhtar ya goyi bayanta yayi ma Fareeda gagarumin cin mutunci. Sai ga shi buƙatarta bata biya ba.

"Tashi mu tafi."

Ya bata umarni.

Gyalen da ta warware ta rufa a kanta ta wuce gaba yana biye da ita a baya har zuwa ɓangarenta. Kamar tayi mishi maganar ledojin da ya shigo da su ya bari a falon Fareeda, sai kuma dai taja bakinta ta tsuke.

Nan falonta taja ta tsaya shi kuma ya wuce cikin ɗakinta, sai ga shi ya fito wuf kamar wanda wani abu ya biyo.

"Fatima? Wani irin iskanci ne haka za ki bar shimfiɗa kaca-kaca tun yadda na fita da safe na barshi?"

Ta fara kame-kame ya dakatar da ita ta hanyar daka mata wani gigitaccen tsawa da ya saka ta durƙushe ƙasa tana riƙe cikinta da taji lokaci ɗaya ya ƙulle a guri guda.

"Kin ga, ba na ciki da iskanci da rainin wayau! Kar ki kuskura ki ce za ki kawo min banzar uzurin baki da lafiya. Ƙazanta, shi ne babban abinda zai sa a fara jin kanmu da ke, ba na son ƙazanta ko kaɗan, ba na ƙaunar ƙazama, ko na minti biyar ba na jin zan iya jure zama kusa da wacce na san ba ta da tsafta. Minti ashirin na baki ki tabbatar kin gyara ko ina ƙalƙal. Kina ji na?"

Yayi mata tambayar cikin tsawa.

"Eh! eh! eh na ji. Kayi haƙuri. Zan kiyaye"

Ta amsa bakinta na rawa.

Ficewa yayi daga ɗakin gaba ɗaya ya koma can ɗakin baƙi. Ransa a ɓace, in banda ƙazanta irinna Fatima ko singiletin da ya cire ya aje a gefen gado ta kasa kawar da shi daga gurin balle tayi tunanin wankewa? Da alamun akwai wasu notocin kanta da basu gama ɗauruwa da kyau ba, shi kuwa zai ɗaure mata su gam don ta san shi ba irin sakarkarun mazannan bane da suke jure ƙazanta daga matayensu.

Ko da ta gyara ɗakunan zuwa falo ya leƙa bayan ya dawo sallar magrib babu wani walwala a fuskarsa.

Abincin Fareeda ya ɗauka da yara ya miƙa mata, ya kwaso mata waɗancan kulolin na jiya. Ya dawo ya zauna a falo yana ta daddana wayarsa. Ko abincin da ta jera mishi cewa yayi sai yayi sallar isha'i zai ci.

Haka ta rakuɓe gefe ɗaya, kallo ɗaya za'ayi mata a gane a ɗarare take. Allah Allah take gobe tayi a kawo mata magungunan da ta siya ta fara amfani da su, don ita a ganinta waɗannan matsaloli guda biyu su ne manyan dalilan da suka sa Mukhtar ya juya mata baya a lokacin da ya kamata ace yana tsananin tarairayarta.

Haka suka kwana zuciyoyinsu babu daɗi. Kamar yadda yayi sammakon ficewa gurin aikinsa jiya, yau ma haka ya fice bayan ya karta mata kashidin saura tayi lattin abinci, ko kuma ya dawo ya tarar bata gyara ɗaki ba.

Ƙarfe ɗayan rana aka kira ta a waya, kwatancen gidanta aka tambaya, tana faɗi babu ɓata lokaci cikin minti talatin ɗan saƙo yakai mata magungunanta ta bashi kuɗin mota.

Jiki na rawa ta shige can ƙuryar ɗaki ta kira Farida da Zainab Maman Mujaheed a waya suka yi mata cikakken bayani na yadda za tayi amfani da maganin biyu.

Saboda zaƙuwa tun a wannan lokacin ta fara amfani da su, sai fatan dacewa. Bata yi kuskuren yin lattin abinci kamar jiya ba, ƙarfe biyu saura kwata taje ƙofar Fareeda ta dangwara kuloli biyu a bakin ƙofar sannan ta ƙwanƙwasa ƙofar da ƙarfi sau biyu tai wucewarta, ba tare da damuwar Fareedan ta ji ko bata ji ba.

Inda Allah ya taimaki Fareeda a lokacin suna zaune a falo ita da yaranta. Ta jika musu Conflakes a kofi suna sha, taji wannan ƙwanƙwasa ƙofar.

Ko da taje ta buɗe sai kulolin ta gani. Tsaki taja ta kwashe su tayi ciki, kan dining ta ajiye, tana buɗe babbar kular taga farar taliya, a ƙaramar kuma miyar tarugu ce da aka soya ta ɗanye-ɗanye.

Rufe kular tayi ta koma gurin yayanta ta cigaba da kallon da take yi.

*****

Da ɗoki sosai a tattare da Mukhtar ya koma ɓangaren Fareeda. Ko a mugun saƙa irinna tunani bai taɓa kawowa a ransa matsala makamancin ta rannan za ta maimaitu tsakaninsa da Fareeda ba. Sai ga shi an kuma, washe gari ma haka aka sake maimaitawa.

Izuwa yanzu sosai lamarin ke bashi tsoro da kaɗa mishi yayan hanji. Duk tunaninsa ya ƙuƙe ne akan ta yaya za'ayi haka? A gurin Fatima lafiyarsa ƙalau a gurin Fareeda ba lafiya ba.

Me yake faruwa? A ina matsalar take? Ganin Fareeda ko a jikinta bata nuna lamarin ya dameta ba yasa shi kasa sanar da ita a gurin Fatima fa ba ya fuskantar irin wannan matsalar. Kawai sai ya bar zancen a cikinsa, zuciyarsa cike da tunanin wani irin al'amari ne wannan mai sarƙaƙiya?

*_Laifin daɗi aka ce ƙarewa😍😍😍 Promon maganin Sanyi na Zee maman Mujaheed ya ƙare. Yanzu maganin ya koma farashinsa na ainahi wato 4k! Ya ke yar'uwata mai karanta labarin RABON AYI, a gurin neman lafiya daga wannan fitannen ciwo na infection da yake damun mata da yawa, ko dubu ɗari kika kashe wajen siyan ingantaccen maganin sanyi bakiyi asara ba. Lafiya ta fi komai a duniyar nan yar'uwa□□ sai da lafiyarnan za ki kankaro ma kanki mutunci da daraja a gurin Oga 😘. Ki tuntuɓi Maman Mujaheed ta wannan lambar wayar domin sayen naki akan farashi mai rahusa 0816 285 9027_*

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

_*24*_

Ku zo ku sayi data a gurina sai ku cigaba da karatu□□□□□□😘😘

Ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ki tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online ki kira ni ta 09077591726. In sha Allah cikin daƙiƙu ƙalilan datar da kika siya zai sauka a wayarki□□

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

10GB□□ N2500

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Na mu ba irin na su bane shi yasa farashin daban yake da nasu☺☺

Kafin a saukar da ko wace irin cuta, sai da aka fara saukar da maganinta. Sai dai idan bawa baiyi dace da magani ba sai ayi ta wahala, a faɗa cikin ƙunci da ƙaƙanikayi.

Cikin kwanaki biyu da Fatima ta fara amfani da magungunan da ta karɓa babu abinda za ta ce sai godiya ga Allah. Duk da basuyi arangama da Oga Mukhtar ba, ita kanta tana ji a jikinta e lallai fa an samu gagarumin sauyi.

Zo kuga baki har kunne, duk wani ƙunci da baƙin cikin da maganganun Mukhtar suka dasa ma zuciyarta ta kawar da su gefe ɗaya, jira kawai take su gamu yasha mamaki.

Kwanaki shida bayannan ranar girkinta ne. Mukhtar ya waiwayeta ba don tunanin jin daɗi ba sai don kawar da matsuwar da yake ciki, tunda ɓangaren Fareeda dai har lokacin sifili ne.

E lallai fa Mukhtar ya sha mamaki, har ma fiye da yadda Fatima ta so ya kasance. Mukhtar ya amsheta cikin haba-haba da rawar jiki, an kuma an sake kumawa an kuma ƙara kumawa. Ita kanta duk wannan zafi da raɗaɗin da take ji ko kaɗan bata ji ba.

Bayan kammaluwar komai bai juya mata baya ba, kamar yadda ta daɗe tana muradi, ruƙunƙumeta yayi a ƙirjinsa suna sauke ajiyar zuciya. A sannu a hankali kuma wani nannauyar barci yayi awon gaba da su, zuciyar Fatima cike taf da wani irin matsanancin jin daɗi da alfaharin da ko kaɗan bakinta bazai iya baiyanawa ba.

Ita kaɗai ji take kamar tana yawo a sararin samaniya saboda tsabar shauƙin soyayyar Haskenta.

A wannan rana, hatta sallar asubah ita da shi basu samu sararin gabatarwa ba sai ƙarfe bakwai da rabi na safe. Saboda tsabar soyayya ma a tare suka yi wanka, suka ɗauro alwala. Ta bi bayanshi yaja su sallar asubahi.

Yana kishingiɗe akan kujerarta mazaunin mutum uku wani nishaɗi na ratsa zuciyarsa ta kawo musu abin kari. Nan gefenshi ta zauna, ta ɗora kanta a kafaɗarsa suna karyawa cikin wani irin salo da soyayyar da ta ci burin ya faru tun a kwanaki ukun amarcinta, amma ko yanzu ma bai zo a makare ba.

"Fatina"

Mukhtar ya kira ta da sunan soyayyar da tun darenta na farko bai sake faɗa mata ba.

"Na'am Haskenah"

Ta amsa a hankali haɗe da sakar mishi fari da ido. Sai kuma ta ƙalle mishi ido ɗaya ta ƙara da cewa

"Ya aka yi? Ko kana buƙatar ƙari ne?"

Farantin dankalin turawar da ke ajiye a gabansu ya kalla, sai yaga ko rabi basu ci ba. Nan take zuciyarsa ta tunano mishi ƙarin da take magana akai, sai yayi murmushi kawai, ya mayar da fuskarsa kalar zai mata magana mai muhimmanci ya ce

"Wai ni ya aka yi haka ne? A gurin Fareeda fa ba na iya taɓuka komai. Anan ne kawai nake namiji lafiyayye. Ko kin san abinda ke janyo irin wannan matsalar?"

Wani irin tsallen baɗake zuciyarta tayi daga gabas zuwa yamma. Ta zazzaro idanu warwaje tana kallonshi tana jujjuya maganarsa a cikin zuciyarta, sai kuma tayi tsam ta ƙura ma guri ɗaya idanu, banda luguden daka babu abinda ƙirjinta ke yi.

"Kin yi shiru, ki ce wani abu mana. Ni kam na ma kasa tattauna maganar da Fareeda saboda ban san ta inda zan fara faɗa mata anan ina iya kusantarki ita ce ba na iya komai da ita ba."

"Uhmmmmm!"

Taja wani nannauyar ajiyar zuciya ta sauke. Lokaci ɗaya kuma tayi narai narai da idanunta ta tara ƙwallah. Hannayensa biyu ta riƙo a cikin nata, tayi ƙasa ƙasa da murya sosai da wani irin matsanancin damuwa a fuska da muryarta ta ce.

"Haskenah! Ka roƙi Fareeda, ka roƙe ta. Idan ka damu da rashinta ka roƙe ta, idan ta kama ko durƙusa mata a ƙasa ne ka durƙusa, ka tabbatar mata da cewa aurena da kai ba shi zaisa ka juya mata baya ba. Idan za ka iya ma kayi mata ƙaryar kai fa tunda ka auro ni baka taɓa kusantata ba. Idan ta so, za ta baka maganin ciwonka, daman ita ta ƙirƙiri cutar da gangar ka ga kuwa makarin ciwon na hannunta..."

"Ban... gane..ba. Me kike nufi?"

Ya tambayeta bakinsa na rawa.

Hannayensa ta sake ta zuba tagumi da hannu bibiyu.

"Ta ya zan faɗa maka sirrin da daga ni sai ita sai Allah muka sani? Ko ni da ta san juyin juya hali irinna ƙaddara zai kaimu ga matakin da zan zamo matarka baza ta taɓa faɗa min wannan maganar ba."

Cak ya ɗaga ta daga kan kujera ya ɗaura kan cinyarsa. Ya kamo fuskarta ya riƙe cikin tafin hannayensa. Ya ƙureta da kallon soyayya mai ratsa masoya na tsawon wasu daƙiƙu, sai da ya tabbatar ta nuna luguf, jikinta ya mutu murus, sannan ya fara magana a tausashe, da wata irin siga ta matasan da suka ƙware a soyayya.

"Fatina. Kin san ina bala'in son ki ko?"

Saboda yadda jikinta ya mutu ta kasa buɗe baki ta amsa mishi, sai kai ta iya ɗagawa.

"Ashe a duniya akwai wani sirri da za ki iya ɓoye min? Na zaci ni ɗin abokin sirrintakanki ne? Akwai wani abu ɓoyayye da yake tsakaninmu ne?"

Nan ma dai kai ta iya kaɗa mishi alamun babu.

"To faɗa min! Kin ji yɑr matata? Rabin raina, masoyiyata, abar ƙaunata. Kogin zuma ta..."

Kwantar da kanta tayi a hankali ta fara cewa

"Fareeda, ta taɓa rantse min da girman Allah duk ranar da mijinta yayi gangancin yi mata kishiya za tayi amfani da maganin da bazai ƙara samun damar da zai kusanceta ba.

Kai baka yi mamakin irin kwanaki casa'in casa'in ɗin da tai ta ƙara mana ba? Ta ƙara ne saboda ta san ko ka je can ɗin babu wani abu da za ka samu daga gare ta..."

"Fatima, kar ki faɗa min ƙarya fa"

Ya katse ta muryarsa na bayyana shiga cikin gagarumin tashin hankali. Sai kuma ya sake ɗago fuskarta yana kallon cikin idanunta a rikice.

"Na san ke aminiyarta ce, baza ki ƙirƙiri ƙarya ki faɗa min don kawai kiyi mata sharri ba. Faɗa min gaskiya don Allah, ki ce min wasa kike min. Ta ina Fareeda za ta sami irin wannan maganin?"

"Hmmm! Kana tantama ko? Kai baka yi mamakin yadda duk matsanancin kishi irinna Fareeda ko kaɗan bata tashi hankalinta jin za muyi aure ba? Ka tambayi masana magunguna ka ji, tabbas akwai maganin da mace za ta matsa a al'aurarta daga zaran namiji ya nemi kusantarta zai kwanta ligif."

Tsam ta tashi daga jikinsa ta shige cikin ɗakinta, ta barshi zaune cikin zazzafan tunani.

Hannayensa biyu yasa ya tallabe gemunsa. Ya ƙanƙance idanu ya ƙura ma guri ɗaya idanu tsawon lokacin da shi kanshi bazai ce ga iyakarsa ba.

Tunani yake yi, zuciyarsa cike da ƙila wa ƙala. Ya kasa samun matsaya guda ɗaya. Idan wani sashen na zuciyarsa ya fara kore maganar Fatima, da saurin gaske eani sashen yake ƙara tabbatar masa da gaskiyar zancen, idan ya tuna yadda Fareeda

take ta ko in kula da al'amarinsa tun ɓullar zancen zai aure ta har zuwa sa'adda aka yi auren.

Bayan kuma shi kanshi shaida ne kan irin matsanancin kishin da take da shi. Da walakin goro a miya, lallai biri yayi kama da mutum.

Akwai alamun gaskiya dumu-dumu a cikin wannan maganar. Idan ya ƙara tuna ko a yanzu, shi kaɗai yake nuna damuwarsa idan lamarin ya sake maimaituwa. Ko sau ɗaya bazai iya tuna wani lokaci da yaga damuwa a fuskar Fareeda kan lamarin ba.

Karyawan da basu ƙarasa yi ba kenan. Ita tun da ta shige cikin ɗaki bata fito ba, shi kuma da yake ya gama shirin tafiya gurin aiki daga nan bai koma cikin ɗaki ba. Wayarsa da makullin mota ya ɗauka ya fice zuwa ɓangaren Fareeda.

A hanya sai saƙe-saƙe yake yi, ransa ya ɓaci sosai da jin wannan magana da ya gama haƙƙaƙe ma zuciyarsa gaskiya ne. Amma sai yake ta tunanin yai mata magana ko kar yayi mata magana? A ƙarshe dai sai ya yanke shawarar ya zura mata ido yaga iya gudun ruwanta, zai ga cikin su biyun wa zai fi shan wahala da jigatuwa? Shi da yake da wata matar ko kuwa ita da tayi ma kanta sagegeduwa?

Da wannan shawarar yayi ƙoƙarin faɗaɗa fuskarsa da murmushin yaƙe sannan ya buɗe ƙofar ya shiga bayan yayi sallma an amsa mishi daga ciki.

Tana zaune a tsakiyar ɣayɣanta tana biya musu ƙulhuwallahu ahad! Amsawa suke da hausarsu da bata fita tana sake maimaita musu.

Sun yi kwalliyarsu tsaf, gwanin ban sha'awa da burgewa. A guje yaran suka tashi suna mishi oyoyo, bayan ya zauna kan kujera suna jikinsa ta gaishe shi.

Idanunshi na kanta ya amsa, wani irin kallo yake bin ta da shi tun bayan shigowarsa. Kallon da ya jefa ta cikin tsarguwa, har sai da ta ce

"Abee, irin wannan kallo Allah yasa dai ba laifi nayi ba..."

"Uhmmm! Laifi dai Fareeda? Wani labari ne na jiyo da ya ɗaga min hankali."

Ya amsa yana sake ƙure ta da kallo.

"Tooo...! Allah ya kyauta."

Ta amsa fuskarta ɗauke da yanayin jimami.

"Fareeda, wai da gaske saboda kishi mace za ta iya yin abinda zai hana komai ya shiga tsakaninta da mijinta?"

Ya tambayeta.

"Kishi fa ka ce Oga?"

Sai ta ɗanyi murmushi.

"Kishi halitta ce da Ubangiji yayi a cikin zukatanmu. Ko wace mace tana da kishi, sai dai na wata ya fi na wata. Baka taɓa jin labarin matan da saboda matsanancin kishin da suke da shi suna halaka mazajensu sannan su halaka kansu ba? Amma da yake komai na duniya yana da linzami, linzamin baƙin kishi mace ta tsananta addu'a, sai kaga komai ya zo mata da sauƙi. Allah dai ya ƙara sassauta mana."

"Hmmm! Ameen"

Ya amsa a hankali, a zuciyarsa yake ta auna maganganunta, bai hangi komai a ciki ba face ƙara samun gamsuwa da maganar Fatima.

Bai sake wata maganar ba yayi mata sallama ya fice daga ɗakin, zuciyarsa cike da mamakin wannan al'amari.

Ita kuwa ko bayan fitarsa bata ɓata lokacinta gurin yin wani tunani ba. Amsa ta bashi da zuciyarta ɗaya ba tare da tunanin da wata a ƙasa ba. Hidimarta ta cigaba da yi ita da ƴan ƴaƴayenta da ko kaɗan ba su da rigima ko ɗaga hankali irinna wasu ƴanbiyun.

*****

Da ƙarfi ta ƙwanƙwasa ƙofar, ta haɗa da buɗe murya ta rafka sallama, fuskarta cike taf da murmushi.

"Alaikissalam! Ina zuwa."

Ta jiyo muryar Fareeda ta amsa daga can ciki.

Sai da ta kintaci ana daf da buɗe ƙofar sai ta buɗe murya ta fara waƙar

"Hooohotihoooo, hotihoooo, hotihooooooo, hotihoooo. Baaaaa ki da amfaniiiiii, sai dai zaman yʻayʻaaaa, ko in ce zaman hoooootihooooo hotihoo."

Da mamaki Fareeda ta ɗaga idanu tana kallon Fatima da har lokacin da ta buɗe ƙofar bata daina rera wannan waƙa da ƙarara yayi kama da habaici ba.

"Lafiya dai ?"

Ta jefa mata tambayar da ɗaurarriyar fuska.

"Hotiho, au Fareeda uwargida. Me kika ce?"

Fatima tayi maganar tana wani irin dariya mai bayyana isgili da tsantsar wulaƙantarwa.

Wani kakkausan kallo Fareeda ta watsa mata, ta mayar da ƙofarta za ta rufe da saurin gaske Fatima tasa hannu ta tare.

"Saurin me kike yi Hajjaju? Abincinki na kawo miki, ki ci, ki sha, kiyi ƙaton kashi. Ko kina da wani amfanin da ya wuce wannan a gidannan Hotiho?"

Wani kakkauran miyau ta haɗiye, ta lumshe idanunta tana addu'a a zuciyarta haɗe da ƙoƙarin danne ɓacin ranta, ba ta son biye ma Fatimar, ita a tsarinta ko da miji bata cika son ta dinga yawan cece kuce ba balle kishiya. Tun rannan da suka yi a gaban mai wanki da ganin irin yadda Fatima ta nemi juya zancen bayan dawowar Mukhtar yasa ta shan alwashin in sha Allah ta bar ƙara biye ma Fatima suyi cacar baki. A karo na biyu ta sake turo ƙofar za ta rufe.

"Ke Hotiho, ki saurara min. Wallahi Tallahi idan kika kulle ƙofar nan komawa zanyi da abincina..."

"Kin daɗe baki koma da shi ba. Useless"

Baam ta mayar da ƙofarta ta rufe haɗe da jan dogon tsaki.

Tana jin muryar Fatima tana zazzaga tsiya a bakin ƙofar haɗe da kiranta da munanan sunaye, har tana cewa taje dai ta bincika cikin su biyun wacece mare amfani a gidan? Akwai ma ƙatotuwar hotiho irinta? Wacce sam ba ta iya amfanawa miji komai sai dai ta cinye mishi abinci...

Waɗannan jimlolin na ƙarshen maganganunta, su suka tsaya ma Fareeda a zuciya. Tayi tsai a tsakiyar falon tana tunani.

Sai kuma maganar da Mukhtar yayi mata da safe ya faɗo mata arai. Ƙirjinta ne ya buga daram!! Wani jiri da ya fara ɗibanta yasa da saurin gaske ta dafa kujera, a hankali ta laluba ta zauna.

"Kar dai ace Mukhtar ya faɗa ma Fatima ba ya iya komai da ni?"

Tunanin hakan kawai yasa hawaye gangarowa daga idanunta.

"Amma kuwa wallahi da ya gama da ni, kuma in dai yayi hakan bazan taɓa yafe masa ba. Zai dawo gidan ai, zan ji ta inda maganganunta suka samo asali, babu rami me ya kawo maganar rami?"

Daƙyar ta iya rage damuwar maganar a cikin ranta ta kwanta lamo akan kujera, ba ta son saka ma kanta damuwa. Ƙaramin ciki ne da ita, ba tun yanzu ba tasan ba ƙaramin illah damuwa ke haifarwa ga mace mai ciki ba.

Tana wannan kwanciyar sai ga su Sayyid sun fito daga ɗakinsu, hannun Shahid riƙe da sabon ƙwallo, ɗaya daga cikin tarkacen kayan wasan da Hajiya ta haɗo su da shi.

Har sun fara buga mata anan cikin falo sai ta buɗe musu ƙofa ta ce su buga anan harabarta. Ɗan sakaya ƙofar tayi ta koma kan kujera ta kwanta, a hankali ta fara addu'ar kau da damuwa da gaggawa a zuciyarta, a hankali ta dinga jin sauƙi sauƙi har wani daddaɗan barci ya fara kawo mata farmaki...

*_Ya ke yar'uwata mai karanta labarin RABON AYI, a gurin neman lafiya daga wannan fitannen ciwo na infection da yake damun mata da yawa, ko dubu ɗari kika kashe wajen siyan ingantaccen maganin sanyi bakiyi asara ba. Lafiya ta fi komai a duniyar nan yar'uwa sai da lafiyarnan za ki kankaro ma kanki mutunci da daraja a gurin Oga😘. Ki tuntuɓi Maman Mujaheed ta wannan lambar wayar domin sayen naki ingantaccen maganin sanyin akan farashi mai rahusa 0816 285 9027_*

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

_*25*_

Ku zo ku sayi data a gurina sai ku cigaba da karatu□□□□□□😘😘

Ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ki tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online ki kira ni ta 09077591726. In sha Allah cikin daƙiƙu ƙalilan datar da kika siya zai sauka a wayarki□□

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

10GB□□ N2500

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Na mu ba irin na su bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

https://hikaya.bakandamiya.com/lokaci-babi-na-daya/ Ƴan'uwa ku danna wannan link ɗin, kai tsaye zai kai ku page ɗin Bakandamiya hikaya domin karanta sabon labarin da ni Fareeda Abdallah nake rubutawa, sunan labarin LOKACI, daga babi na ɗaya za ku cigaba da danna *Next* zai kai ku har babi na huɗu.. Da fatan za'a nuna

min ƙauna ta hanyar yin dafifi wajen karantawa, comment, yin rating ɗin labarin. Na gode😘😘😘

Kamar a mafarki, Fareeda ta ji muryar Sayyid da Shahid sun yanka wani rikitaccen kuka mai cike da ƙara da taratsi. A firgici tayi wani irin juyi ta dirgo ƙasa daga kan kujera, da sassarfa ta fice don gane ma idanunta abinda yake faruwa.

Ƙanƙance idanunta tayi da wani irin bala'in ɓacin rai tana kallon Fatima da ta riƙe hannayen Shahid da hannunta ɗaya, ɗayan hannun kuma babu tausayi babu jinƙai ko tunanin ƙaramin yaro ne a gaban Fareeda ta sake ɗaga hannu ta tsinka ma yaron mari.

Da Shahid da aka tsinkawa mari, da Sayyid yake tsaye gefe ɗaya ya ƙanƙame hannayensa a ƙirji yana makyarkyata cikin tsoro da firgici, a tare suka sake ƙwalla ihun kuka.

Ita kuwa Fareeda kawar da kanta tayi da sauri ta lumshe idanu, nan take suka cicciko da hawaye. Wani irin zafi ya lulluɓeta lokaci ɗaya, har wani ƙaiƙayi take ji a kumatunta kamar ita aka tsinkawa mari.

Da wani irin fusata da ɓacin rai matsananci ta buɗe idanunta da suka canza launi lokaci ɗaya, ta ɗaga ƙafa a fusace za ta ƙarasa gurin Fatimar sai taja ta tsaya cak, tunawa da tayi da wata magana ta Malam bahaushe da yake cewa.

"Ka so naka, duniya ta ƙi shi. ka ƙi naka, sai duniya ta so shi."

Fatima da take kallon yanayin Fareeda ta ƙasan idanunta ganin ta ja ta tsaya sai ta sake ɗaga hannunta na dama fuska cike da murmushin mugunta ta sake fallawa yaron mari, sannan ta saki hannayensa haɗe da ture shi ya faɗi ƙasa yana rusa kuka.

"Don Uwarka waccan da take tsaye zan nuna maka kai ƙaramin mare kunya ne. Idan ita gantalalliya ce ta kasa baka tarbiya mai kyau ni zan koya maka."

Da gama faɗin haka sai taja ta tsaya ta riƙe ƙugunta, jira take Fareeda ta zaburo ta naɗa mata nata marukan kamar yadda tayi ga ɗanta.

Sai taga ko da Fareeda ta ƙarasa gurin ɗanta ta ɗaga jikinta na rawa ta rungumeshi a ƙirjinta. Ta ƙarasa kusa da Sayyid ta kama hannunsa suka nufi ɓangarenta, har lokacin jikinta bai daina rawa ba.

Tana jin sa'adda Fatima taja mata wani dogon tsaki haɗe da cewa

"Sakarya kawai."

Daƙyar ta iya ƙarasawa cikin falonta. Nan kan kafet ta zauna ta rungume yayan a jikinta ta fashe da ƙaƙƙarfan kuka, zuciyartaa in banda tuƙuƙi da suya babu abinda take yi.

Fatima ba fin ƙarfinta tayi ba, amma ko kaɗan ba ta son zubar da mutuncinta ta hanyar biye mata su dinga kace-nace kamar wasu dabbobi. Balle irin yadda Fatima ta dinga marin yaron kowa zai san da gayya tayi, ta yi ne domin ta tanka mata. Ita kuwa in Allah ya yarda baza ta ƙara biye mata suyi cacar baki ba, ba ita ce sa'ar yin ta ba, Mukhtar ne, don haka zai dawo gidan shi zaiyi wannan shari'ar, ita kam baza ta iya ba. Tana lallaɓa lafiyarta asa ta cikin wani mummunan hali na tashin hankali da ko kusa ba ta fatan shigarsa.

Acan ɓangaren Fatima kuwa tana shiga ɗakinta wayarta ta ɗauko, ta nemi gurin zama akan kujera ta lalubo lambar Mukhtar ta danna mishi kira.

Yana ɗagawa daga can ɓangaren sai ta sakar mishi kukan kissa. A rikice ya fara tambayarta menene? me yake faruwa? Wa ya taɓa mishi ita?

Sai da ƙyar ta iya sassautawa da kukan ta fara magana

"Haskenah! A tunanina ko ban aure ka ba yayan Fareeda yayana ne?"

"Haka ne! Me yake faruwa?"

Ya tambayeta cikin zaƙuwa.

"Wai kawai don na ji su Sayyid suna wasa a tsakar gida na fita ina tsokanarsu nan take Fareeda ta fito a fusace ta janye yayanta. Ta saka su sukai ta min rashin kunya suna zagina, kalaman tozarci ta dinga faɗa musu da turanci tana nuno ni su kuma suna kwaikwayonta haɗe da min daƙuwa. Na tausaya maka Haske, wallahi idan baka yi da gaske ba, Fareeda sai ta lalata maka tarbiyar waɗannan yayan da kake alfahari da su, ba don komai za tayi hakan ba sai don baƙin kishi irin nata, idan za ka ji shawarata, ka ɗauki mataki da gaggawa tun kafin lokaci ya ƙure maka."

Ta sake fashewa da kuka sannan ta katse wayar, daga bisani ma sai ta kashe wayar gaba ɗaya yadda ko ya kira bazai same ta ba.

Nan kan kujera ta miƙe ƙafafu tana ƙyalƙyala dariya ita kaɗai kamar sabuwar kamu.

Daƙyar da suɗin goshi ta samu yayan suka yi barci. Daƙyar ta rarrashi kanta ta tsayar da kukanta, ta fara rarrashin su biyun da suka urunce da kuka kamar duk su biyun aka mara.

Bayan tsawon lokaci suka yi shiru, lamo sukai kwance a jikinta suna sauke ajiyar zuciya. Jikinsu ya ɗauki zafi sosai, da ta kalli fuskar Shahid sai wasu zafafan ƙwalla su sake taruwa mata saboda yadda shatin yatsun Fatima suka fito ruɗu ruɗu.

Kan kujera ta lallaɓa ta kwantar da su, ciki ta shige ta haɗa musu ruwan wanka. Ko da ta fito sai ta tarar duk sunyi barci. Kamar za ta tashe su, sai kuma taga yadda jikinsu yayi ɗumin nan ga ajiyar zuciyan da suke ta saukewa duk da suna barci gara ta bari idan sun tashi sai tayi musu wankan.

Ɗaya bayan ɗaya ta ɗaukesu zuwa cikin ɗaki ta kwantar da su kan gado. Falon ta koma ta zauna, tagumi ta buga da hannu bibiyu, zuciyarta cike da tunanin inda ta taɓa kuskure ma Fatima a mu'amalar ƙawance da suka gudanar na tsawon shekaru.

"Ashe ƙauna da yarda suna juyewa su zama matsananciyar ƙiyayya da jin haushi? Tun bayan da Mukhtar ya auro Fatima cikin gidannan babu abinda take kallo a cikin idanunta sai matsananciyar tsanarta da jin haushinta. Ga shi yanzu abin har ya fara gangarowa kan yayanta.

Ko dai akwai wani mummunan abu da ta taɓa yi ma Fatiman a baya ne da take burin ɗaukar fansa a yanzu?

Tayi imani da Allah, ta san aure tsakanin Fatima da Mukhtar ko kaɗan babu haramci a ciki. Kalmar ana barin halas ko don kunya bai taɓa samun matsuguni a zuciyarta ba balle har ta ƙullaci Fatimar.

A tunaninta ko basuyi zaman daɗi ba, za suyi zama ne irinna kowa tasa ta fisshe shi. Amma na miye duk wannan tsana da ƙiyayyar da take nuna mata?"

Tun daga bakin ƙofar falonta take jin yadda Mukhtar yake ƙwallah mata wani irin mahaukacin kira. A gigice ta miƙe tsaye tana zare idanu, ya buɗe ƙofar ya shigo fuskarsa na bayyana wani irin ɓacin rai da fusata da ta daɗe bata gani a tare da shi ba.

"Mmmmme ya faru? Menene?"

Ta tambaye shi cikin rawar murya.

"Fareeda, me nayi miki da zafi da za ki dinga nuna min irin wannan matsananciyar tsanar? Kin nesanta kanki da ni, yayan nawa da nake gani ina jin daɗin samunsu daga gare ki su ma so kike ki nesanta su da ni ta hanyar lalata min tarbiyarsu?"

Idanunta a warwaje, fuskarta cike da mamaki da tsoro, a ƙwaƙwalwarta take ta jujjuya maganganunsa don gano inda ya dosa amma sam bata gane ba.

Da sassarfa ta taka ta haɗe tazarar da ke tsakaninsu, ta miƙa hannuwa za ta riƙo nasa da sauri ya janye hannayensa kamar wacce ta nufe shi da bakin wuta. Ta buɗe baki za tayi magana yayi saurin dakatar da ita da wani irin gigitaccen tsawa.

Daman tun safe akwai fushi da ɓacin ran jin maganar ita ke amfani da magani don kar ya samu damar kusantarta. Don haka yanzu da ya samu damar da zai wanke ta wani irin tsiya na bala'i yake zazzaga mata kamar bai taɓa sanin wacece ita ko kuma daga ina ta fito ba. Daga ƙarshe ya ɓuge da maimaita mata abinda Fatima ta ce ita da yaran sunyi mata ya kuma kora mata kashaidin kar ta kuskura ya sake jin makamancin irin wannan shirme da dabbancin, idan ba haka ba zai ɗauki mummunan matakin da bata taɓa tsammani ba.

Fareeda ta kasa kuka, sai wani irin ajiyar zuciya take saukewa cikin zafin rai. Tun tana tsaye tana saurarenshi, bata san sa'adda ta sulale zuwa ƙasa ba, mamaki da ɓacin rai haɗe da baƙin ciki ke neman sumar da ita. Bata san sa'adda ya fice ba, kawai buɗe idanu tayi taga baya falon.

Minti uku ta ƙara durƙushe a gurin tana nishi kamar mai naƙuda. Sai kuma ta miƙe a zabure ta nufi cikin ɗakinta, har lokacin su Sayyid suna kwance suna barci.

Tun a tsakar ɗakin ta fara cire kayan jikinta tana hurgi da su, har ta zama daga ita sai rigar mama da ɗan kamfai. Durowar kayanta ta buɗe ta fara janyo kayan cikin sauri tana ɗaɗɗagawa har ta ciro wasu sakakkun riga da wando ƙananu, wandon iya gwuiwa, rigar kuma da kaɗan ta ɗara cibiyarta.

A gurguje ta saka kayan a jikinta, ta fice daga ɗakin gudu-gudu kanta babu ko ɗankwali, daman shekaran jiya ta tsefe kan, yalwataccen gashinta ya kwanta a saman kafaɗunta.

Silifas ɗin da take sakawa a cikin ɗaki tana tafiya saboda sanyin tiles shi ta zura a kafafunta ta fice daga apartment ɗin gaba ɗaya. Kai tsaye ɓangaren Fatima ta nufa da sassarfa, idanunta sun kaɗe sunyi jajur.

Wani babban sa'a da ta ci shi ne tana murɗa hannun ƙofar ya buɗe, aikuwa ta afka cikin falon a guje kuma a haukace.

Mukhtar na kwance kan doguwar kujera, Fatima ta sa gwuiyawunta a ƙasa tana mishi tausa kawai Fareeda ta afko cikin falon babu ko sallama.

Ko kafin suyi wani yunƙuri na magana ko na miƙewa tuni Fareeda ta isa ga Fatima ta damƙi wuyarta ta miƙar da ita tsaye, da wani irin ƙarfi kamar ba ita kaɗai ba ta wujijjiga Fatiman sannan ta haɗa ta da bango, ta shaƙe ta da hannu ɗaya hannu dayan kuma ta fara gaura mata mari, tana marinta tana cewa

"Ni za ki gwadawa makirci?"

Ko kafin Mukhtar ya samu nasarar ɓanɓare Hannayen Fareeda a wuyan Fatima ta yi mata maruka sun kai sha biyar.

Fatima kamar wacce aka riƙe ma hannaye ta kasa wani kataɓus na ramawa ko kuma yunƙurin ƙwacewa, ihu kawai take ƙwallawa tana faɗin Haskenah ka ceceni, ta haukacee za ta kashe ni.

A haukace Fareeda ta damƙi damtsen hannun Mukhtar na dama ta kai bakinta ta gantsara mishi wani matsiyacin cizo kamar za ta gutsure fatar gurin. Saboda azaba Mukhtar bai san sa'adda ya ƙwallah ihu ba.

Ita dai Fatima tunda ta samu tsira ko ta kan Mukhtar bata bi ba da rarrafe ta shige ɗakinta ta rufe ƙofa.

Daƙyar da gumin goshi ya samu nasarar ɓamɓare hannunsa a bakinta bayan yayi mata wani mugun damƙa a gashinta, yadda Fatima ta shige da rarrafe haka ya bi bayanta yana yi yana waigen ko Fareeda ta biyo bayansa...

Ina da mare lafiya, jiya a asibiti na kwana sai da yammannan na dawo gida. Sannan ina da biki wannan satin. New update sai kun ji ni lahadi ko litinin in sha Allah

*_Laifin daɗi aka ce ƙarewa😍😍😍 Promon maganin Sanyi na Zee maman Mujaheed ya ƙare. Yanzu maganin ya koma farashinsa na ainahi wato 4k! Ya ke yaɗar'uwata mai karanta labarin RABON AYI, a gurin neman lafiya daga wannan fitannen ciwo na infection da yake damun mata da yawa, ko dubu ɗari kika kashe wajen siyan ingantaccen maganin sanyi bakiyi asara ba. Lafiya ta fi komai a duniyar nan yaɗar'uwa sai da lafiyarnan za ki kankaro ma kanki mutunci da daraja a gurin Oga 😘. Ki tuntuɓi Maman Mujaheed ta wannan lambar wayar domin sayen naki akan farashi mai rahusa 0816 285 9027_*

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

*_26_*

Kina da fama da matsalar rashin haihuwa ko dogon jinkiri ba tare da wata ƙwaƙƙwaran dalili ba tsakanin wannan haihuwar da wancan haihuwar? Ko kuma kina da yaɗar'uwa ko ƙawa da kika san tana fama da wannan matsalar?

Magani ne zan tallata muku. Amma wannan maganin ni Fareeda ba ni nake sayarwa ba. Kauyenmu muka je biki, ƙanwar mamana tayi mentioning maganin ga wata yaɗar'uwata da ta daɗe bata sake samun ciki ba. Kamar wasa muka je gurin mai

maganin muka karɓa, dubu biyu kuɗin magani. In taƙaice muku zance Wallahi tana gama shan salalar maganin na kwana sha biyu sai ciki.

Ko da muka sake zuwa wani sha'ani take faɗa ma ƙanwar mamanmu magani an dace, sai mata da yawa a gurin suka tabbatar mana su ma maganin suka karɓa suka dace. Ashe har daga gari-gari zuwa ake ana saye maganin a gurin wannan mata mai magani. Kuma bayan maganin rashin haihuwa ko dogon jinkirin haihuwa daga mace har maganin matsalar rashin haihuwa na maza tana bayarwa. Shi ma dubu biyu ne kamar yadda na mata yake. Idan kuma matsala ya shafi mata da mijin sai ku amshi maganin duk biyu. 4k kenan.

Amma ku sani ni ina kaduna ne, kawai dai ba na rasa mai zuwa daga can ƙauye da za'a kawo maganin zuwa gidana a kinkinau musabaƙa. Amma kai maganin inda mai siye take ko ina ne wacce ta siya ita za ta biya kuɗin mota ko mashin.

Masu son magani da gaske ga acc no su saka kuɗin magani, 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai su turo min shaidar sun biya da bayanin inda suke ta private a lambar wayata 07039080978. Don Allah don Annabi duk wacce ta san ba da gaske take yi tana son magani ba kar ta tuntuɓeni, don Allah□□□□□□□□□□□□□□□

Kaso arba'in da biyar cikin ɗari na baƙin cikin da suka ƙunsa mata ya ragu sanadiyyar wannan matakin da ta ɗauka a kansu. Ko banza ta rama ma Shahid ninkin ba ninkin marin da Fatima tayi masa.

Shi kuwa Mukhtar! Ƙaƙƙarfan ƙwafa ta sake tana jijjiga kai, alamun da ke nuna basu gamu ba tukun! Za dai su gamu.

Ƙofar ɗakin da suka shige ta gallawa wata matsiyaciyar harara, sannan ta fice da sassarfa zuwa ɓangarenta. Ko da ta leƙa yayan har lokacin barci suke yi, har ta juya za ta shiga banɗaki sai kuma ta juyo da sauri ta sake kallonsu.

Barci suke yi, amma suna ta ɗan rawar ɗari alamun suna jin sanyi. A gaggauce ta ƙarasa ta taɓa jikinsu sai taji zafin ya ninninka na ɗazu. Hankalinta ne ya ƙara tashi.

Idanunta suka cicciko da hawaye. Bargo ta janyo ta rufa musu sannan ta faɗa banɗaki ta ɗauro alwalar sallar la'asar. Jikinta a sanyaye ƙwarai, akai-akai take sharar ƙwallah har ta kusa idar da sallar.

Tana sujuda a raka'ar ƙarshe tana fara addu'a hawaye ya ɓalle mata. Cikin kuka take faɗa ma Allah ga halin da take ciki ya dubeta ya kawo mata mafita da gaggawa.

Bayan ta idar ta daɗe zaune kan sallaya, babu abinda take yi sai istigfari, tasbihi, hailala. Gaba ɗaya zuciyarta babu daɗi, lokaci bayan lokaci take ɗaga idanu ta kalli yaƴan da suke barci da zazzaɓi a jikinsu.

****

"Hello! Hajiya kina ji na?"

Ta tambaya bayan ta ji ntwk ɗin wayar kamar ya fara rawa. Ba sosai take jin muryar Hajiyar na fita ba.

Tsinkewa kiran yayi, kafin ta sake kira sai ga kiran Hajiyarmu ya shigo cikin wayarta. Sabon gaisuwa ta sake yi ma Hajiyar a ladabce, da muryarta a sanyaye ƙwarai, har sai da Hajiyarmu ta ce

"Ina jin ki Fareeda. Me ya samu muryarki? Kina mura ne?

"A'a! Lafiyata ƙalau Hajiya."

Sai kuma ta ɗanyi shiru, kafin ta cigaba da cewa

"Hajiya ga su Sayyid kwance babu lafiya. Don Allah, idan babu damuwa ki aiko direba ya kwashe su zuwa gurinki."

Sai muryarta ta fara rawa, alamun ko wane lokaci za ta iya fashewa da kuka.

"Zafin jikinsu ƙara hauhawa yake yi tun da rana. Tsoro nake ji, don Allah ki aiko..."

Kʼit wayar ya sake katsewa a karo na biyu.

Ajiye wayar tayi a gefe ɗaya ta kifa kanta hannun kujera, hawaye wasu na korar wasu a idanunta. Yanzu gurin awa huɗu da rabi kenan suna kwance, tun suna barci da rawar sanyi da zafin zazzaɓi sama-sama, yanzu jikin nasu ya sake ɗumewa sosai da zazzaɓi. Sun farka, sai suka fara wani irin nishi sama-sama suna kuka suna surutan da sam ba ta gane me suke cewa.

Ko da tayi yunƙurin ɗaga su zuwa jikinta sai suka zame suka ƙara kwanciya kan gado. Shahid da ya fi Sayyid zafin zuciya har wannan lokacin bai daina sauke ajiyar zuciya ba. Farar fuskarsa ta ƙara wani irin jaaaa, shatin yatsun Fatima sun sake fitowa ruɗu-ruɗu a yʻar ƙaramar fuskarsa.

Da da ne da bata shiga cikin hankalinta kan fita ba da izinin mijinta ba a fujajan za ta kwashe su zuwa asibiti. Amma a yanzu baza ta iya ba, ko kusa baza ta iya sake maimaita makamancin kuskuren da ta dinga aikatawa a baya har ya janyo mata faɗawa cikin ƙaƙanikayi a yanzu ba.

Wani irin fushi ne ta ɗauka da Mukhtar, ko da zazzaɓin yaran zai ninka haka ya sake ninkawa ba ta jin za ta iya ɗaga wayarta ta kira shi balle har ta sanar da shi halin da suke ciki. Kuma ba ta son kiran yʻan'uwanta ta ɗaga musu hankali.

Tsoron kar yaran su mace mata ita kaɗai a cikin ɗaki yasa ta yanke shawarar kiran Hajiyar, ta sanar da ita halin da yaran suke ciki.

Wai aka ce abin cikin ƙwai ya fi ƙwan daɗi, jika wahal da kaka. Fareeda da take ta saka idon ganin direba ya zo kwasan yaran sai ga Hajiyar da kanta, wani abu da Hajiya ta kwana biyu bata yi ba shi ne tuƙa mota da kanta zuwa unguwa. Amma yau saboda zaƙuwa da son ganin halin da yʻan biyun jikokinta ke ciki ta kasa jiran ƙarasowar direba, tun da ta kira shi ya ce mata yana hanya taga an shafe mintuna

goma bai zo ba kawai sai ta tuƙo motar da kanta, ga dare ya fara shiga, lokacin ƙarfe bakwai da rabi na yamma.

Ƙarfe takwas da minti ashirin sai ga sallamar Hajiya a ƙofar falon Fareeda, sai kuma ta ƙara da ƙwanƙwasa ƙofar da ɗan ƙarfi ta yadda duk inda mai ɗakin take za ta ji.

Ta fito daga kicin kenan ta haɗo musu tea ɗan kaɗan ko za su sha ta tsinkayi ƙwanƙwasa ƙofar. Da gaggawa ta ƙarasa ta buɗe, suna haɗa idanu da Hajiyar ta kasa riƙe kanta, sai kawai ta faɗa jikinta ta fashe da kuka mai ƙarfi.

Da walakin goro a miya. Tun daga yadda Hajiyarmu ta ji muryarta a waya ta san ba damuwar ciwon yayan bane ya ɗaga hankalin Fareeda haka. Tana riƙe da ita a jikinta taja ta zuwa kan kujera suka zauna, tsawon lokaci tanz sharɓen hawaye kanta na kwance kan kafaɗar Hajiya. Kafin ta fara ɗan bubbuga bayanta alamar rarrashi.

"Ya isa haka. Ummm?"

Daƙyar ta samu ta tsayar da kukan da take yi, ta zame ƙasa ta gaishe da Hajiya, idanunta sun kaɗa sunyi jajur, har wani ɗan kumbura suka yi.

"Me yake faruwa? ina yaran?"

Hajiyar ta tambayeta.

"Suna cikin ɗaki."

Ta amsa tambaya ta biyu kanta a ƙasa.

Bata sake cewa komai ba ta miƙe ta nufi cikin ɗakin, Fareeda na biye da ita a bayanta. Ganin wani irin kwanciya da yaran suka yi yasa hankali tashe Hajiyar ta zauna gefen gadon haɗe da janyosu zuwa jikinta.

"Subhanallahi, Inna lillahi wa'inna ilaihi raji'un! Wani irin zazzaɓi ne haka ya rufe su lokaci ɗaya? Ko sun daɗe suna ciwon ne?"

Ta jero tambayoyin a ruɗe tana kallon Fareeda. Sai kuma ta mayar da hankali kan yaran, ta taɓa jikin wannan ta taɓa na wancan, hankalinta a tashe. Karaf idanunta ya faɗa kan fuskar Shahid, idanu warwaje ta shafa gurin shatin yatsun a tsorace

"Miye nake gani haka? Wannan ai kamar shatin yatsun hannu ne. Dukansa kika yi? Fareeda wannan ɗan ƙaramin yaron kika mara haka? Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un... Fareeda kin haukace ne...?"

"Hajiya ba fa ni na mare shi ba."

Ta faɗa cikin rawar murya.

"Amaryar Mukhtar ce ta mammareshi."

Ta ƙara da faɗin haka don wanke kanta.

Tsuru Hajiyar ta ƙura ma Fareeda idanu, kamar wacce ta warke makanta, bakinta a buɗe, don tsananin mamaki.

"Ta mam-mare shi?"

Ta figo maganar daƙyar daga maƙogwaronta.

"Marin ma ba ɗaya ba? To me yayi mata?"

"A kan idanuna tayi mishi mari biyu. Ni ma bazan ce ga takaimaimai abinda yayi mata ba. Fita suka yi suna buga ƙwallo ina kwance kan kujera na jiyo ihunsu."

Wani irin matsanancin ɓacin rai ne ya mamaye mamakin da ke kwance male-male kan fuskar Hajiya. Ta yunƙura ta miƙe tsaye da Shahid rungume a jikinta.

"Ɗauko Sayyid ki fito min da shi."

Ta umarci Fareeda. Sannan ta fice daga cikin ɗakin.

Ko da suka fita falo ita Fareeda ta zaci Hajiya za ta fita da yaran zuwa gurin motarta ne sai taga Hajiyar ta zauna kan kujera. Ta ɗauko wayarta a cikin jaka ta danna ma Mukhtar kira.

A can tsakar gidan shi kuma Mukhtar ya dawo sallar isha'i kenan ya ci karo da motar Hajiya. Mamaki ne ya kama shi, da sassarfa ya nufi ɓangaren Fareeda, fuskarsa a ɗaure tamau. Zuciyarsa cike da tunanin irin zazzafan matakin da zai ɗauka kan Fareeda. Duk a tunaninshi ko Fareeda ta kai ƙararshi ne gurin Hajiyarsu, wato ita ne mai bakin kai ƙara bayan duk irin haukan da ta zuba musu ɗazu ko? Lallai zai nuna mata ita ƙaramar mara kunya ce.

Fatima tana zaune a gefen gado, hannunta riƙe da ɗan ƙaramin madubi tana kallon kumatunta da suka tasa saboda marukan da ta sha a hannun Fareeda. Man zafi ne ajiye a gefenta, idan ta dangwalo man zafin sai ta shafa a kumatun, zuciyarta a ƙuntace da ɓacin rai. A zamanta gefen gadon ta tsine ma Fareeda ya fi baki ɗari.

Kwatsam kira ya shigo wayar Mukhtar da ke ajiye a gaban madubi. Kamar baza ta ɗauka ba, sai kuma ta miƙe a hankali ta ƙarasa gurin tana kallon fuskar wayar.

Gabanta ne ya ɗan faɗi ganin sunan wacce take kiranshi. Ta san mahaifiyarsa ce, don ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba ta sha raka Fareeda gidansu Mukhtar ɗin. Ta san yayanta gaba ɗaya har Fareeda da Hajiyarmu suke kiranta. Kamar baza ta ɗaga ba, sai kuma wata zuciyar ta ingiza ta ta ɗaga kiran, ta lanƙwashe murya sosai cikin firirita ta fara gaishe da Hajiyar.

"Keh! Wacece ke da har za ki ɗaga kiran da nayi ma mamallakin wayar?"

Aka faɗa mata cikin tsawa daga can ɓangaren ba tare da an amsa gaisuwarta ba.

"Kiyi haƙuri Hajiyarmu. Baya nan ne ya tafi masallaci. Amaryarsa ce, Fatima, ina yini?"

A daidai wannan lokacin Mukhtar ya murɗa hannun ƙofar falon Fareeda ya shiga ciki, bakinsa ɗauke da sallama.

Tsakanin Hajiya da Fareeda babu wacce ta amsa sallamarsa a fili. Hajiya ta kalle shi da wani irin fusataccen kallo ba tare da ta katse wayar ba ta ce

"Wace yar iska ce ka ba damar ɗaga min waya idan na kira?"

Tsuru yayi cikin dambarwa yana kallon Hajiyar, ya rasa ta cewa. Abinda ya sani kawai shi ne ya bar wayarsa a ɗakin Fatima, amma shi bai bata umarnin idan an kira shi ta ɗaga ba.

A can ɓangaren Fatima cikin sauri da tsoro ta katse wayar. Tayi saurin ajiye wayar a inda ta ɗauka. Jikinta a saɓule ta koma gefen gado ta zauna. Ta buga tagumi da hannu bibiyu. Sai kuma ta miƙe zumbur ta nufi falonta, labule ta yaye ta leƙa tsakar gidan. Ganin baƙuwar mota a fake yasa ƙirjinta bugawa da ƙarfi.

"Hajiyarmu na cikin gidannan ke nan? ko dai Fareeda ne ta kira ta?"

Ta tambayi kanta.

"Na shiga uku!!"

Ta faɗa a fili, idanunta a warwaje ta ɗora hannu akai.

Nan take ta fara safa da marwa a tsakiyar falon cikin ruɗu da tashin hankali. Cikin ƙanƙanin lokaci ta haɗa zufa tayi kashirɓin. Sai tufka da warwarar maganganun da za ta faɗa don kare kanta a gaban Hajiya take yi. Ruwa ba ya tsami banza, zuwan sarkuwar nasu bagatatan a wannan dare dole akwau dalili.

Tana wannan zurga zurgar sai ga Mukhtar ya buɗe ƙofar falon ya shigo babu ko sallama. Fuskarnan a ɗaure tamau. Ya kalleta ya aika mata da wani mugun kallo.

"Me yasa kika ɗaga min waya?"

Ya tambayeta a fusace.

Ƙwalƙwal tayi da idanunta, ta lanƙwasa kanta a hankali ta ce

"Kayi haƙuri. Na ga Hajiyarmu ce..."

"Hajiyarki ko tawa?"

Ya daka mata tsawa da wannan tambayar.

Shiru tayi ta sunkuyar da kanta ƙasa, jikinta sai kyarma yake yi a tsorace.

Yayi ƙwafa, ya juya ya nufi hanyar fita yana cewa

"Ki biyo ni zuwa falon Fareeda. Hajiya tana son ganinki, saura kuma ki tsaya ɓata mata lokaci ki ga yadda za mu kwashe da ke a darennan"

Ko da ya koma can falon ya sanar ma Hajiya ga Fatima nan zuwa kamar yadda ta buƙata juya mishi da fuskar Sayyid tayi yaga abinda ke kwance a kumatunsa.

Don ɗazu da ya shigo hankalinsa na kan Hajiyar, duk a tsammaninsa yaya barci suke yi, Shahid a jikin Hajiya Sayyid a jikin Fareeda.

Ckin fushi da fusatar da ya daɗe bai gani a fuskar Hajiyarmu ba ta ce

"Ka ga fuskar Shahid ko? To ba shatin komai bane wannan sai shatin yatsun amaryarka. Idan ita shafaffiya da man taka ta shigo, ka tambaya min ita me wannan ɗan ƙanƙanin yaron yayi mata da zafi da har za ta yi mishi irin wannan marin na tsantsar zalunci da rashin tausayi. Ina so ka sani, ko tana da ƙwaƙƙwaran hujja sai na rama ma wannan ɗan tatsitsin yaron marin da tayi mishi. Idan kuwa ba ta da ƙwaƙƙwaran hujja hukuma ce za ta raba ni da ita."

A daidai lokacin Fatima ta sanyo kanta cikin falon, karaf maganar Hajiya ya sauka a kunnuwanta. A kiɗime ta zube ƙasa tun daga kan kafet ɗin bakin ƙofa.

"Na tuba Hajiya. Na bi Allah na bi ki. Don girman Allah kiyi haƙuri ki yafe min."

Ta faɗa a tsorace da saurin baki, hankalinta a tashe.

A cikin su ukun babu wanda ya tanka mata. Fareeda kawar da kanta tayi gefe ɗaya tana jin yadda sabon ɓacin rai ya lulluɓeta da ganin Fatima.

Hajiya kuwa ƙura ma Fatima idanu tayi, zuciyarta cike da mamakin yadda a mafiyawancin lokuta soyayya ke kauce hanya. Lallai so hana ganin muni ko rashin

dacewa. Saboda Allah mai dirarriyar mace kamar Fareeda me idanunsa za su hango a jikin Fatima?

Mukhtar dai tun da yaga fuskar yaron yayi suman tsaye na tsawon wasu daƙiƙu, idanunshi a warwaje baki a buɗe. Kamar wanda aka sheƙa ma ruwan sanyi haka ya dawo hayyacinsa a firgice ya juya gurin Fatim. Bakinshi na rawa kamar mai taunan ƙanƙara a lokacin sanyi.

"Fffffffffatima...? Me yayi miki kika mmmmmmare shi?"

Ya ƙarasa da wani irin in-ina a muryarsa.

Sai kuma ya juya jikinsa na rawa ya ƙarasa kusa da Hajiya ya karɓi yaron da jikinsa yake ligif, kamar wanda ya suma.

"Na shiga uku! Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Hajiya, ai kamar ma baya motsi. Na shiga uku!! Shi kenan ta kashe min ɗa saboda zalunci da son zuciya..."

A bazata wani jiri ya taho zai kifar da shi da saurin gaske Hajiya ta karɓe yaron hannunsa, ta galla mishi harara ta ce

"Idan za ka faɗi, ka kifa kai kaɗai. Kowa ya ɗeɓo da zafi bakinsa."

Ta mayar da hankalinta kan Fatima ta ce

"Keh! Ban kira ki nan domin ki min magiya ko daɗin baki ba. Kin ga waɗannan"

Ta nuna yan'biyu, sai ta cigaba da cewa

"A yanzu na fi ƙaunarsu akan mijinki. Don haka maza faɗa min abinda yasa kika yi mishi irin wannan ɗanyen hukunci."

Ta ƙarashe da tsawa sosai a muryarta.

Hannu bibiyu Fatima ta ɗora akai ta cigaba da sharɓan kuka. Ko da tayi katarin kai idanunta cikin na Mukhtar da yanayin neman agaji wani irin mahaukacin kallo da ya aika mata kamar zai cinya ta ɗanye ba shiri ta janye idanunta daga cikin nashi.

Sunkuyar da kanta ƙasa tayi, sai kuma ta ɗago ta kalli Hajiyar. Kwarjini da haibar da ke fuskar Hajiya yasa duk ƙarerayin da ta shiryo daga ɗakinta suka ɓace ɓat a ƙwaƙwalwarta.

Ba ta da yadda zata yi dole ta faɗi gaskiyar abinda ya faru. Ashe suna buga ƙwallo ne sai Shahid ya ɗauki ƙwallo ya ruga da gudu ɗan'uwan na bin bayansa suna dariya. Yana wannan gudun har ya ƙarasa ƙofar ɗakinta, ita kuma a daidai lokacin ta buɗe ƙofa sai ya faɗa jikinta.

"Shi ne na ɗan mare shi..."

"Kika mare shi?"

Mukhtar da Hajiya suka haɗa baki gurin tambayarta a mamakance.

Saboda tsananin kunya da muzanta ta kasa amsawa. Sai ƙarfin gudun hawayenta da ya ƙaru.

"Mari nawa kika yi mishi?"

Hajiya ta tambayeta.

Shi kuma Mukhtar a zafafe ya ce

"Amma ni mai kika faɗa min ta waya? Ƙarya kika yi min kenan?"

"Hajiya don Allah kiyi haƙuri, ki yafe min. Mari uku kacal nayi masa, nayi mishi ɗaya kafin fitowar Fareeda nayi mishi biyu kuma a gabanta, ki tambayeta..."

Tsakanin Hajiya da Fareeda babu wanda ya lura da miƙewar Mukhtar da ƙarasawarshi kusa da Fatima kamar wani walƙiya, kawai dai sun ji kakarinta ne saboda wani irin muguwar shaƙa da yayi mata daga tsugune. Idanunsa sun kaɗa sunyi jajur yake cewa

"Ɗan ƙaramin yaron nawa za ki yi ma mari har uku saboda ke ɗin azzaluma ce muguwa mare imani? Ɗana za ki kashe Fatima? Ɗan nawa za ki kashe? To bari ni in fara kashe ki tun kafin watarana ki kashe min ɗaya daga cikinsu."

Daƙyar Hajiya ta samu nasarar ɓamɓare hannun Mukhtar a wuyan Fatima. A lokacin ta galabaita iya galabaita, gwanin ban tausayi. Ta ma kasa miƙewa tsaye, tana kwance wanwar a tsakar ɗakin tana jan numfarfashi a wahalce.

Fareeda dai tana zaune kakim kamar dutse, ko kallonsu bata yi ba. Ita fa Allah ya sani gaba ɗaya lamarin Mukhtar da Fatima sun ƙarasa fice mata arai.

Daman tuntuni ta aje lamarin Fatima a gefe ɗaya ne. A yanzu ta yanke shawarar ƙarasa ajiyeta gefe ɗaya, babu wani abu da zai zo ya gitta a tsakaninsu in Allah ya yarda. Idan kuwa ita Fatiman tayi kuskuren sake shiga harkokinta za ta daka ta ne, tsakaninsu yanzu ba sanyi ba sanyayawa.

Shi kuwa Mukhtar, wani irin zama ne ta ƙudura a ranta za su juya yi ita da shi. Zama shigen na mace mai sayar da ruwa da mijinta mai faskare, idan ya ɗauke mata gammo ta ɗauke mishi gatari.

Tana kallon yadda Mukhtar yaja Fatima kiiiii a wulaƙance kamar kayan wanki ya fice da ita daga falon Fareeda. Duk yadda Hajiyar ke mishi faɗan ya tallafeta a hankali bai saurara ba sai da ya kaita waje ya yasar.

Hankali tashe ya sunkuci Sayyid a jikin Fareeda Hajiya ta riƙe Shahid suka fice da nufin kai yaran asibiti.

"Ki taho mu kaisu asibiti."

Ya faɗa ma Fareeda a tausashe.

Wani irin kallo da tayi mishi kamar na ƙyama da sauri gaske ya kawar da fuskarsa daga gare ta.

"Kuje kawai. Ko kuma ka tafi da Fatima ita mai tarbiyya wacce ta iya bayar da tarbiyyah"

Ta faɗa mishi cikin gatse da gatsali.

_Hds jewelleries and more babban kamfani ne da muke bayar da kayayyakinmu akan farashi mai rahusa. Ƴar'uwa kina buƙatar ganin samfur ɗin kayayyakinmu don sayen nagari ki mayar da kuɗaɗenki gida? Ki shiga group ɗinmu ta wannan link ɗin□□ Ko kuma ki tuntuɓemu a wannan lambar a kaiki group don ganin irin kayayyakinmu +234 814 496 5394

https://chat.whatsapp.com/LpxLzmsKFFfBatQoY8q1jA

□□Domin ganin irin kayayyakin da muke sayarwa, danginsu laces, atamfofi, shadda, material, kayan kicin, dogayen riguna tsala-tsala ƴan dubai masu bala'in kyau da sauƙin kuɗi□□□ Ƴan kunnaye da sarƙoƙinsu masu bala'in kyau waɗanda idan kika saka za'a miki kallon zinari kika sanya□□😘😘 Kuma wani abin jin daɗi shi ne muna aika kayanmu ko ina kuma a gaggauce□□□□□□ Muna maraba da masu sayen ɗaiɗai ko sari. Sai kun zo❤❤❤

Kuyi haƙuri. Ku ƙara min uzuri don Allah. Wallahi wani irin rashin wuta ne muke fama da shi yanzu, sai a hankali. In sha Allah ko ɗan yaya ne zan dinga samu ina muku posting ko babu yawa. Na gode□□□□

Ƴar'uwa ciwon sanyi ne ya dame ki? Har bakya jin sha'awa ko ɗanɗano idan kun leƙa can babban birnin maji daɗi😘😘? Ki tuntuɓi Zee maman mujaheed +234 816 285 9027 domin siyen maganin sanyi mai kyau sosai akan farashi mai rahusa😍😍□ □□□□□ Baza kuyi da na sani ba in Allah ya yarda

RABON AYI

©Fareeda Abdallah

_*27*_

Ku zo ku sayi data a gurina sai ku cigaba da karatu□□□□□□😘😘

Ki tura kuɗin tsarin datar da kike so a wannan acc ɗin 5407827015, Farida Abdullahi, FCMB. Sai ki tuntuɓeni ta whatsapp akan 07039080978, idan ba ni a online ki kira ni ta 09077591726. In sha Allah cikin daƙiƙu ƙalilan datar da kika siya zai sauka a wayarki□□

MTN data price□□

500 MB □□ N150

1GB □□ N280

2GB □□ N550

3GB □□ N800

4GB □□ N1100

5GB □□ N1350

6GB □□ N1600

10GB□□ N2500

AIRTEL data price□□

300MB □□ 120

500MB □□ 150

1GB □□ N300

2GB □□ N600

5GB □□ N1350

10GB □□ N2500

20GB □□ N5000

GLO data price□□

1GB □□ N500

2.9GB □□ N1000

4.1GB □□ N1500

5.8GB □□ N1950

9MOBILE data price□□

500MB □□ N500

1.5GB □□ N1000

2GB □□ N1250

3GB □□ N1600

4.5GB □□ N2000

Na mu ba irin na su bane shi yasa farashin daban yake da nasu😉😉

_LOKACI mai zuwa da baƙin al'amura□ Tarihi ba shi tausayi komai kayi za'a bada labari walau na kirki ko akasin haka😩 Mai jini a jika yakan ji shi kamar babu wanda

ya kaishi izzah Shi yasa yake cin karensa babu babbaka ba tare da tunanin LOKACIn da zai girbe shukar kyawawan ayyukansa ko akasinsu na nan zuwa ba. Wannan a dunƙule tsokaci ne dangane da Labarin LOKACI wanda ni Fareeda Abdallah nake rubutawa. Masu karatu wai yaya ne? Cikakkiyar ƙaunar da za ku nuna min shi ne kuyi dafifi wajen siyan labarin lokaci a N500 kacal a Hikaya Bakandamiya. Wani ƙarin garaɓasar shi ne, da wannan ɗari biyar ɗin da za ku biya za ku samu damar karanta littattafan manyan marubuta irinsu Sumayya Abdulƙadir, Rufaida Umar, Lubnah Sufyan, Fatima ibrahim garba ɗan borno, da sauransu. Ku sauke app ɗin Bakandamiya hikaya a play store, duk wacce bata iya reg ba ta tuntuɓeni a 07039080978 zan koya mata yadda za tayi. Na gode

https://hikaya.bakandamiya.com/lokaci-babi-na-daya/ Domin karanta ɗanɗanon labarin, a danna wannan link ɗin.

Kwanansu Shahid biyu a asibiti aka sallamesu, Alhandulillahi sun warke garas, kamar ba su ne aka fice da su ranga-ranga ba. Daga asibiti kai tsaye Hajiyarmu gidanta ta wuce da su ba tare da neman shawara ko amincewar Mukhtar ba.

Shi ɗin ma dai bai ja da zafi ba, ganin yadda Hajiyar ke ciki da shi lallaɓawa yake yi su rabu lafiya. Bai gane tara shi take yi ba sai da aka sallamesu daga asibiti suka koma gida. Wankin babban bargo tayi mishi ƙal kan yadda ta fuskanci yana tafiyar da lamuran zamantakewar iyalanshi.

Ta kuma ƙara da faɗa mishi matuƙar bai zama jajurtaccen namiji mai iya danne zuciyarsa lokacin fushi ya dinga bincike a nutse lokacin da aka faɗa mishi faruwar wani abu tabbas zai rusa gidanshi da kanshi.

Sunkuyar da kanshi ƙasa yayi yana bata haƙuri har ya fahimci ta gama. Da gaske kuma ya gano kuren da ya aikata wajen yanke ma Fareeda hukunci, amma in Allah ya yarda zai kiyaye gaba wajen sake ɗaukar mataki da gaggawa kan duk abinda zai ji daga sama.

Acan gidanshi kuwa, wani irin zama ne ake yi mare daɗi ko kaɗan tsakaninshi da matan biyu. Gagarumin fushi yake yi da Fatima, duk yadda ta kwashe kwana tana jinyar shaƙan da yayi mata kallo bata ishe ba. Ya kulle duk wata ƙofa da zai bata damar da za tayi mishi wani bayani nata da yake ɗauka na ƙarya da rainin wayau.

Ɓangaren Fareeda kuma shi yake cusu cikin kwantai. So yake su shirya da gaske, ita kuma ta ƙi bayar da damar hakan. Bata kuma fito fili kai tsaye ta nuna mishi fushi take yi mai tsanani da shi ba, wani irin gashin ƙuma take yi masa sannu a hankali. Wasarere take yi da al'amarinsa kamar auren dole aka yi mata da shi.

Kai tsaye take yaɓa mishi duk irin baƙar maganar da tazo bakinta. Ya rasa ta yadda zai bi da ita, a ƙarshe sai ya koma ya saka mata idanu yana jiran yaga iya gudun ruwanta. Daman ai shi ma tayi mishi laifi, bai manta amfani da maganin da tayi don kar ya samu damar kusantarta ba. Yana dai bin ta ne don kawai irin hukuncin kai tsaye da ya ɗauka na maganar su Sayyid ba tare da ya bincika ba.

Yana kwana a ɗakin matan nashi, amma kashi tamanin da biyar cikin ɗari na rayuwarshi ya koma yi ne a ɗakin baƙi. Sai dare ya fara shiga sosai sannan yake tafiya ɗakin wacce take da girki ya kwanta.

Ga Fareeda dai wannan mataki ko a jikinta wai an tsikari kakkaura. Hankalinta kwance yake sosai fiye da ake tsammani. Tun daga faruwar wannan abin kuma ta daina ba Fatima abinci, itama acan ɓangarenta bata sake dafawa da ita ba. Tunda abin ya faru kuma har yau ita da Fatima basu haɗu ba.

A ɓangaren Fatima kam ta damu matuƙa gaya, hankalinta na tashe yake ƙwarai da fushin da Mukhtar yake yi da ita. Duk yadda ta so kalallame shi da kalaman ban haƙuri da daɗin baki kamar yadda ta saba a wannan karon ya ƙi bata fuskar haka.

Tun a ranar farko da ya shiga ɗakin ta zube a gabanshi cikin kuka ta haɗe hannayenta ta buɗe baki za ta fara magana ya daka mata wani gigitaccen tsawa ya ce idan ta kuskura ta ce za ta bashi hakuri igiyar da ta ƙulla tsakaninsu zai datse su a darennan. Saboda tsananin tashin hankali da firgicin jin abinda ya ce da jan mazaunai ta bar gabanshi ta koma can gaban madubi ta haɗe kai da gwuiwa tana rusa kuka.

Falo ya fice, bayan ya galla mata harara sannan yaja mata dogon tsaki. Tun daga wannan rana zaman doya da manja ne a tsakaninsu, idan zai shiga inda take kamar

mai ciwon baki yake cijewa yayi mata sallama. Idan ta gaishe shi daƙyar yake amsawa.

Amma wani ikon Allah a maimakon ta rame sai ta yi kumari. Ingantaccen haɗin damun kunu na maganin nono da take sha wanda ta siya a gurin Farida ba ƙaramin karɓarta yayi ba. Kwantattun nonuwanta duk da basu taso sun tsaitsaya ba a hankali take jin suna ciccika, tuwon tsoka na cikowa ta cikin lamusassun fatan. Ganin wannan cigaba da aka samu yasa duk tashin hankalin da take ciki bata taɓa fashin dama kunun safe da dare ba. Farida ta faɗa mata za ta iya shan maganin sau ɗaya idan tana harkar maneji, idan kuma tana so taga cika aiki da gaggawa to ta dinga sha da sassafe kafin ta ci komai, da kuma daddare idan za ta kwanta. Shi yasa idan da hali tun farko in za ki sayi maganin idan da hali ki sayi bokiti biyu domin kar maganin ya yanke ba tare da kin sha na aƙallah sati biyu ko uku kamar yadda ake so ba *_□□09077591726 lambar mai maganin nono_*

Kullum idan ya shiga kwanciya haka za ta tasa shi gaba ta saka gwuiwa a ƙasa gaban gado ɓangaren da yake kwanciya tana hawaye. Ba ta taɓa tanka mishi har sai ta ji ya fara jan numfashi alamar yayi barci.

A tsorace take sosai, tunda ya ce idan ta kuskura tayi mishi magana kan abinda zai faru shi yasa take kiyayewa. Tsoronta Allah tsoronta Mukhtar ya ce zai sake ta, ita kam da tashin alƙiyamarta ta tsaya, kada Allah ya nuna mata wannan rana. Idan tayi tunanin haka har wani tuf-tuf take yi ta tofar da mugun miyau.

Shi kuwa Mukhtar kamar dutse duk yadda za ta tasa shi da koke-koke bai taɓa ɗaga ido ya kalleta ba. Idan ta ishe shi da jan shesshеƙa ne sai ya juya mata baya, ya ɗauki filo ya danne kansa har barci ya ɗauke shi. Ranar da yan tsiyan ke kusa kuma tana fara kuka zai fatattaketa ya kora ta falo. A haka har suka kwashe sati biyu basu samu daidaito ba.

******

Tsawon lokaci Ibrahim yana kallon Mukhtar da wani irin maɗaukakin mamaki kwance ɓaro-ɓaro kan fuskarsa. Sau uku yana buɗe baki yana rufewa, ya kasa cewa komai don mamaki da takaici.

Daga ƙarshe dai yayi ƙumajin buɗe baki daƙyar ya ce

"Ban taɓa sanin kai ɗin daƙiƙi bane sai yau Mukhtar. Yanzu saboda Allah da Annabi kai ka yarda da wannan tatsuniyar tunda kai ƙwaƙwalwarka dusa aka zuba a ciki?"

Da wani irin bala'in fushi da ɓacin rai Mukhtar ya ce

"Ni kake zagi kake tozartawa haka Ibrahim? Babu komai, ba laifinka bane. Laifina ne da na kwaso damuwata na faɗa maka don tunanin kai ɗin amini ne na gari. Ka ga tafiyata."

Ya yunƙura zai miƙe tsaye a fusace Ibrahim ɗin ya janyo rigarshi da ƙarfi ya zauna jaɓar kan kujera.

"Ai wallahi baka isa ba. Yadda muka faro maganar nan sai mun ƙarasata. Dole ka zauna ka saurari duk abinda zan faɗa maka. Wai ni kam Mukhtar anya ma Fatimar nan haka ta barka? Tsohuwar mace duk ta sa ka susuce ka zama wani maloho da kai, sai wauta kake zubawa baka san ko cikin abokai ana zunɗenka ba? Hmmm! Ai babu komai Mukhtar, da irinku ne kuke ja mana mata suke yi mana kuɗin goro wajen cewa mu ba ɣaɣan goyo bane.

Yanzu kai ka manta irin matsananciyar ƙauna da soyayyar da Fareeda ta nuna maka tun zamanin neman aurenta har zuwa bayan aure? Ka manta irin yadda Fareeda tai ta haƙuri da murɗaɗɗun halayenka waɗanda ko mu abokanka ba ma iya haƙuri da su? Ka manta yadda na sha faɗa maka a zamantakewarku da Fareeda kai ke da kaso sittin cikin ɗari na matsalar zaman aurenku?

Bari in sake maimaita maka abinda na daɗe ina faɗa maka. Zamantakewar aure nau'i ne na zaman amana, yarda, musayar ra'ayi tsakanin juna. Ba wai zaman bautarwa ko takura ko ƙuntatawa ba. Ni ban baka shawarar ka saki Fareeda ta dinga fita sakaka ba, amma abubuwa da dama ya kamata ka ɗan buɗa mata.

Balancing ake yi Mukhtar, kai da iyalinka in dai ba zarginta kake yi ba, ya zama dole ka dinga kawar da kai kana sakar mata wasu abubuwan ko da zuciyarka ba ta son haka.

Ko ka ƙi ko ka so yanzu zamanin ya canza. Dole mu karɓi wannan canjin da rayuwa ta zo da shi. Irin yadda mata suka bautatu ma maza a baya, na yanzu sam baza su iya haka ba. Me yasa kaga yanzu sakin aure ba'a ɗauke shi a bakin komai ba? Saboda Maza masu cusasshen tunani da bahagon ra'ayi irin naka sun kasa gane yanayin zamantakewa, da kuma abinda ake nufi da zamantakewar shi kansa. Ni dai a ganina, a kuma irin karatun da nayi ma mace, wallahi banga wani abun tafi da ita kamar zuma da sai na yi ta shuna mata wuta ba.

Amma tunda dai kai ba ka jin shawara, kaje kayi abinda kake so Mukhtar. Tunda dai kai har ka yarda Fareeda da gaske ta yi amfani da maganin da ba ka iya kusantarka, to menene amfanin zamantakewar aurenku? Ka sallameta kawai ta ƙara gaba ka riƙe Fatimarka."

Yayi wani dariya kafin ya cigaba da cewa

"Ai wallahi da kana ji kana gani ɗan hakin da ka raina zai tsole maka ido. Mamaki sai ya kusa ajalinka kan irin mazan da za kaga suna gogoriyo wajen neman aurenta. Ina tabbatar maka ko cikin abokanmu ɗaiɗai waɗanda baza su sa kai ba, ko ni nan..."

"Ibro don girman Allah kayi shiru da waɗannan maganganun. Allah ma bazai sa haka ya faru ba in sha Allah, ni da Fareeda mutu ka raba takalmin kaza. Yanzu dai don Allah ka bani shawara, ya zanyi? Me zanyi? Wani mataki zan ɗauka don gano gaskiyar abinda yake faruwa?"

Ya ƙarasa maganar a marairaice.

Tunda Ibrahim yaga Mukhtar ɗin yayi laushi ya sauke kanshi ƙasa. Sosai ya saki jiki ya bashi shawarwari ƙwarara waɗanda ya bashi tabbacin in dai ya bi su kamar yadda ya karanta mishi, to nan da kwanaki ƙalilan babu abinda zai wanzu tsakaninshi da iyalanshi sai zaman lafiya da kwanciyar hankali.

Da fara'a sosai a fuskarsa suka rabu da Ibrahim ɗin. Daman a cikin abokansu in dai ɓangare na gyaran zamantakewa ne tsakanin miji da mata Ibrahim shi ne gaba-

gaba. Allah yayi masa wannan baiwar, in sha Allah da ya shiga cikin matsala ya tattauna da miji da matan cikin ƙanƙanin lokaci matsala za ta kau, a samu daddaɗan zamantakewa da kwanciyar hankali.

A wannan ranar ya kama girkin Fatima ne. Kai tsaye kasuwa ya shiga ya siya kayan ciki da yawa yayi cefane ya wuce gida. Da kallon fuskarsa kawai za'a fahimci yana cikin walwala.

Ganin wannan fara'a da ke shimfiɗe a fuskarsa yasa hankalin Fatima ya ɗan kwanta, da rawar jiki ta tarbeshi ta karɓi kayan hannunsa zuwa kicin. Ita da take tsoron yi masa magana sai ga shi da kanshi yake janta da zance cikin kulawa da soyayya.

Kamar a mafarki take kallon lamarin, tun tana ɗari-ɗari har dai ta saki jikinta suka cigaba da hira cikin walwala. Shi ya taya ta suka raba naman gida biyu, ya ce tayi farfesun rabi, ta soya rabi. Cikin hanzari ta fara aikin yana kama mata da ƙananun abubuwa.

"Ina abincin Fareeda da nata farfesun?"

Ya tambayeta bayan ya ga ta gama komai bata ce mishi ga na Fareeda ba. A lokacin har an idar da sallar isha'i.

"Taɓ! Tuntuni fa mun daina girki tare, tun lokacin da wancan rikicin ya faru washe gari da girki ya koma kanta bata bani abinci ba, har girki ya fita kanta bata kawo min ba ni nake girka nawa. Ganin haka ni ma sai na daina dafawa da ita..."

"Ikon Allah! Me yasa baki faɗa min ba?"

Ya tambayeta cikin sanyin murya, kamar ba Mukhtar wannan mai yawan faɗa da hargagin ba.

"Kayi haƙuri. Na yi tunanin ko ita ta faɗa maka ne."

Ta amsa a tsorace bayan ta saukar da ƙwayoyin idanunta ƙasa.

Bai ce komai ba. Miƙewa yayi ya shiga kicin ɗin ta. Duk abinda ta dafa sai da ya ɗiba ma Fareeda a wadace kafin ya ɗauki kulolin ya fice da su, bayan ya ba Fatima uzurin yana zuwa.

Ko da ya isa can abinci ya samu tana ci, da alamun hankalinta kwance. Idanunta na kan T.v tana kallon shirin taron ƙauna da ake haskawa a tashar arewa24.

Ko da yayi sallama ta amsa bata kalle shi ba. Nan gabanta ya ajiye kulolin abincin ya zauna a gefenta, sai kallonta yake yi. Ta ƙara wani irin kyau mai sanyi, daman ita haka ciki ke mata a farko-farko, kyau take yi sosai sai cikin ya kusa fita sai ta koma yadda take.

"Ƴanmata na. Ba tayi?"

Ya faɗa da murmushi sosai a fuskarsa bayan ya riƙe cokalin hannunta.

Tsai tayi da ranta, idanunta na kan hannunsa da ya riƙe mata cokali. Sai kuma ta ɗanyi murmushi, ta ɗago fuskarta ta kalle shi a sakalce tana ɗan jujjuya idanunta.

"Ƴanmata tana can ka baro ta a ɓangaren da ka fito. Miye wannan ka kawo min? Sarauniyar taka bata faɗa maka na daina karɓan duk wani jagwal da zai fito daga hannunta bane?"

"Ta faɗa min. Ina so ku cigaba da girki kamar yadda na tsara muku da farko, shi yasa na ɗauko wannan na kawo miki..."

"Bazan ci ba. Kuma na rantse da girman Allah bazan sake haɗa girki da wata mace a gidannan ba. Iya zallar gaskiyar magana kenan Mukhtar."

Ta faɗa kai tsaye tana kallon cikin idanunsa ba tare da shakka ko tsoro ba.

Lallai giwa ta fara lafiya. A maimakon ya balbaleta da faɗa kamar yadda ya saba sai cewa yayi

"Allan ya baki haƙuri uwar huɗuna. Allah ya sauke ki lafiya."

Yayi maganar da murmushi a fuskarsa. Ganin tana mishi wani irin kallo yasa shi faɗaɗa murmushinsa.

"Uwargida sarautar mata, Fareeda ikon Allah, ja gaba ki shige sauran mata sai dai su bi ki a baya. Duk namijin da bai da mai sunan Fareeda a cikin matanshi ina tausaya mishi kan mummunar asarar da ya tafka a rayuwar duniya."

Kaɗa kai ta iya yi kawai ta kawar da kanta zuwa kan T.v da take kallo. Ita ɗin ba sakarya bace da zai zo yana mata wani daɗin baki da sam ba halinsa bane. Ta sanshi kamar yunwar cikinta, don haka bazai zo yana mata wasu tsamayen kalamanshi ta saurareshi ba. Abinda bai fahimta ba shi ne, gishiri ya sauka daga kan kaza, ta ajiye shi ne gefe ɗaya.

Ko ba'a rabu ba, ita a tsarin rayuwarya baza ta taɓa ajiye namiji a zuciyarta har ya haddasa mata wani mugun ciwo ba. Da igiyoyin aurensa da komai za ta yakice shi ta cigaba da rayuwa lafiya kalau.

_Hds jewelleries and more babban kamfani ne da muke bayar da kayayyakinmu akan farashi mai rahusa. Ƴar'uwa kina buƙatar ganin samfur ɗin kayayyakinmu don sayen nagari ki mayar da kuɗaɗenki gida? Ki shiga group ɗinmu ta wannan link ɗin□□ Ko kuma ki tuntuɓemu a wannan lambar a kaiki group don ganin irin kayayyakinmu +234 814 496 5394

https://chat.whatsapp.com/LpxLzmsKFFfBatQoY8q1jA

□□Domin ganin irin kayayyakin da muke sayarwa, danginsu laces, atamfofi, shadda, material, kayan kicin, dogayen riguna tsala-tsala ƴan dubai masu bala'in kyau da sauƙin kuɗi□□□ Ƴan kunnaye da sarƙoƙinsu masu bala'in kyau waɗanda idan kika saka za'a miki kallon zinari kika sanya□□😘😘 Kuma wani abin jin daɗi shi ne muna aika kayanmu ko ina kuma a gaggauce□□□□□□ Muna maraba da masu sayen ɗaiɗai ko sari. Sai kun zo❤❤❤

Kuyi haƙuri. Ku ƙara min uzuri don Allah. Wallahi wani irin rashin wuta ne muke fama da shi yanzu, sai a hankali. In sha Allah ko ɗan yaya ne zan dinga samu ina muku posting ko babu yawa. Na gode□□□□

Ƴar'uwa ciwon sanyi ne ya dame ki? Har bakya jin sha'awa ko ɗanɗano idan kun leƙa can babban birnin maji daɗi😘😘? Ki tuntuɓi Zee maman mujaheed +234 816 285 9027 domin siyen maganin sanyi mai kyau sosai akan farashi mai rahusa😍😍□ □□□□□ Baza kuyi da na sani ba in Allah ya yarda

RABON AYI

28

©Fareeda Abdallah

Dangane da batun mai bayar da maganin rashin haihuwa. Mata da yawa sun biyo ni ta private da ƙorafin iyakar magungunan da take bayarwa kenan? Nayi ta bin su da cewar zan tambaya. To a jiya dai Allah ya nufa na tafi har can ƙauyenmu mun gana fuska da fuska da wannan mata, saboda ita ba ta da wayar da zan kira inyi magana da ita kai tsaye.

*Bayan maganin rashin haihuwa na maza da mata. Tana bayar da maganin sanyi, idan mace ta san tana fama da ciwon sanyi, akwai wasu ɗaurin sauwoyi da ta nuna min duk guda ɗaya 500, jiƙa shi ake yi da mazarƙwaila, citta, kanunfari, idan ya jiƙu sai a dinga sha da Oga da yara gaba ɗaya. Akwai wani garin magani da ta nuna min shi ma dai duk na sanyin ne, irin sanyin haihuwar nan musamman masu jego, ko wacce take fama da sanyi tun na haihuwa, garin maganin ɗaurinshi 500, za'a haɗa

shi a cikin yaji ne a dinga cin abinci da shi. Tana bayar da maganin gyaran nono ga masu ciki da masu shayarwa, shi ma ɗaurinshi 500, idan mace ta dimanci shan maganin tun tana da ciki da yaddar Allah da ta haihu baza ta fuskanci matsalar ruwan nono ba. Mai shayarwa ma idan ta fara amfani da maganin za taga yadda nononta zai gyaru, yaronta yayi tubarkallah. Ko da yaron ya yanƙwane da yaddar Allah zaiyi kumari, hatta ƙurarrajin ko ela da yara ke yi idan mace tana shan garin maganin da yaddar Allah ɗanta bazai yi ba. Ina matan da suke fama da matsalar rashin jin sha'awa? Har suna ji a dole mazajensu ke kusantarsu, wasu ma har aurensu ke mutuwa saboda wannan matsalar, sai a dinga cewa ko suna da aljannu? Matar tana bayar da haɗin magunguna da yaddar Allah in dai mace tana da rabo za taga yadda za ta samu waraka cikin sauki. Matan da mazajensu ba su da kuzari, sanyi da basir ya musu illar da sai ayi watanni basu nemi iyalansu ba, su ma akwai maganin da take bayarwa a jiƙa ma miji, cikin lokaci za ki ga yadda lafiya za ta wadatu a jikin mijinki, hatta kuzarinsa sai kin ga ya ninnika na da.* Masu buƙatar ɗaya daga cikin maganin matsalolin da na bayyana a sama idan sun san da gaske suke yi su tuntuɓeni ta wannan lambar 07039080978, don Allah duk wacce tasan ba da gaske magani take so ba kar ta tuntuɓeni balle har mu ɓata ma juna lokaci□□□□ □□□□□□

Ƙara matse mata waje yayi, a hankali ya riƙo tsintsiyar hannunta yana ɗan matsawa

"Ina son ki Fareeda."

Ya faɗi kalaman cikin salo a rarrabe.

A yanzu ma dai kallonshi ta sake yi, sai kuma ta taɓe baki ta mayar da fuskarta ga t.v.

"Haushi na kike ji?"

Ya tambayeta, da muryarsa a sanyaye.

"A'a"

Ta amsa daƙyar bayan ta ɗauki tsawon daƙiƙu tana jan fasali.

Ya buɗe baki zai sake magana ta katse shi da cewar

"Haba Mukhtar, saboda Allah abincin ma baza ka barni in ci cikin kwanciyar hankali ba? Sai da safe ce ya kawo ka ko? to na amsa, Allah ya tashe mu lafiya. Don Allah ka kwashi kulolinnan ka koma gurin matarka, bazan ɓoye maka ba Allah ya sani na fi jin daɗin zama ni kaɗai ba tare da wani a kusa da ni ba."

Ta faɗi maganganun da dukkan gaskiyarta.

Ya daɗe yana kallonta, zuciyarsa a jagule. Ya kasa ce mata komai, wai yau shi Fareeda ke ce ma ta fi jin daɗin zama ita kaɗai ba tare da shi a gefenta ba. Ya murgina kai gefe ɗaya abin tausayi, ya sani, Ibrahim ya faɗa masa. Shi da kanshi ya ƙona sunkurun kashinsa, don haka fushin fari ba nashi bane. Dole zai cigaba da bin ta yana lallaɓata har zuwa sa'adda za ta sakko don kanta ba tare da ya tilasta mata ba.

"Fareeda, ni dai ina neman afuwa. Allah ya huci zuciyarki. Bari in tafi, Allah ya tashe mu lafiya."

"Ameen"

Ta amsa da sauri.

A kasalance ya miƙe ya nufi ƙofar fita.

"Ka kwashe waɗannan kulolin, ka mayar mata da kayanta."

Ta faɗa ganin zai bar mata abincin Fatima a gabanta.

A hankali ya juyo, gabanta ya tsuguna ya ɗauki kular abinci ya bar mata na kayan ciki. Ya kalli cikin idanunta, a marairaice ya ce

"Zan mayar da abincin, waɗannan biyun kayan ciki ne, farfesu da soyayye. Don darajar fiyayyen halitta SAW kar ki ce baza ki ci ba ko kuma ki ce in mayar. Don Allah"

"Shi kenan! Allah ya ƙara buɗi."

Ta faɗa saboda darajar waɗanda ya haɗa ta da su. Ya ɗaure ta da jijiyoyin jikinta, sun fi ƙarfin a roƙe ta yin abu don su ta ce a'a.

"Bari in juyo ka mayar da kulolin."

Har za ta miƙe sai ya dafa kafaɗunta ya komar da ita ta zauna.

"Yi zamanki Baby. Bari in ɗauko wasu kulolin in juye a ciki."

Ko da ya shiga kicin ɗauko kulolin sai da ya haɗo mata da faranti da cokali, ko da za ta ɗiba ta ci ba sai tayi wahalar tashi ba. Duk da ya ga ruwa a gabanta sai da ya ɗauko wani ya ƙara ajiye mata.

"In ɗiba miki ko kaɗan?"

Ya tambayeta sa'adda yake juyewa a kulolinta.

Abinku da mai ƙaramin ciki, tun sa'adda ya buɗe kular ƙamshin farfesun ya daki hancinta miyaun bakinta ya tsinke. Amma saboda ta tankwaɓe shisshigin da yake mata sai ta ce

"A'a! Ba yanzu zan ci ba. Pls rufe kular, ƙamshin ya fara hawa min kai."

Da sauri ya rufe jikinsa na rawa. Bawan Allah sai sannu yake jera mata ganin yadda take yamutsa fuska. Bai tashi a gabanta ba sai da yaga ta daina ɓata rai, haka ya fice gwuiyawunsa a saɓule, kamar wanda yayi amai da gudawa.

Ko da ya koma can ɓangaren Fatima duk tsawon lokacin da ya ɗauka gurin Fareeda tana zaune gaban abincinsu tana jiranshi. Duk da ranta ya sosu da daɗewar da yayi, ko kaɗan bata nuna mishi ba.

"Sannu da zuwa Haskenah"

Ta faɗa da fara'a sosai a fuskarta.

"Ya Auntyn tawa take? Ina fatan ka tarar da ita lafiya kalau?"

Ta sake faɗa kafin ya amsa sannu da zuwan da take mishi.

Da murmushi a fuskarsa ya amsa mata. Sosai ya ji daɗin yadda ta tambayi lafiyar Fareeda, ya tuno yadda ita Fareeda ta gama kushe lamarin Fatima yanzunnan kafin ya baro wajenta. Hakan ya saka shi jin babu daɗi kaɗan a zuciyarsa, bai bari tunanin yayi nisa ba ya watsar da komai ya zauna cin abinci.

Bayan sun gama tana tattare kwanonin zuwa kicin shi kuma yana zaune kan kujera, wayarsa ce a hannunsa yake dannawa. Jefi-jefi yana ɗaga idanu ya kalli Fatima da take zirga-zirga a gabansa.

Ta zo za ta gitta ta gabanshi ya riƙo hannunta ɗaya haɗe da cewa

"Zo nan in gani Amaryata"

Ya janyo ta a hankali ya zaunar kan cinyarsa.

Yana kallon idanunta ya ɗaga hannunsa a hankali ya zura ta saman rigarta. Idanu ya ɗan bubbuɗe jin tudun da ya shafo, tun dazu da take wucewa yana ta kallonta gaba da baya ya zaci cikon da ya hana ta yi ne tayi. Shi yasa ya yanke shawarar dubawa don kar ma ya tambayeta ta faɗa mishi ba daidai ba.

"Iyyeeeee... Amaryar tawa ce haka? Yaushe aka samu wannan gwaggwaɓar cigaban ba ni da labari?"

Ya tambayeta yana ɗan mammatsa mazaunanta yana jin yadda tsoka ya fara rufa ma ƙasusuwan gurin asiri, da murmushi a fuskarsa.

Hajiya Fatima dai ta kasa magana, a yangace ta ɗan saki siririyar haɗe da kwantar da kanta a ƙirjinsa.

"Au! Abin yʻar haka ne? Baza ki faɗa min ba Fatina?"

Ya raɗa mata a kunne yana taya ta dariya.

"Haskenah ka ga ka bari, ba na so."

Ta faɗa a shagwaɓe tana ɗan dukan ƙirjinshi.

Aikin da bata ƙarasa a wannan dare ba kenan. Tun a nan falon wasan ya sauya salo, daga ƙarshe dai cak ya ɗauketa kamar wata baby zuwa cikin ɗakin barcinsu.

A wannan dare, Mukhtar ya shayar da Fatima zallar madarar farin cikin da ta daɗe tana burin kwankwaɗa a auren matashi sabon jini. Irin wannan salon soyayyar ta indiyawa ne yasa a mafiyawancin lokuta zamanin marigayi take cizon yatsar auren tsoho. Ta zaci a wancan ranar ne da ya tabbatar ta samu lafiya ne suka ci amarci, ayau ta tabbatar wancan ranar ba'a yi komai ba illah shafar mai. Yau ita ce ranar da suka ci uwar sabada ita da Haskenta. A daren ta ƙara tabbatar da Haskenta wani Haske ne mai muhimmanci a cikin rayuwanta, tun yanzu ya fara tsundumata cikin wasu daɗaɗan duniyoyi da ko kusa basu taɓa ziyarta ita da Babansu Ummee ba ina ga can gaba sun ƙara dunƙulewa ta hanyar zama abu ɗaya?

Haka ya sake ɗaukarta cak suka shige banɗaki, bayan wankan tsarki a tare suka yi na soso da sabulu. Yana cuɗa mata baya tana cuɗa mishi, kamar wasu ƙananun yara har da su wasan watsa ruwa da shafe-shafen kumfa bayan an ɗauraye jiki. Wannan wanka a lalace suka ƙarasa shi sannan suka fice daga banɗakin.

Da sauran awa ɗaya kafin a kira sallar asubah, don haka suka bi lafiyar gado. Tana kwance luf a ƙirjinshi tana sauke ajiyar zuciya sannu sannu.

"Barci za kiyi Fatina?"

Ya jefa mata tambayar bayan ya ji numfashinta ya fara canzawa.

"A'a! Kawai dai na ɗan gaji ne."

Ta amsa a kasale.

"Na san kin gaji. Sannu da ƙoƙari, ki daure muyi sallar asubah sai mu kwanta. Yanzu dai tashi muyi magana."

A hankali ta zare jikinta daga cikin nashi ta zauna a tsakiyar gadon. Shi ma zaman yayi, amma sai ya juya yana fuskantarta. Hannayenta biyu ya kama ya riƙe a cikin nashi, babu alamun ɓacin rai ko kaɗan a fuskarsa, sai ma wani ƙayataccen murmushi da yake sakar mata akai-akai.

"Fatina, tambayarki zanyi. Amma ina so ki ɗaukar min alƙawarin duk abinda na tambaye ki za ki faɗa min gaskiya tsakaninki da Allah da ya haliccemu."

Ƙure shi da kallo tayi, zuciyarta cike da tunanin me zai tambayeta.

"Tambayar mecece?"

"Ai baki ɗaukar min alƙawarin ba..."

"Na ɗauki alƙawari. In dai na sani zan faɗa maka gaskiya tsakani da Allah."

Ta katse shi da ƙagauta a muryarta.

Shiru yayi yana tunanin ta inda zai fara magana. Can sai ya daure ya ce

"Fatina, a gurin binciken abinda ke damuna har yake hana ni kusantar Fareeda an tabbatar min matsalar ba daga ita bane, daga ni ne..."

"Daga kai kuma? to taya ni baka fuskantar irin matsalar a gurina?"

Tayi mishi tambayar tana yatsuna fuska.

"Mai maganin da ya faɗa min haka ya ce, da yawan mata idan za suyi aure musamman zawarawa sukanyi amfani da magunguna daban daban domin su gyara jikinsu. Idan kuwa gidan da za su shiga akwai wata matar suna ninninka yin magunguna saboda su sha gaban uwaren gidansu. Shi ne mai maganin ya ce in tambayeki, wata ƙila a irin haka kika gamo ni da wannan matsalar ba tare da kin sani ba..."

"Wani tsinannen mai magani ne zai ƙulla min wannan sharrin?"

Ta katse shi a fusace. A zabure ta ƙwace hannunta daga cikin nashi ta dira ƙasa daga kan gadon tana zazzare idanu.

"Banyi komai ba. Ni kam babu abinda nayi na wani shirmen magani can. Mu gidanmu da muke ahlussunnah ta ina za'a bar mutum yayi wani magani? Babu abinda nayi, ba ruwana. Kar shegen da ya kuskura ya ƙulla min jakar tsaba balle kaji su bi ni da tsattsaga. Alum da bagaruwa kawai na san nayi ta tsarki da su shi yasa ka ji ni a matse, bushewar da ka ji nayi a farko kuma saboda ban haɗa da lalle wajen tsarki bane. Yanzu da na fara amfani da lalle shi yasa ka ji ni zam-zam yadda ake son ko wace mace mai ni'ima..."

Haka ta saki baki tana ta zuba shaaaaa, ta kamo wannan maganar ta saki wancan. Duk a ƙoƙarinta na wanke kanta daga maganganun da Mukhtar ya tunkaro ta da shi.

Shi dai yana ta kallonta, yana ƙara karantarta. Bai ga komai ba illah naɗe tabarman kunya da hauka da take ƙoƙarin yi. Ganin ta yi shiru tana zare idanu yasa shi ƙara kamo hannunta a karo na biyu, kusa da shi ya zaunar da ita.

"Fatima. Kinga ni magana ce nazo miki da ita na nutsuwa da fahimtar juna. Don Allah ki saurara min, ki kwantar da hankalinki, ki zurfafa tunani ki faɗa min, a cikin matan da kika sayi magani a hannunsu babu wacce ta ambata miki magana makamanciyar wannan matsalar tawa kan wani magani?"

A maimakon ta amsa, ko kuma ta nutsu ta zurfafa tunani yadda ya ce, kawai sai ta fashe da kuka. Ta ƙwace hannayenta ta fara yarfe su kamar wacce ta tsoma a ruwan zafi

"Na shiga uku! Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un. Haskenah zargina kake yi? Daman na sani ba ka so na, ba ka ƙaunata, ka aure ni ne don kawai Fareeda ba ta jin maganarka, na sani. Amma ina so ka tuna abu ɗaya, soyayya da ƙauna ce tasa na aure ka. Ni ina son ka Mukhtar, na daɗe ina son ka, ko don soyayyar da nake maka ban cancanci irin wannan wulaƙancin da tozartawa ba."

Izuwa yanzu, zuciyarshi ta fara kaiwa ƙololuwa gurin ɓaci. Sanyayan halayen da ya aro ya yafa kan halayenshi na zafin rai tuni sun fara yin nasu wajen. Ya fara dawowa asalin Mukhtar ɗinshi mijin Fareeda.

Kamar ba shi ne yanzu ya gama ɗaga ta sama yana rirriƙewa cikin soyayya kamar jaririya ba. Wani gigitaccen tsawa da ya daka mata a take ta haɗiye kukan da take

yi kamar ɗaukewar ruwan sama. Ya kalleta da jajayen idanunsa, alamun rashin gaskiya ne ƙarara a tattare da ita.

"Baza ki faɗa min gaskiya ba ko Fatima?"

"Gaskiya nake faɗa maka. Wallahi gaskiya ne nake faɗa, na rantse da Allah. ka yarda dani don girman Allah..."

Tsam ya miƙe tsaye ya fice daga ɗakin kafin ta kai ƙarshen maganganun da bai ɗauke su a komai ba illah tsagwaron ƙarya.

Ta zaci ya bar maganar kenan. Ta gyara zama haɗe da takurewa tana sauke ajiyar zuciya kawai sai ga shi ya dawo cikin ɗakin, a hannunsa takarda da biro ne.

"Hasssssskkkkkeeeh! Mmmmmmmme kakkkkkkkeeeee ƙoƙƙƙƙƙƙarinnnnnn yiiiiiii?"

Ta tambayeshi bakinta na rawa da wani balaɣaɣɣen in-ina a muryarta.

Gefen gadon ya zauna, ya buɗe takardar ya yago falle ɗaya, ya ɗora biron akai alamun zai fara rubutu. Ya kalleta a ɗage

"Fatima tunda kin ƙi faɗa min gaskiya na rantse da girman Allah babu abinda zai hana ni datse igiyoyin auren da ke tsakaninmu. Banga amfanin don kawai na auro ki wata ƙozai ƙozai da ke ki shiga ki fita ki hana ni kusantar matata abar ƙaunata ba. Gara ni da ke duk muyi biyu babu."

Ya sauke idanunshi ƙasa, cikin sauri ya fara rubuta

"Ni Mukhtar..."

"Na sani, wallahi tallahi na sani, zan faɗa maka gaskiyar, don ya rasulullahi kar ka sake ni Mukhtar"

Ta faɗi maganganun cikin ihun kuka na tashin hankali haɗe da fincike biron hannunsa...

Ma su buƙatar yin sub don karanta labarin LOKACI, ba sai sun sauke app ɗin ba. Su shiga ta wannan link□□ɗin suyi reg,

https://hikaya.bakandamiya.com/

*Gurin rubuta password su saka a harhaɗe abcd da 123, misali □□ Aliya*123. Abinda baku gane ba sai ku tuntuɓeni a lambata da ke sama*

_Hds jewelleries and more babban kamfani ne da muke bayar da kayayyakinmu akan farashi mai rahusa. Ƴar'uwa kina buƙatar ganin samfur ɗin kayayyakinmu don sayen nagari ki mayar da kuɗaɗenki gida? Ki shiga group ɗinmu ta wannan link ɗin□□ Ko kuma ki tuntuɓemu a wannan lambar a kaiki group don ganin irin kayayyakinmu +234 814 496 5394

https://chat.whatsapp.com/LpxLzmsKFFfBatQoY8q1jA

□□Domin ganin irin kayayyakin da muke sayarwa, danginsu laces, atamfofi, shadda, material, kayan kicin, dogayen riguna tsala-tsala ƴan dubai masu bala'in kyau da sauƙin kuɗi□□□ Ƴan kunnaye da sarƙoƙinsu masu bala'in kyau waɗanda idan kika saka za'a miki kallon zinari kika sanya□□😘😘 Kuma wani abin jin daɗi shi ne muna aika kayanmu ko ina kuma a gaggauce□□□□□□ Muna maraba da masu sayen ɗaiɗai ko sari. Sai kun zo❤❤❤

Kuyi haƙuri. Ku ƙara min uzuri don Allah. Wallahi wani irin rashin wuta ne muke fama da shi yanzu, sai a hankali. In sha Allah ko ɗan yaya ne zan dinga samu ina muku posting ko babu yawa. Na gode□□□□

Ƴar'uwa ciwon sanyi ne ya dame ki? Har bakya jin sha'awa ko ɗanɗano idan kun leƙa can babban birnin maji daɗi😘😘? Ki tuntuɓi Zee maman mujaheed +234 816 285 9027 domin siyen maganin sanyi mai kyau sosai akan farashi mai rahusa😍😍□ □□□□□ Baza kuyi da na sani ba in Allah ya yarda

RABON AYI

29

©Fareeda Abdallah

_Yʻar'uwa ki tuna, kafin saukar da ko wace irin cuta, sai da aka saukar da maganinta. Don kinyi magani da yawa baki dace ba ba shi zai sa ki yanke tsammani daga samun waraka ba. Ki gwada maganin da muke karɓa ma al'ummar Annabi SAW, wata ƙila warakarki a wannan maganin yake baki sani ba. Haihuwa kike nema? Baki taɓa yi bane ko kuwa jinkiri ne kike samu tsakanin haihuwar? Sanadiyyar planning ne kika samu jinkirin ko kuwa sanyi ne yake damunki ko haka kawai? Matsalar rashin haihuwar daga mijinki yake? Muna da ingantaccen magani garanti wanda aka gwada muka tabbatar da aikinsa, in Allah ya yarda ko me ya shafi mahaifar mace da mararta wanda ya hana ta haihuwa in dai tayi amfani da saiwoyin maganinmu za ta samu biyan buƙata da yaddar Allah. Matsalar mace ko namiji 2k ne.

Akwai ƙullin maganin da muke sayar da shi 500, in dai matsala ta shafi nonon mace da yaddar Allah za ki samu waraka. Mai ciki, mai shayarwa, mare shayarwa duk za su iya amfani da wannan magani. Ko da matsalar ciwon daji ne da ya shafi nono in sha Allah za ki sami waraka sanadiyyar amfani da wannan magani. Akwai garin maganin sanyi da za ki haɗa a cikin yaji, shi ma 500. Akwai ingantaccen maganin sanyi da za ki saya muku ke da Oga, 2k ne. In Allah ya yarda za ki sha mamakin yadda lafiya zai wadace ku ke da Oga, za ki ga yadda za ku dawo kamar sabbin amaren da suke mararin junansu😍. *Akwai ingantaccen haɗin magani na gyaran nono wanda ni Fareeda Abdallah nake sayarwa, bokiti 1litter 2500, yʻar'uwa in dai za ki juri dama kunun garin maganin safe da dare, za kiga yadda ba cikowar

nono kaɗai ba, hatta fatar jikinki sai ta canza, za kiyi kuɓul-kuɓul😍, sa'annan ni'ima bazai taɓa yanke miki ba in Allah ya yarda saboda irin haɗe-haɗen da ke cikin wannan magani. Ga duk mai buƙatar ɗaya daga cikin maganinnan da gaske ta tuntuɓeni ta whatsapp a 07039080978, idan kira ne a kira ni ta 09077591726. Duk jihar da kike a ƙasar nan za mu iya aika miki da maganin amma ke za ki biya kuɗin mota, har ƙasar nijar muna aikawa kan farashi ƙalilan. Don Allah yɗan'uwa□□□□□□ idan ba da gaske kike yi ba kar mu ɓata ma juna lokaci.*

"Ina saurarenki."

Ya faɗa mata da fusata a muryarsa, fuskarshi a ɗaure tamau. Ganin ta ƙi magana, ta duƙar da kanta ƙasa tana ta rusa kuka.

Daƙyar ta iya sassauta kukan da take yi, idanunta na kallon ƙasa kamar wacce ke gaban surukinta. A hankali ta fara magana

"Tabbas na biya kuɗi don ayi aikin da za'a salamta Fareeda. Amma wallahi ni ban ce ayi aikin da za ka kasa kusantar Fareeda ba. Don girman Allah..."

"Idan kika sake haɗa ni da girman Allah sai na zubar miki da haƙora. Za ki tafi kai tsaye kiyi min bayani dalla-dalla na abinda ya faru ko sai na miki wani mugun shaƙa da zai sa ki fara jiyo ƙamshin mutuwa?"

Ya katse ta da faɗin haka cikin tsawa.

Ta sani Mukhtar ya daɗe da wuce saninta. Duk abinda ya ce zai aikata tabbas sai ya aikata shi. Jikinta na rawa ta buɗe baki za ta cigaba da magana ya sake katse ta a karo na biyu

"Sauka ƙasa ki zauna."

Ya faɗa cikin gadara da iko.

Ita da gadon kwanciyarta haka ta sauka ƙasa ta zauna kan dandaryar tiles tana fuskantarsa. Kamar baiwa a gaban ubangidanta.

Nishi yake ja a fusace yana kallonta. Zuciyarsa cike da wani irin takaici da baƙin cikin da ko kusa baki bazai iya baiyanawa ba.

"Wani tsinannen mai magani ne yayi miki wannan aikin?"

Da rawar jiki ta buɗe bakinta ta fara faɗa mishi tun farkon yadda al'amarin ya kasance.

Maman Murad wata tsohuwar mai aikatau ce da Fatima tayi tun tana da cikin Ummee. Daga bisani zamansu baiyi tsawo ba bayan haihuwar Ummee, saboda su biyun da mun gamu ne da mun dace. Maman Murad ɗan banzan ƙwaɗayi da roƙo, ita kuma Fatima balaɣaɣɣen rowa da wayau. Ko da tafiyar ta ɓaɓe lokaci bayan lokaci Maman Murad tana kai ma Fatima ziyara. Haifaffiyar garin Gusau ce a jihar zamfara, amma tana zaune a hayin rigasa da ɣaɣanta da mijinta.

Wata rana ta kawo ma Fatima ziyara sai ta cimma Ramlah a gidan, ta kawo ma Fatima wasu magunguna, a gabanta kuma suke ta maganar maganin ba tare da tunanin ita da take zaune gefe ɗaya kan kafet ba. Ko da Ramlah ta tafi, sai Maman Murad ta gyara zama ta ce ma Fatima

"Hajiya Fatima, ni kuwa na ce da irin waɗannan magungunan da ake kawo miki na ƙila wa ƙala me zai hana in haɗa ki da Kawuna ki biya shi kuɗi ƙalilan yayi miki aikin salamta kishiya?"

"Ban gane ba. Miye kuma salamta kishiya?"

Fatima ta tambayeta da mamaki sosai a fuskarta.

Ko da Maman Murad tayi ma Fatima bayanin abinda kalmar take nufi, ta kuma kira ƙanin mamanta wanda yake aikin a waya ya ƙara yi ma Fatima cikakken bayanin yadda aikin yake, da irin nasarar da mace take samu a gidan miji idan aka yi ma abokiyar zamanta irin wannan aikin. Jikinta na rawa ta ɗauko dubu ashirin ta damƙa ma Maman Murad. Dubu goma aka ce mata kuɗin aikin, amma saboda son ayi mata zazzafan aiki yasa ta bada dubu ashirin.

Duk da zuciyarta na ƙila wa ƙalan idan aikin zai tabbata kamar yadda Maman Murad da kawunta suka faɗa, amma tana fatan ko ɗan yaya ne aikin ya ci. Babban burinta a duniya shi ne tasha gaban Fareeda ta ko wane ɓangare a zaman gidan Mukhtar.

Za ta so ganin yadda Fareeda za ta wulaƙanta a gurin Mukhtar. Shi yasa ba ta jin ƙyashin kashe ko nawa ne wajen siyan maganin da aka tabbatar mata da asiri aka haɗa shi.

Bayan kwana uku Maman Murad ta sake komawa gidan, ta tabbatar mata aikin salamta kishiya angama. Bayan aure ta zuba ido tasha kallon abinda zai faru. Saboda tsananin farin ciki kyautar dubu biyar ta ba Maman Murad.

Bayan bikinta ganin babu wani canji na rashin daɗi tsakanin Mukhtar da Fareeda sai tayi tsammanin duk magungunan da tayi asarar kuɗinta tayi. Bata san aikin ya ci ba sai da Allah ya matsi bakin Mukhtar ya faɗa mata shi fa baya iya kusantar Fareeda.

A lokacin tayi mamaki ƙwarai, domin ba irin aikin da aka ce za'a yi mata ba kenan. Amma da yake ita ɗin mai bala'in wayau ce da iya samar ma kanta mafita cikin sauri nan take ta shirya ma Fareeda gadar zare, shi kuma ya hau ya zauna daram. Tonuwar asirin maganar cikin ƙanƙanin lokaci haka abu ne da bata taɓa tsammani ba.

Ƙara sunkuyar da kai ƙasa tayi bayan ta gama faɗa mishi duk abinda ya faru.

Mukhtar kallonta yake babu ko ƙyafta idanu. Zuciyarsa cike da tsoro da mamakin halayen yaryan Adam. Kiyi tarayya da ƙawa zuciyarki ɗaya ashe ita ko kaɗan ba ta ƙaunarki ba ta ƙaunar ci gabanki. Ya kasa haƙuri sai da ya ce

"Fatima, ko dai akwai wani abu ne da Fareeda ta taɓa miki na mugunta tun kuna yara wanda har yanzu kike riƙe da shi a zuciyarki?"

"Babu komai. Wallahi Allah bata taɓa min komai na mugunta ba. Alkhairi ne tsakanina da ita..."

"Dalla rufe min baki algunguma. Ita kaɗai ke nufinki da alkhairi. Me yasa ke ba kya ƙaunarta?"

Ɗif tayi, ta kasa cewa komai. Sai mutsu-mutsu take yi tana ƙara sunkuyar da kanta ƙasa kamar wacce tayi ƙarya a gaban sarki.

"Ki zauna anan ƙasa har a kira sallar asubah. Ko yunƙurin miɕewa kika yi sai na miki wani hamɓari da zai sa ki faɗi ki karye, ki zubar da haƙora, ki fasa baki, da bala'in ƙarfi zan tokareki ta yadda zan tabbatar kin ƙarasa gaban tsohon madubinki kin fasa kai. Muguwa kawai."

Ya faɗa mata maganganun da wani fitinannen haushinta a fuska da muryarsa. Ƙaƙƙarfan ƙwafa yayi, yaja tsaki haɗe da galla mata harara.

Kwanciya yayi kan gadon ya juya mata baya, zuciyarsa sai tuƙuƙi yake yi, ko kallonta ba ya son yi.

Haka ta zauna a watangare tana kallonsa yana kwance, ga gajiyar kusan kwana ana harraƙawa, ga wannan fitinannen tashin hankali da Mukhtar ya zo mata da shi bagatatan. Ga wani bala'in fitsari da ya riɕe mararta kam! Amma saboda tsananin tsoron kar ta motsa ya ce ya sake ta ko numfashi a hankali take saukewa. Kwatsam, Allah ya taimaketa ladanin unguwarsu ya kwaɗa kiran sallar asubahi.

Addu'a take tayi a zuciyarta kan Allah yasa Mukhtar baiyi barci ba, ganin ko ƙwaƙƙwaran motsi ba ya yi. Ana gama kiran sallar sai taga ya yunƙura ya tashi zaune, ya miɕe tsaye zai wuce banɗaki. Da sauri ta janye yatsun hannunta na hagu da yake ƙasa ganin yana ƙoƙarin take ta.

Bayan ya gama laƙaiɕaita a banɗaki ya ɗauro alwala ya fito. A gurguje ya shirya saboda yana so ya sallaci raka'atanil fijr kafin a tayar da sallar asubahi. Ya kama hanya zai fice daga ɗakin ta bishi da kallo, idanunta ciccike da hawaye, tana so ta roɕe shi zuwa bayi tai fitsari tana tsoron kalmar da zai fito daga bakinsa.

"Kiyi sallah kafin in dawo. Ki tabbatar kin shirya zuwa gidan tsinanniyar matar nan."

Ya faɗa mata haka yana gaf da ficewa.

Da gudun gaske ta faɗa banɗaki, ko da ta sauke nauyin mararta maimakon ta ɗauro alwala kamar yadda ya umarceta sai ta fito, wayarta da ke ajiye gaban madubi ta ɗauka jikinta na rawa ta lalubo lambar Maman Murad ta danna mata kira. Idanu ta bubbuɗe ta ɗora hannun hagu akai ta fara hawaye jin kamfani na sanar da ita wayar a kashe take.

Cikin daƙiƙu ƙalilan ta kira fiye da adadin da ita kanta baza ta ƙididdige ba, amma duk amsa ɗaya take samu, lambar da take kira a kashe take, bata ankara ba sai jin sallame sallar asubah tayi a masallaci. Da sauri ta aje wayar, a guje ta sake faɗawa banɗaki ta ɗauro alwala.

Tana raka'ar ƙarshe Mukhtar ya shiga cikin ɗakin. Wani irin faɗi da gabanta yayi sai da ta runtse idanunta, ta cije baki. Nan take karatun sallar ya ɓace mata, haka ta ƙarasa ibadar a daburce har ta sallame. Ta daɗe hannayenta a sama tans roƙon Allah ya rufa mata asiri, Allah ya taushi zuciyar Mukhtar a wannan yini duk abinda zai je ya zo kar Allah ya bashi ikon sakinta.

"Ina kwana Haskenah?"

Ta faɗa bayan ta shafa addu'ar tana kallonshi da raunanan idanunta da ƙarara suke bayyana irin tashin hankalin da zuciyarta take ciki.

Kamar mai gadi, haka yake tsaye ƙiƙam a bakin ƙofa yana jiran ta idar. Ko da ta gaishe shi maimakon ya amsa kawar da kansa yayi, hannayensa biyu naɗe a bayansa ya fara takawa zuwa cikin ɗakin har inda take zaune kan sallaya.

"Fatima?"

Ya kira sunanta da wata garjejiyar murya.

"Na'am Haske..."

"Daga yau idan kika sake ce min Haskenki sai na miki ɓarin makauniyar da zai yi sanadiyar zamowarki mai wawulo. Kina ji na?"

"Na ji Aban Twince, Allah ya huci zuciyarka."

Ta faɗa a sanyaye.

"Tashi mu tafi."

Yana faɗin haka ya fice daga ɗakin.

Haka nan ba don zuciyarta na so ba ta bi bayanshi, gwuiyawunta a sanyaye kamar wacce ta kwana tana zawo. Da duku-dukun asubahi haka suka shiga mota, ya fige ta a guje suka bar gidan.

Wani irin tuƙi Mukhtar ke yi na gagari, da yake kuma da duku-duku ne babu cinkoson motoci haka yake ta ƙure malejin mota ba tare da ya fuskanci matsalar go-slow ba. Babu mai cewa uffan a tsakaninsu, Fatima kwantar da kai tayi a jikin ƙofa tana ta jan duk addu'ar da tazo cikin zuciyarta.

"A wace unguwa take?"

Ya tambayeta sa'adda suka shiga hayin rigasa.

"Maƙera"

Ta amsa a taƙaice.

Ko da suka shiga cikin layin maƙera daƙyar ta gane gidan. Sau uku tana nuna mishi layuka mabanbanta, sai sun shiga ta gama waige da dube-dube sannan ta ce mishi ba nan bane. A ƙarshe dai Allah yasa ta nuna mishi wani gida ta bashi tabbacin nan ne gidan Maman Murad.

"Kin tabbatar?"

Ya tambayeta yana ƙure ta da kallo.

"Eh! Na tabbata, nan ne. Bari in je inyi sallama da ita."

Har ta kama hannun ƙofar motar za ta buɗe ta fita ya dawo da ita ta hanyar janye hannunta. A tsorace ta waiga tana kallonshi da alamar tambaya a fuskarta.

Wani baƙin gilas da yake ajiye a gaban motar ya ɗauka ya ƙwama a idanunsa.

"Kin ga na miki kama da ɗan'iska wanda bai san abinda yake yi bane?"

"A'a!"

"To Idan ba haka bane ta ya kike tunanin zan barki ki shiga bayan tun ɗazu ina kallon yadda kike ta danna ma lambar matar kira? Ni da kaina zan je inyi sallama da ita. Fita muje."

Jiki babu ƙwari ta buɗe ƙofar ta fita, yabi bayanta bayan ya kulle motar. Ko da suka isa ƙofar gidan a gefe ta tsaya, shi kuma ya matsa ya ɗauki wani ƙaton dutse ya fara ƙwanƙwasa ƙyauren gidan da yake a kulle.

Bai ɗauki minti ɗaya ba ya ji ana ƙoƙarin zare sakata ta ciki. Don haka yaja gefe ya tsaya, hannayensa naɗe a ƙirji, fuskarnan a ɗaure tamau, kamar bai taɓa sanin wata aba wai ita dariya ba.

"Malam lafiya da sassafennan kake mana irin wannan bugun? wa kake nema?"

Wanda ya buɗe gidan ya tambayi Mukhtar.

"Maman Murad muke nema. Tana ciki? Allah yasa bata nan ta tafi garinsu."

Fatima tayi maganar a daburce cikin rawan baki.

Jin abinda Fatima ta ce yasa Mukhtar dafe bangon gidan yana kallonta da mamaki, sai kuma ya ɗanyi murmushi, zuciyarsa cike da tunanin irin tsiyar da zai shuka ma Fatima idan ba'a samu wannan matar a gida ba.

Shi kuwa wannan mutumi da ya buɗe gidan kallon ƙurilla yake ma Fatima, irin kallon nan na anya wannan lafiyarta ƙalau? Ta faɗi ga wacce suka zo gurinta, amma kuma take fatan ace matar ba ta nan?

"Maman Murad tana nan, jiya da daddare ta dawo daga garinsu. Amma ba ni da hurumin da zanyi muku sallama da ita kai tsaye, bari in kira muku mijinta sai ku nemi izinin ganinta daga gare shi."

Ya amsa musu bayan yayi tunanin lafiyar Fatima ko akasinta ba abinda ya shafe shi bane.

Cikin gidan ya koma. Minti biyar tsakani wani dattijo ya fito ƙofar gidan. Fuskarsa cike da kamala, hannu ya miƙa ma Mukhtar suka yi musabaha. Ko da Mukhtar ya faɗa mishi sun zo ganin mai ɗakinshi ne ɗan jim yayi, sai kuma ya ce

"Malam Muntari Allah yasa dai lafiya?"

"Lafiya ƙalau Baba. Wata harƙalla ce ta shiga tsakaninta da wannan matar a kwanakin baya. To an samu matsala, shi ne muka zo takanas ta kano don a warwara wannan matsala cikin maslaha ba tare da tashin-tashina ba. Amma fa idan ita mai ɗakinka ta bayar da haɗin kai."

Uzuri dattijon ya nema a gurin Mukhtar, ya shiga cikin gidan, can sai ga shi ya sake fitowa, a bayansa Maman Murad ce. Fuskarta dagaje-dagaje da yawun barci, da alamun ko sallar asubah bata samu gabatarwa ba saboda yadda take ta sakin hamma tana mutsuttsuke idanu, alamu ne na wacce aka taso ta daga nannauyan barci.

A ƙyamace Mukhtar yake kallonta, sai kuma ya mayar da hankalinsa kan Fatima da ta raɓe jikin bango ƙirjinta na bugun tara-tara ya ce

"Ita ce wannan?"

Yai mata tambayar yana nuna Maman Murad da yatsarsa manuniya.

A kasale ta ɗaga kai alamar eh, ita ce.

Sai a lokacin idanun Maman Murad ya faɗa cikin na Fatima, faɗaɗa fuskarta da fara'a tayi ta ce

"Maman Ummee, ke ce yau a gidan namu? Bismillah shigo mana? Baban Murad baka gane ta ba? Maman Ummee ce fa wacce na yi ma aiki shekarun baya a unguwar rimi, baƙin alkhairi ne ba na tsiya b..."

"Idan kin so, shi ne za mu zame miki baƙin alkhairi. Idan baki so ba kuwa akasin haka ne zai kasance."

Mukhtar ya katse ta da sauri jin yadda take ta zuba tana cika mishi kunne da zantukan da bai ɗauke su a komai ba sai shirme. Kafin ta ce komai ya cigaba da cewa

"Tunda duk kun gane juna to Alhamdulillah! Ke baiwar Allah, kin tuna aikin da ƙanin mamanki yayi ma wannan matar da kike kira Maman Ummee ko? Ba komai ne ya kawo mu a daidai wannan lokacin ba sai don sanin ta inda aka hau ta nan ake sauka."

"Ban gane ba."

Maman Murad ta faɗa tana yamutsa fuska, bayan ta haɗe girar sama da ƙasa.

Gilashin idanunsa ya cire ya riƙe a hannu, ya sake haɗe fuska sosai, babu alamun rahama ko ƙanƙani a tattare da shi.

"Za ki gane yanzunnan. Ta faɗa min, a wancan lokacin ta waya kawai kika kira kawunki suka gama maganar mugun aikin zaluncin da take so ayi mata kan Uwargidana. To a yanzu dai wannan aikin ba ta buƙatarshi, ni ne mijinta. Don haka ina umartarki ki kira Kawunki yanzunnan ki faɗa mishi ya warware wannan ƙullin da yayi..."

"Taɓɗijan! Wasa ma kenan! Ai wannan aikin aka yi shi anyi kenan. Makarinsa kawai ka saki ita waccan matar ne ka zauna da Maman Ummee ita kaɗai, ina tabbatar maka ko wata matar ka auro haka za ka ji ta Salam, mahaɗar jin daɗi da gamsuwar buƙatarka na auratayya an haɗa shi da Maman Ummee ne..."

Maganarta ya ɗauke ɗif ne, sanadiyyar wani ɓarin makauniyar mari da Mukhtar ya sauke mata ba zato ba tsammani. Ɗif ta ɗauke wuta, babu abinda take ji a

kunnuwanta sai wani irin wiiiiiiiiii kamar jiniyar yʻan sanda. A idanuwanta kuwa babu abinda take gani sai wasu taurari masu bala'in haske da ƙyalƙyali suna shige da fice a jikin junansu.

"Baba kayi haƙuri na ɗora hannu kan iyalinka Na rantse da girman Allah idan matarka da ɗan'uwanta basu warware wannan mummunan asirin da suka yi tsakanina da matata ba hukuma ce za ta shiga tsakaninmu. Daga nan state CID za mu wuce kai tsaye, tun ɗazu na kira babban abokina da yake can na faɗa mishi abinda yake faruwa. Yanzu haka kiran wayata kawai yake jira, zai turo mota yanzunnan a tafi da ita. Idan mun je can aka je har can garinsu aka ɗauko ɗan'uwan nata luguden mintuna goma ya isa su samo hanyar warware wannan ƙullin da suka yi."

"Kayi hakuri Malam Muntari, abin duk bai kai haka ba..."

Ihun da Maman Murad ta ƙwalla cikin azaba shi ya ankarar da su ta dawo cikin hankalinta. Ta buɗe baki za ta sake ƙwallah ihu a gigice da sauri Baban Murad ya janyo ta ya rufe mata baki.

Cikin gidan ya ja ta, bayan yayi ma su Mukhtar umarnin su bi bayanshi zuwa cikin gidan. Duk da gidan haya ne jin irin gaggarumin maganar da ke tafe da su Mukhtar shiga da su cikin gidan shi yafi alkhairi da tsayuwarsu a waje. Ga unguwar irin ghetto ɗinnan ne, duk da safiya ce mutane masu wucewa har sun fara tsayuwa ganin kafcecen marin da aka saukewa Maman Murad.

A tsakar gidanma mata da maza ne tsaitsaye suna hum-hum-humm!

"Baban Murad lafiya kuwa?"

Biyu daga cikin mutanen gidan suka haɗa baki wurin tambayarsa.

"Lafiya ƙalau."

Ya amsa a gundure. Ya bankaɗa labulen ɗakinsu ya shige ciki, su Mukhtar suka bi bayansa. Maman Murad kwance a jikinsa ranga-ranga kamar sumammiya.

Ba fa anan naso tsayawa ba Wlh😩😩😫😫 caji na 3%, kar in tsaya iyayin ƙara yawanshi wayar ta ɗauke. Idan na samu wadataccen caji za ku ji ni gobe, idan baku ji ni ba a cigaba da min uzuri masu karatu□□□□□□□□□. Customers ɗina masu kira na su sayi data I loviyu wujiga-wujiga😘😘😘😘

Assalamualaikum Barkanmu da wannan lokacin AUNTY ZEE TAKU CE ,Ina uwar gida Amarya da yanmata albishir gareku

BONONZA; BONONZA;BONONZA;

Nazo maku da SAHIHIN MAGANIN CIRE TUMBI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI,KINCI GAYU ANA TAMBAYARKI YAUSHE ZAKI HAIHU TUMBI YA HANAKI ADO DA KWALLIYA SHA KURUMINKI NAZO MAKI DA MAGANI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI ZAN DANDANA MAKU SHI AKAN RABIN KUDINSHI DAGA NAN ZUWA SATI DAYA 7K DUK ROBA DAYA KI BIYA 3500 KI MALLAKI NAKI NAN DA SATI DAYA ZAI KOMA 7K

MAGANIN BREAST WANDA ZAICIKO MAKI DA TUWON NONO DAN ALLAH KIJARABA ZAKIZO KINA GODIYA DAN DUK WADDA TA GWADA SAITA DAWO MANYAN MATA SUKE GYARA KAMAR YANDA KUKASANI 8K YAKE ZANKARA TALLATA MAKU SHI KI BIYA 4K KI MALLAKI NAKI

KI BIYA TA WANNAN ACCOUNT DIN KITURA MAN SHAIDAR BIYA

3968303018

ZAINAB SHU AIBU

FCMB

08162859027

RABON AYI

30

©Fareeda Abdallah

_Yʻar'uwa ki tuna, kafin saukar da ko wace irin cuta, sai da aka saukar da maganinta. Don kinyi magani da yawa baki dace ba ba shi zai sa ki yanke tsammani daga samun waraka ba. Ki gwada maganin da muke karɓa ma al'ummar Annabi SAW, wata ƙila warakarki a wannan maganin yake baki sani ba. Haihuwa kike nema? Baki taɓa yi bane ko kuwa jinkiri ne kike samu tsakanin haihuwar? Sanadiyyar planning ne kika samu jinkirin ko kuwa sanyi ne yake damunki ko haka kawai? Matsalar rashin haihuwar daga mijinki yake? Muna da ingantaccen magani garanti wanda aka gwada muka tabbatar da aikinsa, in Allah ya yarda ko me ya shafi mahaifar mace da mararta wanda ya hana ta haihuwa in dai tayi amfani da saiwoyin maganinmu za ta samu biyan buƙata da yaddar Allah. Matsalar mace ko namiji 2k ne.

Akwai ƙullin maganin da muke sayar da shi 500, in dai matsala ta shafi nonon mace da yaddar Allah za ki samu waraka. Mai ciki, mai shayarwa, mare shayarwa duk za su iya amfani da wannan magani. Ko da matsalar ciwon daji ne da ya shafi nono in sha Allah za ki sami waraka sanadiyyar amfani da wannan magani. Akwai garin maganin sanyi da za ki haɗa a cikin yaji, shi ma 500. Akwai ingantaccen maganin sanyi da za ki saya muku ke da Oga, 2k ne. In Allah ya yarda za ki sha mamakin yadda lafiya zai wadace ku ke da Oga, za ki ga yadda za ku dawo kamar sabbin amaren da suke mararin junansu😍. *Akwai ingantaccen haɗin magani na gyaran nono wanda ni Fareeda Abdallah nake sayarwa, bokiti 1litter 2500, yʻar'uwa in dai za ki juri dama kunun garin maganin safe da dare, za kiga yadda ba cikowar nono kaɗai ba, hatta fatar jikinki sai ta canza, za kiyi kuɓul-kuɓul😍, sa'annan ni'ima bazai taɓa yanke miki ba in Allah ya yarda saboda irin haɗe-haɗen da ke cikin wannan magani. Ga duk mai buƙatar ɗaya daga cikin maganinnan da gaske ta tuntuɓeni ta whatsapp a 07039080978, idan kira ne a kira ni ta 09077591726. Don Allah yʻan'uwa□□□□□□idan ba da gaske kike yi ba kar mu ɓata ma juna lokaci.*

Ko da suka shiga cikin ɗakin da yake falle ɗaya, sai suka tarar da kujeran zama mazaunin mutum uku ita kaɗai ce a ajiye ta bakin ƙofa.

Can daga cikin ɗakin gado ne, a gefe guda da sauran tarkacen kayayyaki. Kan kujera Baban Murad yayi musu umarnin zama, shi kuma ya ƙarasa gefen gado ya zaunar da Maman Murad. Jikinsa na rawa ya ƙarasa kusa da fanka yɗar tsaye ya kunna ya matsa da fankar kusa da Maman Murad da tayi wata dagwalooo kamar wata wawuya ta ƙura ma guri ɗaya idanu.

Fatima ce ta ɗan ɗofana mazaunanta kan kujerar, kamar ace ƙyat ta zura a guje. Shi kuwa Mukhtar tsaye yayi a bakin ƙofa ya harde hannaye a ƙirji, fuskarsa a ɗaure tam yana kallon abinda dattijon ke yi.

"Maryam, Maryam, kina ji na?"

Baban Murad ya tambayi Maman Murad bayan ya tsuguna a gabanta, ya riƙe hannayenta biyu cikin nashi.

Tsawon wasu daƙiƙu kamar baza ta motsa ba. Sai kuma ta sauke ajiyar zuciya a zabure ta damƙe hannayen mijinta da ƙarfi. Idanu warwaje take kallonshi, sai kuma ta kalli Mukhtar a tsorace ta nuna shi da yatsa manuniya tana surutai

"Baban Murad kana ganin ya kafta min mari da hannunsa mai kama da dutse baka rama min ba? A gabanka za'a ci zarafin uwar yɗayɗanka baza ka ɗauki mataki ba? Ashe haka soyayyar da kake ikirarin yi min..."

"Maryam! Saurara don Allah! Ki nutsu ki fahimci abinda zan faɗa miki. Kinga wannan mutumin ba da wasa yazo ba. A matsayina na mijinki, ina mai baki shawara tun kafin hukuma su shigo cikin zancennan ki kira Kawu Bello yanzu ki faɗa mishi ya warware aikinnan."

"Hukuma kuma Malam? Me kuma ya kawo hukuma a cikin wannan maganar?"

Ta faɗa jikinta a sanyaye.

"Kwarai kuwa hukuma. Ashe ɗazu baki ji abinda na ce ba kenan? Ke na ga ma kina neman ɓata min lokaci, bari in kira kawai azo a tattara min ke zuwa can, shi ma kawun naki duk inda yake a ƙasar nan cikin ƙanƙanin lokaci za'a damƙo shi"

Har ya fara daddana wayarsa da saurin gaske Maman Murad ta ce

"Dakata Alhaji, Allah ya huci zuciyarka. Don girman Allah maganar ba sai ta je gaba ba. Yanzu zan kira Kawun nawa."

A duniya idan akwai abinda Maman Murad take tsoro bai wuce harkar hukuma ba.

Duk baki da tsananin bala'i irin nata ko fadar mai unguwa aka kaita ta dinga rusa kuka kenan tana bayar da hakuri. Ko da kuwa ita ce da gaskiya, balle ace gurin yɗansanda? ba ta fatan ko maƙiyinta a jarabceshi da zuwa gurin yɗansanda.

Duk da kawun nata ya sha sanar da ita irin wannan aikin bai da makari. Haka nan ta ɗauki wayarta ta kunna, ta lalubo lambarsa ta danna mishi kira, a amsa kuwwa ta saka wayar don Mukhtar ya ji da kunnensa abinda kawunta zai faɗa.

Ringing ɗaya, biyu, ya ɗaga daga can ɓangaren. Duk da jiya ta bar gida, amma ba ya ganin kiranta yaƙi ɗagawa ko me yake yi, saboda ita ɗin abokiyar cin mushensa ce. Hajiyoyi take amso ayyukansu daga birni tana kai mishi yana samun na cin abinci.

"Assalamu alaikum! Mariya? Daɗa in ce kau kin koma gida lahiya? Wallah tun jiya nika biɗat nambarki ba ni samu, nicce ko shigiyat abinga ta sadarwar garinmu tayi mana tsiyat da ta saba..."

"Kawu kana ji na?"

Tayi gaggawar katse shi sanin da tayi shi ɗin uban surutu ne. Yana amsa yana jin ta ta cigaba da cewa

"Ina wannan matar Maman Ummee da nicce maka ita uwarɗakina ce? Har nihhaɗaka da ita ga waya kun kayi magana ta ƙara whaɗi maka yadda taka biɗar aikin da za'ayi ga kishiyarta ya kasance. Ka tuna ta?"

"Kwarai kuwa na tuna ta Mariya. Ta ina zan manta wannan muguwar mata da tacce tana biɗat inyi gagarumin aikin da kishiyatta za tayi muguwar wulaƙanta irin wulaƙancin da bata taɓa ganin wata ɣa mace tayi a duniya ba. Ko ba ita kika magana ba? Wacce har tacce sunanta Fatima kau? sunan mijin da za ta aura Mutari, sunan uwargidan nata Fidda'u take ko Fareeda? Na dai manta. Mi shinka faru? Ko wani aikin taka biɗar a sake yi mata? Kin san dai ko ga wancan lokaci na whaɗi miki ita wannan kishiyar tata ba ta taɓuwa sai wani ikon Allah. Macece mai yawan Ibada da addu'a, ko aikin salamta kasa yi niyyi ga ita, daɗa shi nassa nayi aikin langwai ga mijinta yadda ko kusa ba shi iya kusantar ita matar tasa..."

"Kawu ka saurara mana."

Maman Murad ta katse shi, idanunta ciccike da hawaye. Tana kallon fuskar wayarta tana satar kallon Mukhtar da izuwa yanzu sai girgiza ƙafafu yake yi, tana ganin yadda yake ta dunƙule hannu a fusace kamar zai kai naushi sai kuma ya buɗe hannun.

"Kawu, ita wannan Fatima da ta baka aikin, Ga ta zaune a gefe na ita da mijinta wai ba ta buƙatar aikin. Don Allah kawu ka taimaka min, ka warware wagga aiki da kayyi kan mijinta Mutari, ka ganshi nan tsaye bisa kaina riƙe da bindiga mai jigida a hannunsa. Ɗazu da ya kafta min mari ina rantse maka da Allah tsawon lokaci nikkasa tantance shin a duniya nike ko har na mace ne an whara min hisabi ga munanan ayyukan da niyyi. Daɗa Kawu ashe shi mijinta soja ne, ya ce idan baka warware wagga aiki ba zai kashe ni sannan ya zo har nan garinmu ya kashe ka da duk iyalinka. Daɗa ga Baban Murad yayi maka ƙarin bayani. Don girman Allah kawu ka taimaka min."

Hannunta na rawa ta miƙa ma mijinta wayar. Wasu zafafan hawaye suka gangaro daga idanunta, ta kalli Fatima da duk ita ce ta janyo mata wannan bala'in tana zaman zamanta ta galla mata wata matsiyar harara, har yanzu ɓangaren kumatunta da Mukhtar ya mara bai daina raɗaɗi ba.

Fatima dai bata san tana yi ba, ta rasa inda za ta tsoma ranta ne. Tunda ta ji Malam Bello ya faɗi irin aikin da tace a yi kan Fareeda bata san sa'adda ta sauka daga kan kujerar da take ɗofane ba, ta tsuguna a dandaryar sumintin tsakar ɗakin kamar mai jin kashi.

Hannunta na hagu ɗore a tsakiyar kanta. Idanunta a rufe amma hawaye ne ke tseren gudu a kumatunta. Zuciyarta cike da wani iri da-na sani mai bala'in yawan da

ko kusa baki bazai iya baiyanawa ba. Bata taɓa tsammanin lamarin zai juye haka ba, bata taɓa zaton Malam Bello kawun maman Murad mutum ne mai masifaffen surutu har haka ba. Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Ita dai tata ta ƙare, ta san yau babu abinda zai hana Mukhtar ya lakaɗa mata tsinannen duka sa'annan ya sake ta saki uku!!

Baban Murad ya san halin Malam Bello da taurin kan riƙe amanar aikin bokancin da yake yi. Don haka ya cigaba da ɗorawa kan inda matarsa ta tsaya, sosai ya cigaba da tsoratar da Kawu bello ta hanyar tabbatar masa lallai fa ga Mariya nan an rutsa kanta da bindiga mai jigida. Matserar rayuwarta kawai a warware wannan aikin ne.

"Daɗa amma wannan mata Fatima anyi walakantacciya. Ita ta san mijinta soji ne tammiƙo sunanshi garen da cewa in mata aiki akan matarshi? Ni wha ko lokacin na ga Mutarin mai bala'in zafin zuciya ne. Ni Bello na ga ta kaina, yanzu ya zanyi? ta ina zan whara aikin warware wagga aiki da ban taɓa yi na kunce ba..."

"Au!!! Don abu kaza-kazanka baka san ta inda za ka fara warware aikin ba ko?"

Mukhtar yayi maganar a fusace cikin tsawa bayan ya lailayo wata ƙatuwar ashariya ya maka ma malamin. Da takalmin ƙafarsa ya taka har inda mijin Maman Murad yake ya fincike wayar a hannunsa.

"Wallahi, Tallahi, Na rantse da girman Allah yinin yau da gobe kawai kake da. A daren gobe zan tabbatar ka warware aikin ko baka warware ba? Idan ka cika ɗan halas kar ka warware, za kaga yadda safiyar jibi ba ƙauyenku na Maru kaɗai ba jihar zamfara gaba ɗaya za ta san ka taɓo musu tsuliyar dodo."

Cikin fushi yayi hurgi da wayar ta maku da bango, ya aika ma Maman Murad wani fusataccen kallo kamar mai niyyar haɗiyeta, da saurin gaske ta sunkuyar da kanta ƙasa, a tsorace, jikinta sai makyarkyata yake yi.

Juyawa yayi zuwa inda Fatima ke tsugune ya damƙi kafaɗarta guda ya ɗaga ta tsaye

"Wuce mu tafi."

Yayi mata maganar da tsawa.

Har sun isa ƙofar fita daga ɗakin sai ya waiga ya kalli matar da mijin da suka yi tsuru-tsuru, bayyanannen tashin hankali da tsoro ƙarara a fuskarsu.

Wani taƙaitaccen murmushi da ƙarara yake nuna na mugunta ne ya sakar ma Maman Murad.

"Idan kin so, kina iya gudu daga yau zuwa gobe. Hhhh! Don Allah ina so ki gwada haka. A lokacin ne za ki gane asalin wanene Mutarin da kuke kira, don Allah kar ki saka mugun Kawunki ya warware ƙullin da yayi min ki gane. Muddin kika bari na sake dawowa ɗakinnan..."

Yayi ƙwafa, ya karkaɗa mata ƴar yatsarsa manuniya. Ya sake ƙwafa a karo na biyu, ya girgiza kai sannan ya finciki Fatima da saurin gaske suka fice daga ɗakin.

Saboda yadda hankalinsa yake a ɗugunzume ko damar saka takalmi bai ba Fatima ba. A haka yaja hannunta suka ratsa cinciron matan gidan da suke tsaye cirko-cirko suka fice daga gidan. Bai sake hannun Fatima ba sai da ya buɗe ƙofar ɓangaren mai zaman banza ya hurga ta ciki ya rufe ƙofar da sauri.

A haukace ya figi motar suka bar unguwar, ƙiris ya rage ya kaɗe wasu yara uku da suka zo wucewa Allah ya taimaka ya ci burki da ƙarfin gaske, su kuwa yaran da bala'in guda suka ƙarasa wucewa da karaɗin ihu irin na waɗanda suka tsallake rijiya da baya.

A tsorace Fatima ta zaro idanu tana kallon abinda ya kusa faruwa. Ganin Allah ya tsare yasa ta sauke ajiyar zuciya, ta kalle shi da raunanan idanunta da har lokacin ruwan hawaye basu daina tsiyaya ba ta ce

"Has... Aban Twince don Allah..."

"Idan kika sake min magana a cikin motar nan na rantse da Allah zan baki mamaki."

Ya katse ta da faɗin haka a fusace.

Gudu ya cigaba da shananawa, ita dai Fatima tun tana hawaye bata san sa'adda ta jingina kanta da kujeran mota ta fara gyangyaɗi ba.

"Sauka"

Ta ji muryarsa yana faɗin haka kamar a mafarki.

Ko da ta ɗaga idanunta da tunanin barcinta yayi nisa har sun isa gida bata sani ba gabanta ne ya rugurguje ya faɗi. Ba gidanshi ya kai ta ba, gidan ƙanwar mahaifitarta ce in da tayi taron bikinsu. Hankalinta ne ya ƙara ɗugunzuma, tun kafin tayi magana hawayen da ta samu suka tsaya daƙyar sanadiyyar gyangyaɗin da ta fara yi suka sake ɓalle mata. Ta ma manta kashedin da ya mata na kar ta sake mishi magana a cikin motar.

"Mukhtar..."

"Ki sauka min a mota. Ki shiga gidanku. Kije ki ƙaro tarbiyya da ilimin yadda ake zama da mutane tsakani da Allah a ƙauna ce su da zuciya ɗaya. Idan kin gyara, ko nan da wata tara ne da yiwuwar in duba in gani, kila, kila, kila in iya zama da ke. Amma a yanzu kam bazan iya ba, kina buƙatar saiti na gaban iyaye Fatima, kin shallake duk yadda na tsammace ki."

Da kanshi ya zura hannu ta jikinta ya buɗe mata ƙofar.

"Fita"

Ya sake bata umarni a karo na biyu.

Maganganun Mukhtar sun daskarar da ita, ko motsi ta kasa yi, Sai hawaye da take kamar an buɗe famfo.

"Za ki fita ne ko sai na ja ki da ƙarfi na fitar da ke?"

Ya tambayeta. A ƙarshe dai ƙin fita tayi, shi da kanshi ya zagaya ta inda take zaune ya fitar da ita, ko da ya sake hannunta sai ta tafi taga-taga kamar za ta faɗi yayi kamar bai gani ba. A dole ta koma ta tsaya, tana ji tana gani yaja motarsa a guje yabar unguwar bayan ya baɗa mata ƙura.

Zaman daɓaro, shi ne abinda Fatima tayi a ƙofar gidan Innarta. Zuciyarta cike da tunanin mafita da hanya mai ɓullewa. Ga hawaye har lokacin bai daina zuba a

idanunta ba. Tana cikin wannan halin sai ga Nura ɗan gidan Inna ya fito daga gidan, ya kalli Fatima ya ƙara kallah.

Sai kuma ya kama haɓa cikin mamaki ya ce

"Aunty Fatima lafiya? Me yake faruwa? wa ya rasu? Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un"

Duk yadda yake ta magana hankali tashe yana jijjaga kafaɗarta ta kasa ce mishi uffan! Afujajan ya koma cikin gida don kiran mahaifiyarsu, ko kafin su fito har Fatima ta tare mai mashin ta haye, suna fitowa sai bayanta suka hanga ana ɓanana wuta da ita akan mashin.

"Allah ya kyauta. Ko ma menene za muji daga baya. Yanzu dai kai ka tafi gurin harkokinka. Idan na shiga gida zan kira Yaya (Mahaifiyar Fatima) duk abinda yake akwai zan ji, idan na tashin hankali ne zan kira in sanar da kai."

*****

Mai mashin ɗin da ya ɗauketa bai aje ta ako ina ba sai a ƙofar gidan Hajiyar Muktar, can unguwar dosa. Ta hanga ta hango a daidai wannan gaɓar da take ciki Hajiyarmu ita ce last hope ɗinta. Tunda dai Allah yasa har Mukhtar ya sauke ta bai furta mata kalmar saki ba, to lallai aure tsakaninta da shi mutu ka raba. Indai wannan girman laifin bai sa shi sakinta ba bata ga wani laifi da za tayi mishi a duniya ya sake ta ba.

Haƙuri ta ba mai mashin ɗin ta shiga cikin gidan gurin Hajiyarmu ta amso dubu ɗaya ta kai mishi.

Ko da ta koma cikin gidan da fuska ƙozai-ƙozai sai kallonta Hajiyarmu ke yi. Da ganin fuskar Fatima za'a gane ta sha kuka. Bayan gaisuwa da ya shiga tsakaninsu da yake Hajiyar ba macece mai son shiga abinda ba'a kasa da ita ba sai bata fara tambayar Fatima abinda ke faruwa ba.

Fatima ce ta gaji da mutsu mutsu ta sake muskutawa a inda take zaune. Tayi rau-rau da idanu nan take suka tara tuwan hawaye, ta buɗe baki za tayi magana sai ga Sayyid ya fito daga kicin ɗin Hajiya hannunsa riƙe da ɗan ƙaramin faranti an ɗora soyayyiyar indomie da ƙwai akan farantin. Lokaci ɗaya ƙamshin abinci ya game falon gaba ɗaya.

Lokaci ɗaya zuciyar Fatima ya fara tashi, cikinta ya fara hautsinawa. Ta buɗe baki za tayi magana kawai sai amai ya taho mata. Ai kuwa da bala'in gudu ta miƙe ta shige bayin falon da ta san da zamanshi tun zamanin tana rako Fareeda idan wani abu ya faru a gidan.

"Lafiya kuwa? Me yake damunki haka?"

Hajiyar ta tambayeta da kulawa, ganin irin aman kumallo da tayi sa'anna ta zauna ta dafe kanta da cewar yana mata ciwo kamar zai faɗi.

"Hajiya kaina... kaina... wayyo Allah na..."

Abinda Fatima take iya faɗe kenan tana runtse idanu da cije baki.

Aunty Jimmalo babbar nurse ce a unguwarsu Hajiyarmu. Gida biyu ne tsakaninta da Hajiyar, akwai kyakkyawar mu'amala tsakaninsu. A ƙarshe dai dole ita Hajiya ta kira ta duba Fatima.

Bayan duk wasu gwaje-gwaje da ya kamata ayi a gaggauce sakamako ya nuna Fatima tana da shigar ciki."

Wannan ciki da aka tabbatar ma da Hajiyarmu Fatima tana ɗauke da shi, shi ne abinda ya sanyayar da jikin Hajiyar gaba ɗaya. Ta zauna kan kujera tayi shiru tana jinjina ƙarfin iko irinna Ubangiji.

Wato ƙaƙƙarfan rabo ke a tsakanin Fatima da Mukhtar! Iko sai Allah.

Lokaci bayan lokaci takan tashi daga falon ta leƙa ɗakin da Fatima take kwance tana barci cikin nutsuwa. Awa biyu ta ɗauka cif tana barci kafin ta farka da wani gigitaccen yunwa, daƙyar ta iya wanke baki ta fita falon gurin Hajiya.

Bayan tambayar ya jiki teburin cin abinci Hajiyarmu ta nuna mata da yake ɗauke da kayan tea da dafaffen abinci. Cikin ɗaki Hajiyar ta shige don ta ba Fatiman damar cin abinci a nutse ba tare da takura ba.

RABON AYI

31

©Fareeda Abdallah

_Ƴar'uwa ki tuna, kafin saukar da ko wace irin cuta, sai da aka saukar da maganinta. Don kinyi magani da yawa baki dace ba ba shi zai sa ki yanke tsammani daga samun waraka ba. Ki gwada maganin da muke karɓa ma al'ummar Annabi SAW, wata ƙila warakarki a wannan maganin yake baki sani ba. Haihuwa kike nema? Baki taɓa yi bane ko kuwa jinkiri ne kike samu tsakanin haihuwar? Sanadiyyar planning ne kika samu jinkirin ko kuwa sanyi ne yake damunki ko haka kawai? Matsalar rashin haihuwar daga mijinki yake? Muna da ingantaccen magani garanti wanda aka gwada muka tabbatar da aikinsa, in Allah ya yarda ko me ya shafi mahaifar mace da mararta wanda ya hana ta haihuwa in dai tayi amfani da saiwoyin maganinmu za ta samu biyan buƙata da yaddar Allah. Matsalar mace ko namiji 2k ne.

*Akwai ƙullin maganin da muke sayar da shi 500, in dai matsala ta shafi nonon mace da yaddar Allah za ki samu waraka. Mai ciki, mai shayarwa, mare shayarwa duk za su iya amfani da wannan magani. Ko da matsalar ciwon daji ne da ya shafi nono in sha Allah za ki sami waraka sanadiyyar amfani da wannan magani. Akwai garin maganin sanyi da za ki haɗa a cikin yaji, shi ma 500. Akwai ingantaccen

maganin sanyi da za ki saya muku ke da Oga, 2k ne. In Allah ya yarda za ki sha mamakin yadda lafiya zai wadace ku ke da Oga, za ki ga yadda za ku dawo kamar sabbin amaren da suke mararin junansu😍.* *Akwai ingantaccen haɗin magani na gyaran nono wanda ni Fareeda Abdallah nake sayarwa, bokiti 1litter 2500, yɜar'uwa in dai za ki juri dama kunun garin maganin safe da dare, za kiga yadda ba cikowar nono kaɗai ba, hatta fatar jikinki sai ta canza, za kiyi kuɓul-kuɓul😍, sa'annan ni'ima bazai taɓa yanke miki ba in Allah ya yarda saboda irin haɗe-haɗen da ke cikin wannan magani. Ga duk mai buƙatar ɗaya daga cikin maganinnan da gaske ta tuntuɓeni ta whatsapp a 07039080978, idan kira ne a kira ni ta 09077591726. Don Allah yɜan'uwa□□□□□□idan ba da gaske kike yi ba kar mu ɓata ma juna lokaci.*

Mamaki mai tsanani ne ya lulluɓe shi ganin Fatima kwance kan doguwar kujera a falon Hajiyarmu. Ƙam ya tsaya guri ɗaya yana ɗan murza idanunsa, da tunanin ko tsananin caja mishi kai da take yi ne yasa ta fara yi mishi gizo.

Ganin bata ɓace ba yasa shi tabbatar da Fatima ce a gaske.

"Me ya kawo ki gidannan?"

Ya tambayeta cikin tsawa da ɓacin rai.

A kasale ta miƙe ta zauna tana yamutsa fuska. Tunda tayi amannan har yanzu ƙarfin jikinta bai dawo ba. Ta buɗe baki za tayi magana da saurin gaske ya dakatar da ita.

"Tashi ki fita! Wai ke wace irin mayya ce? Na zaci har ƙofar gidanku na kai ki amma shi ne kika sake biyo ni nan? Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Ya Allah kayi min tsari da wannan bala'i..."

"Mukhtar!!!"

Ta kira shi da asalin sunanshi, abinda ta daɗe bata yi ba.

"Ka yi hauka ne? Iyalin taka ce kake kira da bala'i?"

Hajiyarmu ta tambayeshi da tsawa sosai a muryarta.

Ya kasa amsawa, sai sunkuyar da kanshi ƙasa yayi yana jin yadda ranshi ke ƙuna da raɗaɗi.

A hankali Hajiyarmu ta tako cikin nutsuwa har zuwa kusa da su biyun. Da yatsarta manuniya ta nuna su, fuskarta a ɗaure tamau.

"Ku biyunnan, ku kuka ga junanku kuka nace kuna so ba tare da son ran mu iyayenku ba. Don haka, Mukhtar duk wani fate-fate na azaba da Fatima za ta dama maka dole kai kaɗai za ka sharɓi abinka. Ke kuma"

Ta nuna Fatima da yatsarta manuniya, kafin ta cigaba da cewa

"Ina da labarin duk irin tsiyatakun da kika tsula ma mutane kika nace har sai da aka ɗaura wannan aure. Cikin waɗanda kika bijere ma har da mahaifiyarki, don haka kuka baki ma fara ba tukunna! Bazan hana ki zuwa gidannan ba, amma daga yau kar ki kuskura ki sake zuwa min gida da wani ƙara ko ƙorafi. Ku ji da kanku ku biyun, kun ce kun ji kun gani, don haka mun barku da junanku."

"Hajiya..."

"Ban nemi ƙarin bayani ba. Ba na son jin komai. Riƙe maganarka a cikinka. A cikin ko wace irin zamantakewa haƙuri, kawar da kai, yi ma juna uzuri su ne ja-gaban da suke kai ma'abota zamantakewar ga tudun mun tsira.

Don haka kuje kuyi ta haƙuri da juna, wata rana sai labari. Ɗauki matarka ku tafi."

Hajiyarmu ta katse Mukhtar da ya kira sunanta a raunane yana niyyar yi faɗa mata abinda Fatima tayi masa.

Hankalinsa ne ya ɗugunzuma jin ta ce ya ɗauki Fatima su tafi. Tsananin tashin hankali bai san sa'adda ya zube gwuiyawunsa a ƙasa gaban Hajiyarmu ba. Ya kalleta cikin ido, idanunshi ciccike da ƙwallah, ji yake kamar ya ɗora hannu biyu akai yai ta rusa ihu ko Hajiyarmu za ta bashi dama yayi mata abinda yake faruwa.

Tsakanin ɗa da mahaifi sai Allah. Yanayinsa ya taɓa mata zuciya, amma alƙawari ne tayi ma kanta tun sa'adda ya cije ma auro Fatima baza ta taɓa shiga al'amarin su biyun ba. Ko kwanaki da tayi magana don lamarin ya shafi su Sayyid ne.

Kawar da kai tayi, ta ɗan sassauta fuskarta kaɗan sai ta dawo da kallonta gare shi.

"Sai ka fara tanadi. Ɗazu Aunty Jimmalo ta tabbatar da ciki a jikin Fatima..."

"Ciki? Na shiga uku!! Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un!!!"

Ya jero maganganun cikin tashin hankali da ɗimuwa. Ƙasa ya duƙar da kanshi. Wani abin mamaki da Hajiya baza ta iya tuna lokaci na ƙarshe da taga faruwarsa a fuskar Mukhtar ba shi ne saukar hawaye a idanunsa, kawai ɗiɗɗigarsu ta gani a jikin farar yadin boyel ɗin da ke sanye a jikinsa.

"Uhmmm!"

Ta faɗa cikin mamaki da tu'ajjibi. Hannayenta ta fara tafawa tana sallallami, sai kuma ta riƙe haɓa ta ce

"Kuka kake yi don na faɗa maka masoyiyar maƙwallaton zuciyarka na ɗauke da ciki? Halan ku biyun abu ne da baku taɓa tsammani ba? Itama nan ta gama sussunne kai tana sharar ƙwallah. Madallah! Ɗan so ko yʻar so an tabbatar da ƙyanƙyasan ƙwayayensu ai dole kuyi kuka. Amma a shawarce ba kuka ya kamata kuyi ba. Godiya ga Allah za kuyi da addu'ar Allah ya raba lafiya. Ɗauki matarka ku tafi, aji tsoron Allah a dinga kiyaye adalci tsakanin mata biyu."

Mukhtar sai da ya ɗauki tsawon mintuna uku yana matsar hawaye kamar mace. Sannan ya iya miƙewa tsaye, idanunsa sun kaɗa sunyi ja sosai. Ya ɗan duƙa kaɗan ya ce

"Hajiyarmu a huta gajiya. Na gode. Allah ya kara lafiya da nisan kwana."

Ya ƙarasa gurin Fatima ya jefa mata wani kausasshen kallo da idanunsa sannan ya ce

"Tashi mu tafi."

A tsorace ta kalle shi, sai kuma ta kalli Hajiya. Ta sake kallonshi ta kalli Hajiya. Marairaice fuska tayi idanunta na kan Hajiyar ta ce

"Hajiya don Allah ki barni anan..."

"Wa ce za ta barki anan? Allah ya kiyashe ni. Tashi tsaye maza sawunki a likkafa ki bi mijinki ku sha soyayya. Yadda aka ƙyanƙyashi ɗan so ai ya kamata a reni wannan ƙwai cikin tsananin soyayya da tarairaya."

Da saurin gaske Fatima ta sunkuyar da kanta cikin jin kunya. Kalaman da ta faɗa ma ƙawarta ɗazu a waya cewa ita da Haskenta sun jajurce a cikin kwanaki ƙalilan sun ƙyanƙyaso ƙwayayen ƴaƴan soyayya shi ne Hajiyar take saƙa mata su. Ko kaɗan bata zaci Hajiyar na jin ta ba, da baza ta saki baki tai ta surutu haka ba.

Kamar kazar da aka tsoma a ruwan zafi aka cire haka ta miƙe a ɗarare ta bi bayan Mukhtar. Daƙyar ta iya buɗe ƙofar mota ta shiga ciki, ta matse jikinta guri ɗaya ta duƙar da kanta a ƙasa.

Tsabar tayi nisa a lissafin dokin rano ko kusa bata san sun isa gida ba, sai da taji ya kashe motar, ya buɗe ƙofa ya fita haɗe da buga ƙofar motar da ƙarfi.

A kasale ta buɗe ƙofar ta fita, tana kallonshi ya shige ɓangaren Fareeda. Haka taja ƙafafunta a sanyaye zuwa ɓangarenta.

******

Agogon bangon ɗakin ya kalla, ƙarfe uku da minti arba'in da biyu na yammaci. Jikinsa a sanyaye ya ƙarasa cikin ɗakin ya haye kan gadon. Barci take yi, hankalinta kwance, irin barcin nan da a kallon bawa za'a gane barci ne na nutsuwa, kuma ana jin daɗin barcin nan.

Baya son tashinta, amma a daidai wannan lokacin ba shi da yadda ya iya. Ita ɗin kawai yake buƙatar jin ɗumin jikinta. A hankali jikinsa na rawa-rawa ya ƙarasa jikinta ya ruƙunƙumeta da ɗan ƙarfi. Lokaci ɗaya hawayensa ya dawo.

Cikin barci kamar a mafarki Fareeda ta ji an rungumeta, da fari ta zaci mafarki take yi. Amma daga baya da ta tabbatar da gaske ne ga kuma ƙamshin turaren Mukhtar da har ya fara kama jikinsa kawai sai ta fara mutsu-mutsu tana ƙoƙarin ƙwacewa, idanunta a rufe.

Da saurin gaske ta buɗe idanu jin kamar ana jan shesshe ka. Mukhtar ne ke kuka, Mukhtar ɗin da ta sanshi a mutum mare haƙuri, Mukhtar mai juriya da jajurcewa. Jaruminnan da abu ɗai ɗai ne ke nasarar karya mishi zuciya, wai yau shi ne ke riƙe da ita yana kuka. Matsanancin mamaki ne ya lulluɓeta, sai take tunanin kamar ba kukan gaske yake yi ba. Domin share ma kanta tantama da saurin gaske ta ɗaga fuskarsa da hannunta na dama. Hawaye ne ta gani, ga su nan kace-kace a fuskar

"Wwwwwwwa ya rasu?"

Tayi mishi tambayar bakinta na rawa.

Daƙyar ya iya girgiza mata kai alamar babu kowa ya sake mayar da kansa jikinta ya cigaba daga inda ya tsaya. A hankali ta ɗan sauke ajiyar zuciya, sai tayi luf tana saurarensa, ita bata cigaba da yunƙurin ƙwacewa ba sannan bata tambayeshi me ya same shi yake kuka ba.

Tun tana jin shesshe karshi har ya koma sauke ajiyar zuciya, can kuma sai ta ji shi yayi shiru, yana sauke numfashi a hankali.

Ɗan motsawa tayi kaɗan bayan ta yi tunanin zai iya yin barci.

"Zan yi sallah, lokacin sallar la'asar yayi."

A hankali ya fara sassauta riƙon da yayi mata, har ya sake ta gaba ɗaya. Yana kallonta ta sauka akan gadon har ta shige banɗaki. Tsoro ne ya kama shi, ganin babu wata damuwa a fuskar Fareeda. Yaushe yayi kwantan da har kukanshi bazai

jefa ta cikin tsananin ruɗani da tashin hankali ba? Lallai ya tafka kura-kurai da dama a ginanniyar zamantakewar da suka faro ta da ƙaƙƙarfan tubali na gaskiya da riƙon amana.

Lallai ya kamata ya gyara tun kafin kwaɓar ta idasa yi masa ruwa. Sai ya tuna irin yadda a baya, kafin shigowar Fatima cikin rayuwarsu, ko damuwa a fuska ya fita ya dawo mata da shi hankalinta ba ya taɓa kwanciya sai taga walwala a fuskarsa.

Yana wannan tunanin ta fito daga bayi. Ko kallonshi bata yi ba, gurin kayanta ta nufa kai tsaye ta ɗauki doguwar riga da hijabi ta saka ta shimfiɗa sallaya ta fuskanci gabas. Sai a lokacin ta ɗan waiwaya ta kalleshi da fuska ba yabo ba fallasa.

"A masallaci dai har an idar da sallah. Gara ka miƙe ka sauke farali, bayan nan idan kwanciyar za ka cigaba da yi sai ka koma gurin matarka..."

"Kora ta kike yi?"

Ya katse ta, da muryarsa a sanyaye.

"Ai kam dai korarka nake yi Mukhtar. Ban ga dalilin da zai sa kazo kayi min kwance da ranar nan alhali ba girki na bane. Ni zanyi sallah"

Kafin ya ce wani abu har ta fara tayar da iƙama.

Shi ma bai cigaba da kwanciyar ba, banɗakinta ya shiga bayan gama biyan buƙatarsa yayi alwala. Bai fita daga ɗakin kamar yadda ta so ba ya ɗauki sallaya ya shimfiɗa nesa da ita kaɗan ya tayar da sallah.

Tana zaune tana lazimi har ya idar. Bayan istigfari da gajeren addu'a juyawa yayi gaba ɗaya ya fuskanceta.

"Don Allah, ki shafa addu'a ki ɗan bani minti biyar daga cikin lokacinki. Don Allah ba don ni ba..."

Haka nan ba don zuciyarta na so ba ta bi umarninsa. Fuskarnan a ɗaure, baki a gaba. Allah ya sani a yanzu ta tsani ko ɗan yaya ne ya matse mata guri. Bakinnan a gaba ta tsattsare shi da idanu tana jiran jin abinda zai ce da ita.

"Fareeda, a yanzu na gane kuma na tabbatar a zamantakewar auren da muka yi a baya kafin in ƙaro aure, kashi sittin da biyar cikin ɗari na irin saɓanin da muka yi ta samu ba kowa ne ya janyo haka ba face ni. Amma da yake a wancan lokacin ina kan wani ɓigiri ne da Malam bahaushe yake kira ƙaramin sani ƙuƙumi. Don girman Allah kiyi haƙuri ki yafe min, irin yadda nayi ta ƙuntata rayuwarki a baya tun daga aurenmu har zuwa yau ɗinnan da nake miki magana.

Fareeda, na rantse miki da Allah ban auro Fatima don in tozarta ki ba. Ina son ki har gobe Fareeda, a tunanina auren Fatima da zanyi shi ne abu na ƙarshe da zanyi wanda zai sa ki shiga hankalinki da gaggawa.

Ban gane ni ɗin ba ni da wayau ba, kuma na tafka gagarumin kuskure sai tsakanin jiya da yau da wata irin nutsattsiyar tattaunawa ta shiga tsakanina da wani mai buɗaɗɗe kuma wayayyen tunani. Ashe ba maganin matsala na ɗauko ma kaina ba, wata gaggarumar matsalar mai zaman kanta na ɗauko na ɗora ma kaina.

Ban gane ni ɗin ba mai godiya ga ni'imar da Allah yayi mishi bane sai ayau ɗinnan."

Ya duƙar da kanshi, wata sabuwar ƙwallar ta cicciko a idanunsa. Babu abinda yake tunani a zuciyarsa sai Fatima da cikin da aka ce tana ɗauke da shi.

Aka ce a nemawa ɣayɣa uwa ta gari. A cikin kwanakin zamantakewarsu yayi ma Fatima wani irin karatu ne na nutsuwa, ya gane duk yadda yake tsammaninta ta shallake tunaninsa. A haƙiƙanin gaskiya ma tsoro take ba shi, ta ina zaiyi farin cikin haɗa zuri'a da Fatima?

Daƙyar ya iya haɗiɗiye ƙwallarsa ya kamo hannunta guda ɗaya cikin nashi, a raunane ya cigaba da magana bayan yayi ƙoƙarin kawar da tunanin Fatima daga zuciyarsa.

"Duk wani dogon bayani a yanzu ba shi da amfani Fareeda. Na san duk abinda zan faɗa a yanzu za ki dinga kallonshi a ihu ne bayan hari.

Amma a karo na barkatai zan ƙara roƙonki, ki bani dama ta ƙarshe don darajar iyayenki da suka rigayemu gidan gaskiya. Don Allah SWT, don darajar Fiyayyen halitta SAW abinda ya wuce ki barshi a wanda ya wuce. Mu fuskanci gaba, ki ajiye duk wani baƙin ciki da ɓacin rai da na cusa miki cikin yɑan kwanakinnan da waɗanda suka gabace su. Ni kuma ina tabbatar miki in Allah ya yarda za ki same ni a sabon Mukhtar ɗin da baki taɓa tsammani za ki gani a cikin taƙaitaccen lokaci haka ba. Don Allah..."

"Me nace ka yi ne Mukhtar? Ni fa ban ce kayi komai ba balle ka dinga haɗa da girman Allah da Manzonsa. Ban ƙullace ka ba, kawai na kame kaina ne daga duk abinda zai janyo min ɓacin rai da shiga tashin hankali, ko ka manta yanayin da nake ciki? Tunda dai har Allah yasa ka gano kuskurenka Alhamdulillah! Nima ina roƙon ka yafe min irin saɓa maka da nai tayi a baya. Amma don Allah ka tsahirta min, ko mun ƙi ko mun so tunda kiɗa ya canza dole tsarin rawarmu ya canza. Kaje ka ji da matarka, yau ba girkina bane. Idan da sauran magana gobe in Allah ya kaimu sai a ƙarasa."

A sanyaye ya fice daga ɗakin ta raka shi da idanu. Yana fita daga ɗakin ta taɓe baki ta cigaba da tasbihin da take yi.

Kai tsaye ɗakin baƙi ya nufa daga na Fareeda, buɗewa yayi. Cikin ƙanƙanin lokaci ya zage ya gyara ɗakin ƙal. Sai da ya gamsu ɗakin yayi yadda yake so sannan ya fice zuwa ɓangaren Fatima.

Ko da ya shiga tana zaune akan kujera. Ta yi wankanta har da kwalliya a fuskarta. Kallo ɗaya yai mata ya ɗauke, ko sannun da take mishi bai amsa ba. Ɗakin barcinta ya shige, ita dai tana zaune sai ganinsa tayi yana fitowa da suturunsa da yake cikin akwatinta.

Gabanta ne ya faɗi, da saurin gaske ta miƙe tsaye hannayenta dafe da ƙirji. Bai ko kalleta ba ya fice da kayan a hannunsa, da saurin gaske ta bi bayansa ta leƙa, a zatonta ɗakin Fareeda zai kai kayan, sai taga ya nufi ɗakin baƙi da su.

Daƙyar ta iya komawa mazauninta ta zauna a lokacin da yake daf da dawowa cikin ɗakin, haka ta dinga raka shi da idanu har ya gama kwashe suturunsa tas da duk wasu muhimman kayansa da suke cikin ɗakinta ya mayar ɗakin baƙi.

Sau takwas tana yunƙurin yi mishi magana sai ta rasa ta inda za ta fara, har yayi fita na ƙarshe da tunda ya fita bai dawo ba.

Kuyi haƙuri. Labari ya taho gangara in Allah ya yarda.

Assalamualaikum Barkanmu da wannan lokacin AUNTY ZEE TAKU CE ,Ina uwar gida Amarya da yanmata albishir gareku

BONONZA; BONONZA;BONONZA;

Nazo maku da SAHIHIN MAGANIN CIRE TUMBI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI,KINCI GAYU ANA TAMBAYARKI YAUSHE ZAKI HAIHU TUMBI YA HANAKI ADO DA KWALLIYA SHA KURUMINKI NAZO MAKI DA MAGANI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI ZAN DANDANA MAKU SHI AKAN RABIN KUDINSHI DAGA NAN ZUWA SATI DAYA 7K DUK ROBA DAYA KI BIYA 3500 KI MALLAKI NAKI NAN DA SATI DAYA ZAI KOMA 7K

MAGANIN BREAST WANDA ZAICIKO MAKI DA TUWON NONO DAN ALLAH KIJARABA ZAKIZO KINA GODIYA DAN DUK WADDA TA GWADA SAITA DAWO MANYAN MATA SUKE GYARA KAMAR YANDA KUKASANI 8K YAKE ZANKARA TALLATA MAKU SHI KI BIYA 4K KI MALLAKI NAKI

KI BIYA TA WANNAN ACCOUNT DIN KITURA MAN SHAIDAR BIYA

3968303018

ZAINAB SHU AIBU

FCMB

08162859027

RABON AYI

32

©Fareeda Abdallah

_Yʻar'uwa ki tuna, kafin saukar da ko wace irin cuta, sai da aka saukar da maganinta. Don kinyi magani da yawa baki dace ba ba shi zai sa ki yanke tsammani daga samun waraka ba. Ki gwada maganin da muke karɓa ma al'ummar Annabi SAW, wata ƙila warakarki a wannan maganin yake baki sani ba. Haihuwa kike nema? Baki taɓa yi bane ko kuwa jinkiri ne kike samu tsakanin haihuwar? Sanadiyyar planning ne kika samu jinkirin ko kuwa sanyi ne yake damunki ko haka kawai? Matsalar rashin haihuwar daga mijinki yake? Muna da ingantaccen magani garanti wanda aka gwada muka tabbatar da aikinsa, in Allah ya yarda ko me ya shafi mahaifar mace da mararta wanda ya hana ta haihuwa in dai tayi amfani da saiwoyin maganinmu za ta samu biyan buƙata da yaddar Allah. Matsalar mace ko namiji 2k ne.

Akwai ƙullin maganin da muke sayar da shi 500, in dai matsala ta shafi nonon mace da yaddar Allah za ki samu waraka. Mai ciki, mai shayarwa, mare shayarwa duk za su iya amfani da wannan magani. Ko da matsalar ciwon daji ne da ya shafi nono in sha Allah za ki sami waraka sanadiyyar amfani da wannan magani. Akwai garin maganin sanyi da za ki haɗa a cikin yaji, shi ma 500. Akwai ingantaccen maganin sanyi da za ki saya muku ke da Oga, 2k ne. In Allah ya yarda za ki sha mamakin yadda lafiya zai wadace ku ke da Oga, za ki ga yadda za ku dawo kamar sabbin amaren da suke mararin junansu😍. *Akwai ingantaccen haɗin magani na gyaran nono wanda ni Fareeda Abdallah nake sayarwa, bokiti 1litter 2500, yʻar'uwa

in dai za ki juri dama kunun garin maganin safe da dare, za kiga yadda ba cikowar nono kaɗai ba, hatta fatar jikinki sai ta canza, za kiyi kuɓul-kuɓul😍, sa'annan ni'ima bazai taɓa yanke miki ba in Allah ya yarda saboda irin haɗe-haɗen da ke cikin wannan magani. Ga duk mai buƙatar ɗaya daga cikin maganinnan da gaske ta tuntuɓeni ta whatsapp a 07039080978, idan kira ne a kira ni ta 09077591726. Don Allah yɷan'uwa□□□□□□idan ba da gaske kike yi ba kar mu ɓata ma juna lokaci.*

Tun da yabar ɗakinta a yammacinnan bata ƙara ganinsa ba, har aka wayi gari. Ta leƙa tsakar gida ta windonta ya fi sau goma ko za ta ga giftawar Mukhtar, amma ko alamarsa bata gani ba.

Ranta ne ya ƙara ɓaci. Minti ɗaya biyu sai ta ɗaga hannu ta shafi lafaffen cikinta. Ita kaɗai take sakin murmushi akai-akai idan ta tuno tana ɗauke da cikin Haskenta.

A jiya da lamura suka ɗakko kwaɓe mata har suka ziyarci gidan Maman Murad zuciyarta cike take da nadama mai tarin yawa. Amma bayan tabbatuwar ciki a jikinta daga bakin da bazai mata ƙarya ba sai duk wani ɓurɓushin nadamar da ta fara yi ya kau. Ta san zama tsakaninta da Mukhtar a yanzu ba alfarma bace, dolen dole ne. Ga ta ɗauke da gudajin jininsa me zai sa shi sakinta? Ita fa ta riga ta san tun da Fareeda ta haifi yɷayɷa biyu wataƙila ita da yɷan uku za ta fara a gidan.

"Hehehehe! Shagali! Wa ka ganni da yɷayɷa uku rigis a gidannan? Hmmm! Na rantse da girman Allah Fareeda za ki gane shayi ruwa ne."

Ta faɗa a fili tana dariya irinna bosawa.

Agogo ta kalla taga ƙarfe bakwai da kwata na safe. Tsam ta miƙe tsaye ta shige cikin ɗakinta, doguwar rigar barcin da yake jikinta ta cire, ta ɗauki wata ɓingilar riga da gajeren wando ta saka.

Ta ɗauki Hijabi iya gwuiwa ta saka. Gaban madubi ta ƙarasa ta ɗan goga powder a fuskarta ta ɗauki wayarta ta fice daga ɗakin.

Ɗakin baƙi inda Mukhtar yayi ƙaura ta nufa, tafiyarta lafiyar Allah take yi a tsakar gidan.

Amma tana isa ƙofar ɗakin tasa hannuwa biyu ta dafe mararta, ta duƙe ƙasa kaɗan, ta takwarkwashe fuska sosai, tsawon minti ɗaya tana matse-matsen idanu daƙyar ta samu nasarar matso hawaye daga cikinsu. Nishi ta fara sas-saukewa sauri-sauri. Daƙyar tasa ƙafa ta tura ƙofar, ta faɗa cikin ɗakin a galabaice.

Bawan Allah Mukhtar yana kwance akan darduma a tsakar ɗakin. Ga Alƙur'ani da casbaha ajiye a gefe ɗaya, daga irin kwanciyar da yayi za'a gane irin barcin nan ne da ba'a shirya mishi ba ya samu nasarar ɗauke shi.

'Wani abu da Mukhtar ya daɗe baiyi ba shi ne tashi a tsakiyar dare yayi sallah. Ko a can baya a mafiyawancin lokuta yana ji da zarar ƙarfe huɗu da rabi na dare yayi Fareeda za ta raba jikinta da nashi, ta shige bayi ta ɗauro alwala ta fara nafila, shi kam sai dai ya gyara kwanciya.

A daren jiya bayan shafe awoyi cikin tunani kyakkyawan alwala ya ɗauro ya fara jero nafilfili. Zuciyarsa cike da tunanin rahamar Ubangiji ga bayinsa. Shi Ubangiji mai gafara ne mai jin ƙai, duk yawan saɓon bawa sai dai in bai nemi gafara ba, abinda kawai ake so shi ne bawa yayi tuba cikakkiya da niyyar bazai ƙara komawa ga irin laifin da yake aikatawa ba.

Bayan cikakkun awoyi uku da suka shafe shi da Ibrahim suna tattake guri akan matsalolinsa. Ibrahim ɗin ya sake jaddada masa kacokan abubuwan da suke faruwa da shi a yanzu na rashin daɗi shi ke da kaso tamanin bisa ɗari na faruwar komai. Ya kuma jaddada masa matuƙar bai ɗauki hanyar gyara ba tabbas bai ga komai ba, ya shirya ganin taɓarɓarewar al'amura ninkin ba ninkin na yanzu da yake gani.

A matsalarshi da Fareeda baya da yanzu, shi ne ya taka muhimmiyar rawa gurin ɓata komai. A tsakaninsa da Fatima tun farkon fari ba haka ya kamata su faro tafiyar ba.

_Da yake a shirye yake da karɓar gyara ta ko wane ɓangare. Bai kawo suka ko ƙoƙarin kare kansa ba, da hannu bibiyu ya karɓi laifukansa, sannan ya buɗe kunnuwa sosai yana karɓan shawarwari daga bakin Ibrahim da yake kallon mace a

matsayin wata sassauƙar aba wajen tafiyarwa. Daga ƙarshe ya ƙarƙare da ce ma Mukhtar ɗin_

"Ban ce maka babu hatsabibai kuma shaiɗanun mata ba. Waɗanda idan bawa za ka zame musu wajen hidimtawa da tarairaya baza su taɓa yi maka da daɗi wajen zamantakewa ba. Akwai irinsu da yawa, waɗanda kamar ƙuli-ƙuli suke gurin rashin gane gabansu. Amma ni abinda na yarda da shi shi ne kaso tamanin cikin ɗari na matan da muke aure rashin fahimtarsu ke sa muke fuskantar matsala da su."

Ya ɗauki aniyar gyara ta ɓangaren Fareeda da Fatima. Amma Fatima ta yi mishi laifukan da baya jin zai iya ƙyale ta taci bulus ba tare da ya ɗauki wani ƙwaƙƙwaran mataki da zai sa ta gane lallai tayi ba daidai ba. Tsakani da Allah cikin da aka ce mishi tana ɗauke da shi ko kusa baiyi murna da samunshi ba. Da irin waɗannan halaye na Fatima ta ina mutum mai cikakken hankali zai so haɗa zuria da ita?

To amma ya ya iya? Rabo ya rantse tsakaninshi da ita. RABON AYI aure ta samu ciki da shi Mukhtar yasa komai ya faru a baya. Lallai wannan shi ake ce ma ƙaddara ta riga fata. Tsakani da Allah ta gama sire masa a cikin zuciya, gaba ɗaya maa jikinsa ne yayi wani irin sanyi da al'amarin rayuwar duniyar. Yana tare da matarsa suna zaune lami lafiya ƙaddara da rashin jin magana irinta Fareeda da rashin haƙuri irin nashi suka ja mishi gora wajen ɗakko ma kanshi ƙajaga. Ko da ya idar da sallah a cikin addu'o'inshi sai da ya saka Fatima, babbar addu'arshi gare ta shi ne Allah ya shirye ta, Ubangiji ya cire mata ƙyashi, hassada, baƙin ciki, ƙarya, munafurci, rashin yin abu don Allah da duk wasu miyagun halaye da take da su. Matar da kuke shirin haɗa zuri'a da ita ko ɗan yaya ne dole ka dinga saka ta cikin addu'o'inka.

Fareeda kam bayan addu'ar Allah ya huci zuciyarta kan fushin da take yi da shi, ya daɗe yana addu'ar Allah ya kawar da shaiɗanin da yake tsakaninsu. Ubangiji ya ƙara musu danƙon ƙauna da soyayya, Allah ya raya musu zuria ya kuma sauketa lafiya. Ya ƙarƙare da roƙon Allah yasa yadda take uwargidanshi anan duniya ta zama uwargidansa a aljannah.

_Ga kanshi kuma sosai ya ɗauki tsawon awanni yana addu'ar Allah ya sassauta mishi zafin zuciya, kishi, rashin haƙurin da yake ɗawainiya da shi. Ya roƙi Allah ya yaye mishi duk wani hali nashi da yake taka rawa gurin samun matsaloli tsakaninsa da iyalansa. Bai samu nutsuwa ba sai da aka kira sallar assalatu. Ya sallaci raka'atanil fijr a gida sannan ya fice zuwa masallaci. Bayan an idar ne ya dawo gida yayi azkhar, ya cigaba da karatun Alƙur'ani. Jin barci na neman fin ƙarfinsa ne yasa

shi ajiye Alƙur'ani da casbahan ya kishingide nan kan dadduma. Shi ne har Fatima ta shiga ɗakin bai sani ba._

Ganin yana barci yasa ta miƙe tsaye daga duƙewar da tayi, harara ta maka masa. A zuciyarta take ayyana yau fa cikon kwana ɗayan girkinta ne, amma maimakon su kwana suna rungumemeniya yana shafa cikinta shi ne ya wulaƙantar mata da kwanan ba tare da ta mori abinta ba.

"Ai wallahi baka ci bulus ba, za ka biya bashi in dai Fatima ce. A yanzu ne zan fito maka da asalin wacece ni tunda mun riga mun ƙarasa haɗewa. Yo me ya rage? Jinina da naka sun gauraya wajen samar da gudajin jinainai da za su zamo rayayyu nan gaba kaɗan ai dole in dama kunu na yadda nake so."

Tayi maganar ƙasa-ƙasa ta yadda ita kaɗai take jin abinta, laɓɓanta da ke motsi ne kawai za su saka a fahimci maganar ciki take yi.

A ɗan fusace ta ɗauki Alƙur'ani da carbin ta ajiye gefe ɗaya, hijabin jikinta ta cire ta hurga kan katifa, ta ɗaga vest ɗin jikinta zuwa sama sosai sannan ta raɓa ta bayansa ta kwanta haɗe da ruƙunƙume shi tana aikin goga mishi ƙirjinta.

Nishi take yi a wahalce kamar wacce take cikin wani matsanancin ciwo. Idan ba sani aka yi bama yadda take goga mishi ƙirjin za'a zaci irin bugun ciwon nan ne take juye-juye ba tare da saninta ba.

Kamar a mafarki yake jin nishinta, da yake da riga a jikinsa bai farga da abinda take masa a bayansa ba sai daga baya. Ko da ya tabbatar ba mafarki yake yi ba a firgice ya buɗe idanunsa.

Da saurin gaske ya janye jikinsa daga nata ya miƙe zaune fuskarsa a tamke tamau.

"Miye kike yi haka? Me ya kawo ki nan?"

A maimakon ta amsa tambayoyinsa ko kuma ta faɗi wani abu daban kawai sai ta saka kuka. Tasa hannu biyu ta dafe saitin mararta ta cigaba da juyi tana hawaye da shessheƙa.

"Kin ga, idan baza kiyi magana ba salin-alin ki tashi ki fice min daga nan."

Yayi maganar cikin dakiya da ɗaurewar fuska.

"Has...Aban twince cikina... marata.... bayana ciwo... zan mutu.... wallahi jiya kwana nayi banyi barci ba... har wasiyya na rubuta na aje maka a gefen gad..."

"Kina jin irin ciwukan da kika lissafa ne har kika samu damar rubuta wasiyya?"

Ya katseta da tambayar, a zuciyarsa yake girmama ƙwarewarta a wajen sharara ƙarya.

Ɗif tayi bata amsa ba, can kuma sai ta cigaba da jan shessheƙa.

"Tashi ki zauna"

Ya bata umarni.

A sakalce ta miɕe ta zauna tana mutsutsuke idanu da tura baki. Har ta fara jan hanci za ta cigaba da kuka ya daka mata tsawa a dole ta haɗiye kukanta.

"Fatima? Wai ke wace irin macece? Yanzu don Allah bayan abinda ya faru jiya har kin samu ƙwarin gwuiwar da za ki iya fuskanta ta da wasu ƙarerayi naki?"

"To ba tun jiya Hajiya ta ce kayi haƙuri ba..."

"Banyi haƙurin ba. Ke saurareni kiji da kunnen basira."

Ya miɕe tsaye daga ƙasa ya koma kan katifa ya zauna, har lokacin fuskarnan ba wasa.

"Ke bakiyi mamaki da duk irin abinda ya faru jiya me yasa ban sake ki ba?"

Wani irin rugurgujewa ƙirjinta yayi ya buga daram. A tsorace ta zaro idanu tana kallonsa, ta kasa cewa komai.

"Hmmm! Bari kiji, ni a tsarina ko? Duk rashin haƙuri irin nawa saki shi ne mataki na ƙarshe da zan bi da mace wajen ladaftarwa. Akwai matakai iri-iri da ya kamata abi kafin rabuwar aure, tunda dai ke mayya ce na kaiki gidanku kin ƙi zama, to ki cigaba da zama anan ɗin. Amma na rantse da Allah na ƙaurace miki kenan har zuwa sa'adda ni a karan kaina zan gamsu da gyaruwar halayenki. Bazan hana ki ci da sha, sutura, gurin kwana da nema miki lafiya ba, hakkinki ne tunda ban sake ki ba. Amma mu'amala da miji, kulawa, soyayya, tarairaya sai dai ki gani a maƙwafta. Idan kin so ki hankalta Fatima, idan baki so ba kar Allah yasa ki hankalta ki gyara halayenki. Abu ɗaya da zan tabbatar miki shi ne daga wannan matakin idan baki gyara ba za mu kai iyaka ne tsakanina da ke. Tashi ki fitar min a ɗaki, kuma daga yau duk abinda kike buƙata ki aika min saƙo ta waya ne, kar ki sake takowa cikin ɗakinnan, idan ba haka ba Wallahi zan shayar da ke mamaki mai girman gaske. Kuma ki saka a zuciyarki ni Mukhtar na jefa ki a cikin layin maƙaryata, daga yanzu har zuwa sadda zan gamsu kin gyara halaye ko baki gyara ba Allah ɗaya kawai za ki ce min in yarda dake. Tashi ki fita tun kafin ki hassalani"

Haka ta miƙe jiki ba ƙwari za ta fita a ɗakin. Maganganunsa sun daki jikinta ba kaɗan ba.

"Haka za ki fita tsirara? Ko da yake je ki, daman akwai ƙarancin abinnan, fita a yadda kike so."

A kasale ta juya ta ɗauki hijabinta da ke ajiye kusa da shi ta saka, ta fita a ɗakin ba tare da ko kallonsa ta sake yi ba. Tana tafe tana haɗa hanya har ta ƙarasa falonta, nan kan kujera ta zube tana hawaye, ta buɗe baki za ta kwarma ihu sai muryar Mukhtar ta ji a gefenta yana cewa

"Duk da nasan ƙarya kika sharara min cewa kin kwana cikin ciwo. Ga dubu biyar nan ki tafi asibiti, na baki kuɗinnan ne kawai don kar Allah ya tuhumeni kin ce ba ki da lafiya ban kula da ke ba."

Bai jira ta karɓi kuɗin ba ya ajiye a gefenta ya fice daga ɗakin yana jan tsaki ƙasa-ƙasa.

*****

Da matuƙar mamaki ta buɗe baki, sai kuma tayi dariya tana kallon Kamalu da ya kasa haɗa idanu da ita.

"Dan ƙanina, wai duka-duka yaushe maganar tayi ƙarfi ne har aka shirya maganar aure a gaggauce haka ban sani ba? Na zaci iyayen Jamilar sun ce sai tayi shekara uku a jami'a sannan za'ayi maganar aure?"

Wanda ta kira Kamalu dai ba baka sai kunne, ƙara sunkwui da kanshi ƙasa yayi cikin kunya yana murmushi.

"Fitsararre, ai dole kaji kunya mana tunda a gaban Fareeda ne. Wallahi a gidan in kika ga yadda ya tasa mu gaba da fitsara iri-iri za ki sha mamaki. Da fa Honey cewa yayi mu bari gobe lahadi mu shiga kasuwa haɗo lefen, amma da ya taso mu gaba da naci har da yar ƙwallarsa ai babu shiri muka fito a gatse-gatsen ranar nan. Allah yasa dai bamu takura miki ba Fareeda, duk mun sanki da sanin kyawawan kaya kalar yan birni shi yasa muka ce tsinke baza mu siya na lefennan ba sai kina gurin..."

"Au! Wai yanzu kina nufin kasuwa za mu shiga Aunty Kareema?"

"Eh mana babbar Yayata. Don Allah kar ki ce baza ki samu zuwa ba. Ya Mukhtar don Allah kasa baki, Wallahi tun da aka saka bikinnan kullum sai Jamcy ta jaddada min in tabbatar an zuba mata zaɓaɓɓun kayayyaki kuma masu tsada a cikin lefenta."

Ya ƙarasa maganar yana kallon Mukhtar da Fareeda a marairaice.

Shi dai Ibrahim ɗan dariya kawai yayi yana kallon ƙanin nasa. Hmmm! Ta yaro kyau take ba ta ƙarko, bai san a cikin rayuwar auren kashi saba'in da biyar na zamantakewar haƙuri ne jagoranta ba.

Mukhtar a tausashe ya matsa kusa da Fareeda yana rarrashinta da tausasan kalamai kan ta daure su shiga kasuwar.

"Ba sai kun jigata kanku wajen gama haɗa kayayyakin ayau ba. Abinda baku siya ba gobe ku leƙa ku ƙaro, jibi haka, har dai ku gama siyan duk abinda ake buƙata."

"Ni fa ban ce bazan je ba Abee. Tunani nake yi, da mu wahalar da kanmu wajen shiga kasuwa me zai hana Ya Ibrahim ya faɗi iya adadin kuɗin da yake so mu haɗa komai na lefennan, yanzunnan zan kira *Hds jawellerys and more* mu tura musu kuɗaɗen su haɗa mana duk abinda muke buƙata..."

"Hds jawellerys and more? Su wanene kuma haka?"

Su ukun suka haɗa baki gurin tambayar Fareeda da mamaki a fuskokinsu.

"Hds jawelleries and more business name ɗinsu ne. Kawai abinda za mu yi yanzu shi ne za mu kira Sister Hadiza mace mai haba-haba da iya tarbar jama'a a fili da cikin waya kan lambarta 08144965394. A garin kano suke, adireshin babban shagonsu suna nan kan titin gwarzo unguwar kabuga bayan gidan man AYM SHAFA..."

"Haba Fareeda, duk shagunan da suke nan kaduna sai mun tsallaka kano?"

Kareema tayi maganar tana ɗan ɓata fuska.

"Ke kam Aunty Karima kin cika gajen haƙuri. Ki bari in kaiki mana. Kin tuna kayan da nasa da yamma nayi fitan bikin amaryar Abee da su? Har kina tambayata inda na siya lace da atamfar da sarƙa da yankunne haɗe da warwaraye masu kyau na ce miki Aunty Binto ce tayi min siyayyar? To ai a gurinsu ta siya min. Muna daga nan za mu aika mata da kuɗi gobe zuwa jibi da sassafe saƙonninmu za su iske mu har nan kaduna.

Kuma ko rantsuwa nayi babu kaffara za kuyi mamakin irin haɗaɗɗun kayayyakin da za zuba mana a cikin akwatunan. Ke ni fa na huda ne naga jini, in kunji ana faɗin garanti trust kuma sayen na gari don mayar da kuɗi gida to kayan *Hds jawelleries

and more ne*. Kuma ƙarin armashi shi ne idan da kanmu muke so mu zaɓa yanzunnan muna kiranta za ta antayo mana da hotunan sabbin yayi na kayyaki mu zaɓa mu darje.

Suna da group a whatsapp da suke tallata hajojinsu

https://chat.whatsapp.com/LpxLzmsKFFfBatQoY8q1jA

Ke ko ruɗewa kikai wajen zaɓin kala da kin tura mata hoton kalar fatarki za ta zaɓa miki atamfa, ko lashi, ko material, ko shadda, ko abaya wanda zai shiga da ke sosai da sosai, duk inda kika shiga da suturan da kika siya gurinsu ayita kallonki ana tunanin ina kika sai wannan ɗanɗasheshen zanin..."

"Taɓɗijan! Ni kam na ga gurin zuwa haɗo lefen Sweet Jamcy my heart. Yaya Ibrahim kawai a kira Hds jawelleries and more su haɗa min lefen amaryata."

Ango Kamal ya faɗa cikin karaɗin murna.

Nan dai dukkansu suka haɗu kan shawarar a kira Sister Hadiza 08144965394, sun san halin Fareeda ƙwarai. In dai ta yaba da abu, to tabbas wannan abu fa yayi ne ɗari bisa ɗari.

*_Lissafin rayuwa a wannan lokaci da muke ciki_*

Sunana Rumanatu Bashir Abubakar.

Yʻar'uwata ko ban faɗa ba kin san rayuwar duniyar kullum ƙara sauyawa take yi. Matuƙar kina so al'amuran cefane a gidanki ya tafi dai-dai sai da lissafi, tsari, da bin hanyoyin da za ki mallaki duk abinda kike so cikin sauƙi ba tare da kin ɗaga hankalin maigida ba.

Duk wacce ta gane sirrin rayuwar idan an ciza sai a hura, sai kuma aɗan dakata aga sakamakon da hakan zai haifar. Da fatan Ubangiji Allah ya shige mana gaba a dukkan al'amura. (Ameen)

Azumi na ta ƙaratowa, a yanzu haka da nake wannan maganar saura bai fi kwanaki hamsin da wani abu ba. Wane tanadi kike yi don mallakar kayayyakin da za su ƙayata girke-girkenki na azumi? Ko kuwa jira kike sai azumin ya zo kaya sun ninka farashi a kasuwa kizo groups kina surutun yʻan kasuwa Allah ya musu kaza da kaza? Bari in sake faɗa muku ko mu so ko mu ƙi komai yanzu sai da tsumi da tanadi.

Kin ga yʻar'uwata. Muna sayar da dankalin turawa, fruits, vegetables akan farashi mai rahusa. A jos muke da zama, amma idan kika ce kina son kayanmu duk jihar da kike za mu aika miki da shi cikin ƙanƙanin lokaci.

Malam bahaushe ya ce mai kwarmin ido da wuri yake fara kuka. Haka zalika Hajiyoyi manyan mata idan kuka bi wannan tsarin da zanyi magana akai da zaran azumi ya zo za ki karɓi dankalin turawa, fruits, vegetables kamar kyauta aka baki□ □□. Ko maigida yaga kaya turus an aiko miki da shi ba tare da kin caje shi maƙudan kuɗi a lokaci ɗaya ba za ki bani labarin yadda zai kwashe kwanaki talatin cif na azumi yana zunduma miki albarka❤□. Kamar gonar auduga haka za ki dinga ganin talatin da biyunnan a waje ko wane lokaci. Yo taya bazai miki dariya ba bayan shi a ganinshi ya tsinci

dami a kala? Yana miki kallon biri kina mishi na ayaba ba tare da sanin a jikinshi kika tatsi kuɗaɗen da kika zuba a asusunmu don mallakar kayan buƙatar yau da kullum ba😂

Wannan tsarin da nake muku magana akai adashi ne za ki zuba, akwai ɗan kullum akwai na duk sati😍 amma idan lokacin kwasa yayi za ki kwashi Irish, fruits, vegetables□□. A taƙaice dai Iya kuɗinki iya shagalinki Hajiyata😍□□

Waɗanda suke buƙatar yin adashi da gaske domin samun cikakken bayanin yadda tsarin zubin yake ku tuntuɓeni akan lambar wayata □□ wa.me/2348065530483

*_RABON AYI_*

©Fareeda Abdallah

33

Yʻan'uwa da gaskiyar Mal Bahaushe da ya ce komai yayi farko tabbas zaiyi ƙarshe. A labarin RABON AYI mun taho gangara. Ku adana lambobina guda biyu domin siyan DATA na ko wane irin layin waya. Da sauran kayayyakin da muke saidawa don taimaka ma Al'ummar Annabi Muhammad SAW. 09077591726, 07039080978

Yʻar'uwa kina fama da matsalar rashin haihuwa ko dogon jinkiri? ko kuma matsalar daga mijinki yake? Muna bayar da magani da yaddar Allah. 2k matsalar mace, 2k matsalar miji.

Sanyi ne matsalarki? Irin infection ɗinnan mai sa zubar ruwa, bushewa, ƙaiƙayi, ƙuraje? Muna da kalolin maganin sanyi masu kyau in sha Allah, waɗanda ni da kaina na gwada na tabbatar da ingancinsu, 2k za mu baki kala uku, kala ɗaiɗai kuma 1k.

Matsalarki rashin sha'awa ce? Za mu haɗa miki magunguna kala daban-daban, in Allah ya yarda cikin ƙanƙanin lokaci za kiyi mamakin yadda za ki ji a jikinki. 3k ake harhaɗa magunguna.

Mijinki ne baya harka yadda ya kamata a shimfiɗa? Sanyi da basir sun gama tatake shi? Shi ma akwai magani, 2k za'a haɗa miki magani.

Muna da yajin sanyi, tsohon sanyi da sabo duk zai magance miki in sha Allah, 500.

Muna da maganin gyaran nono ga mai ciki, mai shayarwa, mare ciki duk za su iya amfani da shi. Ko da matsalar ciwon nono ya shafi daji da yaddar Allah wannan

magani namu zai magance cutar, 500 ɗauri ɗaya, amma fa girmanshi bai kai cokali ɗaya ba.

Akwai kuma ingantaccen haɗi na garin SABAYA wanda ni Fareeda Abdallah nake haɗawa da kaina. Maganina ba shi da wani cutarwa, nau'ikan abincine da muke ci nake harhaɗawa har kaloli goma sha biyu. Mai shayarwa za ta iya amfani da maganina, za ta ga yadda nonuwanta zai ƙara cika, kuma zai wanke mata ruwan nono hatta yaronta za taga yadda zaiyi ɓulɓul in Allah ya yarda. Yar'uwa da kike buƙatar cikowar nono da mazaunai ki gwada garin maganina, in Allah ya yarda cikin ƙanƙanin lokaci za kiga biyan buƙata. Bazanyi muku ƙaryan nonuwan da suka kwanta lakaf za su miƙe su tsaya ƙyam ba, amma fa za su ciccika gwanin ban sha'awa. Rashin tuwon nono shi ke sa nono ya kwanta kamar silipas, to maganina zai taimaka miki gurin ciko da tuwon nono. Ko basu miƙe ƙyam ba za su ciko, za kiyi kwalliyarki da su ko babu brezia a jikinki. Mazaunanki za su cicciko, duk wata komaɗa da take rame a jikinki za ta cika in Allah ya yarda. Kuma za kiga yadda shan maganin zai sa ki kasance cikin ni'ima ko da yaushe, hatta fatar jikinki za kiga yadda za ta dinga sheƙi, saboda kina dama kunun kayan abinci masu gina jiki. 2500 bokiti 1litter.

5407827015

Farida Abdullahi

FCMB.

A tura da kuɗin maganin da ake so ta acc ɗina sai a tuntuɓeni ta lambobin wayata da bayanin irin maganin da ake so. Muna aikawa ko wace jiha a faɗin nigeria amma wacce ta sai magani ita za ta biya kuɗin mota.

Customers ɗina na data ina fatan ko babu rubutun RABON AYI za ku riƙe min amana😘😘😘 da naji ƙyalan ni kuma zan muku ƙililin kun dai gane ai😍😍□□😘😘😘

Sa'adda ya nufi hanyar gadan-gadan a tare ita da shi ɗin suka riƙe numfashi cak suna jiran ganin abinda zai faru. Wani abun mamaki shi ne yana nan da ƙarfinsa, bai kwanta lakaf kamar lagwani ba. Ya tashi tsaye ƙyam a matsayin jarumin nan Mukhtar.

A tare ita da shi ɗin suka sauke wata iriyar nannauyan ajiyar zuciya. Bawan Allah Mukhtar sai hawaye. A fili da zuciya yake kabbara, haihala yana godiya ga Allah. Kwanaki bakwai ya kwashe yana tsayuwan dare kan Allah yasa a samu nasarar magance matsalar nan, ga shi kuwa Allah maji roƙon bawa ya amshi addu'arsa. Lallai duk wanda ya dogara ga Allah ya isar masa. A wannan dare albarka kam Fareeda ta sha shi kwando-kwando daga bakin Mukhtar. Da wani kewa, zakwaɗi, ɗoki, farin ciki, zafin nama yake aikata komai.

A ɓangarenta duk da ta ji daɗin samun warakar matsalar da ke tsakanin su biyun, ta ji daɗin ganin yadda ko ina na jikinsa ke rawa yana ƙara rirriƙeta. Ta ji daɗin jin yadda yake ta shi mata albarka. Ko kaɗan bata nuna mishi jin daɗinta a fuska ba. Aka ce haihuwa ɗaya horon mahaifa. Ta yafe mishi tabbas, kuma a cikin kwanakin tana ganin yadda yake ta ƙoƙarin canzawa daga wancan Mukhtar ɗin mai murɗaɗɗen hali zuwa wani mai sanyin hali. Ƙudurtawa tayi a ranta baza ta sakar mishi fuska lokaci ɗaya kamar wata sakarya ba, ya zama dole ta ja ajinta, ta kame mutunci da kimarta don ƙara sama ma kanta girma da kwarjini. Amma fa hakan ba yana nufin za ta dinga wulaƙantar da shi bane.

Ko bayan kammaluwar komai haka ya riƙe ta a jikinsa yana sharar ƙwallah. Zuciyarsa cike da wani irin rauni da fargaba. Daman ya sani, shi da Fareeda kamar hanta ne da jini, baza'a taɓa raba ɗaya da ɗaya ba.

Har ta fara gyangyaɗi ya tashe ta a hankali, yana riƙe da ita a gefen kafaɗunsa suka ƙarasa banɗaki. Wanka suka yi sannan suka koma kan gado, hannayensa biyu ya buɗe ya saka ta a ƙirjinsa.

Akai akai yake sauke ajiyar zuciya, wani irin riƙo ne yayi mata, kamar wanda ke tsoron za'a ƙwace mishi ita. Bai matse ta yadda za ta wahala ba, amma yayi wani irin kanainayeta da hannayensa ta yadda ko ita ce tayi yunƙurin ƙwacewa baza ta iya da gaggawa ba. Ba tare da ɓata lokaci ba wani nannauyan barci ya kwashe su biyun, a lokacin sha biyu da rabi na dare. Agogo na buga ƙarfe huɗu na dare Fareeda ta farka, tun tana saka alarm a wayarta yanzu ta daina. Yau da kullum ta fi ƙarfin wasa, tashi a daidai irin wannan lokacin har ya bi jikinta.

Tana tunanin yadda za ta motsa da jikinta wayar Mukhtar ta fara ƙarar Assalatu khairun minannaumi. A take shi ma ya buɗe idanu, karaf idanunta suka faɗa cikin

nasa. Tsawon daƙiƙu biyu suna kallon juna a cikin madaidaicin hasken ɗakin sai ya haske ta da tattausan murmushi.

Bata mayar mishi da martani ba, ta ɗan kawar da fuskarta gefe sannan ta ce

"Zan tashi, ɗan sassauta min."

Babu musu ya sassauta riƙon da yayi mata. Da basmala a bakinta ta miƙe zaune, salatin Annabi SAW tayi da addu'o'i sannan ta miƙe zuwa banɗaki. Tana fitowa bai ɓata lokaci a kwance ba ya shiga ya ɗauro alwalar, tana gefe yana gefe kowa ya fuskanci gabas suna kai kukansu ga rabbil Izzati. Wani ikon Allah kamar haɗin baki, a wannan dare ita da shi gaba ɗaya addu'arsu ta tattara ne ga Allah ya musu maganin damuwoyinsu, ya haɗa kansu, ya raya musu zuri'arsu, ya kawar da shaiɗan a tsakaninsu.

******

Kwanci tashi ba wuya a gurin mai kowa mai komai. In da rai da lafiya komai mai zuwa da wucewa ne. Haka zalika babu wani laifi da baza'a iya gyarawa ba, sai dai in shi wannan bawan bai ɗauki aniyar gyara tsakaninshi da mahaliccinshi ba.

Mukhtar yayi niyyar gyara, ya haɗa da addu'a. Sai Allah ya taimakeshi akan ƙudurinsa, a hankali yana danne zafin kishi da zuciyarsa yana kuma addu'ar Allah ya tama mishi sai ga shi an samu gwaggwaɓar canji da cigaba tsakaninshi da Fareeda. Yanzu wani irin tsarin zama ne suke yi na gaskiya da gaskiya, ba ɓoyo ba ƙumbiya-ƙumbiya. Sukanyi musayar ra'ayi cikin mutunta juna, ƙauna da girmama juna. A yanzu manyan turakun da suke riƙe da zamantakewarsu uku ne.

Ƙauna

Haƙuri

Uzuri ga juna.

Waɗannan matakai su suka samar da wata sassanyar zama mai daɗi da armashi a tsakaninsu. Tsawon watanni biyu kenan cif Fareeda da Fatima basu sake ganin juna cikin ido ba, da yake Fatima ce mai yawan leƙe ta window tana yawan hangen Fareeda idan za ta fita unguwa ita kaɗai ko kuma ita da Mukhtar.

Ga Fareeda kuwa ta manta da wata Fatima, ko a cikin tunani ta shafe babinta. Kuma duk tsawon lokacin nan bata taɓa sani akwai rikici tsakanin Mukhtar da Amaryarsa ba.

Kwanakin girkinta su kaɗai yake ba ta, ranar da ba nata ba tun magrib yake mata sallama ya koma ɗakin baƙi. Bata taɓa mayar da hankali ta lura da abinda ke wakana ba, to ko ma ta lura meye ruwanta a ciki? Har a sallah addu'a take Allah ya mantar da ita Fatima da lamuranta.

A ɓangaren Fatima da Mukhtar kam lamarin ƙara tsami yayi sosai. Tun da ya mata wannan korar karen ta janye jikinta, bata ƙara gigin zuwa ɗakin baƙi ba. Amma ta mayar da shi kamar wani Atm na tatsar kuɗinta, kwana ɗaya biyu za ta tura mishi saƙon ta kwana bata yi barci ba, ya bata kuɗi za ta asibiti. Ta haɗa da akawun ɗinta na banki ta tura mishi.

Da yake ƙoƙarin canja halayensa yake yi ta ko wane ɓangare na rayuwarsa bai taɓa ƙorafi ba. Sai dai yayi murmushi kawai, ya tura mata dubu uku ko biyar ya haɗa da addu'ar Allah ya shiryeta. A cikin duk kwanaki biyu na girkinta sau ɗaya rak yake leƙawa ya duba lafiyarta, shi ɗin ma ba wata magana da take shiga tsakaninsu.

Duk in ta tura mishi saƙo za ta unguwa, bai taɓa hana ta ba. Amsarshi ɗaya da zai bata shi ne

"Allah ya tsare."

A take zai tura mata 1k ya rubuta kuɗin napep.

Duk wannan yaji da Mukhtar yayi ma Fatima har yanzu Allah bai sa ta fuskanci inda yake so ta fuskanta ba. Tsanar Fareeda kullum ƙara ninkuwa yake a zuciyarta, kullum addu'arta ɗaya shi ne Allah ya bata dama ko ɗan yaya ne tai yaga-yaga da Fareeda.

Mukhtar kuwa tara shi take yi, ta barshi ne har zuwa sadda Allah zai sauketa lafiya. Ta san da ta haihu yaga kyawawan jarirai a gidansa tana zaune zai fara bikonta, a lokacin ne za ta gwada mishi lallai shiru-shiru ba tsoro bane, gudun magana ne.

******

Tana shiga cikin ɗakin ko zama bata yi ba ta fara zazzaga bala'i kan shariyar da ƙannenta suka mata, sun ganta amma suka nuna kamar basu san wacece ita ba.

"Inna kina kallon yarannan ko? Yanzu saboda Allah da Annabi ni ba ni da alfarmar da zan shigo gidannan su miƙe su tarbeni cikin farin ciki da nuna ƙauna? Miye laifina? Ko don an ga yanzu ba ni cikin daular da nake ciki ada? Sunnar Annabi SAW da na raya shi ne abinda zai janyo min tsana da hantara a gurin ku?"

Sai kuma tayi takwaf-takwaf da fuska kamar za ta saka ihu.

"Aure ne nayi fa Inna ba karuwanci na tafi ba. Don Allah don Annabi ki yafe min. Ki fahimce ni mana. Kinga fa saboda fushin da kike yi da ni har yanzu na kasa cimma abinda nake burin cimmawa a aurennan. Rabo ne tsakanina da Mukhtar Inna, ƙaƙƙarfan rabo. Ni abinda nake so ki dinga tunawa wani bai taɓa auren matar wani, ni da Fareeda tun fil-azal Allah ya ƙaddara sai mun auri miji ɗaya. To menene laifina don rubutacciyar ƙaddara ta tabbata a kanmu...?"

"Ba ki da laifi Binta, ko kusa ba ki da laifi."

Uwar ta faɗa idanunta a ƙasa tana cigaba da ƙullah kukan miya da take sayarwa.

"Rabo kuma da kike magana akai Allah ya kawo masu albarka..."

"Ai ya ma kawo Inna"

Sai kuma ta sunkuyar da kanta tana murmushi.

"Ciki nake da shi Inna, Wata uku kenan"

Tsam Inna ta ɗaga kanta tana kallon Fatima. Sai kuma ta jinjina kai, ta ɗan muskuta tana mamakin cikin da Fatima ta ce tana da shi. Lallai iko sai Allah Al'musawwiru.

Tsawon wasu mintuna shiru ne a tsakaninsu. Can sai Inna ta katse shirun da cewa

"Ya Fareeda da yʻayʻanta? Ina fatan duk suna nan lafiya?"

Yamutsa fuska tayi jin an taɓo inda yake mata ƙaiƙayi, sai ta nemi guri a gefen gadon ɗakin ta zauna.

"Inna Fareeda tana ɓangarenta ina nawa. Babu wacce ta san ya lafiyar yʻar'uwarta take. Domin ku ne kuke mata kallon wata mutuniyar arziki, wallahi kwanaki daga ɗan faɗa ya haɗa mu kar kiso kiga yadda ta zage ni ta uwa ta uba..."

"Duk da ba ni na haifeta ba na san haliinku ɗaya bayan ɗaya. Idan za ki dafa Alƙur'ani ki rantse bazan taɓa yarda ta zage ki ba tare da ke ce kika janyo rikici a tsakaninku ba. Ni dai na faɗa miki, ba baki nake miki ba Binta. Ba kuma fushi nake yi da ke ba. Wallahi matuƙar baki tsarkake zuciya kin nufi kowa da alkhairi ba matsala baki ga komai ba, duk wacce kike ciki somin taɓi ne.

Ni na haife ki Binta. Baza ki taɓa layance min ba. Tun kina yʻar ƙanƙanuwarki ako wane lamari da zai taso ke macece mai bala'in son kanki. Idan za ki dafa Alƙur'ani ki rantse bazan taɓa yarda bayan son raya sunnar aure babu wani abu a zuciyarki ba game da auren mijin aminiyarki ba.

Aure tsakaninki da Muntari ko kusa babu haramci a cikinsa. Amma ni abinda naso, da kinyi haƙuri kin kawar da kai, da idanun duniya basu dawo kanki haka ba. Da kin nuna ƙin al'amarin a fili ko da zuciyarki tana tsananin so, da bakunan da za suyi Allah wadarai da al'amarin basu kai yawan haka ba. Da kin nuna ma Fareeda da alkhairi da zuciya ɗaya kika shiga gidanta, da danganta a tsakaninku bata yi tsami haka ba. To amma Binta duk baki bi waɗannan hanyoyin ba, ana nuna miki Annabi kina runtse idanu, duk wanda yaso nusar da ke sai ki fitittike kiyi ta zuba rashin mutunci, kina ganin nema ake a hana ki auren Mukhtar da kike tsananin so da ƙauna. To an ƙyale ki kin aure shi, kin ga Mukhtar shi ma ya ganki, sai ku cigaba da zama. Allah ya bada sa'a. Fatana da addu'ata ako wane lokaci Aniyar kowa ta bi shi a cikin ku ukun!!"

Wani irin ƙunci da ɓacin rai mai tsanani ne ya lulluɓeta a sanadiyyar jin kalamin da ke fita daga bakin Innarsu. Ita da ta je gidan da niyyar yini har yamma lis, saboda tun da tayi aure bata taɓa zuwa gida ba sai a ranar. Ko minti uku bata ƙara ba ta tattara komatsanta a cikin jaka ta fice a gidan, fuskarta a ɗaure.

Da murmushi uwar ta raka ta. A zuciyarta ta bi ta da addu'ar shiriya.

Daga nan tayi niyyar zuwa gidan Inna Rabi, har ta ce ma mai mashin ga inda zai kaita sai kuma ta canza shawara.

"Malam kai ni Askulaye. Na manta zan je dubiyar mare lafiya."

Ƙasa-ƙasa yaja tsaki, jin ta ce dubiya za ta je shiyasa baiyi ƙorafi ba. Nan take ya juya akalar mashin ɗin ya fara wani irin tuƙi na ganganci yana walagigi da ita a tsakiyar hanya.

Daga can tsallaken titi da saurin gaske Idriss ya taɓo Mukhtar yana nuna mishi, Fatima da suke tsakiyar titi wani mai mota ya kusa kwashe su ya watsar tsakiyar hanya, Allah ya taƙaita dai hatsarin bai faru ba. Shi ne fa mai mashin ɗin ya tsaya yana ta zazzaga bala'i da masifa don ganin suntumemiyar motar da ta kusa kwashe, ciyarsa cike da fatan ya ƙwamuso wasu miyagun kuɗaɗe a hannun Alhajin. Ita kuwa Fatima da zuciyarta ɗaya take taya mai mashin zazzaga tsiya, go slow har ya fara taruwa, ga jama'a sun tsaya kallo gefe da gefe.

"Mukhtar? Wancan ba amarya Fatima bace?"

Ko kafin ya ɗago kai sai da gabanshi ya faɗi. Kallo ɗaya yayi mata ya kawar da kanshi, yana jin wani irin muzanta da kunya na lulluɓe shi.

"Idriss pls bar maganarta. Ita ce ko ba ita bace ba abinda ya shafe ka bane. Muje don Allah."

Ya ƙarasa maganar daƙyar kamar wanda ya haɗiyi taɓarya. Wai yanzu shi ne matarshi a ke hayaniya da ita haka a tsakiyar hanya? Uhmmm! Ba komai, rayuwa

ce wata rana sai labari. Ya ayyana hakan a ransa, yana jin yadda zuciyarsa ke suya da tafarfasa.

******

A gaban madubi ta tsaya kamar yadda aka umarce ta. A hankali ta zuge zip ɗin jakarta, ta ciro ƙullin ruwan maganin da tun a hanya take riƙe jakar cikin lallaɓa da tarairaya kamar wacce ta ɗauko ɗanyan ƙwai.

Rashin ganin motar Mukhtar a tsakar gidan ba ƙaramin farin ciki tayi ba. Da zafi zafi ake bugun ƙarfe, gara tun yanzu tayi amfani da maganin tunda sharaɗin shi ne ta tabbatar mijinta ba ya gida.

Ruwan maganin ta huda ta tsiyaya a hannu ta kurkura bakinta sau uku! Sannan ta wanke fuskarta da ragowar maganin. Ta fuskanci kudu, ta runtse idanunta ta kira sunan Fareeda sau goma sha shida.

Ta gumtse baki tsam ta fita daga ɓangarenta. Kai tsaye gurin Fareeda ta nufa, zuciyarta cike da yaƙinin babu abinda zai hana wannan magani aiki kamar yadda malam mai gani har hanji ya faɗa mata. Duk yadda Ramlah tai ta kururuta mata shaharar malamin bata wani yarda ba sai da suka je ta gani ma idanunta. Irin manyan matan da tags suna mishi layi yasa taji a ranta lallai ta zo inda za'a share mata hawaye. Nan take ta watsar da duk wani ɗari-ɗari da tsoron me zai je ya dawo ta miƙa ma Malam imani da yardarta ɗari bisa ɗari.

Tana kama hannun ƙofar Fareeda ta murɗa kofar ta buɗe, da saurin gaske ta cusa kai cikin falon tana zare-zare idanu.

Fareeda na zaune akan kujera tana ɗaye gam ɗin da tayi ƙunshin gargajiya a yatsunta sai murɗa ƙofarta ta jiyo, ko kafin ta ce komai sai ganin Fatima tayi tsaye a kanta tana ƙare mata kallo.

Kirjinta ne ya buga dam!!! da sauri ta runtse idanu tayi addu'o'i. Cikin ƙarfin hali ta buɗe baki daƙyar ta ce

"Lafiya za ki shigo min ɗaki..."

"Fareeda tashi yanzunnan ki fita a haukace tuburan ki bar min mijinki Mukhtar har abada.!!!"

Fatima ta faɗa da ƙarfi sosai kamar yadda Malam mai gani har hanji ya kwatanta mata.

A karo na biyu ƙirjin Fareeda ya buga daram!! A zabure ta miƙe tsaye tana jin yadda kanta ya fara wani irin juyawa, ta fara ganin komai bibiyu.

"Inna... lillahi... wa.. inna.. ilaihi... raji'un..."

Ta finciko da ƙyar daga can ƙasan maƙoshinta, wani ƙaƙƙarfan jiri ne ya rufe mata idanu. Ta tafi yuuuuu za ta faɗi ƙasa da gudun gaske Mukhtar da ya fito daga cikin ɗaki ya tare ta.

Abinda Fatima bata sani ba shi ne. Tunda Mukhtar ya hangeta a kan titi tsakiyar maza tana kumfan baki hankalinsa ya gaza kwanciya. Daman ba wannan ne karo na farko da take ce mishi za ta unguwa sai ya hangeta a inda bai taɓa zato ba. Na yau ne dai ya fi bashi haushi. Wankin mota ciki da waje suka kai shi da Idriss, motarsa bata bushe da zai iya hawa ya tuƙa zuwa gida ba, ga shi kanshi ya fara ciwo yana buƙatar kwanciya. Kawai sai ya hau napep zuwa gida bayan sunyi sallama da Idrees ya ce da yamma zai je ya ɗauki motarsa.

"Ddddddddddama kkkkkkkkkana ggggggggidah?"

Fatima ta tambayeshi bakinta na rawa, hankalinta a bala'in tashe. Tana nuna shi da yatsarta manuniya.

Matuƙar kika yi kuskuren aikata abinda aka umarceki a kunnen mijinki duk abinda kike taƙama da shi a aurenku zai zo ƙarshe.

Maganar Malam ya faɗo mata arai.

"Na shiga uku!!!"

Ta faɗa da ƙarfi a tsorace tare da ɗora hannunta biyu akai, sai kuma ta fashe da ihun kuka ta fara ja da baya da baya, jikinta babu inda baya rawa kamar wacce ake kaɗawa ganga. A haukace ta juya za ta fice da saurin gaske Mukhtar ya ce

"Fatima, na sake ki, saki uku!!!"

Cak ta tsaya guri ɗaya kamar wacce aka yi ma umarni. Lokaci ɗaya mararta yayi wani irin murɗawa mai ƙarfin gaske, kafin ƙiftawa da bismillah jini a guje ya fara gangarowa ta ƙasan ƙafafunta.

Ganin jinin da ke zuba yasa ta ƙwallah wani gigitaccen ihu. Hankali a bala'in tashe ta tallabe mararta da hannu biyu.

"Gudajin jininmu Mukhtar!!! Ka gani, za kasa muyi asararsu. Na rantse da Allah baka isa ka sake ni ba. Idan ka isa shegiya nake. Ni da kai mutu ka raba don ubanka!!"

Tayi maganganun a ruɗe cikin ficewar hayyaci.

Mukhtar ko kallonta baiyi ba. Yana tallabe da kan Fareeda da ko kaɗan ba ta a hayyacinta, hankalinsa a ɗugunzume yana tofa mata duk addu'ar da tazo bakinta.

Fatima a ruɗe ta fice da sassarfa zuwa ɓangarenta, kamar idan ta je can ɗin tana da wani abinyi. Hannayenta duk biyu dafe da mararta tana rusa ihun kuka, kai tsaye banɗaki ta wuce. Bata damu da yadda duk ta ɓata tile ɗin falo zuwa cikin ɗakinta ba. Kamfai ta cire ta durƙusa a tsakiyar bayin don ƙara tabbatar ma da kanta wai jinin nan daga ƙasanta yake fita? Ai kuwa kamar jiran ta tsuguna ake yi nan take guda-guda ya fara biyo bayan jinin da yake bin ƙafafunta. Ga mararta da ya ƙara riƙe mata da bala'in ciwo kamar za ta mutu, sai ihu take ƙwallawa gwanin ban tausayi.

"Fareeda kin ci nasara a kaina, Allah ya isa tsakanina da ke!!! Ramlah shegiya gantalalliya, Allah ya tsine miki albarka. Mukhtar mugu macuci azzalumi, Allah yai fata-fata da namanka!!!"

Bayan gama faɗin maganganun zaman yan bori tayi akan gudajin jinin, ta ɗauke wuta ɗif!!!

***** ****** *****

Bayan wata biyar abubuwa da dama sun faru, Masu daɗi da akasin haka. Ga Mukhtar da Fareeda dai abubuwa masu daɗi sun fi yawa. Yanzu hankalinsu a kwance yake sosai har ma fiye da farkon aurensu, wata iriyar zama ce suke yi ta ƙauna, soyayya, tarairaya. Har rige-rige suke wajen faranta ma junansu rai. Suna rainon cikinsu da yai wani irin bala'in girma, a wasu lokutan ma idan ta zauna sai an taimaka mata gurin tashi, duk kuma yadda cikin yayi girma sun ƙi yarda a faɗa musu yaya nawa ne a cikin, sun ce idan Allah ya sauketa za su gani, abu ɗaya da likita ya tabbatar ma da Mukhtar shi ne ba ɗa ɗaya bane a cikin. Ko kaɗan Fareeda ba ta sha'awar mai aiki, duk yadda Hajiyarmu tayi ta nacin Fareeda ta koma gidanta da zama tunda cikin ya tsufa Mukhtar zillewa yayi ta yi, a ƙarshe dai ƙanwar Hajiyarmu wacce mijinta ya daɗe da rasuwa ke zaune da ita.

Yau tunda ta tashi da asubah Mukhtar yana lura da yanayinta, sai cije baki take yi tana yamutsa fuska. Ƙafarta ɗaya ya riƙe ƙam, tayi ta motsa ta kasa, sai shi ne ya taimaka mata daƙyar suka isa bayi, a tsaye tayi fitsari saboda yadda cikin ya takure ya cure waje ɗaya ta ƙasan mararta.

"Ammatana, ko dai in yima Inna Halima magana mu tafi asibiti...?"

Wata ƙaƙƙarfan damƙa tayi ma kafaɗunsa sanadiyyar wata masokiya da ta taso daga ƙasan mararta ta cake ta a gadon bayanta.

"Abee, kamar kashi nake ji, kama ni in gani ko zan iya in hau masai."

Ta faɗa daƙyar tana runtse idanu tana buɗewa, ta haɗa zufa tayi kashirɓin.

Har zai taimaka mata ta hau ta zauna tayi kashin sai kuma tunanin kar a haifa mishi yaya a cikin masai ya faɗo mishi arai.

"Kiyi haƙuri Babyna, sannu! Kila fa haihuwar ce, kin ga muje ɗaki ki zauna, idan ma kashin ne kiyi a ɗakin sai in gyara gurin."

Ya faɗa bakinsa na rawa.

Daƙyar, da dabara, da salati da sallallami ya iya taimaka mata daƙyar suka koma cikin ɗaki. Zanin jikinta tuni yayi nasa gurin, daga ita sai rigar barci doguwa har gwuiwa, a dabarance tana wash-wash ya zaunar da ita akan kafet ɗin da yake bakin gado.

Jikinsa na rawa ya fice kiran Inna Halima, suna sawo kai cikin ɗakin kukan jariri na musu maraba. Har suna bangaje kafaɗun juna saboda rige-rigen su shiga ɗakin.

Naƙuda ce ta taho ma Fareeda gaba ɗaya da zafi-zafinta. Ko da yaro namiji ya faɗo wani azababben ciwon ne ya sake turnuƙeta. Idan tayi salati, tayi nishi sai ta kama maimaita ayar Summas sabeela yassara. Minti uku tsakanin faɗowar Hassan duniya Usaina ta biyo baya da kukanta inyaaaa inyaaaa fiye da na ɗan'uwanta. Nan take mahaifa ta faɗo. Fareeda sai aka koma sauke numfashi a hankali saboda yadda take jin ta sakayau, kamar an zare mata ƙaya a maƙoshi.

Inna Halima hawaye Mukhtar hawaye. Sun jera mata sannu ya fi baki dubu. Sai hamdala suke yi suna kirari ga mahaliccin sammai da ƙassai. Jiki na rawa ta fara ƙoƙarin yanke cibiyar yayan Mukhtar yana taimaka mata da miƙo min wannan miƙo min wancan. Cikin awa ɗaya da rabi yayan da uwar sun fito shar da su, Mukhtar ya kwashe su a mota zuwa asibiti don ƙara duba lafiyar jikinsu.

******

A guje Jiddah ta faɗa cikin ɗakin tana numfarfashi, ƙiris ya rage ta taka ƙafar Fatima da sauri ta janye tana galla mata harara. Ba tare da damuwa da hararar Fatima ba ta mayar da idanunta kan Innarsu ta ce

"Innah, kin ji Aunty Fareeda ta haifi yan biyu mace da namiji?"

"Da gaske? Alhamdulillahi Ma sha Allah!"

Inna ta faɗa cikin matsanancin farin cikin da ya gaza ɓoyuwa kan fuskarta.

"Wallahi da gaske, yanzunnan ta kira ni a waya. Wai don Allah in faɗa miki, kuma wai in baki haƙuri yau kwana uku da haihuwar bata sanar da ke da wuri ba. Kuma ta

ce inje gidan Aunty Binto anjima in karɓo mana ankon suna turmi uku, ni ɗaya, salma ɗaya, ke ɗaya..."

"Har turmi uku Jiddah? Nawa suke? Allah yasa dai babu tsada?"

Innah ta tambaya da tunanin kuɗin atamfofin a wannan yanayi da ake ciki na rashin kuɗi.

Da karaɗin murna Jiddah ta ƙyalƙyale da dariya sannan ta amsa ma Innar

"A kyauta fa ta bamu Innah, ta ce dai saura ni da Salma muƙi zuwa gurin taron suna za ta gamu da mu."

"Allah sarki Aunty Fareeda. Baiwar Allah mutumiyar kirki, Allah ya saka da alkhairi."

Salma ta faɗa da yanayinta na sanyin hali, fuskarta cike da murmushi.

Kyawawan addu'o'i na shi albarka, Allah ya raya zuri'a, Allah yasa a gama lafiya Inna ke ta jerowa ga Fareeda kawai sai ji suka yi Fatima ta ƙwalla ihun kuka, hannayenta biyu doƙe da kunnuwanta tana harba ƙafafu a ƙasa kamar ƙaramar yarinya. A Zuciyarta take ta tsine ma Mukhtar da Fareeda.

Da mamaki ƙannen da uwar ke kallonta. Tunawa da abinda take ma wannan borin yasa ƙannen kwashewa da dariya suka tafa hannayensu, ita kuwa Inna ficewa tayi daga ɗakin ta kama harkokinta, a zuciyarta take addu'ar shiriya ga Fatimar.

******

Da gaske dai Mukhtar ya canza. Bayan ɗinkuna kala uku masu tsada da yayi ma Fareeda na fitar suna, bayan akwatuna uku da ya shaƙo da siyayyar kayan babys, bayan manya-manyan raguna guda huɗu da ya siya na raɗin suna. Naira dubu ɗari

biyu ya tura ma Kamfanin Hds jawelleries and more ya ce a haɗo mishi zannuwan da zai sa ma Fareeda a kayan goyo. Ya kuma gargaɗi Sister Hadiza 08144965394 kar a kuskura a saka mishi zanen ƙasa da dubu ashirin.

A bayan siyayyar da Mukhtar yayi mata ita ma Fareeda bata tsaya sanya ba wajen fitar da kuɗi a ribar da ake tura mata na kiwon kaji ta ce Aunty Hadiza ta fitar musu da zani mai matsakaicin kuɗi na anko.

Kasancewar duk kaya a gurin Hds jawelleries and more 08144965394 kan farashin sari suka fi bayar da shi sai ga kwaɗeɗiyar zani an fitar mata da shi na anko. Ko da ta ce zanin yayi nan take aka buga lissafi Aunty Binto ta ƙara akan kuɗin da Fareeda ta bayar suka siyo zannuwan da yawa. Da yake Fareeda ta mutane ce kwana biyar da haihuwa zannuwan sun ƙare tas har ana nema.

Fareedan Mukhtar fatan ayi taron suna lafiya a tashi lafiya□□□□□□□□□□□

Alhamdulillahi Alaaa kulli halin!! Anan na kawo ƙarshen labarin RABON AYI. Idan kuna ƙaunata ni Fareeda Abdallah kuma kuna ƙaunar rubutuna cikakkiyar ƙaunar da za ku nuna min shi ne kuyi Reg da bakandamiya Hikaya kuyi sub na 500 ku karanta labarina mai taken LOKACI. Idan baku iya bakandamiyar ba ku tuntuɓeni zan koya muku yadda ake yi, biyo ni a tafiyar labarin LOKACI shi zai tabbatar min da lallai ana tare😍□□□

https://hikaya.bakandamiya.com/lokaci-babi-na-takwas/

Godiya ta musamman ga duk waɗanda suka bi ni wajen karatun labarin RABON AYI. Na gode, na gode, na gode😍😍😍😍 Gaisuwar fatan alkhairi, da fatan haɗuwarmu da juna😘😘😘□□□ Waɗanda na ɓatawa rai a labarinnan don Allah su yafe min, fahimta fuska ce kowa da irin tasa, kuma ɗan adam ajizi ne☹□□😩

Yʻan'uwa adashinmu na dankalin turawa zai fara gobe ne juma'a. Zubin namu a sauƙaƙe ne, sati sati ko ɗan kullum, cikin ƙanƙanin lokaci za ki tara kuɗin da za ki sayi dankali buhu, ko rabi, ko kwata. Ga duk wacce take sha'awa ta tuntuɓi yʻar'uwa Rumanatu a wannan lambar http://wa.me/2348065530483

Assalamualaikum Barkanmu da wannan lokacin AUNTY ZEE TAKU CE ,Ina uwar gida Amarya da yanmata albishir gareku

BONONZA; BONONZA;BONONZA;

Nazo maku da SAHIHIN MAGANIN CIRE TUMBI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI,KINCI GAYU ANA TAMBAYARKI YAUSHE ZAKI HAIHU TUMBI YA HANAKI ADO DA KWALLIYA SHA KURUMINKI NAZO MAKI DA MAGANI CIKIN SATI DAYA ZAKI BAN LABARI ZAN DANDANA MAKU SHI AKAN RABIN KUDINSHI DAGA NAN ZUWA SATI DAYA 7K DUK ROBA DAYA KI BIYA 3500 KI MALLAKI NAKI NAN DA SATI DAYA ZAI KOMA 7K

MAGANIN BREAST WANDA ZAICIKO MAKI DA TUWON NONO DAN ALLAH KIJARABA ZAKIZO KINA GODIYA DAN DUK WADDA TA GWADA SAITA DAWO MANYAN MATA SUKE GYARA KAMAR YANDA KUKASANI 8K YAKE ZANKARA TALLATA MAKU SHI KI BIYA 4K KI MALLAKI NAKI

KI BIYA TA WANNAN ACCOUNT DIN KITURA MAN SHAIDAR BIYA

3968303018

ZAINAB SHU AIBU

FCMB

08162859027